NIDA KISHIYOYINA

NA SADNAF

E.W.F

PAID BOOK

BISMILLAHI RAHMANIR RAHEEM

Page 1

1am

LUBA

"Alhaji Alhaji"

"Ummm wai mai haka ne Luba bazaki barni nayi bacci na huta ba fisabillahi"?

"Taya zakayi bacci ka huta bayan ka ajiye mu? ai tunda ka ajiye mu kace mu biyu bamu isheka ba ai baka ga hutu ba Alhaji.

jiya da kake d'akin Hindatu ai ba bacci kayi ba kwana kayi Kuna abu sai da ka zagayo dakina zaka zo ka ringa baccin gajiya Alhaji tashi ka bani hakkina"

"Luba dan Allah ki bari sai da safe kafin na tafi aiki wlh kaina ma ciwo yake ni kwana biyun nan ma bana iya komai wlh sabida gajiya"

"Eee kwarai baka iya komai fa shiyasa jiya naga ka dade baka fito daga d'akin hindatu ba,dama kasan bakada kwarin rike mata uku ka Kara aure ai tunda har kaga zaka iya nima bazan iya daga kafa a tauyeni ba bana Jin bacci ka bani hakkina"

"Innalillahi wa Inna ilaihi rajiun"

Alhaji salis yace tare da mik'ewa zaune Yana kallon luba da ke zaune dirshan a tsakiyar gadon ta ma yaye bargon daya rufa sai wani girgiza take yasan ba wani bukata da take tsabar rigama ce ba inda yake samun bacci mai dadi da nutsuwa sama da dakin Aisha amma indai kwanan hindatu da Luba ya zagayo haka zasu sako shi a gaba kamar su kashe shi ya rasa wanan masifa da me tayi Kama

"Luba nace miki kaina ciwo yake ki bari da safe kafin na tafi aiki nifa ba injin bane ba"

"Alhaji jiya bakace wa hindatu kanka ciwo yake ba sai da kwanana ya zagayo dan ka raina min hankali ka bani hakkina sai ka sha baccinka"

Ya riga yasan halin Luba indai baiyi din ba bazata tab'a barinsa yayi bacci ba.

"Tunda na gaya miki bazan iya komai ba Kika dage sai kiyi luba"

Kansa ta fada ba dan ransa naso ba ko Yana da wani bukata ba yayi.

Yana jin tana masifar ita daya ya mata kad'an ai ba daya yakeyi a d'akin Hindatu ba yaja tsaki tare da juya mata baya daya ga ma zata dame shi ya sauka daga kan gadon yayi kwanciyarsa a kasa nan da nan bacci yayi awon gaba dashi.

Hayaniyar da ya ringa jiyowa daga Palo yasa ya bude ido yaga gari yayi haske ya mik'e da sauri Yana "Innalillahi wa Inna ilaihi rajiun gari fa ya waye wanan wane irin masifa ne"

Kullum sai hindatu da Luba sunyi fadan daya zame musu farilla ya rasa wanan masifa Kamar suna ganin hanjin junansu ace karfe shidda na safe har sun fara fada.

Bai fita waje ba ya fada bandaki yayi wanka a gurguje yazo ya tada sallah,Yana sallah ma hankalinsa na wajen palon dan har lokacin Yana jiyo zage zagen da sukeyi yasan har makota ma ana Jin hayaniyar su.

Yana sallamewa yayi waje da sauri Yana bude k'ofa takalmin da hindatu ta jefowa Luba ya sauka a kansa.

Ya dafe kansa Yana sallati

"Na Riga da na kafu a gidanan wlh ba yanda zakiyi dani luba mutuwa ce zata rabamu mumunar banza mumunnar wofi ni bansan ma mai Alhaji ya gani a jikinki ya auroki ba Alhaji ma yace hakuri yake yi dake"

"Ke da sadakarki aka bashi ko lefe fa baayi miki ba ni kuwa ki tambayi kowa kiji ba karamin kudi ya kashe a auroni ba tsabar kwantan da kikayi sadaki ma yafe Masa akayi sabida tsabar kin rasa mai aurenki"

"Ya isa ya isa haka"

Alhaji Salisu yace a tsawace Yana mulmula goshinsa dake Masa zugi "Wanan wane irin balai da masifa ne da asususban nan zaku fara masifa wai wanan wane irin rayuwa ne Hindatu Nagaji Luba na gaji Wai ku yarane?ace da manyan yayanku ku addabeni ku hanani sukuni,ba dama na dawo gidanan na tab'a samun kwanciyar hankali dan balai idan na doso gidana haka zan ta fargaba a wane dalili? Haka kuka ga Aisha nayi domin Allah bazakuyi koyi da ita ba to wlh Nagaji idan kuka kaini bango ko duniya kuka haifa min wlh sakinku zanyi kowace ta Kama gabanta"

Ya koma daki a fusace har Yana tuntube

Luba taja tsaki tana "Ai baka ga komai ba tunda ka auro wanan mai zubin samudawan Ina zaka taba samun kwanciyar hankali"

"Hindatu kuwa dakinta ta shige tana masifa kasa kasa.

Wajen karfe bakwai da rabi yaran duk Suka fito cikin Shirin tafiya makaranta dan bangarensu daban da na iyayen matan an ware musu dakinsu daban mazan ma dakinsu daban Afrah itace babba a Mata tana matakin karshe a secondary ita take kula da sauran kanen nata, inka d'auke Ashraf da Abubakar da suke karatu a A b u zaria.

Basu tsaya neman abinci ba dan sun san sai dai a biyo su dashi indai Luba ce da girki d'akin Aisha suka nufa da suke cewa Hajiya Umma Kamar yanda Suka Saba sai da suka gaisheta suka fito Suka nufi kitchen Inda suke Jin motsin luba iya yayanta ta amsawa gaisawar ko kallon Afrah da yayan hindatu batayi ba a daidai lokacin da hindatu ta fito daga dakinta tana "Kuzo ku wuce ku tafi karku yi latti dan jarraba bazaa fito da wuri a dorawa yara abinci su ci su tafi dashi ba har sai sun makara"

Ta ja hannun kananan Suka yi hanyar waje duk sai da ta bisu da manyan biscuit ba Wanda ta ware dan ita bata kishi da yara kamar yanda Luba keyi sai da driver ya jasu suka tafi ta koma ciki.

A Palo tayi zamanta tana Jin luba na kanana haibaice habaice itama tana daga palon ta daga muryarta yanda Luba zata jita tace "tsabar kwadayi da san zuciya wata ta Kashe aurenta ta baro yayanta tazo ta auri mijin kawarta tur wlh da wanan cin amana ace "

Fitowar Alhaji Salis daga d'akin luba yasa Hindatu yin shiru a daidai lokacin da Luba ta fito fuska a had'e tana "Alhaji wlh kayiwa hindatu gargadi ta fita daga harkata"

Ko kallonsu baiyi ba ya nufi d'akin Aisha bashida burin daya wuce ma ya bar gidan daga luba har hindatu kaddara yasa ya auresu da tunda ya auresu yayi bankwana da wani abu Wai shi farinciki .

A hankali ya tura k'ofar dakin Aisha da sallama har a yau da aka tafi shekaru nauyinta da kunyarta yake ji.

Yana ji ta amsa sallamar ciki ciki har ya isa gefen gadon ta ya zauna ita Kuma ta cigaba da gugan da take.

Yasan ko zasu shekara a haka bazata tab'a ce Masa komai ba Yana bakin cikin yanda ya zama bakon karfi da yaji a wajenta tamkar ba Aisharsa Mai kaunarsa ba.

"Anjima zan tafi Abuja sai nayi sati uku kafin na dawo"

"Allah ya kiyaye hanya"

Shiru ne ya ratsa d'akin Alhaji Salisu yace "Aisha dan Allah dawo nan zamu yi magana"

Sai a lokacin ta dago ta kalleshi suka hada Ido ta d'auke kanta tana "Ina jinka daga nan"

"Aisha Abu baya wucewa ne a wajenki dan Allah kiyi hakuri nasan na miki ba daidai ba shekara goma tsakani da Allah kin kasa cire abinda ya faru a ranki"

Murmushin takaici tayi tana "Alhaji wai nikam kaji na fito na ce maka da wani Abu a zuciyata Kai kadai kake kidanka kake rawarka ni ba komai a raina"

"Wlh da wanan abin da kike min gwara ki fito kimin fada ki zageni kimin koma mene da ki kawo ido ki zuba min kin maidani tamkar hoto ki Kara nesanta kanki daga wajena wlh bana Jin dadin irin rayuwar da muke tunda yanzu har da zuria a tsakani an tasa Kuma ai sai ki cire komai a ranki"

"Ba komai a raina Kai kake damun kanka a yanzu banida wani damuwa nikam"

"Hmmm Aisha kenan to ni zan tafi na damka amanar gidana a hannunki dan Allah kisa min ido Kar suyi min hauka da suka saba,wlh sabida ke nake dawowa gidanan amma matan nan caza min Kai suke"

"Allah ya kiyaye"

Mik'ewa yayi ya ajiye mata kudi a gabanta Yana sai ya kirata a waya Yana fita taja tsaki batasan mai yasa ko kadan bata ganin farinsa ba duk kuwa abinda zai Mata.

Yana fita ya ci Karo da luba a bakin k'ofa ta cika tayi fam "Ranar girkin nawa ma Alhaji sai anci amanata tsakani da Allah ran girkinta kana zuwa dakina ka dade haka"?

"Dan Allah bani hanya na wuce"

Ya bangajeta tabi bayansa tana masifar Shiga d'akin Aisha da yayi ya dade ita dai idan amanarta akaci bata yafe ba hindatu kuwa na zaune a tsakiyar palon sai dariya take kasa kasa dan sosai take ganin haukar Luba ko lissafi ma bata dashi ai ko kwana zaiyi a d'akin Aisha a ganinta ko A bai dace tace ba.

D'akin Luba ya shiga dan ya dauki akwatin kayansa Luba kuwa ganinsa da akwatin Kaya yasa tayi turus tana "Alhaji ya naganka da akwati gafa abincinka nan a palo"

"Zanyi tafiya ne zuwa Abuja akwai aikin da zanje nayi sai nayi sati uku kafin na dawo"

"Alhaji yanzu tsakani da Allah ka rasa ranar da zakayi tafiya sai ranar da kake dakina"

"Luba bani hanya na wuce banida lokacin kananan surutu "
ya fice daga d'akin.

Yana fita ya tsaya a tsakiyar falon fuska a had'e Yana "Luba bana San tashin hankali Hindatu na hadaku da girman Allah karku min hauka a gida ku ba Yara bane ba,ku daina zubar min da mutunci a unguwa wlh idan dai har a ka kirani aka fadamin kun min hayaniya a gida wlh zan dauki mumunan mataki akan ku kunji na rantse muku"

"Nifa idan bata Shiga harkata ba wlh ko kallo bata isheni ba Alhaji ni iskanci ne kawai bazan d'auka ba dan ba dan ita kadai aka yo ka ba,
bata da burin daya wuce taga ta mallake ka ita kadai wanan ne dai bata isa ba"

Hindatu tace tana hararar Luba

Luba kuwa tayi kwafa dan ji take Kamar ta shako hindatu ba wacce ta mata Karen tsaye a rayuwa sama da hindatun har a yau burinta taga ta raba ta da Alhaji.

Alhaji Salisu bai Kare ce musu komai ba yasa Kai ya fice Luba ta rakashi har wajen motarsa sai da ya fice daga gidan ta koma ciki.

AISHA

Mace ce da ta koyi hakuri ta karfi da yaji ta koyawa kanta k'au da kai,a duk abinda mijinta Salisu keyi,ta kulle zuciyarta dake neman kamuwa da hawan jinin da mijinta ke k'ok'arin dora mata ta fahimci wani zubin namiji bai cancanci ki kashe kanki a kansa ba wani zubin Kuma basu San kunya ba sau tari takan zauna tayi nadamar sakin jikin da tayi da kawarta da ta Mata mumunan tabon da har ta koma ga Allah batajin zai gogu a zuciyarta a yanzu zaman 'ya'yanta kawai take da Kuma Neman Aljannarta ba dan wai akwai burbushin kaunar mijinta a ranta ba tasan Kuma koman daren dadewa Allah zai mata sakayyar cin amanar da ya mata yanzu suna da shekara Ashirin da biyar da Aure yaranta biyar Ashraf,Afrah,Abubakar Aliyu da Ummi.
NI DA KISHIYOYINA

NA SADNAF

E.W.F

PAID BOOK

BISMILLAHI RAHMANIR RAHEEM

LUBA

Mutane da dama suna ganin na aikata abin kunya nayi abin fade naci amana Wanda ni banga aibun abinda nayi ba tunda a musulunce ba haramun na aikata ba so so ne amma san Kai yafi,Ina san Jin dadi a rayuwata Ina san duk abinda nake so a rayuwata ya zama na samu,kina mace Ina mace ba abinda zaki gaya min Ina so naga na Zama mowa a wajen mijina ya zama ba matar data isa ta hada kafada dani Zan iya kashe ko nawa ne,Zan iya zuwa
Ko'ina Ina dan na samu cikar burina.

Waiwaye

Aisha

Zuciyata cike take da farinciki dawowar da uban yayana zaiyi.

Ya shafe shekara biyar a waje dan ya Karo karatun da yana dawowa zai zama cikakken likita Allah yasan nayi kewarsa Kamar na mutu Ashraf da Afrah ma sai murna suke Abbansu zai dawo,nasan ashraf da wayonsa a lokacin da ya tafi yasani Afrah ce dai take da shekara biyu lokacin daya tafi.

Salisu bashida komai a lokacin da mu kayi Aure dan zan iya cewa auren gata aka masa nima da yake a wajen yayana nake Yana kuma da dan rufin asiri Ina gama secondary school ya nemi salis daya fito da a lokacin ba wani aiki yake ba sai wani karamin chemist da yake dashi,da taimakon iyayen sa dai ya turo kudin aure gidanmu aka sa mana Rana wata shidda masu zuwa.

A lokacin cikin tsananin farinciki salis ya bugo katin engagement na raba wa kawayena,a lokacin banida aminiya sama da Luba da a lokacin makaranta daya muka yi jinin mu ya hadu da ita sosai ba Wanda baisan kawancen mu ba, har ana mamakin yanda akayi tamu tazo daya da ita dan ni Sam bana San hayaniya ita kuwa akwai zuciya da fada gata masifafiya masifarta yasa lokacin samari ma basu fiye zuwa wajenta ba.

A ranar da na bata labarin salis ya kawo kudin aurena mamaki ta ringayi tana mai salis yake dashi da zan aureshi ita har yanzu bata ga kalar Wanda zata aura ba.

Dariya na sa mata ina nidai Ina sansa luba ni dama nafiso na auri Wanda bashida komai idan munyi aure mayi arzikin tare.

Anan ta hade rai Wai taso muyi aure rana daya bazata so na rigata aure ba cikin dariya nace ta bada himma nan da wata shidda ta samo mijin aure ta tab'e baki tana ita dai taga Kamar nayi gaggawa.

A kwana a tashi ba wuya sai gashi mun fara kirga sattikan Aurena,duk wani shiri da Luba muke yi dan itace gaba wajen fito da anko duk da ba wani shiri take da salis ba amma da ta ga dai shi zan aura ta fara sakar masa fuska a haka har aka sha shagalin bikina Luba tayi k'ok'ari sosai dan ba karamin gudunmawa tayi min ba haka ma a gidansu anyi min gudumawa na Kuma ji dadi matuka.

Duk da na rigata aure ban canza mata ba,
wai dan ganin yanzu ni inada aure hasali kawancen mu kara karfi yayi,dan ba abinda nake b'oye mata game da rayuwar Aurena itama ba abinda take b'oyemin ba ta ma fiye zuwa gidana ba amma idan dai tazo zata wuni a gidana ko da salis ya dawo ma haka zamu hadu mu uku muyi ta hira duk abokanan Salis da suke Santa duk tak'i su a fadarta tafisan ta samu mai rufin asiri sosai,a haka na samu cikin Ashraf har na haihu nan ma sai da ta hidimanta min na ringa addua Allah ya gwada min aurenta nima na rama abinda tamin.

Na tafi shekara biyu da Aure na, aka kawo kudin luba murna kamar nayita rawa har salis na tsokanata akan ko a bikinmu banyi murna haka ba,daga yanda naga luba na shiri tana kuma facaka da kudi nasan ta samu irin wanda take so ta aura wato mai kudi,tamkar dai lokacin bikina nima haka na dage muka ringa shirya bikinta,har asusu na ringayi dan inaso naga na mata fiye da abinda tamin.

A wajenta nake jin labarin Wanda zata Aura Hamza a wani company Yan China yake aiki Kuma babba ne acan.

idan har sunyi Aure zata Masa magana ko zai iya samawa Salis aiki a companynsu.

Har a zuciyata naji dadi dan zanso Salis ya ringa aikin da zai na shigo Masa da kudi,dan a chemist din ma ba wani kudi yake samu ba,amma Yana iya k'ok'arinsa wajen kula damu duk da yayana bai barni haka ba yana yawan yimin aike.

A cikin irin aiken da yake min na yiwa luba gudunmawa sosai har da zannuwan gadona wajen biyu masu dan tsada da ban taba amfani dasu ba.

Gidan Luba yayi kyau sosai Iyayenta Kuma sunyi k'ok'ari wajen yi mata jere Luba an samu abinda ake so sai falli take,har tana cemin ita dai taga nayi gaggawa da ace banyi gaggawa ba da sai na samu mijin dayafi salis,nidai inasan salis Kamar yanda yake kaunata duk da gidan haya muke ban damu ba dan indai da rai da rabo Yana Kuma iya k'ok'arinsa wajen kyautata min.

A haka muka Sha bikin luba, kawancen mu ya Kara k'arfi fiye da baya.

Watan ta hud'u da Aure watarana tazo gidana naganta a firgice daga yanda na ganta nasan ba kalau ba Salis ma ko fita baiyi ba.

Tana zama ta rushe da kuka hankalina ya tashi anan na hau tambayarta mai ya faru dak'yar ta tsagaita Kukan da take take labarta min wai ta gano Hamza karya yayi mata Ashe mai gadi ne da kudin ajiya duk yayi facaka ya aureta yanzu haka jiya Yan sanda suka zo suka tafi dashi akan Mai company ya dage sai ya biyashi duk kudinsa ta Kara da "wlh ban taba tunanin Hamza makaryaci bane Aisha mai gadi fa kinsan kuwa gidan ma ashe hayane ba nasa bane"

Nidai sallati kawai na ringa yi ita kuwa ta cigaba da rusa kuka dak'yar na bata baki tayi shiru ta ringa rantsuwar sai Hamza ya saketa ita bazata zauna da mai gadi ba,a haka Salis ya fito ya same mu ganin yanda mukayi cirko cirko yasa ya hau tambayar mu mai ke faruwa

Shiru nayi dan Ina tunanin kamar sirrinta ne bai dace na fada masa ba,ita kuwa ganin banida niyyar magana yasa ta hau bashi labarin duk abinda ya faru,Salis kuwa ya hau sallati yana Yanzu Hamza na kulle shine tazo ta zauna ai Kamata yayi asan yanda zaayi a fito dashi a takaice a ranar salis bai fita shago ba haka aka ringa cuku cukun yanda za'a fito da Hamza dan Salis har wajen mai gidan sa yaje dak'yar dak'yar ya yarda akan a saki Hamza zai nemi rabin kudin ya biya shi inyaso ya cigaba da biya a hankali.

Duk salis ke bamu labarin yanda sukayi dan luba na gidana tace ita bazata ma koma masa ba so take ya bata takardar ta ta tafi gidansu kamar ba mijinta ba ta ringa auna masa zagi.

Luba sai da ta samu sati guda a gidana wulakanci kuwa haka ta ringa yiwa Hamza Kamar ba mijinta ba,sai da Salis ya samu Iyayenta suka saka baki ta yarda zata koma gidansu hamzan kafin ya samu wajen zama.

Ni tausayinta ma na koma ji dan ta saka damuwa a ranta sosai gashi tana d'auke da ciki.

Ba'a kwana biyu bata zo gidana ba,idan tazo haka zatayi ta mita tana tsinewa Hamza akan ya cuceta a irin wanan halin Nima na samu cikin a lokacin Ashraf ya tafi shekara uku.

Nidai zan iya cewa banida matsala komai dan Asirina kam a rufe yake dan banida wani matsala a gidan aurena daidai gwargwado salis na kyauta ta min.

Cikina wata biyar Luba ta haihu Sanin halin da suke ciki yasa na zage sosai wajen hidimanta mata Salis ma baa barshi a baya ba duk da bashida kudi.

Nidai nasiha da shawara ke rabani da luba da ta balain raina Hamza ni nasan da baya Santa da tuni ya saketa dan Abubuwan da ya mata ma duk sai da ta raina burinta ma kawai ta kashe auren.

A haka nima Allah ya saukeni lafiya na haifi Afrah a haihuwan nan Salis ya min hidima ba kad'an ba,tunda na haihu Luba bata tab'a d'auke kafarta daga gidana ba tun safe idan tazo sai dare take tafiya,kayan fitar sunan da salis ya siyamin take ta juyawa a hannunta tana "Kinsan kuwa tsadar atamfar nan Ina Salis ya samu kudi haka"?

"Kice atamfar nada tsada wai Ashe tunda nasamu ciki ya Shiga adashe shine fa Ina haihuwa ya karbi Adashen ni Ina nasan ma zanin nada tsada"

"Aikuwa da tsada yayi k'ok'ari gaskiya ni Ina naga arzikin Rabin atamfar nan ma wlh Hamza ya cuceni gashi yak'i sakina"

Zama nayi a gefenta Ina "kiyi hakuri Luba mai nema Yana tare da samu ai da ace baya nema sai ki fida rai amma tunda har Yana nema watarana za'a dace insha Allahu Kuma zakiji dadi tunda Yana kaunarki"

"Hmmm kinsan ko Napkin baya iya siyawa Sultan wlh ba irin rayuwar nan na tsarawa kaina ba"

Kwalla ya zubo mata ta share a daidai lokacin da Salis ya daga labule suka gaisa daga bakin k'ofa ya mikomin ledar daya shigo dashi ya fita.

Da zan ajiye ledar sai Kuma na bud'e ledar naga Kayan jarirai ne sai sarka da dankunne da mayafi kala biyu ganin tana ta kallon ledar yasa na fito da kayan ciki na nuna mata ta ringa juya kayan tana yabawa a cikin turamen zanin da aka kawo daga gidanmu na dauko daya na bata dak'yar ta karba tana da na barshi ita wanan haihuwar da nayi bata da abin bani.

Koda tazo tafiya ma sai da Salis ya bata kyautar kudi,na rakata ta tafi.

Ahaka akayi sunan Afrah banaso na sosa mata zuciyarta taji ba dadi Kaya kala biyu kawai na saka.

A haka rayuwa ta ringa tafar mana daidai gwargwado Ina k'ok'arin taimakawa luba indai ta kawomin kukanta zan k'ok'arta naga na share mata hawayen ta Afrah ta tafi shekara biyu wataran Salis ya shigo gidan da takarda a hannunsa cikin tsananin murna Yana nuna min sunansa ya fito a cikin wayanda suka ci scholarship da zasu fita Kara karatun da zai zama cikakken likita.

Ji nayi Kamar na zuba ruwa a kasa na sha dan murna dan duk Wanda yasan Salis yasan burinsa kenan yan uwa da abokanan arziki kuwa sai taya mu murna ake ciki kuwa har da Luba da ke fama da tsohon ciki duk ta fice a hayyacinta sabida damuwa da ta sa a ranta.

Duk kudin da salis ke dashi ya ajiye min akan zai na min aike,a haka ya shirya kayansa ranar tafiya na sha kukana na gode Allah Kamar bazamu rabu ba gashi lokacin sai dai sako ba yawaitar waya ya damka amanarmu a hannun Iyayensa ya tafi.

A takaice bayan tafiyar Salis da shekara biyu komai namu ya Kare kudin haya ma ya Kare gashi banaso na ringa dorawa Iyayensa nauyi dan suma suna da nauyin kannensa akansu sosai,a haka Yayana ya ringa hidima dani, ganin ni kadai ce ba Kuma a yanzu Salis zai dawo ba, yayana yace na dawo gidansa na zauna har zuwa lokacin da Salis zai dawo,dan iyayen mu suna katsina tunda yayi Aure shekara da aurensa rukona ya koma hannunsa.

Yayana shi ya ringa hidima damu ya saka yarana a makaranta.

Luba kuwa tana ta fama ba yanda ba tayi dan ta kashe aurenta ba Hamza yak'i sakinta har magana nayiwa yayana akan ya taimaka mata da ko jarine sabida kawai ta kwantar da hankalinta

Amma duk da ya bata jarin burinta taga ta kashe auren wulakanci kuwa kwando kwando haka ta ringa Masa.

Nidai tsakanina da ita shawara ne abinda nake dashi iya Karfina Kuma Ina taimaka mata dashi a haka kwanaki suka ringa juyawa zuwa sati,satika zuwa watani,watani zuwa shekaru,tunda Salis ya tafi sau biyu kawai ya tab'a Mana aike.

A takaice Kamar Wasa sai gashi har Salis ya tafi shekara biyar saura Masa watani ya dawo ya turo kudi ta hannun yayana aka siya masa katon fili aka fara Masa gini.

Koda na gayawa Luba murna ta ringa yimin tana "Aisha Allah ya baki wasa wasa mijinki ya zama mai kudi"

"Luba kema dan kin k'i kwantar da hankalinki ne ba abinda baya wucewa mijjnki Yana nema ai watarana zai dace insha Allahu"

"Hmm banga ranar ba Aisha nidai banida burin daya wuce ya sakeni dan bazan iya ba"

Shirye shiryen dawowar salis na farayi dan baifi saura wata biyu ya dawo ba shekara biyar ba Wasa ba daga irin ginin da ake kerawa nasan Salis ya samu kudi ni bashine a gabana ba nidai burina ya dawo naganshi dagani har yarana munyi kewarsa.

Saura sati uku ya dawo naje gidansu da yara anan mahaifinsa ke cemin ya turo kudi akan aka ma mana haya.

A takaice gidan hayan ma da aka kama Mana katoton gaske kayan dakina kuwa duk na siyar dan sun zama tsohon yayi a kudin dayayi saura Wanda ya turo na cika na

sake sababin kayan d'aki Kamar dai amarya yayana ya taimaka min shima dan ba karya yayana Yana ji dani.

Luba kuwa sai saintyn gidan hayan take tana ai Salis ya zama mai kudi da dukan alamu saura na wulakantata na juya mata baya ni dariya ma take bani dan bana Jin ko mai Zan samu zan ari halin da ba nawa ba ni bana ma fada mata komai,yanzu dan Kar taga Kamar da biyu nake bata labari amma kullum tana tafe dole ta ringa sanin halin da nake ciki...

Presently

Yaran duk suna zaune a palo suna kallo Hindatu itama tana zaune a palon.

Fitowar Aisha daga d'akin yasa ta saki murmushi tana "Hajiya kin fito"

Murmushi Aisha ta saki tana "Eee wlh wai da so nake na leka gidan sunan na idan banje yanzu ba bazan samu zuwa ba"

"Bari na saka mayafina na rakaki"

Hindatu na k'ok'arin mik'ewa Luba ta fito daga dakinta tana "ke dai anyi shugaban munafikai Sam bakiji dadin rayuwarki ba wlh idan ma duk so kike ku hada kai dan ku cutar dani wlh ba abinda zaku iya min"

"Allah ya baki lafiya ku tashi ku koma karamin Palo kafin ta fara kawo muku duka"

"Kambalai kina nufin ni mahaukaciya ce"?

"Toh da fa kina da hankaline.....

MG'S SKINCARE

Dame akafiki yar uwata?
Kyan fatar ko iya gyaran fatar?
Ina riba g macenda t Maida kanta sauran mata?
Shin haryenzu labarinmu kikeji ko kike bayarwa?
Hajiyata miye matsalar?
Fatar takice abun se lahaula?
Kingwada kingwada harkinsare?
Tsakanida Allah yaushe daren yayi balle wayewar garin?

Inbakida labarin MG'S wacce tasanki tasansu,
Gawurtaccen Kuma shahararren kamfanin gyaran fatane,duk lalacewar jiki,duk hautsinewar fata,duk yenda jikinki yazama abun kunya gareki, Ina tallata maki me gabadaya,

Muntarkato,munwarwaro,munqullo duk wani Abu daze maidaki wanke hannu kataba mun qara a cikin kayayyakinmu,muncire,muntsife,munfidda,mun tantance mun hadamaku wasu irin hadaddun lafiyayyun kaya masu masifar goge fata,wallahi duk fitinar fatarki inshallah,kinzo bustop,kisiya kiyikyanda ko mace,kan juyo ta waiwayo ta dubi halittar Allah,

Ga product din kamar hka,
Sabulu 4500

Mg's beauty kit
Karamin kit 12k
Body soap
Facial soap
Body cream
Face cream
Glow oil
Pink lip balm

Flawless skin beauty kit
Babban kit 20k
Body soap
Facial soap
Body cream
Face cream
Scrub
Glow oil
Pink lip balm

Note kowanne d kalanshi nd yanayin packaging dinma aren't the same,

Tsakanida Allah kigafa
Duk wannan garabasar Kuma kinazaune hba taso a dama dake a harkar yar uwata,

Ayi hakuri da sauyin farashi komi yatashine muma b hka mukasoba
Chat:08062991549,07046881166,07067210195,
Call,+2348064532391

LUBA...

NI DA KISHIYOYINA

NA SADNAF

E.W.F

PAID BOOK

Present

"Hindatu wlh taraki nake karki ga Ina kyalleki wlh zan baki mamaki"

"Ke a yanzu akwai abinda zaki yi ki bani mamaki Luba ai banga abinda dai zaki yi yanzu ki bani mamaki ba, asara dai kinyi ta abin kunya dai kin aikata kowa yasani Idan kina haukarki ki daina zuwa wajena kije can ki karata ke daya"

Ashar Luba ta lailayo ta fara zagin Hindatu da taja tsaki tabi bayan Aisha da ta dade da ficewa daga palon dan idan suna abin su ko tankasu bata yi har yanzu tana mamakin halin Luba.

Tare su kaje sunan suka dawo Aisha sam bata bata fuskar da zata mata maganar luba ba dan tana Jan girman ta duk da Hindatu tana iya k'ok'arinta wajen girmama ta tun daga bakin k'ofa suka fara jiyo ihun ummi Yar gidan Hindatu dan yaran hindatu uku da Alhaji ummi itace karama.

Da mugun gudu Hindatu ta Shiga gidan a daidai lokacin da Luba ta kara daga bulalan hannunta zata zabga mata Hindatu cikin ihu tace "wlh wlh sai na rama dukan da kika mata cikin wani irin super ta dira gaban Luba suka fara wani irin k'ok'awa.

Aisha da sai a lokacin ta shigo gidan har zata wuce su ta tsaya tana "Dan Allah yaushe zaku girma ku daina abu Kamar kananan yara ko akauye ba'a irin wanan rayuwar ace kullum sai kunyi fada kunyi dambe a gaban yayanku wanan wane irin rayuwa ne"? Hindatu cikata"

dak'yar Suka rabu suna hucci dan hindatu ta dan fi Luba tsayi da kib'a

"Kinyi asara wai sabida kina Jin haushina kika hau dukar min 'ya toh wlh daga yau duk ranar da kika Kara tab'a min Yara Allah sai na baki mamaki"

"Kafin ki bani mamaki hindatu ni zan baki mamaki"

Ta shige dakinta da sauri tana shiga ta d'auki wayar ta ta nemo Asabe a waya (itace aminiyar luba)

Tana dagawa tace "Asabe gobe Ina nan tafe inaso na koyawa Hindatu hankali"

"Ta Kara hadoku kenan"?

"Eee idan nazo zan baki labari"

"Sai kinzo"

Ta katse wayar tana jijjiga kafa a duniyarta bata da burin ma taga ta raba Alhaji Salis da kowa tafiso taga ta juya taga ita kadai ce a gidan bata san ya akayi Hindatu taga gadon baccinta haka ba"

Past

Aisha

A ranar da salis zai dawo daga ni har yayana shiri mu ka tayi,duk abincin Dana san yana so na dafa masa dagani har yayana munyi tsaf damu bansan dai karfe nawa zai iso ba amma nasan a ranar zai dawo wajen karfe uku sai ga luba tazo wai tazo yiwa salis sannu da zuwa dariya nayi Ina ta kyauta,sosai nake Jin luba a raina tamkar Yar uwata tunda duk ta damu da damuwata,abincin da na girkawa salis na zuzubo mata

tana ci muna hira tana bani labarin irin talaucin da Hamza ke fama dashi ko abinci ma babu a gidan,sai naji tausayinta har a raina na yanke idan Salis ya dawo naga yazo da nauyinsa zan masa magana ya taimakawa hamza.

Wajen karfe biyar na yamma muka ji dirar mota a k'ofar gida.

Dagani har yaran muka diba mu kayi waje da gudu shekara biyar ba Wasa ba, ai Salis bai gama fitowa bama na daka tsalle na rungumeshi ina ihun murna,dariya kawai yake Yana na barshi ya d'auki yayansa.

Kaninsa sai dariya yake mana driver taxi din Kuma nata fito da akwatuna da jakankunansa kaninsa ya ringa d'auka Yana Kai wa ciki.

Afrah ya d'auka yana ta fadin girman da tayi daya hannun nasa rik'e dana Ashraf nidai tunda ya sakeni kallonsa kawai nake ya balain canjawa kamar bashi ba ya zama wani dan gayu ya goge Kamar wani bature duk sai na raina ma kwalliyar da nayi na tarbarsa.

A haka muka shiga cikin gidan sai da muka je Palo ya sauke Afrah ya juyo Yana kallona da alama bai lura da Luba dake rabe a gefen kujera ba.

"Gaskiya nayi kewarku sosai no place like home indo Kinga yanda kika canja kuwa Anya kinyi kewata"

"Uhum uhum"

Luba tayi gyaran murya ya waiga da sauri ya kalli wajen da take zaune Yana "Kai Luba wai dama kina palon nan ai ban lura dake ba"

"Ya za'ayi ka lura dani likita bokan turai"

Dariya yasa Ya zauna akan kujera a daidai lokacin dana zuba kunun aya dana hada masa na mik'a masa ya karba yana "Yauwa indona kice kawarki tana cikin masu kular min daku"

"Aikuwa Luba kam ba daga nan ba wlh bata bari munyi kadaicinka ba"

"Aikuwa ta kyauta Allah ya bar zumunci ya mai gidan"

Tuni murmushin dake fuskarta ya kau, salis bai ma lura ba sai tambayoyi yake yiwa su Afrah a takaice Luba sai da magriba ta tafi na lura jakankunan da salis ya shigo dasu take so a bud'e nidai tunda na kai d'aki ban bud'e ba,na dauka ma zata tafi da wuri tunda ya Kamata taga dacewar haka,amma bata tafi ba duk da salis ya shige d'aki.

Nima na matsu na keb'e da mijina amma haka na daure na zauna muka ringa hirar a lokacin da tazo tafiya da yake
girkin da nayi da dan yawa a flask na diba mata da yawa canjin daya min saura na bata ta tafi akan sai ta zo karbar tsaraba nace mata sai tazo.

A ranar kusan raba dare muka yi da salis Yana bani labarin rayuwar da yayi a waje da cigaban da ya samu dan ya dage sai ya dawo ne sun bashi aiki acan amma a Yanzu ma ya samu aiki a wani baban asibiti ga Kuma aikin NGO daga labarin da yake bani nasan Salis ya zama mai kudi babban burina naga na taimaka wa Luba kwana biyu

da dawowarsa bayan duk ya hucce gajiyarsa ya dan zaga dangi na shigar Masa da maganar taimakon da nake so a yiwa luba da mijinta.

Cemin yayi zai yi iya k'ok'arinsa amma a Yanzu daya dawo gininsa kawai yake so ya sa a gaba zai bani abunda ya samu na bata kafin ya kamalla gininsa.

Abinda ya bani mamaki Luba bata tab'a sati guda bata zo ba sai gashi tun ranar da Salis ya dawo bata Kara zuwa ba gashi a cikin lodin tsarabar da salis ya kawo mana da yayana na d'aukar mata itama da yayanta tunda itama namiji da mace ne Sultan da Ilham ganin an tafi kwana goma banganta ba yasa na nemi izinin a wajen salis akan zan je na dubata naga ko lafiya danazo tafiya ya bani Dubu Ashirin akan na bata taja jari a lokacin kudine mai yawan gaske tamkar ni yayi wa kyauta haka naji sabida tsabar murna.

A lokacin da na isa gidanta a tsakar gida na sameta Sultan danta a shimfide akan tabarma

Da alama bashida lafiya da sallati na karasa nayi wurgi da ledojin hannuna Ina "Luba dama sultan bashida lafiya"?

"Hmm Aisha kenan yanzu tsakani da Allah tun ba'a je ko Ina ba kin fara juya min baya dan mijinki ya zama mai kudi,har ace baki gani ba kwana goma ko ki nemeni kiji dalilin dayasa ban zo ba"

"Haba Luba Mai yasa kike hakane kefa mai fadawa wani halina ne wlh tunda Salis ya dawo nake ta bak'i Yan sannu da zuwa hankalina na wajenki a yau na samu kaina nace bari nazo na duba ki naga ko lafiya amma har Zaki min mumunan fassara haba mana Allah Kar ya bani arzikin da zai saka na wulakanta mutum wlh banji dadin maganarki ba"

"Aisha kenan Allah ya baki hakuri nidai Ina tsoron kin canja din dan yanzu gani nake ma idan nazo wajenki zaki ga Kamar na takura ki ko nazo maula"

"Allah ya kyauta tashi mu Kai shi asibiti"

Nace dan har ga Allah na ji haushin maganar luba.

Mik'ewa tayi ta Shiga d'aki sai da ta d'auko masa Kaya ta taimaka masa ya cire na jikinsa ta rik'e hannunsa Muna k'ok'arin yin waje sai ga Hamza ya fado gidan da leda a hannunsa.

Luba kuwa ta saki hannun Hamza taje ta cakumo wuyan rigarsa tana "Hamza ka bani takardar sakina na gaji da aurenka maganin naira dari ma bazaka iya siyowa danka ba ka sakeni Hamza bazan iya da wanan auren naka ba"

Hankalina idan yayi dubu sai daya tashi, dan zagi na rashin mutunci haka ta ringa yiwa Hamza.

Luba bata ji bata gani haka ta ringa ihu tana ce Masa idan ya cika dan halak ya saketa sallati na saki da k'arfi a lokacin da naji Hamza ya furta mata saki biyu ita kuwa ta sake shi da sauri tana hamdala akan ya saketa.

Nayi matukar bakin ciki da mutuwar Auren Luba ita kuwa ba abinda ya shafeta sai ma murna da take da ta tashi ma barin gidan iya kayanta ta dib'a tace yaran suyi zamansu a wajen babansu bazata tafi da kowa ba.

Tsananin tausayin Hamza da yaran yasa kudin da Salis ya bani akan na bata na bawa Hamza ya ringa min godiya yana min Addu'a.

Luba kuwa tayi nisa a hanyar tafiya gidansu da kayanta.

Haka naje gida jiki duk a sanyaye.

Koda na bawa Salis labarin abinda ya faru cemin yayi dama Luba bata da hankali ai ya taya Hamza murna da ya rabu da ita.

Present

ANEESA

Ki sake tunani Aneesa taya zaki rasa Wanda zaki aura sai mai mata har uku kije a ta uku mai zakiyi da tsoho bayan ga dan uwanki nan da ya dade Yana kaunarki,nidai wlh bazan barki ki auri mutumin nan ba sai kace kin rasa mijin Aure"

"Wlh Alhaji Salis Yana kaunata Yama ce ba gida daya zai ajiye mu ba nidai shi nakeso na aura"

Aneesa tace tana zumburo baki

"zan ga kuwa mai aura miki shi"

Mama binta tace tare da mik'ewa ta bar palon.

Adaidai lokacin da Kiran Alhaji Salis ya shigo wayar Aneesa tana dagawa yace "Gani nan a waje na karaso"

"Gani nan zuwa"

Aneesa ta mik'e ta Shiga d'aki tare da d'auko hijabinta ta saka tayi waje.....

Nayi typing mai tsayi wlh ya goge

MG'S SKINCARE

Dame akafiki yar uwata?
Kyan fatar ko iya gyaran fatar?
Ina riba g macenda t Maida kanta sauran mata?
Shin haryenzu labarinmu kikeji ko kike bayarwa?
Hajiyata miye matsalar?
Fatar takice abun se lahaula?
Kingwada kingwada harkinsare?
Tsakanida Allah yaushe daren yayi balle wayewar garin?

Inbakida labarin MG'S wacce tasanki tasansu,

Gawurtaccen Kuma shahararren kamfanin gyaran fatane,duk lalacewar jiki,duk hautsinewar fata,duk yenda jikinki yazama abun kunya gareki, Ina tallata maki me gabadaya,

Muntarkato,munwarwaro,munqullo duk wani Abu daze maidaki wanke hannu kataba mun qara a cikin kayayyakinmu,muncire,muntsife,munfidda,mun tantance mun hadamaku wasu irin hadaddun lafiyayyun kaya masu masifar goge fata,wallahi duk fitinar fatarki inshallah,kinzo bustop,kisiya kiyikyanda ko mace,kan juyo ta waiwayo ta dubi halittar Allah,

Ga product din kamar hka,
Sabulu 4500

Mg's beauty kit
Karamin kit 12k
Body soap
Facial soap
Body cream
Face cream
Glow oil
Pink lip balm

Flawless skin beauty kit
Babban kit 20k
Body soap
Facial soap
Body cream
Face cream
Scrub
Glow oil
Pink lip balm

Note kowanne d kalanshi nd yanayin packaging dinma aren't the same,

Tsakanida Allah kigafa
Duk wannan garabasar Kuma kinazaune hba taso a dama dake a harkar yar uwata,

Ayi hakuri da sauyin farashi komi yatashine muma b hka mukasoba
Chat:08062991549,07046881166,07067210195,
Call,+2348064532391
NI DA KISHIYOYINA

NA SADNAF

E.W.F

PAID BOOK

Alhaji Salis k'ofar gidansu Aneesa kawai yake kallo Yana murmushi cikin wata uku da haduwa da Aneesa da bata fi Sa'ar Aliyu ba,duk ta bi ta rikita masa lissafi,asibitin da yake aiki a Abuja taje ganin likitan ido,bata gane office d'in da aka tura ta ba ta fado office dinsa yanda ta saki fuskarta da fara'a ta gaishe shi yasa yaji ta burgeshi anan take ce mishi tana neman Dr Ahmad murmushi ya mata akan ba office din Dr Ahmad bane wanan wanan office din Dr Salis ne idan matsalarta abinda ya shafi mata ne to ta zauna (Dr Salis Gynecologist ne)

Girgiza masa kai tayi tana ita ciwon ido take mik'ewa yayi Yana ta tashi ya rakata wajen sa.

A takaice a yanda ya had'u da Aneesa kenan da yaji kaunarta lokaci guda,zai iya cewa itace mace ta biyu da yaji ya kamu da tsananin santa tunda Kan Aisha bai Kara Jin san wata 'ya mace ba,duk da yana ganin abune mai wuya ma Aneesa ta yarda ta aureshi lura da shi din babba ne,na biyu Kuma taya zaiyi auren ya samu kwanciyar hankali bayan kullum cikin tashin hankali ake a gidansa kuskure kwaya daya tal ya canza masa rayuwa ya hana shi nutsuwa tsawon wanan lokacin.

Kamar wasa daga waya da chatting ya kai wa Aneesa ziyara ga mamakinsa yarinya da alama ta amshi tayin soyayyar sa ba Kuma ya Jin wai dan kudinsa take San shi dan da alama Iyayenta nada kudi.

Wata uku kenan da haduwarsu da ita a wajenta kawai yake Jin wani farinciki dan Aisha ta kulle zuciyarta ya rasa yanda zai goge laifin da ya mata idan hakkinsa ne tana bashi duk wani abu daya rataya a wuyanta tana mishi sai dai sam bayajin dadin yanda ta cire shi a ransa ba abinda baiyi na ban hakuri ba amma duk a banza bata san cewar Shima laifin da ya mata ba a san ransa bane ta Kan dole ya aikata abinda ya aikata.

A yanzu maganar Aure yayi wa Aneesa ta Kuma ce ta amince zata aure shi duk da kasan ransa cike take da fargaba auren baisan Karin auren nutsuwa zai haifar masa ba ko akasin haka,idan ya tuna luba kawai sai gabansa ya Fadi, bai tab'a ganin shuumar mace irinta ba duk tsawon shekarun nan da suke tare bai tab'a kaunarta ba akan dole yake zaune da ita sabida wani boyayyen sirrinsa da yake fatan har ya mutu ba Wanda zai tab'a sani.

Isowar Aneesa da kamshin turaren daya daki hancinsa yasa shi sakar mata murmushi ba ruwan so da tsufa ko yarinta Jin kansa yake Kamar wani matashin Saurayi suka hau hira da yake kuma akwai wayewa sosai a tare da Alhaji Salis tuni ya maida kansa yaro a wajen Aneesa Wanda daga yanda take magana aurensa babu gudu ba ja da baya dan ta bashi go ahead akan yaje ya samu mahaifinta tunda yace bazai tab'a Mata auren dole ba.

Sabida ma Aneesa yake yawan tsiran tafiya Abuja daga luba da Hindatu sun caza masa kai zai bar garin katsina ya tafi Abuja dan a katsina yake zaune wanan kenan.

Dafatan zaku na gane yanda nake tab'o abinda ya faru a baya da yanda nake dawowa cikin labarin banaso ku rikice labarin ne yazo a haka

Past

Aisha

Nidai mutuwar Auren Luba a wajena ba alkhairi bane sam,dan daga lokacin da ta gama idda tayi wani irin gogewa da yake bak'ace sai ta hau shafa mai bata ma bari ta gama idda ba ta ringa sintirin zuwa gidana tana Shan alwashin irin mijin da take so a yanzu ta samu ta aura idan ta tashi min kwatance sai ta ringa cemin "Ni yanzu burina na samu matashin mai kudi wayayye kamar dai Salis mijinki ke fa kin more dan wlh ba ma mai ganin mijinki a waje ya yarda wai ke yake aure dan yafiki wayewa da had'uwa wlh kasar wajen nan gaskiya ta Kara canja shi ya zama wani dan gayu wa zai ce wai Salis mai chemist ne ya dawo haka"

Idan tace haka dariya nakeyi nace Allah ya bata ma fin Salis ba ita kadai ke fadan haduwar salis ba dan ni kaina yanzu sai naga kamar canza min Salis din akayi dan a Rana Salis Yana wanka ya Kai sau uku wani irin tsafta ya Kara koyowa da gayu kananan Kaya kawai yake sawa ni har mamakinsa nake wani zubin nakan ma tambaye shi wanan gayun da yake yi na mene sai yace min yanzu Allah ya rufa masa asiri matsayin aikinsa yanzu sai kana irin wanan shigar sabida raini anan zai hau tsokanata ko dai tsoro nakeji zaa kwace shi ne na kwantar da hankalina ai shi din mijin mace dayane likitoci basa auren mace sama da daya.

Yanda yake siyan sutura haka yake siyamin ya siyawa yarana ni zan iya cewa ma ni wasu kayan ma bansan ya kalansu yake ba dan ba wani bud'ewa nake ba ba Kuma wani fita nake ba ballantana ince zan na sawa iyakacina dai inzan fita naje gidan yayana sai tsirarun dangin babana dake nan.

A lokacin da Luba ta gama idda ta Sako rayuwata a gaba da aron Kaya,ban taba damuwa ba yau zata zo akan na bata aron jaka da takalmi idan na bata bazata dawo dashi ba idan an kwana biyu zata zo aron sarka da dan kunne wlh aron kayana da take bai tab'a damuna wai ko naji a raina bari na hana ta dan Ina ganin ai arzikine ma a ari abu a wajen ka idan ma aka kwana biyu na mata maganar ta dawo min da abinda ta ara sai tace min zata kawo min wlh mantawa tayi idan ta tashi duk zata hado min idan kuwa na sake mata magana anan zata fara "Ke fa matar Mai kudi ce wlh ki dai na haka ke yanzu mai dan ma kin bar min kayan nan yawa kike wlh"

Ta fin k'arfi take rabani da duk abinda ta ara haka zan hakura ban Kuma isa ta Kara aron abu na hanata ba dan yanzu sai tace na mata wulakanci dan mijina ya zama mai kudi.

 duk abin nan ban tab'a bari Salis ya sani ba, ba Kuma Ina b'oye masa bane dan wai zai min fada a'a wai dan Kar ya raina luba.

A irin wanan lokacin watarana muka shirya tafiya bauchi dan akwai bikin Yan uwan matar yayana da za'ayi su biyu da yake itama matarsa da nake cewa Mami Yar bauchi ce yaranta biyar akwai Adam Aliyu Rufai Khadija da muhasim.

A lokacin Ina da kudi dan har rasa mai zanyi da kudi nake dan Salis Yana samu ba kad'an ba aikin NGO din da yake da irin kwangilar da yake samu ba k'aramin kudi yake shigo masa dashi ba ko ginin da yake yi kaf unguwar ban ga mai irinsa ba,gudunmawa mai yawa nayi wa Aunty Mami matar yayana domin ta rik'eni da zuciya daya tun Ina K'arama ta har tasowa ta,tana kyautata min sosai, har yaranta sai da nayi wa dinki,Salis ma ba'a barshi a baya ba dan na bashi labarin yanda nake da matar yayana Ina kaunarta sabida bata tab'a cin zalina ba hasali ma Ina yarinya idan nayi laifi har wani b'oyeni take sabida Kar yayana ya dokeni.

Salis yasan manyan kaya Sosai duk kayana ba kananu har cemin yake bai ga abinda zai min da zai Fadi ba dan na kaunace shi a lokacin da bashida komai na zauna dashi

a lokacin da ko biyar bashida shi,ya tafi ya barni shekara biyar na rike masa mutuncin aurensa yayana ya rik'e mu ya saka yayansa a makaranta baya jin akwai abinda zai iya biyan su dashi.

Ni kuwa ganin ya d'auke min komai yasa bayan Aunty Mami da yayanta na siyawa mahaifina da mahaifiyata kaya sosai sauran kudin ma na b'oye dan na basu duk da nasan Salis Yana yawan musu aike amma nima inaso na samu albarkar su.

Ana saura kwana biyu mu tafi telar da salis ya bawa dinkina ya kawo min wajen kala biyar ni ba wani sanin kaya nayi ba amma Ina ganinsu nasan masu tsada ne.

Ina zaune a palo Ina cikin daga dinkin sai ga Luba ta shigo da sallama taci doguwar rigata baka ya Sha Jan duwatsu a cikin dogwayen riguna na ina balain san rigar Ina ji Ina gani Luba ta rabani da rigar sawa na daya.

Daidai da takalmi da purse din hannunta duk nawane banda ban leka cikin jikinta ba komai na jikinta nawa ne.

Yanzu idan na dan canza fuska sai tace na wulakantata ta hakane yasa na sakar mata murmushi Ina "Hajiya daga Ina"?

"Unguwa naje fa ke na hadu da wani mai kudi yaseen amma bana Jin dai ya Kai Mijin ki kudi gaskiya amma ya zanyi haka zanyi maneji na aure shi kila ya Kara kudi a gaba ki tayani da Addu'a Allah yasa da gaske yake zai aureni ke gidan nan da Salis yake ginawa wlh Kamar wani hotel kawata kin chaba wlh"

Dariya nasa Ina "Allah ya baki fin gidana Luba wlh tunda nake ban taba sa rai zan tab'a tsintar kaina a cikin irin Wanan niimar ba insha Allahu kema Zaki samu"

"Kai kai kawata wanan shegen less din fa kinsan kudinsa kuwa"?

Ta dauki less din da na ajiye a gefena dana ga ta shigo wai Ina addua ma Allah yasa Kar ta gani.

Ai tuni ta jawo duka kayan ta hau dagawa tana ihun nasan tsadarsu kuwa duk ita ta hau fadamin kudin kayan ta mik'e tsaye ta fara Kara kayan a jikinta tana "Allah ya baki Aisha irin rayuwar da nake mafarki Allah ya baki Salis ne ya siyo miki ko dan nasan ba wani sanin kaya kikayi ba"?

"Eee shi ya dinko min na bikin gidansu Aunty Mami kinsan jibi zamu tafi"

"Gaskiya sunyi kyau kawar rufin asiri aikuwa dole ki bani aron daya dan gobe Alhajin nan zai zo kinsan gwara yasan tanadin da zaiyi idan yaga na saka irin wanan less din"

"Luba nace miki fa dinkunan bikin da zamuje ne taya zan baki aro ai sai dai Kuma idan na dawo sai na baki amma yanzu ko bikin ma banje na sa ba, sai na baki aro"

Sai ta saki less din hannunta take fuskarta ya sauya "ke yanzu aro ne bazaki iya bani ba Aisha aro dai ba kyauta ba wlh ban tab'a tunanin wai akwai abinda zan nema a wajenki ki hanani ba arzkin nan muma zamuyi Aisha bamu fidda rai ba dama nasan lokaci na zuwa da zaki wulakantani sabida kina ganin kin samu abin duniya"

"Kai Luba mai yasa kike hakane dan girman Allah kin tab'a tambaya ta abu na hanaki ko abu Kika gani ban taba sawa ba idan kikace na baki aro Ina baki ban taba hana ki ba wanan biki za muje Salis shi ya Kai min dinkin nan da kansa Kuma shima zaije bikin ai bai dace ace bai ga nasa ba ki fahimceni Mana idan Aron less kikeso ai zan iya dauko Miki wani akwai wayanda ma ko sawa ban tabayi ba ai sai ki zaba a ciki"

"Ki barshi kawai Aisha ba komai muma Allah ya Mana arzikin nan"

"Ta dauki purse dinta fuuu zata wuce na rukota da sauri (akwai abinda idan na tuna wlh kamar na rufe kaina da duka Sadnaf hmm)

"Kai Luba wai mai yasa kike haka ne mai na zuciya dan Allah dan annabi toh ki zabi Wanda Zaki ara din Shikenan ban miki rowa ba"

"Wlh ke din ce da haushi Aisha yanda na d'auke ki wlh ba haka kika d'aukeni ba wlh bana fatan Wai yau ace ke ki nemi abu a wajena na hanaki amma ke daga ki bani aro kin tsaya maganganu"

"Toh naji dauki Wanda kikeso din"

Nace Kamar nayi kuka sai addua nake Allah yasa Kar ta dau wanda yafi shiga raina sai kuwa gashi shi ta d'auka iya nan bai isheta ba sai da ta kara aron mayafin da zai Shiga da sarka da dankunne.

Har ta tafi zuciyata cike take da bakinciki wlh ba wai dan aron kayan ba sai dan less din ya Shiga raina Kuma nasan kila nayi bankwana dashi kenan wane kila ai less ya tafi sai dai nayi hakuri.

Koda salis ya dawo ya tambayeni an kawomin dinkunan ce masa kawai nayi eee nama saka a akwati,ya tambayeni sunyi kyau kuwa"?

Nace Masa kyau kai sai ya saki murmushi Yana "Wlh da tsada na siyesu sosai dan inaso duk Inda Kika Shiga asan matar Dr Salis ce ke Kinga wanan ruwan ganyen yafi dukansu tsada ranar da zaku fi taro Zaki saka"

Sai na saki baki Ina kallonsa dan shi Luba ta d'auka na wayance da aikuwa baka ga kyaun da yamin ba"

"Ai nasan dole ya miki kyau dan nasan kalar dake haska ki"

Nidai a ranar haka na kwana Kamar nayi kuka luba dai tamin fin k'arfi ba Wanda na tab'a fadawa addabata da take da aron Kaya sau daya nasan na fadawa Aunty Mami ita kuwa ta ringa min fada akan ya nake Abu kamar doluwa mara wayo na daina haka ai bai dace na ringa bada aron Kaya ba sai dai idan nayi niyya dai na bar mata.

Duk yanda naso d'aukar shawarar Aunty Mami kasawa nayi dan sai nake ganin kamar bai dace Ina da abu Luba ta tambayeni na hanata ba.

A haka muka je bauchi muka yi sati biyu bayan biki na dan huta a gidanmu da su Ashraf ga cikin dake jikina da ya tafi wata biyar.

Ba laifi Salis ba iya iyayena yake yiwa hidima ba har da yan uwana na Kuma ji dadi ba kadan ba.

Naso barin Su Ashraf ma a gidanmu tunda hutun makaranta ake suka k'i ahaka muka dawo a motar da Salis ya aika mana duk dasu Aunty mamy Mu ka dawo da yaranta sai da muka sauka a gidanmu muka huta suka tafi muhasim tace zata zauna har sai an koma hutu zata koma gidansu itace Yar yayana ta biyu a lokacin tana da shekara goma Sha biyar. Ta girmi Ashraf da wajen shekara bakwai.

Ina dawowa da kwana biyu sai ga Luba ta duro a ranar Salis bai fita ba sabida ranar lahadi ne.

Koda na ganta sai da gabana ya yanke ya Fadi.

Dan less dina data ara shine a jikinta.

Nasan Salis indai yaga less dinan a jikinta sai na Sha fada dan kwanaki da ta sako wani atamfata da ta ara data tafi sai da ya tambayeni nace masa tana da irinsa ba nawa bane yace "Aa toh dan da nakine wlh sai munyi fada kinsan wanan kawar taki bata da hankali Ina tausayawa Wanda tsautsayi zai saka ya aureta"

Murmushi kawai na Masa a lokacin dan har a raina bana Jin dadin yanda yake Mata.

Tana shigowa nayi sauri na mike na fara k'ok'arin janta dan mu Shiga d'akin Yara.

Ai ba muje bakin k'ofa ba naji Muryar Salis a bakin k'ofar d'akina Yana kirana gabana ya yanke ya Fadi na juya a hankali ita kuwa Luba ko a jikinta ta juya itama tana "aa likita bokan turai ashe kana nan?

Bai amsa ba naga ya fara Mata kallon sama da kasa take naga ya hade rai ya juyo ya kalleni Yana "Aisha wanan ba less dinan bane da na siya miki?Mai yake yi a jikin Luba"?

Runtsa idona nayi dan Sam banso Salis yamin haka ba

"Kai likita bokan turai mai dan kayanta ne Ni da ita fa dayane ko ka manta"?

"Na manta me ya zaayi na siyowa matata Kaya kizo ki ara kice min ke da ita daya ne ke na siyowa ko ita? A wane dalili zan siyo wa matata kaya mai tsada sai kizo ki ara ki saka"

"Dan Allah ka bari Abban Ashraf zan maka bayani"

"Bayanin me Zaki min Aisha dama idan na siyo miki Kaya dan kisa kawarki kike bawa sabida wulakanci kwanaki naganta da kayanki kikace min ba naki bane irinsa ne da ita?dama baki San ciwon kanki ba Aisha an gaya Miki kudin banza ne dani? Ko an gaya miki bansan zafin kudina ba na ciri kudi mai tsada na miki dinki ki bawa wata banzar kawarki"?

"Kaga dakata Mallam karka sake ka fadamin maganar banza kai har wani arziki kayi da zaka min rashin mutunci karka manta fa tare kaganmu da ita baka isa ka rabamu ba ko ni keda kayan da take dashi zan bata fin wanan har nawa kayan nan suke da zaka tsaya min rashin mutunci"

"Luba mai haka kikeyi"?

Nace hankalina a tashe dan naga salis idonsa ya kada yayi ja

"Cire min kayana tunda ba ubanki ne ya siya ba wlh sai kin cire ban damu ki tafi ko tsirara ba wlh zan nuna miki ni din banida mutunci maza ciremin kayan nan yanzu idan kawarki bata da hankali ni zan koya mata hankali idan taga kinyi tsirara maza ciremin kayana

Tunda nake da Salis ban taba ganin bacin ransa haka ba ganin ya nufomu yasa na tsaya a gaban Luba Ina "Dan Allah Abban Ashraf kayi hakuri dan Allah ka bari taje gida ta cire ta Aiko min dashi na hadaka da girman Allah"

"Ai wani iirn tureni yayi yana "ba bakida hankali ba yau zan gwada miki rashin hankali har na siyi kaya da tsada ki dauka ki bawa yarinya da bata San ciwon kanta ba ta kashe aurenta sabida babu kuma har tana da bakin ta ringa gaya min magana ciremin kayan nan yanzu ki bar gidanan"

Yace Yana fincike mayafin jikinta na saki ihu.

Present

Luba

"Asabe kinsan dai ban yarda da wani asiri asirin nan ba ko to yau Hindatu ta kaini bango inaso na kawo karshen zamanta a gidan Alhaji kinsan banda Ina da zuciya mai kyau da har Aisha na rabasu amma Hindatu dai inaso kije wajen mai miki aiki a raba ta da Alhaji inaso Yana dawowa ya danna mata saki uku mu cigaba da Zama nida Aisha da ta zama hoto sabida kishi"

"Luba kenan ai kece tun farko kika bar ta ta sake haka har ta raina ki ai idan haka kikeso tare zamuje wajen mallamin"

"Aa ba wani zuwa da zanyi nidai zan baki kudi ayimin aikin kawai Alhaji na dawowa ya saki Yar iska"

Ta zuge Jakarta ta d'auko kudi ta bawa Asabe ta mik'e tana "bari naje gida kafin ta kira Alhaji tace masa na fita"

Har bakin motarta ta rakata ta shige tana sai sunyi waya.

Alhaji Salis...

MG'S SKINCARE

Dame akafiki yar uwata?
Kyan fatar ko iya gyaran fatar?
Ina riba g macenda t Maida kanta sauran mata?
Shin haryenzu labarinmu kikeji ko kike bayarwa?
Hajiyata miye matsalar?
Fatar takice abun se lahaula?
Kingwada kingwada harkinsare?

Tsakanida Allah yaushe daren yayi balle wayewar garin?

Inbakida labarin MG'S wacce tasanki tasansu,
Gawurtaccen Kuma shahararren kamfanin gyaran fatane,duk lalacewar jiki,duk hautsinewar fata,duk yenda jikinki yazama abun kunya gareki, Ina tallata maki me gabadaya,

Muntarkato,munwarwaro,munqullo duk wani Abu daze maidaki wanke hannu kataba mun qara a cikin kayayyakinmu,muncire,muntsife,munfidda,mun tantance mun hadamaku wasu irin hadaddun lafiyayyun kaya masu masifar goge fata,wallahi duk fitinar fatarki inshallah,kinzo bustop,kisiya kiyikyanda ko mace,kan juyo ta waiwayo ta dubi halittar Allah,

Ga product din kamar hka,
Sabulu 4500

Mg's beauty kit
Karamin kit 12k
Body soap
Facial soap
Body cream
Face cream
Glow oil
Pink lip balm

Flawless skin beauty kit
Babban kit 20k
Body soap
Facial soap
Body cream
Face cream
Scrub
Glow oil
Pink lip balm

Note kowanne d kalanshi nd yanayin packaging dinma aren't the same,

Tsakanida Allah kigafa
Duk wannan garabasar Kuma kinazaune hba taso a dama dake a harkar yar uwata,

Ayi hakuri da sauyin farashi komi yatashine muma b hka mukasoba
Chat:08062991549,07046881166,07067210195,
Call,+2348064532391

NI DA KISHIYOYINA

NA SADNAF

E.W.F

PAID BOOK

Alhaji Salis

A lokacin daya je ya samu mahaifin Aneesa akan turo manyansa izini ya bashi akan ya turo dan Aneesa tace ita tana San shi Kuma mahaifin Aneesa ya dan yi bincike akan Alhaji Salis bai ga Yana da wani matsala ba.

Sati ukun da yayi niyyar yi ya fasa ya d'auko hanyar gida dan ya fadawa Iyayensa ko da wasa bai tab'a kawowa kansa sake aure ba, hasali ma addu'ar sa kullum bai wuce Allah ya raba sa da Luba da Hindatu cikin sauki ba, ya zauna da Aisha uwar yayansa Wanda tunda ya aureta sai dai Santa ya karu a zuciyarsa sai gashi kaddara yasa ta maida shi hoto shi yasan akan dole take zaune dashi sai gashi kaddara ta sake hadasa da Aneesa dayaji Santa a zuciyarsa kwatankwacin irin san da yake yiwa Aisha har a yau da yake da manyan Yara Allah ya hore masa lafiya Yana bukatar nutsuwa a rayuwarsa sabida k'in da Aisha take Masa yasa baya samun nutsuwar da yake so a wajenta tunda shi kadai yake kidansa yayi rawarsa Hindatu da Luba kuwa baya kaunarsu ballantana yaji a zuciyarsa Yana samun nutsuwa dasu, hasali har fargabar kwanansu ya zagayo yake,ko a yanzu da yake san auren Aneesa kasan zuciyarsa cike take da fargaba da tsoro dan Luba ba k'aramin daga masa hankali tayi a auren Hindatu ba ko tunawa baya so yayi kalar cin mutunci da ta masa, tayi dambe kuwa da Hindatu tun kafin ma ya aureta yafi a kirga Inda yake dan samun sauki shine Hindatu itama ba kanwar lasa bace sau tari Yana so ya samu ko wata daya ne a gida ya samu lokaci da yaransa ya samu ya cigaba da rarrashin Aisha sai dai bai isa ba dan tashin hankali Luba da Hindatu ke saka shi tafiyar da bai shirya ba.

Ko daya iso garin katsina sai da ya fara zuwa gidansu mahaifinsa shekara biyar kenan da rasuwarsa mahaifiyar sa ce kawai ta rage masa.

Sai da yaci ya koshi ya fada mata Auren da ya keso ya Kara.

Sai da ta jima bata yi magana ba kafin ta sauke ajiyar zuciya tace "Yanzu Aure zaka sake yi Salisu? Yanzu baka girma da Aure ba? na dauka zaka cemin Afrah ma aka sawa rana, mai zakayi da Aure yanzu tsakani da Allah Salisu? matan ka gasu nan har uku banda tashin hankali da kake so ka Kara karowa kanka tunda ga lokacin da ka tsiri aure aure kayi bankwana da farinciki Aisha dai itace matarka ta rufin asiri daka tashi mata sakayya sai ka auro kawarta Kai ma tunda kayi auren ka sake wani baka Kara samun kwanciyar hankali ba baka tsaya ma a gidanka ba yanzu kana zancen dauko aure anya Karin auren nan naka Mai yuwa ne kuwa?

"Hajiya ya zanyi banida bambancin da Wanda bashida aure shekara da shekaru Ina bawa Aisha hakuri ita kawai nake Jin dadin zama da ita kema wai a haka arzikinki naci Aisha take zaune dani har yanzu.

Luba da Hindatu kaddara tasa na aure su hajiya auren nan da zanyi wlh na dolene kawai da ace Aisha zata yafe min laifin da na mata wlh da ba wani aure da Zan sake to ya zanyi kimin addua kawai dan ko na auren ba gida daya zan ajiye su ba yarinya ce ma wacce zan aura bata fi Sa'ar Aliyu ba"

"Kai yanzu sa'ar Yar cikinka zaka auro cikin manya manyan matan nan naka Salisu kanka daya kuwa ai wahala kawai Yar mutane zata zo ta sha a gidanka ko ka manta suwaye matan naka? Ina laifi ma kace babba ka d'auko zaka aura?ai daga lokacin da ka aikata kuskuren auro kawar matarka ka tusa mata bakin cikin da nasan har ta

mutu bazata tab'a mantawa ba Kai ma fa ba zaka tab'a samun farin cikin da kake so ka samu a rayuwar aure ba wlh ba baki nake ma ba hakki ba Wasa bane ba ni nasan Aisha cewa kawai take ya wuce amma ba yafe maka tayi ba"

"Hajiya Kun kasa ganewa kaddara yasani auren kawar Aisha Kuma rabon Yara uku ko inaso ko bana so tunda Allah ya kaddara da rabo a tsakanin mu sai na aureta bansan mai yasa Aisha ta kasa ganewa ba wlh bata kaini bakin cikin zama da Luba ba duk tsawon shekarun nan hajiya wlh ban tab'a kaunarta ba zaman hakuri kawai nake Hindatu Kuma kema kinsan kaddarar da ta saka na aureta mahaifinta ya kakab'a min aurenta nidai kawai ki cigaba da tayani da Addu'a ayiwa su kawu magana suje su kai kudin auren da sadaki tunda mahaifin yarinyar yace wata biyu za'a saka"

"Tom Allah ya bada sa'a Salisu bani wayata na kira kawun naka"

Alhaji Salis ya mik'e ya d'auko mata wayar a gaban mudubin d'akin ya Nemo lambar kawun yayi dailing tare da sakawa a handsfree.

Koda Hajiyar ta fadawa kawun tambayarta kawai yayi yaushe za'a je dan Alhaji Salisu Kam ba wanda baya san faranta masa sabida hannunsa a bud'e yake har dangi na kauye yana hidimanta musu.

Bai bar gidansu ba sai karfe shidda dan ji yayi ma Yana fargabar zuwa gidan bai san mai zai je kuma ya tarar ba idan a tsarine yau d'akin Aisha ya Kamata ya kwana tunda har yayi wa Luba kwana daya amma dan masifa sai ya karasa mata wanan kwana dayan idan ba haka ba kuwa bai Isa ya runtsa ba.

Koda ya isa gida da Bismillah ya doshi bangaren da yake na yaran dan part wajen uku ne a gidan masifar Luba yasa duk suka zaune part daya duk da katone na gaske sai daya part din daya hade da nasu sabida yara.
Ta k'ofar tsakar gidan ya shiga part din yaran a Palo ya tarar da su duk a zaune Afrah tana Kan doguwar kujera a zaune,Aliyu na gaban tv sai yaran Luba Faisal fawazz da bintu, sai na Hindatu da sune kusan Yara a gidan Mubarak Ummulkhairi sai Ummi.

Duk suna ganinsa Suka yi wajensa da gudu banda manyan.

Ya saki murmushi yana shafa kansu tare amsa gaisuwar da suke masa.

Sai da ya gama amsa gaisuwar su ya samu waje ya zauna dan bama yaso ya Shiga Bangaren iyayen duk da sun san daga tafiya yake hakan bazai Hana su daga Masa hankali ba.

Afrah dake k'ok'arin mik'ewa ya kalla Yana "Ina Nana banganta ba"?

"Tana wajen hajiya umma wai zata mata kitso Abba bari na d'auko ma ruwa"

"Ki barshi kawai daga gidan hajiya nake lokacin sallah yayi ku je kuyi alwala kuyi sallah ko nima bari nayi alwala naje massallaci"

Da sauri mazan duk suka kada kansu suka yi waje da Alhaji Salis.

Basu Kuma dawo gidan ba sai da aka iddar da Sallah Isha.

Alhaji Salis ji yake kamar Kar ya Shiga gidan.

A hankali ya doshi bangaren matan gidan hayaniyar da yake ji ya saka shi tsayawa cak ya fara jan sallati muryar Aisha da yaji yasa mamaki Kama shi dan bai tab'a Jin hayaniyarta dasu ba idan dai zasu kwana suna fada bata shiga harkarsu.

Da sauri yayi cikin gidan ya tsaya a bakin k'ofar Yana kallon Aisha dake sanye da hijabi har kasa hannunta rik'e da na Nana da bata fi shekara goma sha uku ba tana ta kuka "duk abinda zakiyi Luba kiyi luba ban hanaki ba amma idan har zaki tab'a Nana wlh bazan d'auka ba ki tab'a kowa daga Kan Ashraf zuwa Kan ummi amma karki sake ki yarda ki Kara tab'a Nana kinji na gaya Miki"

"Sai na tab'a ta Aisha sai dai kiyi duk abinda zakiyi tunda ba fin kowa tayi a gidanan ba wacce wata Nana da bazaa aiketa ba daurin gindin da ta samu a wajenki yasa take yiwa mutane rashin kunya kamar yarinya nan tace baza'a aiketa ba,tunda har yaran gida ma ake aikensu wacce wata agola da baza'a aiketa ba wa ta fi a gidanan aikuwa indan har na aiketa bata je ba wlh sai na doketa idan na daketa ki dau mataki ko a zuciya a maida ta inda ta fito"

"Luba ba fa wai tsoronki nake ji ba duk tsawon lokacin nan kike abinda kika ga dama Ina kyalleki idan shi Salisu asirice shi kikayi ni ba asirceni kikayi ba wuri na baki sabida kiyi duk abinda kikeso kiyi domin hankalina da naki ba daya bane daga lokacin da na fara biye miki mun zama daya dake amma wlh wlh kinji na rantse idan kika kuskura kika Kara tab'a Nana wlh zan baki mamaki"

"Ki bani yanzu idan ke Yar halak ce bari na daketa naga mai zakiyi"

Luba tace tayi wajen Nana da sauri

"Lubaaa ya isheki haka"

Alhaji Salis yace cikin wani irin tsawa daya sa suka juya dukansu suka kalli bakin k'ofa.

Alhaji Salis ya nufi wajensu cikin wani iirn b'acin rai kafin ya Isa wajensu Aisha ta masa wani irin kallo ta ja hannun Nana tayi dakinta da ita.

Luba kuwa ta hau girgiza tana jiran isowar Alhaji Salis

"Yana kuwa isa wajenta ya hau masifa "Luba ke wacce irin mata ce ke? A rayuwarki sam bakya san zaman lafiya kinfi san ayita tashin hankali da ke wanan wane irin balai da masifa ne Luba na gaji fa wlh wlh nagaji bazaki kasheni da raina ba har ace nafi samun kwanciyar hankali a waje akan a gidana Kuma duk gidanan ba mai daga min hankali sai ke a wane dalili"?

"Akan me toh za'a ce kar na aiki Nana wacce Nana da har za'a ringa gindaya min sharruda a kanta wa tafi a cikin yaran mu haka kawai dan San zuciya zaa ringa fifita ta sabida ta hada jini da Aisha toh wlh bazata tab'a sabuwa ba nima Zan dauko ilham ta dawo gidanan da zama ehe ai ba fina tayi a gidanan ba"

"Alhaji kawo jakarka na kai ma d'aki ai yaci ka Saba da halinta kake wani damuwa da abinda tayi ita idan bata San ciwon kanta ba ai Kai kasani haka kawai daga dawowarka zaa saka ma ciwon kai muje ka watsa ruwa kaci abinci na maka tausa"

Hindatu tace tana k'ok'arin karbar jakar hannun Alhaji Salis da idonsa ya Kada yayi ja kansa har wani sara Masa yake

Wani irin duka Luba ta kaiwa hannun Hindatu dake k'ok'arin karbe jaka tana "toh katuwar kwartuwa kafin kija shi d'aki dan jarraba yau kwana na ne ba ruwanki dashi kwana daya yayi a dakina yayi tafiya sai ya karashe min kwana dayan zai koma hannun uwar gida duk jarrabarki sai ki hakura sai kwananki ya zagayo"

"Kefa kwana ya dama da gado Luba tarbar da ya Kamata ki Masa ne bakiyi ba shiyasa nake San na masa,
tunda ke din ba abinda Kika sani sama da masifa da gado"

Wani irin Ashar Luba ta dura wa Hindatu Suka fara zage zage.

Alhaji Salis ya zube akan dogon kujera tare da dafe kansa Yana sallati.

Sosai yake ji kamar ya sa hannu aka yayi ta kurma ihu.

Magana yake musu amma Ina idonsu ya rufe Shirin dambe ma suke.

A hankali ya mik'e hannunsa dafe da kansa yayi d'akin Aisha

Yana tura k'ofar ya sameta a gefen gado a zaune tana ta share hawaye gefenta Kuma Nana ce a zaune a kasa.

Shigowarsa yasa ta dago da kanta ta zubawa Salis ido.

Salis kuwa yaji kirjinsa ya masa wani irin nauyi da ganin Aisha a cikin irin Wanan halin shekara nawa Aisha na zubar hawaye da duk shi ya jefata a cikin wanan halin.

"Aishaaaa"

Ka fita Salisu dan Allah ka fita a yanzu bana san magana ka fita dan girman Allah karka Kara min ciwo akan Wanda nakeji a zuciyata"

Salis a hankali ya juya ya fita daga d'akin Yana hadiyar yawu sabida ji yayi makoshinsa ya bushe har ya koma palon suna masifa akan kujera yayi kwanciyarsa ya runtse idonsa Yana Hindatu idan ban isa da Luba ba ke na isa dake dan Allah ki rabu da ita"

"Shikenan Alhaji ni bansan ma mai ya kaini biyeta ba kayi hakuri"

Tayi hanyar dakinta tana zabgawa Luba harara

"Alhaji tashi mu tafi daki na hada ma ruwan wanka"

"Bazan tashi ba"

"Bangane bazaka tashi ba kasan dai yau a dakina kake ko"?

"Anan zan kwana bazan Shiga d'aki ba"

"Idan kwanan Aisha ko Hindatu ne ai ba a Palo kake kwana ba"

"Idan kina da k'arfi Zaki iya daukana ki kaini d'akin"

"Banida karfin daukar ka amma kasani nima anan din zan kwana nima dan bazan shiga d'aki a ci amanata ba"

Alhaji Salis yaja tsaki dan kansa sosai yaji yana neman rabewa biyu ya gaji da Luba ya gaji ya rasa ya zaiyi da ita Aisha ce tsaye a ransa inama zata barshi da ya kwana a dakinta ya kwana Yana bata hakuri hawayen ta daya gani ba karamin daga masa hankali yayi ba.

A takaice a ranar a Palo ya kwana Luba itama ta d'auko bargo ta kwanta a kasa ta dora kafarta a kan kujerar wajen kafarsa wai kar ma bacci ya d'auketa ya tashi yaje d'akin Aisha tunda nan yafi zuwa idan bacci ya d'auketa.

Past

Aisha

"Dan Allah Abban Ashraf ka bari ka rabu da ita taje daki ta ciremin"

"Wlh sai ta cire kayan nan ba bata da hankali ba"

Ganin dagaske Salis yake yasa na zube agabansa tare da kankame kafarsa na saka kuka Ina magiya Luba kuwa wani irin hucci take da alama da tana da k'arfi sai ta kaiwa Salis duka.

Salis kuwa nasan wuyanta na fara kuka nasan na gama dashi bayasan kukana ko kad'an.

"Dalla sake min kafa wlh sai ta ciremin kayan nan idan bakyaso ni Ina da wayanda zan bawa masu mutunci Kuma wlh daga yau Kar na sake na sake ganin ta a gidanan tunda tace ban isa na rabaku ba sai nagani ta tsaya a matsayinta na bazawara ta nemo zawara Yan uwanta ta cigaba da hulda dasu tana aron kayansu"

"Salisu yau ni kake wa cin mutunci sabida nazo gidanka"?

"Anyi miki cin mutunci idan kin zuciya ki rabu da Aisha Kar na sake ganin kafarki a gidanan dan tunda har ta fara d'aukar kayanta masu tsada tana baki nasan zata iya Jin maganarki ki mata hudubar tsiya"

"Salis dan Allah ka bari haka da kakeyi bai dace ba daga aron kayana bai dace ka mata irin wanan cin mutuncin ba haba salis ka manta wacce Luba ne"?

"Wacce ita wato dan Kinga ban tuje kayan daga jikinta ba ko wlh kafin na fita waje na dawo ta tabbata ta cire kayan nan ta Kuma bar gidanan idan Kuma kin zabe ta a kaina sai ki bita ku tafi amma matsawar a karkashina kike wlh sai kin rabu da ita"

Ya juya fuuu yayi waje.

Luba ta bishi da ido hawaye na gudu a fuskarta na Mik'e tsaye Ina k'ok'arin Magana ta daga min hannu ta Shiga d'akin yarana na bita Ina bata hakuri.

Ta fashe da kuka tare da zuge zip din rigar ta cire rigar ta cire sarka da dan kunnen duk abinda take kuka take sosai nima na fara kukan Ina cigaba da bata hakuri wlh a rayuwata bana san wulakanci Salis ya wulakanta Luba bai kyauta ba tana gama cirewa ta d'auko zanin wanka dake rataye a kan k'ofar bandaki ta daura duk abinan

bata cemin komai ba ta d'auko hijabin dake kan gado tayi hanyar waje tana cigaba da shesheka "Dan Allah Luba kiyi hakuri dan girman Allah wlh ban taba tunanin Salis zai iya min haka ba wlh ko da Wasa ban tab'a fada masa kina aron kayana ba"

Ta juyo da jajjayen idonta ta fara nuna kanta "har ni Salis zai yiwa irin wanan cin mutuncin dan na ari kayanki duk a tunanina yanda na d'auke ki haka Kika d'aukeni wlh ban daukeki kawa ba tamkar Yar uwata nake jinki a raina yau akan abun duniya salis ya murza idonsa yamin cin mutuncin nan ba komai Aisha insha Allahu bazai Kara ganin kafata a gidansa ba wlh ba'ayi namijin daya Isa ya rabani dake ba amma tunda shi ya rabamu shikenan idan naje gida Zan aiko miki sauran kayanki da wanan hijabin nagode"

Tayi waje da sauri tana toshe bakinta.

Na zube a kasa ma fashe da kuka a lokacin wlh har wani daci nake ji a bakina sabida b'acin rai bansan mai ya hau Kan salis yayi mata irin wanan cin mutunci ba Ina laifi ma ya bari ta tafi inyaso duk sai yamin gargadin da zaimin amma irin Wanan cin mutunci Kamar Mai jiran kiris.

A haka ya shigo d'akin ya Sameni Ina kuka

"Kinsan wlh kina bani mamaki Aisha yanzu ke kinyimin adalci kenan na siya miki Kaya Mai tsada ki dauka ki bawa yarinyar da bata San mutuncin kanta ba ta kashe aurenta dan kawai mijinta bashida kudi dan na koreta kike wanan kukan Kamar tare aka haifoki da ita ko idan kun rabu rayuwarki ta tsaya"?

"Haba salis wlh baka kyauta ba dan Adam ba'a abin wulakantawa bane har akan abin duniya ka wulakanta Luba haka Haba Salis ka manta irin hidimar da Luba tayi dani a bikina da yan uwanta tsakani da Allah dan ta nemi aron abu a wajena na bata shine zaka mata haka Salis bansan ka da rowa ba wlh baka kyauta ba arzikin nan naga Allah ne ya baka abaya baka dashi sai yanzu dan Allah ya ma niima baka San wasu su mora wlh baka kyauta min ba"

Tunda na fara magana kallona kawai yake Koda na gama sai cewa yayi "toh yanzu so kike naje gidansu na bata hakuri na maida mata kayan?

"Ni ba haka nace ba wulakanci da ka mata ne banji dadi ba"

"Allah ya kyauta"

Yace tare da mik'ewa ya bar d'akin.

A ranar ban Kara walwala ba dan wlh abinda Salis ya yiwa Luba ya dameni.

Gashi ba waya a lokacin ballantana na kirata na sake bata hakuri kwana uku a tsakani da yamma sai ga wani karamin kanin luba ya shigo da niki nikin leda wai inji Luba tace a kawomin.

Salis na zaune a palo yace masa ya kawo ya gani bakinsa sake cikin mamaki.

Nidai ban motsa ba Salis ya fara fito da duka kayana da Luba ta tab'a ara a wajena Yana ikon Allah "Ai bansan ku biyu nake siyawa Kaya ba Aisha dama kayan duk da nake siya miki Luba kike bawa ni Ina iya k'ok'arina dan naga na faranta miki amma kina bawa kawarki dan baki san zafin kudi ba toh yayi kyau"

"Kai mayar mata da kayan kace ba'aso"

Yacewa kanin Luba ya kuwa dauka ya juya ya fita nikuwa hawaye ya hau wanke min fuska.

A takaice sai da muka tafi sati biyu Salis ya kasa gane kaina daga baya san damuwata nasani tuni ya damu ya hau Kuma rarrashina Yana cemin abinda nayi bai dace ba nace Masa ni a rayuwa bazan iya wulakanci ba bazaa iya tambayata abu nace babu ba wlh ban iya Kuma banaso ya rabani da luba dan banaso taga dan dagasken da na samu niima nida mijina muka wulakanta ta.

Ya saki murmushi Yana toh shikenan bazai kara shiga tsakanina da Luba ba amma shi dai Luba alakata da ita bai ga alheri ba.

Baa san ransa ba ya kawo ido ya zuba min yamin Allah ya isa idan na sake bata kayan daya siya da kudinsa sai dai na siya da kudina na Bata.

Nidai ban damu ba tunda na samu bai datse kawancen mu ba,da kaina na shirya naje gidansu ban sameta ba haka na zauna na jirata ko da ta dawo ta gani sai ta hade rai "ke da mijinki yace ki rabu dani mai Kika zo nema"?

"Dan Allah komai ya wuce Luba kiyi hakuri da abunda ya faru shima yace kiyi hakuri"

Hmm kawai tace bata Kara cemin komai ba nidai nayita janta da hira tana bani amsa sama sama da nazo tafiya ta rakani na bata kyautar kudi.

A yanda na sake dawo da Luba rayuwata kenan.

Amma ta daina aron kayana sai dai ta tambayeni kudi na bata a haka cikina ya isa haihuwa na haifi da namiji aka sa Masa Aliyu arziki Kamar karawa Salis ake yi dan dagaske bansani ba ko lokacin banida wasu burika ne Rabin kudina Luba nake bawa burina ta sake samun miji tayi aure, dan Hamza yayi aurensa Salis ya bashi jari ya bud'e shago a lokacin kafin yayi Aure ma Salis ya sakoni gaba akan na tsara Luba ta koma dakinta wlh zai bata jari da kuwa nayiwa luba maganar kamar ta dakeni akan ko a lahira taga Hamza guduwa zatayi.

A haka muka fara shirye shiryen komawa sabon gidan da aka kwashi shekara uku ana ginawa wlh a lokacin babu Kamar gidan a unguwarmu gida ne Salis ya narka masa mugun kudi,daidai da kayan cikin gidan duk na waje ne.

Duk tsofafin kayana da Suma da kyaunsu haka yace na bada su na kuwa loda a mota aka kaiwa mahaifiyata ba abinda muka dauka a gidan komai sabone.

Har Kaya duk sababi ya mana Salis ne ma ya dan hada Walimar tariya nima na danyi gaya Luba kuwa itace Kan gaba tace har mafarkin gidana take sabida haduwarsa kullum maganarta a Ina zata samo miji Mai kudi irin Salis ai ita tama Raina kudin wanan Alhaji da yake santa.

A ranar da muka tare da yawa Yan uwa sun zo sun Kuma kwana dan duk Wanda yazo sai yaji kamar bazai tafi ba a ranar itama Luba ta kwana a gidan dayake gidan sama da kasa ne sama ne bangaren Salis kasan kuwa duk nawane ba wanda ya hau sama duk muka baje kolinmu a kasa dan wlh Ina balain san mutane yaran yayana suma duk a gidan suka kwana sai saintyn gidan suke Ina dariya Khadija da muhasim suma Suka ce ba abinda zai Mai dasu gidansu sun samu gida.

Wlh banki ma duk Yaya ya barmin su ba amma nasan bazai tab'a barinsu ba yace idan sunyi hutu zasu ringa zuwar min hutu wanan kenan.

Shekara daya a tsakani wani mugun iftilai ya fada mana da bazamu taba mantawa ba muhasim aka Kai gida bakinta a karkace wuyanta baya tsayawa Koda aka zo aka gayamin hankalina a balain tashe nayi gidan yayana Ina zuwa naga gidan a cike taf.

Koda na ratsa mutane na shiga ciki a kwance na tarar da muhasim a tsakiyar kafet aunty Mami idonta yayi luhu luhu Yaya mustapha kuwa jikinsa rawa kawai yake.

Na zube agaban muhasim da bakinta ke dalalan yawu tana binmu da Ido wuyanta shima a karkace.

Cikin tashin hankali nace "Yaya Mai ya sameta haka"?

"Wlh bamu sani ba daga makarantarsu aka kawo Mana ita akan an ganta a yashe a bakin gate.

"Innalillahi wa Inna ilaihi rajiun"

"Mu kaita asibiti mana mai ya sameta haka"

Duk hankalinsu bai Kai su kaita asibiti ba sai da na nemo mota muka dunguzuma muka tafi asibiti.

Present.

Alhaji Salis

Tunda ya tafi massallaci bai dawo gidan ba sai da safe har wani zazzabi yaji yana neman rufeshi.

Yana shigowa suka hada Ido da luba dake karkada kafa ya d'auke kansa tare da nufar d'akin Aisha

Yana Jin Luba tana maganganu kasa kasa ko ta kanta bai bi ba ya tura k'ofar Aisha a hankali sallamar da yayi ta amsa ko dagowa batayi ta kalleshi ba ta maida idonta ta rufe.

Ya zauna a gefen gadon ya zuba mata Ido tsawon minti biyar kafin yace "Aisha dan Allah dan annabi ki tashi muyi magana wlh nagaji da irin zaman da muke yi dake Allah fa muna masa laifi ya yafe Mana haba Mana"

Sai a lokacin ta bud'e idonta ta tashi zaune tana "Wani abu ne ya faru"?

MG'S SKINCARE

Dame akafiki yar uwata?
Kyan fatar ko iya gyaran fatar?
Ina riba g macenda t Maida kanta sauran mata?
Shin haryenzu labarinmu kikeji ko kike bayarwa?

Hajiyata miye matsalar?
Fatar takice abun se lahaula?
Kingwada kingwada harkinsare?
Tsakanida Allah yaushe daren yayi balle wayewar garin?

Inbakida labarin MG'S wacce tasanki tasansu,
Gawurtaccen Kuma shahararren kamfanin gyaran fatane,duk lalacewar jiki,duk hautsinewar fata,duk yenda jikinki yazama abun kunya gareki, Ina tallata maki me gabadaya,

Muntarkato,munwarwaro,munqullo duk wani Abu daze maidaki wanke hannu kataba mun qara a cikin kayayyakinmu,muncire,muntsife,munfidda,mun tantance mun hadamaku wasu irin hadaddun lafiyayyun kaya masu masifar goge fata,wallahi duk fitinar fatarki inshallah,kinzo bustop,kisiya kiyikyanda ko mace,kan juyo ta waiwayo ta dubi halittar Allah,

Ga product din kamar hka,
Sabulu 4500

Mg's beauty kit
Karamin kit 12k
Body soap
Facial soap
Body cream
Face cream
Glow oil
Pink lip balm

Flawless skin beauty kit
Babban kit 20k
Body soap
Facial soap
Body cream
Face cream
Scrub
Glow oil
Pink lip balm

Note kowanne d kalanshi nd yanayin packaging dinma aren't the same,

Tsakanida Allah kigafa
Duk wannan garabasar Kuma kinazaune hba taso a dama dake a harkar yar uwata,

Ayi hakuri da sauyin farashi komi yatashine muma b hka mukasoba
Chat:08062991549,07046881166,07067210195,
Call,+2348064532391

NI DA KISHIYOYINA

NA SADNAF

E.W.F

PAID BOOK

Page 6

Alhaji Salis

"Aisha kin hanani samun nutsuwar zuciya na rokeki nayi miki kuka na sa mahaifiyata ta rokeki duk wayanda kike Jin kunyarsu na hadaki dasu Abba da Umma ma sun baki hakuri akan laifin da na miki Aisha kin k'i ki hakura tsawon shekarun nan Aisha karki manta fa bawa bai isa ya tsallaka kaddararsa ba rabo ne tsakanin nida Luba shiyasa Allah ya hukunta na aureta"

"Toh kaji na ce ma wani abune yanzu"?

"Haba Aisha kafin na auri Luba ai ba haka mu ke zaune da ke ba yanzu kiri kiri nake ganin kiyayya ta a idonki"

"Hmmm daga lokacin da ka auro Luba da ka san kawata ce yaci kasan ka tarwatsa duk wata soyaya dake tsakanin mu da yarda har gobe Zan fada da babban murya wlh tallahi zaman yarana nake da hakuri babu digon kaunarka a raina Koda duk mutanen duniya ne zasu hadu su ringa bani hakuri batun Kuma baka da nutswar zuciya ai ba ni na hanaka nutsuwar zuciya ba tunda kana da luba,da kafi so da kauna ai Ina ganin baka da wani matsala abu daya nakeso.na fada ma shine ka ja mata kunne duk da nasan ba iyawa zakayi ba amma dai zan fada ma kace Kar ta kuskura ta Kara tab'a min Nana da na karbi amanarta wlh duk ranar da ta kuskura ta Kara tab'ata a ranar ba ita ba har kai sai na baka mamaki kaga duk abinda kuka min ban tab'a ce muku komai ba wlh ko Ashraf naga tana duka bazan kalli Inda take ba amma idan har ta tab'a min Nana wlh zan baku mamaki Banda kaddara data gifta mana da ba abinda Nana zatayi a gidanan ballantana har a kirata da agola"

Alhaji Salis kasa magana yayi ya zubawa Aisha Ido duk Yana jin kwarin gwiwar daya zo dashi ya sace.

"Aisha auren nida Luba da Hindatu wlh kaddara ce zan sake rantse miki ba wacce nake kauna a cikinsu".

"Hakane kam tsabar kiyaya ma gashi har da yaransu uku uku nifa daka so su da Kar ka so su Salis ba abinda ya shafeni bane bansan dalilin daya sa kake gayamin ba"

"Aisha rashin samun hadin kanki da rashin bani dama yasa zan sake Aure"

Sai ta saki murmushi har hakoranta suka bayyana tana "Allah ya sanya alheri kace su Luba za'a sake samun sabuwar kanwa"

"Abinda Zaki ce kenan Aisha yanzu banida wani mutunci a idonki da zakiyi kishina"?

"Ina mutuncin yake Salis mutunci ai ya dade da zubewa sai zaman ibada kawai kishi kuma ba sai kana san mutum zaka ji kana kishinsa ba ai ni yau banki Allah ya gwada min ranar da zaka shigo min da takardar saki ba"

Zuwa lokacin ran Alhaji Salis ya Kai kololuwa wajen b'aci

Ya mik'e yana " shikenan Aisha idan saki kikeso insha Allahu mutuwa ce zata rabamu ba abinda zai saka na tab'a sakin ki insha Allahu watarana zaki yafemin"

Daga haka ya fice daga d'akin Aisha taja tsaki.

Koda ya fito a bakin k'ofa yaci karo da Luba ba yau ya fara Kama ta tana labe ba ko a d'akin Hindatu yake haka take zuba laben ya zuba mata wani mugun harara Yana "Baki ji dadi ba wlh duk da kin manyanta kin kasa girma Allah ya kyauta"

"Ikon Allah ni na aikeka wajenta ta ma rashin mutunci da zaka zo ka hucce a kaina"

Bai kulata ba yayi waje ko zaman gidan bayaso yayi.

Sai da ya fara Shiga Bangaren yaran duk ya dubasu dan asabar ta Kama ba makaranta ya shafa kan Nana da murmushi Yana tambayarta mai zai taho mata dashi ta hau lissafa masa ya gyada mata kai tare da yin waje.

Yana Jin maganar luba a bayansa akan ga abincinsa can ko kallonta baiyi ba ya shige motarsa ya nufi gidansu.

Bashida inda zai je sama da can gwara ya wuni a wajen hajiyarsa da dai ya zauna a gidan.

Koda ya isa gidan Hajiyar sa bacci take bata tashi ba hakane yasa yayi kwanciyar sa a 3 seater ya nemo lambar Aneesa bugu biyu ta d'auka muryarta kawai data doki kunnensa ya saka shi sakin Ajiyar zuciya har a zuciyarsa yana kaunarta hira suka farayi ya maida kansa kamar Saurayi kalmomin soyayya kuwa ko saurayi albarka har yanzu Yana mamakin yanda akayi Aneesa ke Sansa duk da tazarar dake tsakaninsu.

Sunfi awa suna waya da ita har hajiyar ta farka ta fito ya hadasu suka gaisa hajiya ta musu fatan alheri ta maida Masa wayar tana jinjina auren a ranta da Jin muryar ta ma yarinya ce zata ga yanda Salisu zai yi da su Luba.

A takaice a cikin satin kawun Salis Suka Kai Dubu dari biyar dari uku kudin aure dari biyu sadaki.

Lefe dama Yayar Aneesa zai bawa ta hada dan haka Aneesa tace sunyi magana.

Duk da shiryen shiryen da yake zuciyarsa cike take da mugun fargaba sam baiji zai iya fadawa Luba da Hindatu ba,yasan kuma Aisha bazata tab'a fada musu ba.

Yana ta nazarin yanda zaiyi kafin auren.

Gidansa kullum cikin tashin hankali ake na yau daban na gobe daban.

Ya rasa yanda zaiyi iya wanan kawai inya gani sai ya ringa hararo Ina ga ya auri Aneesa duk da baiji a ransa zai hadasu gida daya ba warewa Aneesa gidanta zaiyi daban.

Past

Aisha

Duk binciken da likitoci sukayi basu gano abinda yasa muhasim bakinta ya karkace wuyanta yak'i tsayawa waje daya ba sun dai gane tana d'auke da ciki wai har na tsawon wata uku"

Aunty Mami har da sumewarta.

Yayana Kuma ya Yanke jiki ya Fadi dan kafafunsa rawa kawai suke.

Tunda nake bamu tab'a ganin tashin hankali irin na ranar ba kuka kuwa har sai da hawayen idona ya kafe ni ba cikin da aka fada yafi daga min hankali ba yanda bakinta ke zubar yawu,kasan raina Kuma inata mamakin garin yaya Muhasim ta samu ciki dan nidai nasan Yaya Yana da balain tsauri.

A asibitin Salis yazo ya same mu shima cikin tashin hankali kasancewarsa likita yasa ya nemi likitan da file din muhasim ke hannunsa akan Karin bayani.

Bazan manta k'ok'arin da Salis yamin ba a lokacin dan babban asibiti aka Kai mu ba karamin kudi ya kashe ba Muhasim ta sha.gwaje gwaje baa san abinda ya sameta ba, yayana har kwantar dashi akayi shi da Aunty mamy dan suna balain ji da muhasim gashi yarinya ba ruwanta duk a cikin yaran tafi su hankali nima kaina nafi kaunarta.

Haka na tsaya akan yayana da matarsa tamkar nima a bani gadon dangi duk da suka ringa zuwa duba mu ba Wanda yasan muhasim nada ciki dan Ina ganin sirrin mu ne banda ma Salis nasan dole yasani ta wajen likitan da sam bazan so ya Sani ba duk da duk zargin da akeyi Kamar fyade dai akayi Mata dama ana rade raden Yan makarantar su mazan baji suke ba sun tab'a raping din wata Yar ajinsu da yake babbar makaranta ce aka rufe case din.

A yanzu haka an saki kudi dan anyi binciike Wanda yayi wa muhasim wanan aika aikan.

Duk uban kudin da ake narkawa dan Muhasim ta samu sauki bamu ga alamar sauki ba sai a wajen Allah a haka dai ake ta siya mata.maganguna masu tsada.

Luba itama ba laifi kullum sai tazo asibitin duba mu tamin mutunci kwarai tunda ta nuna damuwata damuwarta ce.

Da nasiha da waazi yayana da Aunty Mami suka runguma kaddarar da ta same su Allah yasan damuwarsu nima ya haifa min tsananin damuwa babban tashin hankalinsu yanzu bai wuce cikin jikinta da baa san ko na waye ba dan har Yan ajin su da aka san suna magana da ita sai da aka kama su duk yanda aka so a gane ko su suka yiwa muhasim fyaden ba'a gane ba.

Yayana ma yaso a zubar mata da cikin likitoci suka bada shawarar hatsari zaa Kara jefata idan akace zaa zubar mata da ciki abar mata cikin idan lokacin haihuwarta yayi sai a yi Mata operation.

Abinan daya same mu yasa duk na rage walwala salis ma ba wani samun kulawata yake ba.

Zirga zirga kawai nake daga gidana zuwa gidan yayana.

Daga dogon tunani da shawara muka yanke kai Muhasim Bauchi wajen iyayenmu daga su ba wani bare daya san muhasim nada ciki sai Salis.

Dan ko Luba ban fada mata ba ita cemin ma take Aljannu ne suka shafi muhasim din.

Anan bauchin aka cigaba da bawa muhasim magani ana kula da ita Aunty Mami mace ce mai kib'a daga wanan tashin hankalin daya samu muhasim tayi wani irin zabgewa kamar mai cutar Aids.

Yayana kuwa Rabin kudinsa a nemawa muhasim magani ne dan shima ya fara yarda.shafar Aljannu ne.

A takaice a haka muhasim lokacin haihuwarta yayi aka mata operation aka ciro mata katuwar jaririya mai Kama da ita nima lokacin Ina d'auke da cikin Ummi haihuwa yau ko gobe.

Rashin zaman katsina sosai da zirga zirga yasa bamu fiye samun zama da Luba ba.

Ganin jaririyar Muhasim da aka sawa sunar Aisha da bansan dalilin daya sa yayana ya zabi sunan ba yasa naji kaunar yarinyar har a raina ni da kaina na zabi a ringa kiranta da Nana.

Na lura Kamar daga yayana har Aunty mamy basa san Rainon Nana dan har yayana cewa yayi ko gidan marayu zai kai Nana ni kuwa nace masa ba sai an kai ta ba su bani ita zan riketa.

Yayana cemin yayi ba lailai Salis ya yarda ba nace masa indai Salis ne nasan bashida matsala.

Koda na koma katsina na tari Salis da zancen shiru yayi yana kallona har na fara Jin ba dadi a raina yace min anya zan iya kuwa da wane zanji da rainon cikin jikina ko da rainon Nana sai yake ganin kamar bazan iya ba bayaso na dorawa kaina wahala ko dai maganar yayana zanji a kai ta gidan marayun.

Na girgiza masa kai akan zan iya nidai kawai ya bani izinin karbota.

Kamar dai na masa dole.yace min to Shikenan.

A yanda Nana ta dawo hannuna kenan kaunarta a zuciyata ta daban ce Inda nasan haka ya hada da san da nake yiwa muhasim da tausayin mahaifiyarta da ke fama da larura.

A lokacin da Luba tazo gidana sakin baki nayi Ina kallonta dan wani irin kyau naga tayi Kamar wata amarya,kayan jikinta ma masu balain tsada ta Sha lullubi har saman kanta Kamar dai matar aure.

Ni Ina Kare Mata kallo ita Kuma ta zubawa Nana Ido dake kwance a doguwar kujera tana "A Ina kika Samo 'ya nidai nasan ba haihuwa kikayi ba tunda ga ciki nan a jikinki"

"Wlh yarinyar wata Yar uwarmu ce na karbota dan maman ta tana haihuwa ta rasu.

Ta saki sallati tare da nufo wajen da na kwantar da ita ta d'auketa tana "Allah sarki baiwar Allah kice bata san mahaifiyar ta ba

Kwalla ya zubomin na kashe muhasim da nayi da ranta da tausayin ta hanyar da aka samu Nana Ina "wlh kuwa"

Na share hawayen fuskata Ina cigaba da kallon luba da nidai ta canja min sosai har sai da na kasa hakuri nace "Luba Kinga yanda Kika canja kike kyalli Kamar wata amarya kuwa"?

Ta saki murmushi tana "Ai amaryar ce tunda na kusa shiga daga ciki"

"Dan Allah fa"?

Nace cikin tsananin murna Ina "wa kika samo dan da alama kin samu irin wanda kike so"?

"Wlh na samu Aisha alhamdulillah tunda na kwallafa a raina sai na samo Mai kudi na samu dai"

"Kai Alhamdulillah na miki murna sosai wlh kawata a Ina yake aiki"?

"Gidan mai ne dashi fa sai dan aikin asibiti da yakeyi"

"Kai madalla naji dadi wlh ya turo manyansa?mai mata ne"?

"Ke fa dan baki fiye zama bane amma da duk kin san halin da ake ciki,ya turo manyansa mana a ranar da aka kai kudin kawai aka daura Auren,Yana Kuma da Mata"

"Na saki baki Ina kallon ta cikin tsananin mamaki"

"Wai kina nufin yanzu haka da aurenki"?

Ta saki dariya "kwarai kuwa tarewa ne dai banyi ba sai wani satin"

"Kai wai dagaske kike ko da Wasa"?

"Wlh dagaske nake toh mai abin mamaki nifa ba budurwa bace bazawara ce ni, shima ba saurayi ba wane shiri za'ayi ai kawai Aure aka daura zan tare sati mai zuwa"

Na saki ihu dan har ga Allah wlh kamar na taka rawa haka na ringa ji "Na miki murna kawata wlh bakiji dadin da naji ba Kai Kai Kai ke kinji dadin da nake ji a zuciyata a Ina Kuma zaki zauna"?

"Abuja zan zauna"

"Aikuwa duk da uban cikin jikin nan nawa dani zaa kai ki insha Allahu haba shiyasa wlh da kika shigo naga kina ta walwali Kai Aure ma rahama ne wlh zanso kuwa ganinsa ko baki bashi labarina ba"

"Kai ai yasan da zamanki dan baya garine da dashi zamu zo ku gaisa"

"Ba damuwa idan munje Kai amarya sai naganshi ai"

"Kijiki da wata magana Wai Kai amarya sai kace budurwa ai dagani sai mijina zamu wuce ba mai rakani"

Na saki dariya Ina "Ikon Allah kawata yanzu dai kin Shiga daga ciki kema kin zama matar Aure wlh naji Dadi takaicina daya ba gari daya zamu zauna ba"

"Ke dai bari dadin abin yanzu ai akwai waya kicewa mijinki ya siya miki nima yace zai siyamin sai mu ringa waya"

"Aikuwa wancan sati Salis ke cemin zai siyamin wayar ni kinsan ban wani damu da kyale kyale ba amma ko dan ke dole nasa ya siyamin ko ya zaiji idan nace mishi kinyi aure kullum cikin min yake kice kawarki ta tsayar da hankalinta waje daya tayi Aure"

Ta saki dariya tana "aikuwa dai gori ya Kare an daura min aure"

"Nikam mai zan baki gudunmawa wanan kyalin ma da kike anya angon nan ba Sha zumar amarya ba"

"Toh da ke zai jira"

Na saki dariya tare da mik'ewa dak'yar sabida cikina ya tsufa na Shiga d'aki,dan magangunan da nake siye masu tsada da na jingine a gefe da na daina sha sabida ciki duk na zubasu a leda na bud'e show glass dina da na jera humra da turaren wuta masu balain tsada da aka hadomin daga Maiduguri na d'auko wajen kwalba biyar biyar duk nayi waje na kai mata na ma dai rasa toh mai zan bata.

Ta kuwa washe baki tana min godiya motsin da Nana tayi yasa na d'auketa.

Hira muka yi tayi bata bar gidan ba sai karfe biyar na rakata ta tafi zuciyata fal da farinciki kamar anyi min bushara da gidan Aljanna rabon da na tsinci kaina a cikin irin farin ciki haka har na manta dan tunda yayana ya Shiga tashin hankali nima bana Jin dadin rayuwar amma auren Luba kuwa ya faranta min.

A lokacin da Salis ya dawo ko zama ban bari yayi ba baki a washe nace "Luba kawata tayi Aure"

"Sai naga ya dan zaro ido yana "ya akayi kika san tayi aure"?

"Kai kaji ka da wata magana wlh gidanan tazo dazu nan kasan wlh har ta canza"

Na saki baki na hau bashi labari shi dai ya buga tagumi yana kallona bandai gane maanar kallon da yake min ba"

"Wai dan Allah Abban Ashraf mai yasa baka san kawata ne abin farinciki ya sameta na fada ma ka tsaya kallona"

"Hmm ai wanan kawar taki tsinaniya ce Allah yasa ba ta karfin tuwo ta samo mijin ba"

"Innalillahi haba Abban Ashraf mai yayi zafi haka zaka tsine mata idan bazaka ce Allah ya Sanya alheri ba aikuwa bai dace ka tsine mata ba"

"Hmmm Allah ya kyauta"

Yace tare da d'aukar Nana da ke kwance akan kujera ya hau min wani tambayar duk dan ya Kau da maganar luba.

A takaice sati uku a tsakani na haifi ummi wanan karon banyi wani taro ba amma duk hidimar da Salis ke yawan yimin yamin sosai dan arziki Kam Kara ninkuwa yake inda nafi yarda da sabida Salis nada kyauta da sadaka yasa yake ganin budi,dan ko iya

dangina ma Allah kadai yasan hidimar da yake yi dasu ba karamin daga min daraja yayi a wajen dangina ba duk Inda naje sai an fada min abin alherin da yayi.

Luba kam tana Abuja a ta waya na sanar mata na haihu tace min bazata zo ba zata min aike.

Ta kuwa aiko min da kayan jarirai inda na yanke a raina.insha Allahu idan nayi arbain zanje Abuja gidanta tunda anan Salis ke yawan zuwa aiki sati biyu ko uku idan ya tashi tafiya sai na bishi.

Sai dai Koda nayi arbain din na tuntube shi da maganar ya had'e rai akan bazanje ba shi Yama rabani da ita tunda Allah yayi ba'a garin take Aure ba.

Nidai bansan mai yasa yake haka ba.

A haka rayuwa ta ringa tafar mana rungume da yarana da Nana da nake Jin kaunarta na daban a zuciyata lokaci lokaci nakan je bauchi dan na duba muhasim.

Abinda ya fara dan damuna bai wuce zaman da Salis baya yi sosai ba yanzu bashida lokacin kansa sosai kullum Yana tafe hanyar abuja idan yaje sai ya kusa sati biyu ko uku kafin ya dawo.

Ni Kuma a wanan lokacin bansan dalili ba sai naji Ina matukar bukatar shi a kusa dani,yawan tafiye tafiyen sai ya fara damuna, amma tunda nema ne ba yanda zanyi,idan yayi tafiya zai dawo haka zan ta Shirin tarbarsa Ina murna girki kuwa haka zanyi kala kala Ina dokin ganinsa ba iya ni kadai ba har da yarana.

Idan ya dawo kuwa a gajiye tikis sai an samu kwana biyu ma wani Abu ke shiga tsakaninmu dan bacci kawai yake shara idan ya dawo.

Ko ya dawon ma bazai wuce sati ba zai Kara komawa sai an samu sati biyu ko uku kafin ya dawo nidai hakuri kawai na koma yi.

Har maganar nayiwa luba ta ringa min dariya wai ko dai jarraba na karo ai ko shekara zaiyi bai dace na wani damu ba.

A haka dai rayuwa ta ringa tafiya na ringa kula da Nana da ummi da nake ma jinsu Kamar Yan biyu.

Wata rana Alhmis da yayi daidai da auren Luba ya shekara daya ta kirani akan ta haihu.

Na ringa murna Ina alwashin zanje mata tunda Yara suna hutu zan Kai su gidan Aunty mamy idan naje ma na samu lokaci da Salis dan har ga Allah sai naji Ina sha'awar zuwa Abujan dan ban tab'a zuwa ba zan so zuwa har ga Allah a ta waya na Kira Salis da naji muryarsa Kamar Mara lafiya cikin doki nace masa Luba ta haihu dan Allah ya min izini zanzo Abuja inyaso sai na sauka a gidansa bayan suna sai na dawo cikin Yar murya na nuna Masa inama kwadayin san naga ya garin Abujan yake.

Budar bakinsa sai yace min bazani ba shi nan da kwana biyu ma zai dawo na tanade shi ya katse wayar.

Na sake kiransa yak'i d'auka

Wlh har da kukana dan bansan mai yasa bayaso naje wajen Luba ba abinda ma ba gidan Luba zan sauka ba a wajensa zan sauka astagfurullah a ranar har auna masa zagi nayi a raina Koda Luba ta Kira cikin kuka na fada mata ya hanani zuwa ta saka dariya tana ai bazai so nazo ba Kar nayi mamaki akwai abinda yake b'oyemin wayasani ma ko akwai wacce yake da ita a abujan shiyasa ya hana ni zuwa

Wlh sai naji kirjina yamin nauyi kamar ta kwada min katon dutse a ka ban tab'a zargin mijina ba nasan Salis ko.ina ne zan. Iya Masa shaida.

Sai dai me sai naji maganganunta sunyi balain tasiri a raina dan tabbas da yana da gaskiya bazai tab'a hanani zuwa ba tunda a baya shine me cewa zai ringa tafiya dani idan Yara sunyi hutu.

A ranar Sam ban runtsa ba sai naji dama nasan wajen da yake da naje.

Kwana biyu na matsawa kaina da tunanin na Kuma yarda ya ajiye mace a gidan da yake tunda har ya hanani zuwa.

A irin haka muka yi waya da Luba nace dama nasan wajen da yake Abuja wlh da sai dai ya gani Ina Jin maganarta da kamshin gaskiya ta saki dariya tana baki dai yi niyya ba idan har kinaso ki kamashi ki taho zan bincika asibitin da yake aiki bazaa rasa sanin Inda yake zaune ba.

Ai sai naji ba mai kaunata kamar luba sai naji dama yamma batayi ba da na shirya a yau na tafi.

Sai na barwa washegari karfe takwas na dau hanyar Abuja dan ta turomin address din gidanta.

Akan tunda ranar suna akeyi bayan taron zamu nutsu mu nemo gidan Salis.

Tafiyar awa biyar dai sai gani a garin Abuja da na Kira Luba tace na samu taxi na bawa driver ta gaya masa unguwar da zai kawoni.

Ban Sha wahalar samun taxi ba na hadashi da Luba da nake ta Jin hayaniya a gidanta bansan dai yanda Suka yi ba yaja taxi din muka tafi nidai kalle kalle kawai nake sai na tsinci kaina cikin mugun faduwar gaba da bansan mai ya hadasa min shi ba sai na danganta hakan da satar fitar da nayi ne.

Tafiyar minti Ashirin muka iso wani hadadden gida bashida girma sosai amma ya had'u kafin na sauka na bawa taxi kudinsa na janyo karamin akwatina Ina karewa gidan kallo.

Sai na fara k'ok'arin zuge Jakata dan na Kira Luba dan na tabbatar da a gidan aka saukeni.

Muryar da naji yasani dago da kaina da sauri kirjina Kamar ya fado....

MG'S SKINCARE

Dame akafiki yar uwata?
Kyan fatar ko iya gyaran fatar?
Ina riba g macenda t Maida kanta sauran mata?
Shin haryenzu labarinmu kikeji ko kike bayarwa?
Hajiyata miye matsalar?
Fatar takice abun se lahaula?
Kingwada kingwada harkinsare?
Tsakanida Allah yaushe daren yayi balle wayewar garin?

Inbakida labarin MG'S wacce tasanki tasansu,
Gawurtaccen Kuma shahararren kamfanin gyaran fatane,duk lalacewar jiki,duk hautsinewar fata,duk yenda jikinki yazama abun kunya gareki, Ina tallata maki me gabadaya,

Muntarkato,munwarwaro,munqullo duk wani Abu daze maidaki wanke hannu kataba mun qara a cikin kayayyakinmu,muncire,muntsife,munfidda,mun tantance mun hadamaku wasu irin hadaddun lafiyayyun kaya masu masifar goge fata,wallahi duk fitinar fatarki inshallah,kinzo bustop,kisiya kiyikyanda ko mace,kan juyo ta waiwayo ta dubi halittar Allah,

Ga product din kamar hka,
Sabulu 4500

Mg's beauty kit
Karamin kit 12k
Body soap
Facial soap
Body cream
Face cream
Glow oil
Pink lip balm

Flawless skin beauty kit
Babban kit 20k
Body soap
Facial soap
Body cream
Face cream
Scrub
Glow oil
Pink lip balm

Note kowanne d kalanshi nd yanayin packaging dinma aren't the same,

Tsakanida Allah kigafa
Duk wannan garabasar Kuma kinazaune hba taso a dama dake a harkar yar uwata,

Ayi hakuri da sauyin farashi komi yatashine muma b hka mukasoba
Chat:08062991549,07046881166,07067210195,
Call,+2348064532391

NI DA KISHIYOYINA

NA SADNAF

E.W.F

PAID BOOK

Page 7

Salis ne rungume da farin showel da wasu maza biyu suna "Allah dai ya raya mana Bintu"

Sai a lokacin ya gani nidai lissafi ya kunce min dan bansani ba ko gidansa luba ta saka aka kawoni ba gidanta ba jikina rawa kawai yake dan Luba bata kyauta min ba.

Shi kuwa sallati ya saki da k'arfi Yana "Aishaaaa"

Sai naga yaja da baya a tsorace hannunsa dai rungume da farin showel

Nidai a tsayen da nake wlh banda rawa ba abinda jikina yake Kuma na kasa tunani ko na hasaso mai ke faruwa kamar dai an dasani haka na tsaya ban motsa ba.

Ganin ya koma ciki da balain gudu yasa mamaki kasheni mai ke faruwa ne?

Sai na tsinci kaina da sallati Ina tunanin dai gidansa luba tasa aka kawoni Kuma da kamshin gaskiya kenan Yana tare da wata sai kirjina ya buga da na tuna maganar maza biyun da na gansu dashi suna Allah ya raya musu Bintu"

Ai bansan lokacin da nima na fada cikin gidan aguje ba kirjina na balain faduwa ba dai dagaske Salis yana tare da wata macen ba.

Koda na Shiga gidan canopy naga guda biyu an saka a tsakar gidan Mata da maza a azazaune a fararen kujera da alama dai taro ake.

Sai dube dube nake banga Salis ba.

Sai na doshi cikin gidan a daidai lokacin da wata naga tana k'ok'arin fitowa nayi saurin tareta murya na rawa nace "Baiwar Allah dan Allah waye mai gidanan nazo ne bansani ba ko b'atan hanya nayi"

"Gidan Dr Salis ne ai yau ake sunan Yar sa ko sunan Kika zo ai ki Shiga suna ciki shi da matarsa"

Sai naji numfashina Yana k'ok'arin d'aukewa maganganunta na maimaituwa a kunne na nidai nasan Dr Salis ake ce mishi idan ba ciwon kunne nake ba kamar cemin tayi yau ake suna matarsa ta haihu ?dama Yana da wata matar ne bayan ni? jikina rawar da yake yasa na kasa motsawa sai sallati nake wlh k'ok'awa ma nake da numfashina.

Nafi karfin minti biyar a haka bansan ma Ashe wayata bata hannuna ba Ashe luba da gaske take akwai abinda Salis yake b'oye min shi yasa yak'i barina nazo innalillahi wa Inna ilaihi rajiun.

A hankali na taka dan matatakalar na shiga ciki dan madaidaicin Palo ne sai tsirarun mutane da suke cin abinci idona ya sauka akan kanin luba Nura dake ta loma abinci muryar yayar luba ya doki dodon kunnena "Aa Aisha sai yanzu kika iso"?

Ban iya magana ba sai ido da na zuba mata dan a yanzu Kuma kwakwalwata ta tsayar da aiki inaso nagane wani abu kannen Luba a gidan Dr Salis mai hakan ke nufi mai take nufi da sai a yanzu nazo"

Kallon da nake mata batare da ko kiftawa ba yasa ta ajiye plate din hannunta.

Ta nufo wajena tana "Aisha lafiya kuwa"?

A daidai lokacin da naji muryar Luba kirjina yayi wani irin bugawa na waiga da sauri.

Masifa kawai take tana "Idan bata sani ba yanzu yaushe kake so tasani, salon ka Fadi ka mutu aki yarda cewar na haihu da Kai na gaji da kumbiya kumbiya gwara kawai ta sani a wuce wajen"

Sanye take da shadda ruwan toka ya sha aiki har kasa Ina da irin shaddar har kalar dinkin bambancin nawa yafi nata turuwa ta sha kunshi kina ganinta Kinga mai jego had'a idon da muka yi da ita bai sa ta tsayar da maganar da take ba har sai da ta idda ta Kuma had'e rai tana "Aisha kin karaso"?

Ban bata amsa ba na cigaba da kallonta inaso kwakwalwata ta bani hadin kai na gane mai Luba takeyi a gidan Salisu mijina ita da Yan uwanta.

"Luba lafiya kuwa ya naga Aisha a hargitse haka Ina salisun yake"?

Cewar yayarta ita kuwa tace mata "Yana d'aki yanzu zamu shiga ciki ai"

Aisha kizo mu Shiga daga ciki

Ta juya tare da komawa d'akin da ta fito.

Sai na tsinci kaina da bin bayanta zuwa lokacin nan wlh numfashi jansa nake da k'arfi kaina ma juyamin yake sai inaso nayi tunanin Wai Luba ce matar salis sai na janye tunanin Ina hararo fuskar wata a matsayin matar da Salis ya aura a boye kila matarsa kawar Luba ce shiyasa na gansu a gidan.

Ina tura k'ofar naga salis ya kifa kansa a jikin gado ga jaririya a shimfide a Kan gado Luba Kuma tana jingine da wadrobe din d'akin.

"Salisu"

Na kirashi Kamar an fusgo maganar daga bakina a yanzu tunanina ya bani abinda ke faruwa luba kawata aminiya ta itace Salis ya Aura

"Innalillahi wa Inna ilaihi rajiun innalillahi wa Inna ilaihi rajiun Aisha kiyi hakuri kiyi hakuri innalillahi wa Inna ilaihi rajiun Aisha bazan iya dago da kaina na kalleki ba wlh

ba a san raina haka ta kasance ba Allah ya hukunta sai na auri Luba tunda ga rabon ya mace a tsakaninmu wlh ba cin amanarki nayi ba innalillahi wa Inna ilaihi rajiun"

"Mtssss Wai kai mai hakane ya kake Abu kamar mace auren da muka yi haramune mtsss wlh karka sake cewa baa san ranka ka aureni ba da san ranka sarai ma dan da baka sona bazaka kwanta dani har na haihu ba,da baka sona bazaka kawoni Abuja wajen da kake aiki sabida ma Kar na nisance ka"

Ta juyo ta kalleni tana "Kawata Salisu shekara daya kenan da aka daura mana aure dashi bisa yarjajeniyar bazaki tab'a sanin ya aureni ba wai nan gaba zai fada miki ya zabi ya ajiyeni anan sabida wai karki tab'a sanin munyi Aure ya Kuma zabi aurena ne sabida kawancenmu ya Kara k'arfi domin kina kaunata Ina kaunarki cigabanki cigabana ne Yana da kyau Kuma kaso wa dan uwanka abinda kaso wa kanka nasan islamiyya daya muka yi kinsan haka dan na auri Salis ba haramun bane ba Kuma haka zai saka Wai kawancen mu ya ragu ba a ganina hakan zai saka mu hade kanmu dake muci arziki tare ba wani abu bane ba auren Salis da nayi bai zai rage ki da komai ba tunda bai rage kaunarki ba wani abu bai ragu a jikinsa ba,ni a ganina boye mikin da yake shine munafirci amma ni ko lokacin da muka tsayar da magana wlh naso na fada miki ya hanani ko ranar da nazo dinan Kika ringa cewa kamar amarya nake ba karya kikayi ba kwana uku da daura mana auren ko zuwan da nayi wlh nayi niyyar fada miki sai Kuma na fasa dan ya rokeni sosai akan bayaso kisani,ni sai nake ganin da ya gaya miki sanin da na miki wlh bazaki hana ba dan naga kina balain san nayi Aure duk Yan gidanmu sun d'auka da yardarki akayi auren shiyasa kikaji Aunty Walee na tambayata lafiya kuwa kinsan baa nan take aure ba.

Nidai abu daya danasani boye miki da yayi bai kyauta ba abin na ta damuna taya zaace a boye miki kinsan bana boye miki komai shiyasa na yanke fada Miki wlh sabida halin rayuwa baa san gawan fari ba yazo ya Fadi ya mutu ke bakisan da auren ba Yan uwansa basu sani ba azo rabon gado ace baa san zance ba wlh shiyasa na fada miki dafatan hakan bazai saka wai mu yanke kawancen mu ba kawai mu rungume mijinmu mu faranta masa"

"Luba baki kyauta min ba baki min adalci ba Luba da ace nasan abinda zakimin kenan wlh da bansoma yarda da aurenki ba yanzu da wane ido kikeso na kalli Aisha wane bayani zan mata ta gane Aisha fa kawarki ce karki manta"

"Ikon Allah wai haramune auren nawa ka isa ka aureni ne idan ni din ba matarka bace wlh bana Jin dadin abinan da kake yi kamar kana tsoron Aisha magana ce fa ta fatar baki kayi abu kamar namiji Mana idan bamuyi aure ba Ina zaka Kai rabon dake tsakanin mu zata hana abinda Allah ya hallata ne kaga mallam nidai ka zaunar da ita ka kara.mata bayani kai ya Kamata kayi mata magana ka barni da mata magana Haramun muka aikata kake ta sallati naga dai sai da ka bada sadaki aka daura mana aure kamin lefe ka aureni da daraja to na me a yanzu zaka ringa kame kame agabanta mtssss nidai na baku waje kuyi magana bari na sa a kawo mata abinci.

Ta nufo wajen k'ofa ta karkata ta wuce dan a bakin k'ofar na daskare a tsaye kallon Salis kawai nake Yana ganin ta fita yayi sauri ya juya bayansa duk da duk abinan bai dago mun hada Ido ba sai sallati da yake Yana Aisha kiyi hakuri dan Allah nasan ban kyauta ba dan Allah kiyi hakuri"

Zuciyata wani irin kunna take na kasa gasgata wai Salis da ya balain tsanar Luba shine yau a matsayin mijinta wai har ya mata ciki ta haihu ashe duk tsawon lokacin nan ninkeni baibai suka yi soyayya sukeyi a gaban idona yake nuna Mata kiyayya kawata aminiyata da ba abinda bata sani akaina ba itace Salis ya Aura a matsayin kishiyata,ashe dadewar da Salis yake yi a Abuja sabida auren Luba da yayine yana

nan da kawata Yana Shan soyayya sai ya mata sati biyu uku ya dawo wajena na tafi kunshi nayi ado nayita girke girke Ina murnar tarbar mijina Ina tunanin yanda nake dokin kasancewa dashi haka yake dokin kasancewa dani sabida an dade baa hadu ba,idan ya iso kuwa jikina yayi ta rawa kawo wanan d'auko wancan ni ga mijina ya dawo sai dare yayi yace min a gajiye yake likis cikin tausayi zan raba dare Ina masa tausa dan nasan duk sabida nida yarana yake Neman kudi ashe baccin gajiya da kawata ta tara masa yake, sabida kaunarta da yake ya kai ta abuja sabida ma Kar tayi nisa dashi.

Na d'auke kallona daga kan shi na maida Kan jaririya Wai Salisu ne yayi wa Luba kawata ciki,na runtse idona hawaye na gudu a fuskata kirjina kuwa kamar ya fado Ina Jin numfashi na min wahalar shak'a,na runtse idona dana tuna lodin magungunan da na bata da Sunan ta jiyar da mijinta dadi har tana cemin a waya mijinta ya isheta da jarraba sabida kyan maganin ko aiki yaje sai ya dawo yayi, Ashe Salisu ne ya isheta da jarraba Ashe Salisu take bani labarin yanda yake santa kamar ya hadiyeta har Ina Jin na raina san da nawa mijin yake min.

A daidai lokacin da Luba ta dawo d'akin da farantin abinci ta ajiye a gabana tana "baki gaji da tsayuwa bane ki zauna mana nan ma fa gidanki ne kin kwaso gajiya kici abinci sai ki watsa ruwa kizo kiga diyar taki.

Sai Kuma ta sunkuya ta d'auki abincin da bansan wane kala bane dan wlh a yanzu tsananin mamakin Luba Kuma nake tana ta abu Kamar irin ba komai dinan ta nufo gabana dashi tana "kawata wai me haka dan Allah"

Har lokacin hawaye kawai ke zubomin kalmar kawata da tace yasa na Kara Jin kirjina yayi nauyi kawata Luba dai itace yanzu matar salis har suka haihu tare magangaunta suka Kara dawo min "wlh karka sake cewa baa san ranka ka aureni ba da san ranka sarai ma,dan da baka sona da bazaka kwanta dani har na haihu ba sai na runtse idona tare da cije lebbena da baka sona bazaka kawoni Abuja wajen da kake aiki sabida Kar na nisance ka ba"

Sai naji hannunta saman hannuna "zoki ci abinci nidai matan abokanan Salis suna ta jirana Kinga ba dadi na barsu su kadai"

Sai na fusge hannuna daga nata hawaye sai gudu yake a fuskata na ma rasa Mai zance mata na bud'e bakina da kyar Ina "Luba mai na miki dana cancanci irin wanan cin amanar daga wajenki Luba duk mazan duniyar nan ki rasa Wanda zaki aura sai Salis mijina Luba"? Idan shi baiji kunya ba bai san ana barin halak dan kunya ba ke Sai ki biyeshi ki aureshi kina matsayin kawata aminiyata Luba ki auri mijina shekara guda batare da nasani ba"?

Duk maganar da nake hawaye kawai nake muryata na rawa

Sai ta turo dankwalinta gaban goshinta tana "Tambaya daya zan miki ki bani amsa, Haramun ne dan kawa ta auri mijin kawarta?idan har Kika kawo min Inda aka haramta auren mijin kawa ni Kuma na Miki alkawari Zan saka ya sakeni Aisha dama haka kike ke yanzu wani abune dan mijinki ya aureni"?

Bansan ya akayi ba na ciri hannu na d'auketa da mugun mari kafin ta dawo daidai na kara d'auketa da wani marin kafin na sauke hannuna naji tayi sama dani ta makani da kasa a daidai lokacin da naji duhu na neman rufemin ido numfashina na k'ok'arin d'aukewa naji sallatin Salis sama sama ban Kara sanin Inda kaina yake ba.

Sai bud'e ido nayi na gani a gadon asibiti da Karin ruwa a hannuna sai da na dau tsawon mintuna kafin na tuna abinda ya faru na maida idona na rufe Ina Jin bugun kirjina da kuguna dake min ciwo inaga bugani da kasa da Luba tayi ya haddasa min ciwon.

"Sannu Aisha kin farka"?
Naji muryar Salis a kaina banasan ganinsa haka yasa ban bud'e idona ba"

Ina jinsa ya zauna a gefen gadon murya na rawa ya hau magana "dan Allah dan Annabi kiyi hakuri Aisha wlh nasan ban kyauta ba amma wlh tallahi bana kaunar Luba kaddara ce tasa mu kayi aure wlh baa san raina ba kwanciyar da take magana wlh magani ta saka min a lemo wlh wlh bana kaunarta kinsan bazan tab'a cin amanarki ba,wlh tunda na aureki ban tab'a kallon wata mace naji Ina santa ba bayan ke wlh matsayinki daban yake a zuciyata ki yarda dani matata kar ki bari shaidan ya rabamu wlh burin Luba taga mun rabu dan Allah kiyi hakuri na yarda ki min kowane irin hukunci.

Wlh kamar feshin wuta haka nake Jin maganganunsa a kunnena daga lokacin da na saka kafa a d'akin na hangosa a d'akin na tabbatar da zargina naji sansa na ficewa daga zuciyata tsananin tsanarsa na mamaye min zuciya babban burina yanzu nagani a gidan yayana dan wlh na gama auren Salisu.

Ban tabbatar da muryata zata fita ya jini ba nace "Allah ya isa tsakanina da Kai Salisu wlh har duniya ta nade bazan yafe maka ba duk matan duniya ka rasa wacce zaka Aura sai Luba da kasan kawata ce Aminiyata ySalisu ka aureta ka b'oye min har tsawon shekara guda ka daukota ka kawota Abuja baka Santa kayi mata ciki ta haihu kayi taro tare da gayyatar abokanan aikinka da matansu,ashe Sabida ita ne baka zuwa wajena sai ka shafe sati biyu ko uku baka zo ba,na maka maganarta ka zageta Salisu kawata fa wanan wane irin cin Amana ne Wlh bazan yafe ma ba"

Na fashe da wani irin kuka zuciyata na min k'unna

Hakuri ya cigaba da bani ko muryarsa banaso naji na saki ihu akan ya fita banaso na gansa.

Ina jinsa ya tashi.

Rashin kwarin jiki yasa ban fusge ruwan daga hannuna ba dan burina yanzu naga na bar garin.

A takaice washegari wani likita yazo dubani Ina kallon Salis a rabe a jikin kofa.

Tun jiya wlh hawaye bai tsaya min ba idan na tuna irin cin amanar da Salis da luba suka min.

Koda likita ya gama dube dubensa naga ya cire min robar ruwan da Ina tunanin na Sha ya kai biyar mik'ewa nayi zaune cikin muryata da bata fita sosai nace "Likita ka sallameni tafiya zanyi"

"Hajiya ai baki warke ba ya kallo Salis dake bakin k'ofa Ina tunanin dai asibiti daya suke aiki.

Ni kuwa ban bi takan likitan ba na Mik'e zaune Ina dube dube duk ji nake kamar iska ya d'aukeni Ina ganin mayafina na d'auka tare da cije lebbena sabida kaina da naji ya Sara min.

"Aisha Dan Allah ki bari kiyi hakuri bakida lafiya ki bari gobe sai na Kai ki gida da kaina jininki fa ya hau Aisha dan Allah ki koma ki kwanta.

Kafata ba takalmi inuwarsa ma basan kallo nake ba nayi hanyar wajen.

Ya sha gabana da sauri kallon da na masa yasa ya bani guri nayi waje Ina jinsa a bayana Yana "Aisha ba inda kika sani a Abuja kizo muje gida Dan Allah dan Annabi gobe sai mu tafi.

"Inzo muje gidan Luba ko Salisu"?

Sai yayi shiru

Na girgiza Kai na cigaba da tafiya duk da nasan bansan ma Ina ne Tasha ba amma dai matambayi baya bata.

A takaice taxi na tare akan ya kaini Tasha.

Ina Hawa Salis ya Shiga shima Yana ta magiya.

Shattar mota na dauka ni kadai duk yanda Salis yaso bina na hana driver daukarsa.

Wlh dauriya kawai nake dan har yanzu da zazzabi a jikina kaina kamar ya rabe biyu.

Tafiyar awani ya kawoni garin katsina bai zame dani ko Ina ba sai gidan yayana Koda na Shiga kudin Mai motar kawai na karba na bashi na baje a kasan kafet din palon wani sabon zazzabin na rufeni yarana duk suka yanyameni.
Har da Nana da Ummi Aunty Mamy kuwa duk ta daka musu tsawa akan su bar kaina ta cigaba da tambayata lafiya ta gani haka dan duk Wanda ya gani yasan ba lafiya ba.

A daidai lokacin da naji muryar yayana Yana "Mai ya samu Aisha"?

Present

Alhaji Salis zuciyarsa cike take da fargabar auren da zaiyi a yanzu da lokaci ya matso sai yake Jin zuciyarsa cike da fargaba dan ya nunawa Iyayen Aneesa matansa basuda matsala duk zasu rik'e Aneesa da Amana.

Duk da sunje katsina sunyi jeren dan a cikin gidajensa daya gina na siyarwa ya zabi daya ya gyara dan Aneesa ta zauna kafin yasan yanda zai fadawa su Luba.

Aisha ma ko ta kansa bata bi ballantana yace ta damu da auren da zaiyi.

Sai dai abinda ya daga Masa hankali bai wuce mahaifiyar Aneesa da tace tanaso taje gidansa ta damka wa matansa amanar Aneesa ba,taya mahaifiyar Aneesa zata je gidansa bayan Aisha ce kawai tasan zai Kara Aure.

Har aka Shiga satin bikin zuciyarsa cike take da fargaba Yana ta tunanin yanda zai bullowa Mahaifiyar Aneesa dan tace da ita za'a kawo Aneesa ya lura mahaifiyar Aneesa ba san auren take ba.

A haka har aka fara shagalin biki Sam baiso wani shagali ba dan shi kansa yasan ya girma da haka amma yaga Kan Aneesa na rawa dan dak'yar ya samu ya k'aucewa pre wedding din da ta dage masa suyi dan yana gudun Luba ta gani.

A haka har aka daura Auren shi da Aneesa ranar jumaa akan za'a kawota ranar littinin.

Washegarin daurin auren Alhaji Salis ya nufo katsina zuciyarsa cike da fargaba dan dole ya fada Luba da Hindatu Auren da zaiyi idan ya tuna tashin hankali da Luba tayi a auren shi da Hindatu sai yaji wani sabon tashin hankali ya rufeshi idan Kuma yak'i fada mahaifiyar Aneesa Suka kawota fa yasan halin Luba dambe za'ayi da ita.

A lokacin daya iso gida Luba har wani cancada ado tayi dan itace da girki.

Shima Alhaji Salis ranar ya saki fuskarsa Yana ta janta da hira dan yafi jinta akan Hindatu Luba kuwa sai falli take tana kyakyata dariya sabida ta kunsawa Hindatu bakin ciki ta kuwa ji Dadi tana jinta tana tsaki a Palo tana kananan maganganu.

Shi dai Alhaji Salis har da yan adduoinsa a zuciyarsa kafin ya ruko hannun Luba da ta wani narke tana "Alhaji nawa Ni kadai"

Ya saki murmushin karfin hali cikin dauriyar da ta zo masa yace "kinsan bawa bai isa ya k'aucewa kaddararsa ba ko Kamar dai yanda kike fada,auren nida ke Allah ya rubuta sai munyi Tom yanzu Allah ya kara kaddara min sake Aure a yau aka daura min Aure da wata yarinya Aneesa"

"Kutumar uba Mai kace maimaita min naji"?

Luba tace tana karkada kunnenta.....

INGANTACCEN MAGANIN SANYI TOILET INFECTION MAI WANKO DUK DATTIN MARA KOWANI IRIN SANYI NE ZAI MAGANCE SHI DAYARDAR ALLAH SHIN KINAFAMA DA RASHIN SHA AWA? RASHIN NI IMA RASHIN GAMSUWA SHIN KINYI SHEKARA DA SHEKARU KINA NEMAN HAIHUWA RIKICEWAR JINI CIWON JIKI CIWON MARA YAYIN AL ADA DUKA WANNAN MAGANIN YANA WARKARWA ME CIKI BATA SHAN MAGANIN SANYI NA 4K YAKE INA KATSINA INA AIKAWA KO INA A FADIN KASAR NAN HARDA KETARE MAZA DA MATA MAGANIN SANYI MAI GYARA MU AMALAR AURE AUNTY ZEE MOM MUJAHID
08162859027
KATSINA

NI DA KISHIYOYINA

NA SADNAF

E.W.F

PAID BOOK

Page 8

Luba

Ta mik'e da sauri tana "Alhaji kaga idan Wasa kake min ka daina banaso kai yanzu ko sadakar mace aka Kara baka Kamar yanda aka baka waccan basumudiyar zaka yarda ka karba ne"?

Salis ya had'e rai yana "Luba inaga ban tab'a miki zancen Wasa ba ko karki manta ba ke kadai ce matata ba yanda kike takamar ke matata ce kina Kuma so da kishina haka sauran ke sona Aure dai an daura min jiya ranar litinin za'a kawo ta aure dai da na Kara inaga ba haramun bane tamkar lokacin da kike fada da na aureki akan Karin Aure ba haramun bane tom inaso wanan waazin da Kika min a yanzu sai kiyi wa kanki Yarinya na aura baza'a samu matsala da ita ba idan Allah ya yarda"

"Wlh kaci karya Salisu ka wulakantani har ni zaka cewa an daura ma Aure ka Kara cin amanata a Karo na biyu wancan jakar kace min tilasta ma ita akayi yanzu kuma baka ji kunya ba kace min an daura ma Aure ba ma neman auran kake ba sai da aka daura kazo kana fadamin bayan a yarjajeniyar da muka yi da Kai ba Karin Aure daga ni sai Aisha zaka zauna damu"

"Ba inda muka yi yarjajeniya dake akan bazan sake Aure ba luba na gaji da tashin hankali da kukeyi a gidanan ke da Hindatu Kun k'i ku sama min nutsuwa Karin Aure Yana cikin kaddara ta ban isa na kaucewa kaddara ta ba nidai na fita hakkinki dan ban munafirce ki ba tunda it Aisha a lokacin da na aureki bama tasani ba har aka shekara da haka nayi mi ki sai kice naci amanarki na munafirceki dan haka ranar litinin za'a kawota banasan tashin hankali"

"Idan ka isa Allah ya tsine min ka rasa lokacin da zaka Kara aure sai da na manyanta zaka auro yarinya karama ko kunya baka ji ba dan masifa ka ajiye mata har uku amma sai ka Kara auren ta hudu,a Ina kaga kwarin rik'e mata hudun mu ukun ma da cutuwa nakeyi ko gamsar da mutum baka iya yi kana daya zaka baje ka hau bacci inaga ka karo ta hudu,? idan su basa gamsar da Kai baka isa kace ni bana gamsar da kai ba dan rabin kudina a gyara suke tafiya, wlh Alhaji idan kana san zaman lafiya a gidanan ka janye auren nan idan ba haka ba wlh tallahi ruwa ma bazaka iya sha a gidanan ba Kuma ka jawowa Yar mutane balai dan wlh dukanta zan tayi har sai ta koma gidan iyayenta.

"Wlh baki isa ki hanani Aure ba luba ba'a aurowa aka auroki a lokacin da kikeso na aureki ta karfi da yaji wane irin wa'azi ne baki min akan Karin auren ba? wane irin magana ne baki min ba dan kawai na aureki? Ashe Aisha ita ba mutum bace sai ta yanki jiki ta Fadi tunda ke kawarta ce na aureki ba kuma ki tab'a Jin komai ba kina ganin ma ai ba wani abu bane sai dan yanzu na Kara aure zaki min hauka.

Wlh wlh Luba abinda na dauka a baya bazan dauka ba ayanzu kinji na rantse miki sai dai duk abinda zai faru ya faru"

Ya mik'e fuuu yayi waje

Luba ta bishi tana "Na rantse da Allah kuwa kayi auren nan sai na baka mamaki abinda nayi nima a baya kadan ne akan wanan da zanyi banda jarraba kana da manyan samari zaka Kara aure,kake hadani da jakar matarka ita tasan ciwon kanta ne nida ita ba daya bane wlh sai na baka mamaki wanan karon abinda kake gudu wlh sai ya faru ka Kara auren kagani"

Alhaji Salis kuwa ko kallonta bai Kara yi ba yayi kwanciyarsa a dogon kujera Luba a ranar kwana tayi tana balai ko runtsawa Salis baiyi ba har sai da Hindatu ta fito taji labarin abinda ke faruwa itama ta kadu da Jin labarin aure zaiyi sai gashi itama ta hau masifa dan ita zaa yiwa kishiyar nan amma Luba ta fita Jin zafi.

Aisha tana daga dakinta tana juyosu hayaniyar su, k'arfi da yaji sun hanata bacci sai tsaki take daga dakinta Allah yasan da tana da halin barin gidanan da ta bari dan wlh zaman dole take yi duk tsawon lokacin nan, tana mamakin Halin Luba da Hindatu ko gajiya basa yi da masifa.

Karfe uku nayi ta mik'e ta daura alwala daga lokacin da Salis da luba suka saka mata hawan jini ta koyawa kanta samun nutsuwar zuciya ta hanyar mik'awa Allah lamarinta.

Sai da taji fitar Salis massallaci taji sun daina hayaniyar.

Salis bai dawo gidan ba sai da gari ya waye,ya mugun hade rai, yana Jin zuciyarsa na ingiza masa da ya Shiga d'aki ya rubutawa kowace saki uku ya huta kawai ya gaji da halinsu wani zubin sai yaga Kamar ya shake luba har sai ta daina numfashi.

Ko kallon ita da Hindatu da suka hade kai suna kananan maganganu baiyi ba bai tab'a ganin sun hade Kai suna magana ba sai da ya kara Aure.

Kasan zuciyarsa Kuma Yana fargabar su yi wani Abu su zubar Masa da mutunci a wajen dangin Aneesa su san irin zaman da yake yi dasu shi Kam da Yana da yanda zaiyi da ya hana zuwan mahaifiyar Aneesa da yasan da biyu takeso tazo gidan nasa.

D'akin Aisha ya shiga da sallama bata d'akin Yana Jin motsinta a bandaki

Hakane yasa ya zauna a gefen gadon Yana Jin inama ita kadai ce matarsa inama Yana da damar da zai maida hannun agogo baya,sai ya runtse idonsa yana tuno baya, tunanin daya tafi yasa kirjinsa nauyi Yana Jin tamkar a yanzu Luba ta shigo office dinsa ta canza masa rayuwa ta shigo cikin rayuwarsa daya kasa yakice ta har yau.

Motsinta da yaji yasa ya bud'e jajjayen idonsa akanta.

Inama Aisharsa ta dawo masa tamkar da ya rasa wancan Aishar wanan yanzu zuciyata ba komai Yana Jin karayar zuciya idan yaga yanda Aisha ta maida shi bashida bambanci da hoto a wajen ta har yau.

Bai tab'a tunanin yanda yasanta da Hakuri zata yi irin wanan rikon ba.

Sai da ta zura doguwar rigar ta tayi gaban mudubi da ido kawai yake binta tana nan a yanda take kyaun jikin da take dashi yasa ba mai yarda ta ajiye su Ashraf ko kad'an bata da kib'a shi har yau bai ga canjawarta ba rabon da yaga dariyarta kuwa har ya manta.

Mik'ewa yayi ya nufi wajenta dan bata nuna tasan dashi a d'akin ba manta kawai take shafawa Yana zuwa ya rungumeta ta baya tare da runtse idonsa sai ta cire hannunsa

daga jikinta ta,ta fara k'ok'arin barin gaban mudubin yayi sauri ya ruko hannunta "Aisha har tsawon wane lokaci zamu cigaba da zama a haka Aisha kefa musulma ce a yanzu bazaki iya yafe min komai ya wuce ba Aisha yanzu kinyi min adalci azabtar da zuciyata da kikeyi? Ya Kamata kimin adalci Aisha dan kin maidani hoto ba hakan ke nufin ban damu ba wlh wlh Ina cikin damuwar irin zaman da muke yi Aisha nawa rayuwar nan take gobe zaki iya tashi kiga babu ni haba Aisha dan Allah ki yafemin ko sau dayane ki dawo dani rayuwarki"

"Yanzu wani abu ne ya faru"?

"Yanzu na gama duk maganganun nan Aisha kice wani abu ne ya faru"?

"Tom ba dole na tambayeka ba dan ni bansan Mai ya kawo maganganun nan ba tunda ba wani abu ka nema dayake hakkinka ban baka ba"

"Toh shikenan Aisha tunda kin dage komai bazai wuce ba shikenan amma inaso kisan Allah ma muna masa laifi mu nemi yafiyarsa ya yafe Mana Kuma Allah Yana san bayinsa masu yafiya An daura auren nida Aneesa shekaranjiya gobe za'a kawota mahaifiyar ta zata kawo muku amanarta dan Allah bana so a samu matsala Aisha duk da nasan insha Allahu baza ki bani kunya ba amma kinsan halin Luba da Hindatu"

"Bansan halinsu ba dan Kai ka sansu banida hadi dasu su zaa kawowa ita su ya Kamata ka fadawa tunda banida wani hadi dasu"

"Aisha dan girman Allah ki bari kefa matata ce kinaso kice abinda ya shafeni bai shafeki ba"?

Sai ta saki murmushi tana "Jiya baku bari na runtsa ba Kai da matanka zan kwanta nayi bacci"

Ta nufi wajen gadon ta kwanta tare da juyawa Salis baya.

Salis ya zuba mata Ido cikin mamaki wlh bai tab'a tunanin haka take da zuciya ba da wanan abun da take Masa gwara tayi ta masa rashin mutunci da wanan gashin da take masa.

Fitowa yayi daga d'akin ba inda zaije ma yaji sanyi a zuciyarsa.

Tunda a d'akin luba yake akan dole ya shiga d'akin dan ya shirya ya fita dan Yana tunanin abinda kawai zaiyi shine a kai Aneesa wajen hajiyarsa ta tare kawai dan indai har aka Kai Aneesa gidansa komai na iya faruwa.

Yana cikin shirya wa Luba ta Fado d'akin ta tsaya a bakin k'ofa tana "Salisu wlh ka janye zancen Auren nan idan kana san zaman lafiya a gidanan idan bakaso ka janyowa kanka tashin hankali ka janye auren nan zaka jawowa yarinya lahani wlh zaka jawowa Iyayenta asara taya ma zaka kara Aure a wanan lokacin"

Alhaji Salis ko kallonta baiyi ba ya saka agogonsa ya feshe jikinsa da turare ya nufi bakin k'ofa Luba ta Kara gyara tsayuwarta tana jin wani irin bakin kishi na rufeta dan duk da Alhaji Salis ya manyanta kudin da yake dashi yasa yake nan da kyaunsa har cewa ake duk yafi karfin aurensu Aisha ce kawai ta dace dashi.

"Bani hanya na wuce Luba"

"Bazan baka hanya ba wato wajenta ma zaka je"?

"Wai ke dama mahaukaciya ce bansani ba kinsan Allah idan baki bani hanya ba sai na d'auke ki da mari, wlh ban tab'a kaunarki ba kinsani kaddara ta sani aurenki a yanzu bazan dauki iskancin ki ba wlh sakinki kawai zanyi"

"Kai ma kasan ai bazan saku ba idan ni mahaukaciya ce Kai mahaukaci ne idan banida hankali Kai ma baka ganshi ba dan da kana dashi bazaka tab'a tunanin Aure ba idan Kuma ka sakeni wlh kasan mai zai biyo baya dan sai na aiwatar da abinda nayi niyya sai dai duk abinda zai faru ya faru kowa ya rasa"

Salis kasa magana yayi sabida tsananin b'acin rai Luba kuwa sai girgiza take tana zuba masa harara"Na tsaneki luba wlh bana kaunarki kece kaddarata Allah ya nuna min ranar da zan rabu dake rabuwa ta har abada tunda kika shigo rayuwata ban Kara farinciki ba kinyi sanadin da na jefa Aisha cikin bakin ciki matata mai sona domin Allah sai da kika rabani da ita Luba wlh ko mutuwa zakiyi ba abinda zai hanani tarewa da Amaryata yarinya sharaf mai jini a jiki ba abinda Kika sani sama da hauka da tashin hankali ko kunya bakya ji wacce Kika zo Kika yiwa kwacen miji ma bata haukan da kike ba sai ke dan zaa karo wata kike hauka tunda dan ke aka yoni dalla bani hanya na wuce"

"Duk abinda zaka ce sai dai kace nasan baka isa ka sakeni ba idan Kuma Kai din dan halak ne ka sakeni kagani"

Tsaki yayi ya hankadata gefe ya fice daga d'akin.

Ko amsa gaisuwar su Afrah baiyi ba sabida b'acin rai yana fita ya ja motarsa a guje bai zame ko ina ba sai gidansu.

Kirjinsa kuwa har wani zafi yake masa wlh banda ya haihu da Luba da ba abinda zai hana ya harbeta kawai ya huta.

Dak'yar ya daure ya saisaita kansa amma suna gaisawa da hajiyarsa ta gane Yana cikin damuwa tana tambayarsa ya hau gaya mata dan idan yace zai hadiye maganar zuciyarsa na iya bindiga Allah ya kyauta kawai hajiyar tace dan ta sadakar a ranta asiri kawai Luba tayiwa salis dan banda ta Masa asiri Bata jin zai dau rabin iskancinta da tuni ya saketa ko ita sai da ta dage ya saketa yafi a kirga amma baya iya sakin nata da Addu'a kawai take binsa.

A takaice shawarar Da Salis ya Yanke kenan nasa aka wo Aneesa da danginta gidan Hajiyar sa ya fadawa Yan uwansa akan su zo tarbar dangin Aneesa dan jirgi zasu biyo karfe biyu daga nan za'a wuce a kai ta.

ANEESA

Har a zuciyarta tana balain kaunar Alhaji Salis dan wayayye ne duk da ko a samarin ma za'a dade baa samu dan gayu irinsa ba gashi duk da ya manyantan da kyaunsa tunda aka daura mata aure dashi cike take da tsananin farin ciki sosai ta tanadi irin faranta masa da soyyaya da zata zuba masa.

Idan akwai wacce taga bata farin ciki da auren bai wuce mahaifiyar ta ba dan gani take ta cuci kanta da ta aure shi tunda har mata uku ne dashi ita Kam ba abinda ya shafeta abinda tasani kawai shine kowa ya iya allonsa ya wanke"

Yayarta kuwa gyarata kawai take sabida Alhaji Salis ya sakar musu kudi ba kad'an ba ko a yanzu ma tsaye take a kanta da kofin zuma tana "Karbi maza ki sha nafiso naga

kinfita daban a cikin kishiyoyinki nafiso yaji ki zamzam nafi shekara biyu Ina Amfani da kayan Ammnur mai kayan mata wlh kayanta ba irin wayanda na sauran masu maganin Mata bane kema kinsan nice star ko"?

Aneesa ta gyada Kai cikin kunya a lokacin da ta karbi zumar daga hannunta ta fara Sha yayarta ta cigaba da zuba "Wlh kayan Ammnur yayi ba karya kayanta na gyara Aure wlh zan baki lambarta kiringa siyan kayan da09080070762 kanki dan Allah karki yi Wasa Aneesa ki dage da gyara dan mutuncin mace jikinta idan har kinaso ki Zama tauraruwa a wajen mijinki balle ke da kike da kishiyoyi wlh sai kin dage da gyara da shan maganin Sanyi

Ammnur _kayan mata tazo muku da zafafan kayan matan da babu algus 09080070762

Ina uwargida da ta haihu vjay dinta ya bude tana bukatar taji ta koma budurwa gam ga ammnur Nan ta kawo muku zafafan kayan mata Ina amare masu Shirin shiga daga ciki,Ina Zawara da suke so suji Basu da bambanci da budurwa

Enjoyment doesnt stop just because you have given birth. The afterbirth package is made to take care of you postpartum sexual needs . This package includes sweetner, wetner, tightener infection afterbirth herbs and more

Sauran kaya da zaki duba a wajen su na qara niima dadi da matsi sanan akwai na tsuma jiki na mata da na amare da uwargida Wato Madame package, suna da kayan farinjini, favour da kuma mallaka

1)Euphoria 12
2)Gorontula syrup
3)Her exellency cake
4)Exclusive thumi
5)Milky sweety
6)Magic insert
7)Tightening mallaka saop
8)Tightening honey pill
9)Women 001
10)Ebony lady
11) spiced tea
12)Mallaka chicken soup
13)Tightening powder
14) wetness powder
15) favour set
16) attraction set
17) bakar mallaka
18) shu'umar mallaka
19) hatsabibiyar mallaaka
20) horney honey syrup
21) libido booster set
22) breast enlargement
23) hips enlargement

Nasan kina da lambar mmn mujaheed dadin abin ma garinsu zaa Kai ki Kar ki sake ki yarda maganin sanyinta ya Kare miki har Alhajin ma ki ringa bashi Yana sha akai akai

INGANTACCEN MAGANIN SANYI TOILET INFECTION MAI WANKO DUK DATTIN MARA KOWANI IRIN SANYI NE ZAI MAGANCE SHI DAYARDAR ALLAH SHIN KINAFAMA DA RASHIN SHA AWA? RASHIN NI IMA RASHIN GAMSUWA SHIN KINYI SHEKARA DA SHEKARU KINA NEMAN HAIHUWA RIKICEWAR JINI CIWON JIKI CIWON MARA YAYIN AL ADA DUKA WANNAN MAGANIN YANA WARKARWA ME CIKI BATA SHAN MAGANIN SANYI NA 4K YAKE INA KATSINA INA AIKAWA KO INA A FADIN KASAR NAN HARDA KETARE MAZA DA MATA MAGANIN SANYI MAI GYARA MU AMALAR AURE AUNTY ZEE MOM MUJAHID
08162859027
KATSINA

"Insha Allahu Aunty zanyi yanda Kika ce din"

Shigowar Hajiya Binta yasa yayarta ta bar dakin ita Kuma hajiya Binta ta zauna a gefen Aneesa ta hau mata nasiha Kamar tayi kuka batasan mai yasa taji bata San Auren Alhaji Salis da Aneesa tayi ba.

Karfe daya da rabbi suka nufi Airport tare da rakiyar Yan uwan wajen su takwas da yayar Aneesa da Hajiya Binta da ta dage zata je ta bada amanarta.

Past.

Aisha

Ban iya basu labarin komai ba a ranar sabida zazzabin da ya rufeni hawaye kawai ke zubo min idona a rufe domin Allah sai Wanda aka Masa irin cin amanar da Salis da luba suka min ne zai gane abinda nake ji a zuciyata.

 Bazan yaudari kaina ba Wai nace zan yiwa Salis wani uzuri Kai Luba da yayi abuja ya sa na kara tabbatar da irin kaunar da yake yiwa luba kawata har dan na mari Luba akan cin amanar da ta min ta dagani ta damfarni da kasa.

Yayana har gida yasa aka zo aka samin ruwa aka min allura idona a rufen Ina Jin Yana waya da Salis daya ce Masa Yana hanyar zuwa katsina na bud'e idona Ina "Yaya Dan Allah karka bari yazo wlh bana San ganinsa na tsaneshi Yaya nasan kana kaunata bazaka so ka rasani ba dan Allah ka tsaya min ya bani takarda ta"

Nace Ina fashewa da kuka.
Yayana ya zauna a gefena Yana sallati tamkar yanda Aunty Mamy ta ringa sallati

"Aisha kanki daya kuwa mai yayi zafi haka Mai ya hadaku kike neman saki a wajensa"

"Yaya Salisu yaci Amanata ya hainceni Yaya Aure yayi har tsawon shekara guda bansani ba ya Kuma rasa wacce zai Aura sai kawata Luba"

Hada baki sukayi wajen cewa "Wacce Luba"?

Na Kara fashewa da kuka Ina "Luba kawata Yaya Luba dai da kasani har sun haihu jiya suna ban taba sani ba ace duk matan garin nan dan kawai ya wulakantani ya rasa wacce zai aura sai aminiyata da ta san sirrina wlh Yaya na gama aurensa".....

NI DA KISHIYOYINA

NA SADNAF

E.W.F

PAID BOOK

Page 9

Aisha

Kuka na cigaba da yi Ina Jin Aunty mamy na cigaba da sallati yayana sai da ya dau tsawon mintuna kafin yace "Salisu dai mijinki shi ya Auri Luba kawarki har tsawon shekara daya baki sani ba"?

"Eee yaya ban tab'a sanin suna soyaya ba duk na d'auka aiki yake yi a Abuja bansan Luba ya aura a b'oye ba ya barni anan Yaya Ina fama da Yara shi Kuma ya Kai Luba Abuja Yaya idan Luba zata iya cin amanata ya dace Salis yaci amanata wlh bai tab'a nuna kaunarta a gabana ba kullum cikin kusheta yake tsana kawai yake nuna mata a fili ashe soyayya suke bansani ba sai ya kwashi wata kafin yazo wajena Yana wajen Luba,idan yazo haka zan ga ana ta kiransa yacemin ana nemansa a asibiti a daddafe yake sati daya bashida lokacina bashida na yaransa ashe Luba ya aura"

"Na dade Ina fada miki Aisha ban yarda da kawar nan taki ba a ranar da kuka tare a sabon gidanku idan baki manta ba har daki na kiraki na fada miki sau biyu Ina Kamata tana kallon mijinki kallo irin na soyyaya har ta zauna tana fada miki ita irin Salis take so ta samu ta aura a fakaice har tana baki dace da gidanki ba ita ta dace da gidan Kika sake mata ba inda bata Shiga a gidanki sau nawa na Miki fada anan,yanda Kika San Mara wayo haka Kika maida kanki a wajenta ke gaki bakya so tace bakida mutunci sabida kunyi kudi ai ga irinta nan duk yanda kike da ita ta zage taci amanarki Yan uwanta Suma basuji kunya ba suka hadu aka ci amanarki yanzu Yan uwansa zasu ce basu san ya Kara Aure bane"?

"Basu sani ba Aunty mamy dan a boye ya aureta wai da yarjajeniya baza'a su fadawa kowa ba nidai Aunty mamy ki fadawa Yaya wlh bazan koma gidansa ba ya karba min takarda ta tunda har ya fifita Luba a kaina wlh na bar mata shi"

Yayana Allah ya kyauta kawai yace ya fice daga d'akin na cigaba da kuka Ina nadamar duk saken da nayi da Luba tarin Abubuwan da nayi mata sakayyar da zata min kenan har ta haihu ya hada mata taro ya Kai abokanansa da matansu gidan suka Zama kawayen Luba ni da nake matarsa bansan abokanan aikinsa sosai har muyi wani muamalla da matansu ba na tuno yanda Luba ta goge tana ta kyalli da alama ba karamin kudi Salis ke kashe mata ba ashe duk labaran nan da luba ke bani Salisu ne har yan uwanta suma dan sunji kudi suka hadu aka daura Auren cin Amana dan idan Salis ya tashi zakkan kayan abinci na azumi wlh mai shegen yawa nake sawa akai gidansu luba haka zasuyi tamin addua ba gori ba ba wanda ban yiwa dinki a gidansu ba har mahaifinsu ashe har suma zasu yarda su daura auren Salis da luba da arziki a gidan wasu gwara a nasu kenan"

Na Share kwalar da nake wahalar da kaina wajen sharewa dan ba daina zubowa zaiyi ba.

Dak'yar Aunty mamy ta tilasta min na Sha tea yayana ma na tsaye a kaina sai cemin yake sai na dorawa kaina hawan jini sabida namiji shi dai bazai min dole na zauna da Salis ba amma shi baiga abin daga hankali ba tunda ba haramun bane sai dai ace ana barin halak dan kunya,Kuma Salis bai kyauta da ya boye min ba da ya fadamin ai yasan bazan hana ba.

Karfe bakwai Ina daga d'aki su Ashraf zagaye dani a kwancen da nake Nana na kwance a jikina duk yarana ma ba mai makale min Kamar ita wlh Ina kaunar Nana yarinya tausayi take bani idan na tuno ba'a san waye mahaifinta ba ban tab'a sallah ban roki Allah ya tona asirin wayanda Suka yiwa muhasim fyade ba da yanzu tana gidan mijinta a mutunce tamkar yanda Khadija tayi aurenta tunda su biyu ne kawai Mata a wajen Aunty mamy.

Sallamar Salis naji a tsakar gidan haka yasa na runtse idona wlh muryarsa da naji ya Kara tasomin da wani tsananin bakin ciki ko kaunar ganinsa bana yi jiya da yayi niyya ai zai hau wani motar ya biyoni amma ya koma wajen matarsa sai yau yaga damar biyoni sabida banida wani matsayi a wajensa.

Ina jinsa da yayana a tsakar gidan duk Yana bada hakurin abinda ya faru na auren da yayi a b'oye akan kaddara yasa ya auri luba da Kuma rabon dake tsakani baya so ya fada min ne dan kar ya daga min hankali,dan Allah a bani hakuri yasan bai kyauta ba.

Ina Jin yayana na fada Aunty mamy na sa bakin cin amanar da yamin ba Haushin auren suka ji ba ya rasa wacce zai Aura sai luba Kuma har tsawon shekara daya badan Luba ta fadamin ba da haka zasu ninkeni kenan inta tunanin aiki kawai yake a Abuja.

Ina ji yana ta bada hakuri Yana ya karbi laifiinsa ayi hakuri,kaddara ta riga fata yayana yace shi dai bazai iya min dole ba ya Shiga daki ya Sameni idan zan iya koma masa shi bashida matsala amma tilasta min ne bazai yi ba.

Ina jin lokacin ya nufo d'akin rashin kwarin jiki ya hanani mik'ewa na Shiga bandaki na rufe k'ofar yarana kuwa tuni suka zagaye shi ban bud'e idona ba dan banasan ganinsa.

Sai da duk ya gama yiwa yaran Wasa yace su fita su bamu guri.

Ina jinsa Yana k'ok'arin d'aukar Nana nasan bazata yarda taje wajensa ba dan Kara kwanciya tayi a jikina ya sa hannu ya d'auki ummi.

Ya Kira Sunana yana "Gani a durkushe a gabanki Aisha dan girman Allah kiyi hakuri ki yafemin bansan yanda zaayi ki gane kaddara tasa na auri Luba ba, ba san raina haka ta kasance ba dan Allah ki yafe min Aisha ki dubi girman Allah da yaran mu kiyi hakuri,na yarda idan kin hakura zamu koma Abujan gabad'aya"

"Wlh wlh na gama auren ka ba abinda zai saka na tab'a koma maka,da ka san tsanar da na ma wlh da baka Soma doso Inda nake ba, Salis Luba fa Luba kawata ka Aura ka d'auketa ka kaita Abuja ka munafirceni ka maidani wawiya a gabana ka nuna ka tsaneta idan na maka maganarta kace bakaso,ashe soyayya kakeyi da ita duk matan garin nan ka rasa da wacce zaka hadani kishi sai luba,ka d'auketa Ka kaita Abuja kukayi zamanku Kuna Shan soyayya ni Kuma ka barni da gadin gida da yaranka idan kazo sati daya sai ka juya ka tafi Wlh ban yafe maka wanan cin amanar da kayi min ba ni na yafe mata Kai kuje can ku karata ka bani takarda sakina"

Na karashe Ina fashewa da sabon kuka kirjina wani irin ciwo yake min Luba fa kawata ita Salis ya Aura.

Hakuri ya cigaba da bani Yana magiya da rantsuwar kaddara tasa ya aureta shi baya Santa wlh shi bai hada san kowa dani ba

Sai a lokacin na bud'e idona banida ma kwari sam dan ji nayi jiri na dan dibana na Mik'e zaune Ina "Kace baka santa ka aureta kayi Mata ciki ta haihu kayi taro da gayya ko? A Abujan mutanen ka waya sani a can ita Luba da ta sansu duk baka santa ka hadata dasu ko"? Salis ba dai kace baka santa ba toh wlh idan kana so na dawo gidanka sai ka rubutawa Luba saki uku yanzu a gabana a cikin mu biyu sai ka zabi daya idan ka zabi rabuwa da ita sai na zauna da Kai idan karin auren kake so sai ka Kara da koma wacce ce idan Kuma ita ka zab'a sai ka daina mafarkin ni Aisha zan dawo gareka"

"Innalillahi wa Inna ilaihi rajiun Aisha ki rufamin asiri wanan hukuncin naki yamin tsauri wlh bana kaunar Luba ki yarda Zan saketa anan gaba amma Banda yanzu dan Allah dan Annabi"

"Tashi ka fita Salis idan ka saketa ko nan da shekara Ashirin ne sai na dawo gareka amma bazan hada miji da Luba ba"

Ganin zai cigaba da magiya yasa na saka masa ihu ya mik'e ya fita sauri
Yana fita na Kara fashewa da sabon kuka dan tsananin bakin ciki daga yanda ya nuna min bazai iya sakinta ba nasan ba karamin so yake yiwa luba ba ai tunda har ya Kai ta Abuja nasan matsayina a wajensa.

Haka Salis ya ringa sintirin zuwa ba dare ba Rana har yaransa yasa suka ringa rokona suna min kuka ganin yayana shima yace masa ya daina matsamin ya sakeni kawai tunda ya nuna yafi San Luba yaje ya zauna da iya lubar kawai

Yasa hankalinsa tashi dan ya tabbata dagaske yayana bazai tab'a sa baki na dawo gidansa ba

Washegarin ranar sai ga Hajiyarsa da mahaifinsa sun zo.

Mahaifinsa da ake cewa baffa na zaune a palo Hajiya Kuma ta shigo d'akin da nake kwance.

Har ga Allah tamkar 'ya ta d'aukeni nasan tana kaunata tana shigowa ta hau cewa "Ashe abinda yaron nan ya aikata kenan Aisha"?

Sai hawaye suka hau zubo min ta zauna tana "wlh wlh bamu sani ba sai jiya daddare yaje ya na fada Mana abinda ya aikata har ace Salisu yayi Aure batare da sanin Iyayensa ba ya Kuma rasa wacce zai aura sai kawarki wai ashe har ta haihu ma wlh bai kyauta ba jiya har sai da na buge shi mamana kiyi hakuri matakin da Kika d'auka yayi tsauri taya zaki yarda wata banza tazo ta rabaki da mijinki da tun bashida ko sisi kike tare dashi taya zaki bar mata mijinki?Ina zaki Kai yaranan ki bar mata gidan ita kadai bayan dake aka Sha wahalar ya zama abinda ya zama a yau kinsan mutane basa tsoron Allah wlh karkiyi mamaki asirce shi tayi ya aureta kiga fa ba ke kadai ya boyewa ba har mu da muka tsugunna mu ka haifeshi bai fada Mana ba dan haka kiyi hakuri badan na isa ba ko Zan tilasta miki sai dan girman Allah da yaranki kiyimin wanan alfarmar insha Allahu idan dai har ba dan Allah akayi auren nan ba muna nan

dake sai Kinga yanda zasu rabu bare abu da cin Amana kiyi hakuri kinji mamana bari ma na durkusa miki ai bazan yarda nayi Asarar suruka irinki ba"

Sai ta fara k'ok'arin tsugunnawa na rukota da sauri Ina "Dan Allah ki bari hajiya"

Har ga Allah ta d'aureni da jijiyoyin jikina bana kaunar Salis ban hararo yanda wai zanyi zaman kishi da luba ba,bansan da wane idon zan Kara kallon Salis a matsayin mijina ba domin babu digon kaunarsa a raina.

Kuka na naci na gode Allah dan wlh baa san raina zan koma gidan Salis ba.

Mahaifin Salis ma yasa aka kirani ya Kara bani hakuri ya bawa yayana ya min nasiha akan masu hakuri zanga sakamakon biyayyar da na musu na yarda zan komawa Salis din.

A haka suka Mana sallama suka tafi akan karshen sati zan koma gidana.

Yayana shima ya Kara bani baki

Aunty mamy kuwa itama baa barta a baya ba ta ringa bani shawarwarin yanda zan jawo hankalin Salis wajena itama tasan Luba asiri ta Masa ya aureta idan ba haka ba ita bata ga mai zai yi da wata Luba ba.

A ranar lahadi na koma gidana Salis sai rawar jiki yake ya Zama hoto a wajena domin babu kaunarsa a raina zan sauke masa duk wani hakkinsa daya rataya a wuyana amma batun mu koma Kamar da babu domin Salis da luba sun min raunin da bazai tab'a warkewa a zuciyata ba.

Magiya Kam da rarrashi haka ya cigaba da min Inda ya sakomin zancen komawa abuja ya siya wani gidan daban da Zan zauna inyaso Yara sai ya sama musu wani makarantar idan anyi hutu sai mu ringa zuwa

Na girgiza masa Kai akan ba zanje Abuja ba zanyi zamana anan yaje ya zauna da Luba a Abuja ai inaga dama ban dace da zaman abujan ba shiyasa bai tab'a tunanin ya tafi dani ba inda yaga ya dace dani ya ajiyeni ya barni da yayana kawai anan"

Na lura Sam baiji dadin maganata ba ya hau min rantse rantse ba haka bane na share shi ban Kara bi ta kansa ba.

A daki daya dai muka ringa kwana kafin ya tafi Ina kallon yanda yake boye boyen waya nasan Luba ke kiransa wlh sai naji bana Jin haushi ko wani kishi dan dagaske bana Jin komai a kansa.

Duk yanda yaso mu koma kamar da abu ya faskara shopping kuwa har da na banza.

Ana washegari da zai koma Abujan da yamma naga ya shigo da wata jar mota karama daidai na mata nidai tsakanina dashi idone hirar ma shi kadai yake yi.

Ta window tsakar gidan na gane bada motarsa ya dawo ba

Sai da ya shigo yaci abinci ya zauna a gefen kujerar da nake zaune ya ajiye mukulin mota akan cinyata Yana "Bansan mai zan miki na faranta miki ba Aisha banaso na tafi batare da naga dariyarki ba banaso na tafi batare da ko sau daya kin min hira ba ga

mukulin mota nan naga karamin mota daidai na Mata na siyo miki burina naga na goge laifin da na miki Aisha komai ya wuce dan Allah"

"Ina ganin Luba ta fini bukatar motar nan ko dayake kila ka dade da siya mata da baka wahalar da kanka wajen siyamin ba dan bana wani bukatar ta tunda ni ba ko'ina nake zuwa ba"

"Wlh ban siyawa Luba komai ba ke Kika fi cancanta na siya miki shiyasa na siya miki dan Allah ki daina hada kanki da luba na rokeki da girman Allah dan ba matsayinki daya da ita ba"

Gyada masa Kai kawai nayi burina ma ya bar gefena wlh ban sake ganin farinsa ba ko duk duniya zai ajiyemin bazai tab'a burgeni ba.

Washegari ya dau hanyar Abuja bayan ya ajiye min kudi mai yawa akan Nan da sati biyu zai dawo.

Luba

Kamar tayi karamin hauka a lokacin da taga Salis ya daga hankalinsa akan Aisha har marinta yayi sabida ta nana Aisha da kasa a lokacin da ta kawo mata mari.

Sai gashi tunda ya tafi katsina fiye da sati biyu bai dawo ba kamar ta mutu dan azabar kishi ko ta kira Salis din baya d'auka hakan ya Kara daga hankalinta Inda ta fara shirye shiryen biyo shi sai gashi ya dawo fuskar nan tashi a hade bakin cikinsa mai yasa ta tona musu asiri.

Koda ya dawo banza ya bawa ajiyarta ta ringa masifarta ita kadai.

Abincinta ma ba ci yake ba abu kad'an zata ga ya dau wayarsa ya Kira Aisha da wayar zai karaci ringing bata d'auka ba.

A haka zata bi wayarsa daddare tana karanta messages din da yake turawa Aisha kamar ta hadiyi zuciya ta mutu,abinda ya fara daga Mata hankali bai wuce sati sati da yake tsirar tafiya katsina ba sai ya shafe sati biyu uku bai dawo ba.

Tuni taji zaman abujan ya isheta wani dawowa da yayi ta sako shi a gaba akan itama zata koma katsina da zama bazata yarda da wanan cin amanar da ake mata ba.

Ta karfi da yaji ya amince zata koma katsina ya sama mata karamin gida daidai ita.

Sai dai tana ganin gidan ta dage bazata zauna ba sai dai ya dawo da Aisha gidan ya maidata wancan katon gidan idan bazai iya ba gwara ya hadesu.

Ba karamin tashin hankali suka ringa da Salis ba dan Salis bayaso ya hada luba da Aisha a gida daya sai yake ganin idan Aisha tana ganin Luba a gidan tamkar zai kara jawowa kansa ne a wajenta.

Hakane yasa ya sake nemo gidan da yafi gidan girma amma Luba ta Kara dagewa akan ita yanzu bataso ma tafi so su zauna gida daya da Aisha dan tafiso duk abinda akeyi ya zama tana gani Kar ma Salis ya ringa cutarta Yana cin amanarta.

Har kudi Salis ya bata mai yawa dan ta hakura ta zauna a gida daban taki akan dole ya tari Aisha da maganar hankalinsa a tashe sai dai ga mamakinsa Aisha cewa tayi

su biyun bata da matsala dasu ita samant yaranta take Luba ba kishiyarta bace ba ita ai bata da mijin yanzu"

A takaice da haka Luba ta dawo gidan aka ware mata part din da bai kai na Aisha girma ba.

Tunda kuwa ta dawo gidan bata da burin daya wuce taga ta yiwa Aisha abinda zai saka ta zuciya ta sa Salis ya saketa sai dai haka zata karaci abin ta Aisha bata tab'a tankata ba hasali sai ta kusa sati bata sa Aisha a idonta ba a lokacin da ta gano Jan motar da take gani a tsakar gidan na Aisha ne ba karamin yak'i akayi ba dan sako Salis tayi a gaba akan lailai sai ya siyo mata itama, Salis kuwa ya rantse akan bazai siya Mata ba kullum cikin tashin hankali da fada Idan suna yi Aisha bata yi kamar tasan me suke yi kasan ranta Kuma ta fara yarda da zancen hajiya da Aunty mamy akan asirce shi Luba tayi dan da hankalinsa bata Jin zai dauki rabin iskancinta.

Ganin Abu yak'i ci yak'i cinyewa yasa ta d'auko mukulin motar ta bawa Ashraf akan ya Kai Mata dan taci kwalar rigar Salis akan ba inda zaije sai ya siyo mata nata motar.

Ashraf kuwa Yana zuwa yace ga mukulin mota inji Aisha ta wufce mukulin da sauri tana gwara da aka kawo mukulin da anyi tashin hankali a gidan.

Koda Salis yaje ya samu Aisha akan mai yasa tayi haka ce masa tayi bata bukatar motar indai akan motar suke zubar da mutuncin su a gaban yaranta gwara ta bata kawai.

Kwana biyu a tsakani Salis ya siyo motar da tayi biyun wancan a tsada ya Kara kawowa Aishan

Luba kuwa Kamar ta mutu dan bakin ciki.

Duk takalar Aisha da take da fada da laben da take Mata bata tab'a bi ta kanta ba a haka har suka shekara biyu Allah ya kawo rabon haihuwar Aliyu wata uku a tsakani itama Luba ta haifo danta namiji aka sa Masa Abdul.

Kiri kiri take ganin rawar jikin da Salis yake akan Aisha da ta maida sa baho sosai take kishin Aisha ba yanda zatayi ne.

Aisha ma bata bi ta kanta ballantana su yi tashin hankali da ita.

A irin wanan lokacin Salis yazo da zancen Karin Auren Hindatu Yar Mai gidansa da ya Masa hanyar aikin NGo dan shi ya nemi daya auri Hindatu dan ta gama makaranta ba mijin aure

Salis bazai iya ce masa Aa ba baya kaunar Hindatu amma a haka ya karbi tayin aurenta.

Luba kamar ta hauka ce dan kishi, Salis kuwa ya zagu haka ta nemo gidan su Hindatu taje tayi rashin mutunci inda sai da ya Kai su ga dambe har police station.

A lokacin Hindatu taso ma ta hakura da auren sai kuma taga idan ta hakuran Luba taci galaba akanta.

A haka akayi auren Hindatu da Alhaji Salis ana zuba tashin hankali a gidan

Aisha kuwa tuni ta Kara komawa gefe ta kawo Ido ta zuba musu ba ranar banzan da basa zage zage da Hindatu ko ayi dambe a gaban Yaya suna kallo wanan kenan.

Yanzu Kuma mun dawo labari

Dangin Salisu da hajiya
Tarba mai kyau suka yiwa dangin Aneesa Inda sai a lokacin hankalin mahaifiyar Aneesa ta Dan samu kwanciyar hankali da taga mahaifiyar Salis din tana da mutunci da alama baza'a samu matsala da ita ba matansa ne dai bata sani ba hakane yasa bayan sunci sun Sha lokacin an Kai Aneesa d'akin hajiyar dan da Magriba zata kaita gidanta duk da gidansu Salis din kato ne an Kama musu hotel akan su kwana gobe su wuce.

Mahaifiyar Aneesa kuwa wajen hajiyar Salis tayi tana "zanso na Kara damka amanar Aneesa a hannun kishiyoyinta tunda hajiya Kinga yarinya ce gashi ba gari daya muke ba zanso Kafin a kaita mu fara zuwa can din"

Hajiyar Salis ta saki murmushi tana "karki damu ba sai kinje ba wlh mun karbi Amana matansa basu da matsala abinda ma ba gida daya zasu zauna ba wlh karki ji komai Aneesa ai 'yata ce"

Kwarjinin da Hajiyar ta Mata yasa bata iya Musa mata ba da Magriba suka raka Aneesa dakinta da ya gaji da had'uwa da tsaruwa.

Bayan duk sun mata nasiha Tana kuka haka suka barota suka nufi masaukinsu.

Tafiyarsu da minti Ashirin Salis ya shigo gidan rabonsa da ya tsinci kansa cikin farinciki haka tun kafin ya auri Luba da Hindatu.

Yau tamkar farkon aurensa haka yakeji Yana Kuma doki.

Sai da ya ajiye ledojin hannunsa ya taka ya nufi wajen da Aneesa ke zaune a gefen gado, ya zauna tare da yaye lullubin fuskarta suka hada Ido tare da sakarwa juna murmushi.

Salis ya jawota ya rungumeta Yana sakin ajiyar zuciya wani irin sanyi na tsirga mai a zuciya a yau Yana so daren ya kasance Masa cikin dararakin da bazai manta ba Yana so su raya daren cikin so da kauna.

Dak'yar ya cikata yasan tana kaunarsa bazata wahalar dashi ba kayan ciye ciyen da ya shigo musu dashi suka ci suka koshi ya tafi dakinsa yayi wanka Yana dawowa yaga itama da alama tayi wankan har alwalar ma tayi tana jiransa.

Sai da yaja su suka yi sallah Isha da shafai da wtr ya Kara raka'a biyu sai da ya dan yi musu addua mai tsayi kafin ya shafa ya mik'e fuskarsa d'auke da murmushi Yana bari yaje ya kulle k'ofar gidan.

Yama kashe duk wayoyinsa dan luba sai kiransa take

Yana k'ok'arin danna k'ofar yaga an turo k'ofar da k'arfi Luba ta Fado cikin gidan Tana hucci "innalillahi wa Inna ilaihi rajiun mai kikeyi anan"

"Kai ka Isa ka wulakanta mu ai tunda ka dage ka auri yarinya Nan kayi bankwana da farinciki wlh Allah kana San kwanciya hankali ka rubuta mata sakinta ta tafi gidansu,har mu zaka munafirta kazo ka ware mata gida wacce ita"


Ammnur _kayan mata tazo muku da zafafan kayan matan da babu algus 09080070762

Ina uwargida da ta haihu vjay dinta ya bude tana bukatar taji ta koma budurwa gam ga ammnur Nan ta kawo muku zafafan kayan mata Ina amare masu Shirin shiga daga ciki,Ina Zawara da suke so suji Basu da bambanci da budurwa

Enjoyment doesnt stop just because you have given birth. The afterbirth package is made to take care of you postpartum sexual needs . This package includes sweetner, wetner, tightener infection afterbirth herbs and more

Sauran kaya da zaki duba a wajen su na qara niima dadi da matsi sanan akwai na tsuma jiki na mata da na amare da uwargida Wato Madame package, suna da kayan farinjini, favour da kuma mallaka

1)Euphoria 12
2)Gorontula syrup
3)Her exellency cake
4)Exclusive thumi
5)Milky sweety
6)Magic insert
7)Tightening mallaka saop
8)Tightening honey pill
9)Women 001
10)Ebony lady
11) spiced tea

12)Mallaka chicken soup
13)Tightening powder
14) wetness powder
15) favour set
16) attraction set
17) bakar mallaka
18) shu'umar mallaka
19) hatsabibiyar mallaaka
20) horney honey syrup
21) libido booster set
22) breast enlargement
23) hips enlargement

Naceba♀
Kina bukatan jikinki yazama so fresh ba kwarzane ko daya ballantana kuraje ko tabo, sunburn,acne, ko knuckles? Kije kigwada products na mg's insha Allah zakiga ynd fatarki zedawo fiye da tsammaninki zakigyara jikinki naturally batare da kinbata fatarki ba jikinki yayi fresh kiyi smooth kizama kalar Madara kirar models kiringa walwali kina haskawa duk inda kikayi😍
Kidena kokonto cewa kingwada baki Dace ba insha Allah kijaraba products dinsu bi'iznillah zakiji dadinshi kayansu akwai kamshi especially sabulun kamshin yakama jikinki ko kindade da wanka jikinki zaidinga fidda ni'imtaccen kamshi bayinki ma zakiji kamshin dazai Kama😍sunada kit special domin amare Wanda indai kinyi using kit dinnan Baki bukatar kikara Kai kudinki gurin dilke domin ainihin yanda fatarki zehaska yagoge kidinga shining abun sewanda yagani😍

Mai bukatar kayan mg's chat:08062991549,07046881166,07067210195
Call:08064532391
Hausawa nacewa adade anayi sai gaskiya Kuma siyan nagari maida kudi gida
 tested nd trusted
Natural/organic

WANAN LITTAFIN NA KUDINE BIYA 500 TA WANAN ACCT 0272061655 WEMA BANK NAFISA NUHU KO KATIN MTN KO AIRTEL TA WANAN LAYIN 08033719070 SAI A TURO DA SHAIDAN BIYA TA LAYIN NAN 08033719070 MUTANEN NIGER KUMA KU TUNTUBI WANAN LAYIN
+22796 82 89 84 DUK WACCE TA MIN SHARING NA BAR TA DA *RABBI ZAI FIDDA MIN HAKKI NA DA IZININ ALLAH DOMIN BA YAFEWA NAYI BA*

NI DA KISHIYOYINA

NA SADNAF

PAGE 13

Luba ta dib'a a guje tana ihu a daidai lokacin da Alhaji Salis ya cimmata tare da kai Mata wukar bayanta cikin Zafin nama Ashraf ya rik'e hannun Alhaji Salis dake wani irin kakarwa Luba kuwa sai ihu take

"Ka sakeni Ashraf ka sakeni na kasheta dan dama nace mata nine ajalinta"

"Abba bazan iya bari kayi kisan Kai ba dan Allah ka saki wuk'ar nan kaga ma ka yanketa"

Alhaji Salis kuwa sabida rawar da jikinsa ke yi yasa ya saki wukar Yana Jin Kamar numfashinsa ya d'auke wani irin kunya yasa yaji kamar ya nutse a kasan a yanzu da akwai yanda zaiyi ya suma da ya sume da idon Aishan da yake ji a kansa shekara sha hudu Yana cikin tsananin damuwa da fargaba kullum Addu'arsa Allah ya rufa masa sirrin nan batare da kowa ya sani ba sai gashi Luba ta bankada shi a gaban Aisha a gaban yayansa gabad'aya da yasan duk da wayon su kad'an ne basu da wayo ya zub'e akan gwiwarsa dafe da kansa Yana sallati

Luba kuwa daki ta fada tana ihun bayanta ta kadu sosai dan ta d'auka zai kasheta din ne da Ashraf bai ceceta ba tasan da yau sai Alhaji Salis ya aikata lahira.

wani sabon tashin hankali ne ya sake rufeta data tuna fa Alhaji Salis ya mata saki uku ta dora hannunta a ka sam tunaninta bai tab'a bata akan idan ta bankada sirrinsa zai saketa ba abinda sirrin nasa shine takamarta shine nata rufin asirin shine abinda ya kaita ga samu ta aure shi sai gashi tsabar rashin hankali irin nata tayi hauka abun ya dawo kanta ba'a saki Aneesa ba an dankara mata saki uku bayan ta wani irin zugi yake amma tashin hankalin da take ciki na sakin da Alhaji Salis ya mata yasa bata ji ba ta hau zirga zirga a d'akin tana cije lebbenta da cutar kanta da tayi tuna wai sakin da ya mata na nufin rabuwa dashi na har abada ta bar uban daular da take ciki yasa ta saki ihun kuka ta haka Ramin mugunta ta fada.

Jikinta na rawa ta d'auko wayarta a gaban mudubi ta hau nemon lambar Asabe a waya bata da Kuma Sama da Asabe yanzu ita kadai zata iya taimaka mata dan Sam bata shirya barin gidan Alhaji Salis ba batasan mai yasa tunanin ta bai tab'a bata zai saketa ne idan ta tona Masa asiri sai dai duk Kiran da take wa Asaben yana ringing bata d'auka ba.

Muryar Alhaji Salis kawai ke tashi a palon yana sallati

Aisha kuwa tunda Luba tace Alhaji Salis ne mahaifin Nana taji duk notikan kanta na kuncewa kalmar kuwa maimaituwa kawai yake a kanta kirjinta na daka wani irin tsalle a tsayen da take so take taji Alhaji Salis yace sharrin Luba ne bashine mahaifin Nana ba sai dai kalmar kin kasheni Luba da yace da binta da yayi da gudu akan zai kasheta yasa kafafunta kasa daukarta har sai da ta kai ga zubewa a kasa yaran sukayi kanta gabad'aya Nana itace farkon kamota tana "Ammi" duk a yaran ita kadai kece mata Ammi sauran kuwa Hajiya umma suke ce mata

Sai ta bi Nana da kallo tana hango fuskar muhasim a fuskarta muhasim dake garin bauchi a killace a daki kanta akarkace bakinta ma haka sai ta tafi tunani

"Uncle Salis dan Allah ka koya min home work dinan bangane ba wlh"

"Wasa ya miki yawa muhasim bakida aikin daya wuce Hawa lilo taya zaki gane bazan koya miki ba kije Auntynki ta koya Miki"

"Kai Abban Ashraf tona min asiri kawai kake so kayi ina zan iya wanan maths din nasu"

"Tunda ga Ashraf nan ai sai ya koya mata tunda shi yafita k'ok'ari"

"Salon ka jawo mata raini kenan tana Auntynsa"

Sai Kuma kiyi

Ya haye sama

"Wai wane irin wasan banza kukeyi haka ke namiji ce da zaki ringa ball"?

"Ashraf ne yace nazo muyi ball"

"Dalla shige ki bani guri"

Muhasim ta dib'a a guje tayi cikin gidan

Yana shigowa nace "Gaskiya Abba Ashraf ka takurawa 'yata kiri kiri ake nuna min anfi ji da Khadija kasan fa muhasim ta wajena ce"

"Ai yarinya ce akwai dan banzan Wasa Khadija ta fita nutsuwa"

Ire iren tunanin da Aisha ta tafi kenan akan muhasim da Alhaji Salis da tasan cewar tsakanin su tamkar uba da ya ne shekara biyu kawai ta bawa Ashraf wai Alhaji Salis din shi yayi wa muhasim fyade ta haifi Nana

Ta saki wani irin ihu tare da kankame Nana tana "Dan Allah kuce min karyane ba Salisu ne mahaifin Nana ba dan Allah kuce min karyane ba Salisu ne yayi wa muhasim yata fyade ba Yar yayana yarsa ce fa innalillahi wa Inna ilaihi rajiun innalillahi wa Inna ilaihi rajiun"

"Hajiya kiyi shiru dare ne dan Allah bashi bane sharrin Luba ne Kamar bakisan halinta ba"

"Hindatu ba Wanda yasan asalin Nana nace muku mahaifiyar ta rasuwa tayi na riketa sabida banaso a goranta mata Nana Yar muhasim ce Yar yayana diya ce a gareni rana daya muka wayi gari an mata fyade bakinta da kanta ya karkace tsawon shekara goma sha biyar muhasim na fama da karkace war baki da kai duk kanenta sunyi Aure Bata iya magana komai yi Mata akeyi,duk zargin Wanda ya Mata fyade ne yayi mata haka ko turen Aljannu har yau yayana bai kara samun cikakiyar lafiya ba sabida larurar ta mahaifiyar ta ma haka dan Allah kuce min karyane ba Salisu mijina ne yayi wanan aika aikar ba,
 ba Salisu mijina ne ya kassara rayuwar Yar yayana ba,ba Salisu mijina ne ya Zama silar jefa yayana da matarsa cikin bakin cikin shekara da shekaru ba,
Ba Salisu mijina ne ya haikewa yarinya da bata gama mallakar hankalinta ya cutar da ita Hindatu kije ki tambaya min shi bana so na yarda shi yayi wa muhasim haka ki taimaka min Hindatu innalillahi wa Inna ilaihi rajiun"

Yarana duk suka zagayeni suna nayi shiru na duba wajen da Salis ya zub'e Yana sallati ban ganshi ba. Adaidai lokacin da Hindatu ta mik'e ta nufi bangaren yaran dan can taga Alhaji Salis ya nufa.

Aneesa da Afrah a girme ma ta girmeta ta itama ta matso kusa da yaran ta zube akan gwiwarta hawaye shabe shabe a fuskarta tana "Hajiya dan Allah Mai ke faruwa ne wacce Nana mai Alhajin yayi"?

Na kalli Nana da tunda na fara kuka take kuka wai Salisu mijina shine mahaifinta kirjina Kamar ya fashe haka nakeji jikina wani irin rawa yake na Kai hannuna gefen wuyanta na juyar da fuskarta sak irin bakin tabon wuyan Alhaji shine a wuyan Nana duk sauran yaran ba mai irin tabonsa na Kara zura Mata Ido Ina bin ko'ina na jikinta da kallo sai a yanzu na fara ganin jinin Salisu a jikinta hankalina bai tab'a kaiwa ba wani zubin idan tana tafiya sai naga kamar irin ta Afrah nakan danganta haka da jini ne gashin girarta da set din hakorinta duk irin na Salisu ne,na tuna lokacin da Luba take masifa sai ta daketa Ina jinta a daki tana shegiya mai iirn idon ubanta Ashe duk wanan zagin da take na ubanta Salis ne sai na Kara hada Wai Salisu da muhasim? muhasim fa yata ce fa?

Na tuna lokacin da yazo ya same mu a asibiti da muka Kai muhasim da na fada masa abinda ya faru yanda hankalinsa ya tashi har Yana neman kuka Yana "Wane azzalumun ne yayiwa muhasim haka yarinya karama"

A ranar a asibitin duk Muka kwana har dashi yayana ma ya fishi dauriya dan har yanda ya nuna damuwar sa akan abinda ya samu muhasim yan uwana suka yi ta yabon sa suna masa Addu'a duk matan duniya Salisu ya rasa wacce zai nema sai yar yayana wanan wane irin kwamacala ne kenan shi ne silar cutar muhasim da bakinta ya karkace sabida Kar ta tona masa asiri sai naji kirjina yayi wani irin nauyi Kar dai Salisu ne yayi wa muhasim haka iya fyade bai isa ba ya Kara da karkata mata baki da wuya

Wani irin mik'ewa nayi na Kara zub'ewa a kasa sabida rawar da jikina yake Ashraf yayo kaina da sauri da Afrah dake ta kuka "Hajiya dan Allah mu tafi d'aki ki samu nutsuwa dan Allah kibi komai a hankali"

"Nabi komai a hankali Ashraf na samu nutsuwa?
 ta ya zan samu nutsuwa kasan me ke faruwa kuwa Ashraf Muhasim wai Baban ku ne ya mata ciki ta haifi Nana"?

"Abban bazai tab'a haka ba kema kinsani kila sharrine hajiya umma kibi komai a sannu dan Allah"

"Ashraf cikani samun nutsuwata shine naje ya karyata ba haka.bane Ina addua Allah yasa sharrin aka masa domin wlh wlh idan har dagaske Abban ku shi ya cutar da Yar yayana shine Kuma mahaifin Nana wlh tallahi sai inda karfina ya Kare ka sakeni Ashraf"

Nace a tsawace kirjina sai sama da kasa yake tsawan da na masa yasa ya sakeni a tangal tangal na nufi bangaren yaran Hannuna cikin na Nana.

Muryar Hindatu dake tashi a palon yasa na tsaya a bakin k'ofar tare da dafe kirjina da naji idan ba haka nayi ba zai iya fadowa

"Alhaji nidai ka fito ka fada min gaskiya taya ka Zama mahaifin Nana bayan a fadar Aunty Aisha mahaifiyarta Yar yayanta ce Alhaji da gaske kaine mahaifin Nana? dagaske zaka iya irin wanan cin amanar yarinya da tamkar 'ya take a wajen ka duk matan duniyar nan ka rasa wacce zaka haikewa sai ita yar yayar matarka fa kamin magana Alhaji"

Alhaji Salis ya bude idonsa daya kada yayi jajjur tamkar jini yace "Hindatu ko na sake karya ba abinda hakan zai haifar min sai Karin tashin hankali Hindatu a yanzu tausayina ya Kamata kuji bai Kamata ku hade min Kai ba dan girman Allah kije ki rarrashi Aisha banaso maganar nan ta fita ku rufamin asiri dan Allah dan annabi

Hindatu kaddara ta afka min nine mahaifin Nana har yau bansan ya akayi hakan ta faru ba"

"Innalillahi wa Inna ilaihi rajiun innalillahi wa Inna ilaihi Alhaji kai ne mahaifin Nana fa kace ? Kaine ka yiwa Yar cikinka fyade? Yar yayan matar ka fa wanan wane irin kwamacala ne?wanan wane irin cin amana ne iya cin amanar auren kawar Aunty Aisha bai isheka ba sai ka kara da cutar da ita ta hanyar yiwa dan yayanta fyade Alhaji yanzu ya Nana take dasu Ashraf kenan?ya yayan Aisha zai ji idan yaji labarin Wai mijin kanwarsa ne yayi masa wanan aika aika tur Alhaji tur wlh Allah idan har zaka iya wanan kwamacalar tsaf zaka haikewa Afrah kenan dama haka kake Alhaji innalillahi wa Inna ilaihi rajiun "

"Hindatu dan Allah ki bari Kar Aisha ta jiyo ki haba Hindatu ya kema zaki juya min baya a lokacin da na tsinci kaina a tsaka mai wuya dan Allah mata ta ki rufamin asiri ki tayani bawa Aisha baki wanan sirrin ne bana so ta sani shiyasa na auri Luba wlh wlh ba dan Ina kaunar Luba ba ku yarda kaddara ya afka min ba halina bane Hindatu ni da mazinaci ne zaku sani shekara biyar banida cikakiyar nutsuwa kullum a cikin fargaba nake Luba shekara Sha biyar Tana azabtar dani akan kuskuren da nayi da nima bansan mai ya kaini ba Kuna kallo yanda Luba ke juyani tana gindaya min sharruda wlh duk wai dan Kar sirrin nan ya fita tunda abinan ya faru Hindatu dauriya nake karki zama tamkar Luba ki taimaka min wajen kwantarwa Aisha hankali wlh kunyarta nakeji kunyar yayanta nakeji wlh nasan ban kyauta ba ya zanyi da kaddara da ta gifta min sharrin shaidan ne

"Alhaji wanan ba sharrin shaidan bane san zuciya ne kawai sai kun gama tsula tsiyarku sai ku fake da kaddara da shaidan wlh Alhaji baka kyauta ba wanan kwamacalar ma da ka aikata bansan ya zan iya bawa Aunty Aisha baki ba Kai daka aikata sai kasan ya zaka shawo kanta ciwo akan ciwo ga nacin amana ga na cuta haba dan Allah ni kaga tafiyata"

"Hindatu dawo dan Allah dawo ki rufamin asiri"

Alhaji Salis yace Yana k'ok'arin bin bayanta a daidai lokacin da Aisha ta shigo ciki jikinta na wani irin kyarma Hannunta damke da na Nana

Alhaji Salis yayi sauri ya durkushe tare da saka tafin hannunsa ya rufe fuskarsa.

Hindatu tace "Aunty Aisha sai hakuri nasan kinriga da kinji komai a wanan gabar sai dai nace Allah ya kyauta kawai"

Ta fice daga d'akin

Alhaji Salis kuwa sallati kawai yake zabgawa

Aisha cikin wani irin murya tace "Mai ka yiwa muhasim bakinta ya karkace da wuyanta"?

"Aisha na rantse da Allah bani bane ba ni na karkata mata baki da wuya ba wlh ki yarda dani na yarda ni na Mata fyade amma wlh banida sa hannu a abinda ya sameta wlh Allah Aisha"

"Idan mun hadu a kotu Salisu zaka fada musu gaskiya"

Daga haka ta juya ta bar palon tana Jin jiri na dibarta kafin ta kai palonsu jiri ya kwasheta yaran suka saki ihu tare da yin kanta gabad'aya.

Ashraf da Afrah hankali a tashe suka kinkimeta sukayi daki da ita Aisha nada farinjini duk a wajen yaran sai gashi duk sun rude da kuka Nana duk muryarta yafi na kowa tashi "Ammi ki tashi dan Allah karki tafi kibarni"

Hindatu kuwa ta buga uban tagumi jikinta duk Yabi yayi sanyi tama kasa bin bayansu.

Aneesa kuwa ta ringa rusgar kuka kukan da take yasa Hindatu daka mata wani tsawa tana "dalla mallama ki rufewa mutane baki ki bar mutum yaji da abinda yake damunsa"

Aneesa tayi dakinta da gudu dan itama tsoron Hindatu take.

Alhaji Salis kuwa ji yake kamar ya Yanke jiki ya Fadi kukan yaransa dayake ji da faduwar da Aisha tayi duk akan idonsa.

Duk wanan tashin hankalin Luba ce ta jefa shi a ciki dakinta ya nufa a fusace da mugun karfi ya daki k'ofar take ta bud'u

Luba dake zarya a d'akin yana bugo k'ofar ta saka wani irin ihu tana k'ok'arin yin wajen bandaki

Alhaji Salis cikin zafin nama ya damkota da hannu biyu ya shake mata wuya babban burinsa ya ga ya kasheta inyaso sai a daureshi kawai ya huta

Kakarin da Hindatu keyi yasa Luba mik'ewa da sauri ta nufi d'akin Luba,yanda taga ya daga Luba sama Yana k'ok'arin kasheta yasa ta saki wani wawan ihu tana "KU FITO ZAIYI KISAN KAI DAN ALLAH KU FITO ZAI KASHETA GA LAIFIN KISAN KAI GA NA FYADE ASHRAF KANA INA".....

Posting Monday to Friday zanyi gobe sabida ya fada jumaa posting din sai Kuma Monday idan Allah ya kaimu

INGANTACCEN MAGANIN SANYI TOILET INFECTION MAI WANKO DUK DATTIN MARA KOWANI IRIN SANYI NE ZAI MAGANCE SHI DAYARDAR ALLAH SHIN KINAFAMA DA RASHIN SHA AWA? RASHIN NI IMA RASHIN GAMSUWA SHIN KINYI SHEKARA DA SHEKARU KINA NEMAN HAIHUWA RIKICEWAR JINI CIWON JIKI CIWON MARA YAYIN AL ADA DUKA WANNAN MAGANIN YANA WARKARWA ME CIKI BATA SHAN MAGANIN SANYI NA 4K YAKE INA KATSINA INA AIKAWA KO INA A FADIN KASAR NAN HARDA KETARE MAZA DA MATA MAGANIN SANYI MAI GYARA MU AMALAR AURE AUNTY ZEE MOM MUJAHID
08162859027
KATSINA

Ammnur _kayan mata tazo muku da zafafan kayan matan da babu algus 09080070762

Ina uwargida da ta haihu vjay dinta ya bude tana bukatar taji ta koma budurwa gam ga ammnur Nan ta kawo muku zafafan kayan mata Ina amare masu Shirin shiga daga ciki,Ina Zawara da suke so suji Basu da bambanci da budurwa

Enjoyment doesnt stop just because you have given birth. The afterbirth package is made to take care of you postpartum sexual needs . This package includes sweetner, wetner, tightener infection afterbirth herbs and more

Sauran kaya da zaki duba a wajen su na qara niima dadi da matsi sanan akwai na tsuma jiki na mata da na amare da uwargida Wato Madame package, suna da kayan farinjini, favour da kuma mallaka

1)Euphoria 12
2)Gorontula syrup
3)Her exellency cake
4)Exclusive thumi
5)Milky sweety
6)Magic insert
7)Tightening mallaka saop
8)Tightening honey pill
9)Women 001
10)Ebony lady
11) spiced tea
12)Mallaka chicken soup
13)Tightening powder
14) wetness powder
15) favour set
16) attraction set
17) bakar mallaka
18) shu'umar mallaka
19) hatsabibiyar mallaaka
20) horney honey syrup
21) libido booster set
22) breast enlargement
23) hips enlargement

WANAN LITTAFIN NA KUDINE BIYA 500 TA WANAN ACCT 0272061655 WEMA BANK NAFISA NUHU KO KATIN MTN KO AIRTEL TA WANAN LAYIN 08033719070 DOMIN KI MALLAKI NAKI MUTANEN NIGER KUMA KU TUNTUBI WANAN LAYIN
+227 96 82 89 84 DUK WACCE TA MIN SHARING NA BAR TA DA *RABBI ZAI FIDDA MIN HAKKINA DA IZININ ALLAH DOMIN BA YAFEWA NAYI BA*

Ihun Hindatu yasa Ashraf ya fito da gudu ya shige dakin luba.

Luba kuwa tuni karfin ta ya fara karewa Ashraf ya ringa ihun Alhaji Salis ya cika luba "Abba karka yi kisan kai Abba dan girman Allah ka saketa karka kasheta"

Sai da Ashraf yayi da gaske kafin Alhaji Salis ya saki Luba da ko motsi ba tayi da alama sumewa tayi.

Hindatu kuwa tayi kanta da sauri

Ashraf kuma ya rike hannun Alhaji Salis da numfashinsa ke sama da kasa yayi waje dashi basu zame ko'ina ba sai bangarensu Afrah sai da ya kai Alhaji Salis har cikin dakinsa ya saki hannunsa Alhaji Salis ya zub'e a kasa Yana jan sallati babban tashin hankalinsa yanzu Aisha tace zata fitar da maganar nan da wane ido zai kalli Yayan Aisha da ya d'auke shi tamkar dan uwa,da wane ido zai iya cigaba da kallan Aisha,ya runtse idonsa sai a lokacin ya samu hawayen dake Kona zuciyarsa suka zubo a daidai lokacin da Ashraf ya Kira sunansa ya bud'e idonsa akansa sai ya tsinci kansa da Jin wani irin kunyar Ashraf sai ya kau da kansa

"ABBA nasan bazaka tab'a aikata abinda Aunty Luba tace ba,dan Allah Abba ka fito ka fada mana gaskiya mu samu hankalin hajiya umma ya kwanta"

"Ashraf banida kowa a yanzu sai Allah sai Kai da kake babban dana nasan zaka iya taimaka min ka shawo min Kan mahaifiyar ka dan Allah Ashraf kaje ka rarrasheta banaso a daga maganar nan kowa yaji kasan yanda muke da Yayanta da kunya yaji labari ni na yiwa yarsa haka dan Allah Ashraf ku rufemin sirrin nan nawa"

"Abba kenan dagaske Kaine mahaifin Nana"?

"Nine Ashraf ban isa na tsallaka kaddarata ba"

Ashraf kasa bud'e bakinsa yayi ya Kara magana ya sunkuyar da kansa Yana tuno Aunty muhasim da yarintar su ya kasa yarda Alhaji Salis zai iya aikata haka abin ya masa wani iri taya zai iya aikata irin wanan danyen aikin tambayoyi ne fal cikinsa amma nauyi da kunyar yasa ya hadiye tambayarsa ya mik'e yayi waje.

Shine babba dole shi zaiyi k'ok'ari yaga komai ya daidaita sai dai abin da Kamar wuya idan ya tuno yanda suka taso Aisha na koya musu yanda zasuyi adduar tonuwar asirin wanda yayi wa muhasim fyade.

Koda ya koma d'akin Aisha a jingine ya tadata akan gado ta lumshe idonta hawaye kawai take zubarwa duk yaran sunyi cirko cirko Afrah na daga gefenta itama kuka kawai take

"Duk ku tafi ku daura alwala an fara Kiran sallah"

A hankali Suka fara ficewa daga d'akin Ashraf ya zauna a gefen Aisha tare da ruko hannunta Yana "Hajiya"

A hankali ta bud'e idonta sai Ashraf yaji ya kasa ma mata magana "Ashraf kasan wacce muhasim ko"?

Gyada Kai kawai ya iya yi

"Yar yayana Mahaifinku yayi wa fyade ta haifi Nana duk tsawon lokacin nan da nake addua Allah ya tonawa duk Wanda ya aikata Mana wanan zalincin ashe Mahaifinku ne iya fyade bai ishe shi ba sai ya hada da karkata Mata wuya da Kai Ashraf wlh wlh sai na kwatowa Muhasim hakkinta ko da zaa daure shi ne sai na yi kararsa"

"Hajiya dan Allah kibi komai a hankali wlh Abba bazai aikata haka da gangan ba dan Allah ki rufa masa sirrin nan daga maganar nan tamkar kin shafa mana bakin fenti ne gabad'aya mutunci Abba zai zube da namu uncle zai daina ganin mutuncinsa"

"Ashraf idan na tashi Kai shi kara ka hanani bai San da mutunci ba ya haikewa Yar yarinya sabida munafiki ne shi ko a fuska ban taba sani ba taya Zan kawo Mahaifinku zai iya haka wlh wlh na gama aurensa Kuma sai nayi kararsa.

Ashraf na k'ok'arin Magana Aisha ta daka masa wani uban tsawa akan ya fita ita bazata ji komai ba.

Ashraf bai tab'a ganin ta harzuka haka ba hakane yasa ya mik'e ya bar dakin Yana Allah ya Sanyaya zuciyarki.

Aisha

Nayi Sallah ne kawai amma baa nutse ba har addua nake inama mafarki nake ba dagaske Wai Salisu ne yayiwa yata fyade ba

Sai a yanzu na ringa tuna yanda hankalinsa ke tashi idan Ina tsinewa Wanda yayi wa muhasim fyade akwai ranar da na dawo daga bauchi kenan yanda na baro muhasim baki a karkace duk maganar da zaka mata sai dai ta biki da Ido sai dai a kwantar a tayar duk mai tausayi idan har yaga yanda take wlh sai ya zubar mata da hawaye da tsananin tausayin ta na dawo garin katsina har nayi girki nayi Sallah tana Raina yarinya mai kyau da hankali ji yanda ta koma bata ma tab'a d'aukar Nana ba sai dai ta bita da Ido,

Koda Salis ya dawo hankalinsa tashi yayi dayaga yanda naci kuka idona yayi ja hakane yasa ya hau tambayata mai ya faru cikin kuka nace masa "Wlh tausayin muhasim nake Abban Ashraf Allah ya tsinewa Wanda ya maida ta haka Allah ya tona Masa asiri bazai gama da duniya lafiya ba"

"Kai Kai Aisha wane irin addua kike haka Kamar ba musulma ba kiyi addua kawai Allah ya bata lafiya a cigaba da nema mata magani na me wanan manyan tsinuwar nan haba Mana kamar bakisan kaddara ba"

"Wlh Abban Ashraf har na koma ga Allah Ina addua da laanta Wanda ya mata haka haba Abban Ashraf zalincin yayi yawa dole nayi tsinuwa

Idan har zanyi tsinuwar sai yamin waazi ya hanani ko ya bar wajen ashe duk shi ya aikata laifin.

Na share hawayen da ya zubo min Yayana ya kaunaceni har a yau duk wani abu daya shafeni ba
Ya Wasa dashi shiyasa a duniyata nakesan farin cikinsa tunda wanan abin ya samu muhasim yayana ke fama da mumunan hawan jini har tsoro nake Kar watarana ya Yanke jiki ya fadi,Banda kudaden da yake kashewa wajen nemawa muhasim magani Ashe duk mijina shi ya jefa yarsa a masifa na tuna lokacin da muka je bauchi duba ta dan bana wata biyu banje ba a ranar na matsawa Salis muka je

Koda mu kaje kin Shiga d'akin da muhasim take yayi duk yanda akayi dashi ya shiga yak'i sai da mahaifiyata ta masa dagaske ya Shiga,sai a yanzu na gano dalilin dayasa Muhasim na ganinsa ta hau zubar hawaye shi kuwa ya sunkuyar da Kai Yana kwarara Mata Addu'a ita kuwa da ido kawai ta ringa binsa ni kuwa na ruko hannunta Ina "Zaki samu lafiya muhasim insha Allahu Uncle Yana ta k'ok'ari wajen nema miki lafiya kinji"

Wlh bantab'a zarginsa ba dan nayi haka tamkar nayi sabo ne ma taya zai nemi Yar cikinsa.

A zaunen da nake akan sallaya tunanin baya kawai nake tunanin daya fadomin yasa na mike tamkar iska zai d'aukeni na nufi d'akin Luba a Karo na farko a rayuwata da nasan Zan shiga dakinta akwai tambayoyin da nake so na mata tunda har tasan shi yayi wa muhasim
Fyade dole zata san Mai yayiwa muhasim ya karkata mata wuya.

A rabe na ganta a gefen gado da alama kuka takeyi Ina tura k'ofar ta mike a firgice sai naji yanzu bana Jin zafinta wlh wanan nauyin da nake ji a kirjina a duk lokacin da naganta na auremin miji da tayi duk sai naji babu.

Koda na isa d'akin zama nayi nima a gefen gadon ban kalleta ba nace "Fada min komai Luba fada min sirrikan Salisu da bansani ba tunda har kika san shi yayi wa muhasim fyade duk tsawon lokacin nan Luba baki tab'a nuna min ko a fuska ba ashe kallon shasha kike min hada Kai kikayi da salisu kuka cutar dani,iya auren cin amanar da kukayi bai isheku ba sai Kun hada kai kun cutar da yata Luba ya akayi Salisu ya karkatawa muhasim baki ki fadamin komai dan Sunanki bazai fito a shigar da karar da zanyi ba

Luba ido ta zubawa Aisha tana tunanin abinda ya dace ta fada mata a yanzu babban tashin hankalin ta rabuwa da Salis Wanda tasan wanan dole ne sai sun rabu dan haka itama zatayi duk abinda zatayi dan taga Aisha ta rabu da Salis zata Kara shafa masa bakin fenti yanda Aisha zata tsanesa gwara duk ayi biyu babu

"Kinyi shiru luba ki fadamin"

"Hmmm akwai Abubuwan da nasan idan na fada miki wlh Zaki iya yanke jiki ki fadi ba Wai iya fyade da karkatawa Muhasim Kai Alhaji Salis yayi ba da ace zaki san abinda yake aikatawa da baki zauna dashi tsawon lokacin nan ba da tuni kin Dade da rabuwa dashi dabiunsa ba masu kyau bane ko ni da Kika ga na aureshi domin biyan bukatar kaina ne bawai dan Ina sansa ba"

Tunda ta fara magana na zuba mata ido Ina kallonta kirjina wani irin bugawa yake "Kina nufin Salisu shi ya karkatawa muhasim kai da Baki"?

"Kwarai kuwa shine Kuma yana neman maza ma Salisu fasiki ne mazinaci idan har patient suka je wajen sa tsautsayi yasa yaga jikinsu sai ya kwanta dasu"

"Ya isa haka luba koma dan yankan kaine ba abinda ya shafeni ki shirya zaki min shaida a kotu"

Da sauri Luba ta mik'e cikin tashin hankali tana "Ba ruwana Aisha karki sake ki sa sunana"

Luba sai mun hadu a kotu
Na mik'e Ina Jin jiri na dib'ana Ina koma wa d'aki na janyo akwatina na fara had'a kayana.

Hayaniyar da naji a waje yasa na dan dakata da hada kayan muryar Alhaji Salis nake jiyowa da alama shi da Luba ne

"Ki fita ki bar min gida wlh ko tsinke bazaki dauka ba shegiya tsinanniya"

Alhaji salis yace Yana jan Luba dake tirjewa akan ya barta ta d'auki akwatinta da mukulin motarta

Alhaji Salis sai da ya kai ta har waje yana "nayi freezing acct dinki,na kwace motata kayan naki ma da kudina na siya filayen da kika siya da duk wata kaddara da kike takamar kina dashi na kwace sai da na fada miki idan kika tona min asiri sai naki ya tonu Luba yanda Kika dandana min bakin ciki wlh sai na dandana miki fiye da yanda Kika dandana min shegiya tsinanniya"

Luba bata iya magana ba har ya shige ta dora hannunta a ka tare da bin jikinta da kallo tanadin da tayi na duk ranar da Salis ya saketa ma bazata yi talauci ba sabida kudin da take dashi da filaye sai gashi Salis ya kwace kudin acct dinta kuwa Allah kadai yasan yawan sa dan idan tsiyarta ta motsa tatsar shi kawai take tana ya bata ko ta tona Masa asiri take zai d'auko kudin ya bata ko nawane sai gashi lokaci guda duk shekarar da ta d'auka tana tara dukiya tamkar d'aukewar ruwa Alhaji Salis ya kwace.

Ta fara bin kantamemen gidan da kallo da babu irinsa a unguwar shikenan tayi bankwana da gidan taya ma zata fara zawarci da girmanta a kuma gidan iyayenta da baifi daki biyu ba san abin duniya yasa bata iya canza musu gida ba ji take Kamar ta fasa ihu dan bakin ciki tuna ta riga da ta raba ma Aisha da Salis yasa ta fara Jin sanyi a zuciyarta tasan bayan duk maganaganun da tayi wa Aisha ba abinda zai saka ta Kara Zama dashi sai sun rabu.

Dak'yar taja kafarta ta nufi gidan Asabe ita kadai ce zata iya taimaka Mata ko da akwai aikin da zaayi akan Salis ya dawo da ita.

Alhaji Salis

Yana komawa ciki yayi kicibis da Aneesa a bakin k'ofa tana Jan akwatin ta

Wani sabon zazzabi yaji yana neman rufeshi a gajiye yace "Ina zaki Aneesa"?

"Abuja zan tafi na gaji da wanan auren tunda na aureka daga wanan masifar sai wanan ban taba samun kwanciyar hankali ba wlh nagaji ka sakeni kawai dan bazan iya ba"

Aneesa tace tana share hawayen dake zubo mata

"Baby kece yau kike cewa na sakeki"?

"Kirani Aneesa Alhaji bansan haka aurenka zai zame min ba dama mummy ta fadamin na dage sai na aureka bansan Ashe wanan tashin hankalin ta hango min ba Ashe har wata ma kayiwa ciki har da su ya wlh bazan iya ba ka sakeni kawai na tafi"

Alhaji Salis da ke jin kansa Kamar ya rabe gida biyu ya hau Jan "innalillahi wa Inna ilaihi rajiun Allahuma ajirni fi musibati wa aklifnin khairin minha"

Jikinsa rawa kawai yake bai iya dakatar da Aneesa dake cewa ya Aiko Mata da takardar sakinta ba har ta fice.

Muryar Afrah dake kuka yasa yayi saurin waigawa Aisha ce janye da akwatinta hannunta cikin na Nana Afrah Kuma ta rik'e akwatin tana magiya Aliyu da Ashraf na tsaye Suma da alama rokonta suke.

A daidai lokacin da Hindatu ta fito daga dakinta tana "Ikon Allah yau Kuma a haka muka tashi Luba dai ta hargitsa gida Amarya ta tafi ga Hajiya itama zata tafi innalillahi wa Inna ilaihi rajiun

"Ki cika min akwati Afrah ki cika min nace Miki"

"Dan Allah hajiya umma ki rufa mana asiri karki tafi"

"Wlh sai na tafi banga mai hanani ba Kuna da hankali kuwa taya Zan zauna da azzalumun da ya cutar da Yar yayana wlh sai na yi kararsa an bi mata hakkinta "

Aisha tace cikin ihun kuka tare da fusge akwatin ta Ashraf na Shirin magana tace "Duk Wanda ya Kara cewa na zauna wlh sai na masa baki ku kyalleni"

Ta nufi bakin k'ofa Alhaji Salis ya zub'e a kasa Yana k'ok'arin rokonta ta tureshi tana "Wlh wlh sai nayi kararka"

"Idan kikayi haka Aisha kin tozarta yaranki zaki shafa musu bakin fenti"

ko kallonsa batayi ba tayi waje

Alhaji Salis ya runtsa idonsa ya tafi tunanin lokacin da rayuwarsa ta fara tarwatsewa...

Posting Monday to Friday nayi ne yau sabida jiya na Dora cigaba yanzu sai Monday insha Allahu

Naceba♀
Kina bukatan jikinki yazama so fresh ba kwarzane ko daya ballantana kuraje ko tabo, sunburn,acne, ko knuckles? Kije kigwada products na mg's insha Allah zakiga ynd fatarki zedawo fiye da tsammaninki zakigyara jikinki naturally batare da kinbata fatarki ba jikinki yayi fresh kiyi smooth kizama kalar Madara kirar models kiringa walwali kina haskawa duk inda kikayi😍
Kidena kokonto cewa kingwada baki Dace ba insha Allah kijaraba products dinsu bi'iznillah zakiji dadinshi kayansu akwai kamshi especially sabulun kamshin yakama jikinki ko kindade da wanka jikinki zaidinga fidda ni'imtaccen kamshi bayinki ma zakiji kamshin dazai Kama😍sunada kit special domin amare Wanda indai kinyi using kit dinnan Baki bukatar kikara Kai kudinki gurin dilke domin ainihin yanda fatarki zehaska yagoge kidinga shining abun sewanda yagani😍

Mai bukatar kayan mg's chat:08062991549,07046881166,07067210195
Call:08064532391
Hausawa nacewa adade anayi sai gaskiya Kuma siyan nagari maida kudi gida
 tested nd trusted
Natural/organic

INGANTACCEN MAGANIN SANYI TOILET INFECTION MAI WANKO DUK DATTIN MARA KOWANI IRIN SANYI NE ZAI MAGANCE SHI DAYARDAR ALLAH SHIN KINAFAMA DA RASHIN SHA AWA? RASHIN NI IMA RASHIN GAMSUWA SHIN KINYI SHEKARA DA SHEKARU KINA NEMAN HAIHUWA RIKICEWAR JINI CIWON JIKI CIWON MARA YAYIN AL ADA DUKA WANNAN MAGANIN YANA WARKARWA ME CIKI BATA SHAN MAGANIN SANYI NA 4K YAKE INA KATSINA INA AIKAWA KO INA A FADIN KASAR NAN HARDA KETARE MAZA DA MATA MAGANIN SANYI MAI GYARA MU AMALAR AURE AUNTY ZEE MOM MUJAHID
08162859027
KATSINA

WANAN LITTAFIN NA KUDINE BIYA 500 TA WANAN ACCT 0272061655 WEMA BANK NAFISA NUHU KO KATIN MTN KO AIRTEL TA WANAN LAYIN 08033719070 DOMIN KI MALLAKI NAKI KI MUTANEN NIGER TA KUMA KU TUNTUBI WANAN LAYIN
+227 96 82 89 84 DUK WACCE TA MIN SHARING NA BAR TA DA *RABBI ZAI FIDDA MIN HAKKINA DA IZININ ALLAH DOMIN BA YAFEWA NAYI BA*

Waiwaiye

Alhaji Salis

A rayuwarsa ba wacce ya tsana Kamar Luba kawar Aisha halayen ta na san abun duniya yasa yaji ya matukar tsanarta amma ganin Farin cikin Aisha shine taga tana mu'amalla da Luba yasa ya danne tsanar da yake mata dan ya farantawa Aisha rai,ransa ya b'aci a lokacin da ya gano uban kudin da yake kashewa Aisha a siya mata sutura Ashe Luba take bawa Inda hakan yasa ranar da ya gano ya rufe ido yaci mutunci Luba a ransa Yana tunanin indai da zuciya a kirjinta dole tayi zuciya ta rabu da Aisha.

Sai dai yanda Aisha ta hana kanta walwala ta karfi da yaji har abin na Neman shafarsa yasa ya hakura yace ta cigaba da muamalla da ita.

Dama can ba wani abu dake hadasu sai gaisuwa kafin aurenta ne ma da lokacin da take da Aure suke dan gaisuwar mutunci idan ta kama su tsokani juna idan ta same shi a gida.

Abinda ya fara daure masa kai bai wuce salon da ta bullo masa dashi ba a bayan ya mata rashin mutunci ta cirewa Aisha kayanta ya d'auka ko a hanya ta ganshi ko gaishe shi bazata yi ba ga mamakinsa wata daya a tsakani ranar ya dawo daga wajen aiki a gajiye yaci abinci kenan Aisha na dan mamatsa kafarsa da yaji na masa ciwo yaro ya kwada sallama a tsakar gida wai ana sallama dashi a waje iya saninsa ba wanda suka yi zai zo nemansa har ya ce yaron yaje ya tambayo mai sallama dashi Aisha tace yaje mana kawai yaga mai sallama dashi

Haka kuwa akayi ya fita waje dan ya duba mai sallama dashi

Sai dai ko da ya fita bai ga mai sallama dashi ba hasali mace ya hango nesa da gidan ta saka doguwar riga yana k'ok'arin komawa ciki yaji an Kira sunansa Inda yaji Kiran sunan nasa ya kalla yaga wajen da macen ke tsaye ne cikin mamaki ya nufi wajen da take a tsaye a ransa Yana mamakin wacce wanan

"Kece kike kirana"?

Salis yace cikin mamakin ganin Luba a tsaye

Ta sakar masa murmushi tana ""ee ni nake kiranka"

"Yaushe gidan ya zama bakonki Kuma dama idan Kika zo a waje kike tsayawa Kuma wajena kike zuwa da zaki aika a kirani"?

"Aa gidan ba bakona bane kam ba wajen Aisha nazo ba wajenka nazo shiyasa na aika a Kiraka"

"Ikon Allah toh lafiya"?

Sai ta fara susune kai Salis mamaki yasa yace "Wai kanki kalau kuwa ko Zawarci yasa kin haukace ne mai haka"?

"Hmm Salis kenan kai a rayuwarka kanaso kaga kana cin mutunci na yanzu dan na aika a Kiraka laifine gaisawa kawai zamu yi dama banaso na Shiga ciki sabida dare yayi"

Salis tsananin mamaki yasa yama kasa yiwa Luba dake ta wani karkade karkade magana

"Wai mai kake ta kallona ne"?

"Daga yau karki sake ki Kara min irin wanan haukar ana zaune kalau zaki aika a kirani mai hadina da ke zaki ce gaisawa kawai zamuyi dake Aisha ce kawarki banida hadi dake da wanan zubar da mutuncinki da kike yi da ma wajen uban yayan ki Kika koma ko Kika sake wani auren da yawon bin gidajen mutane da kikeyi kina aron kayan mutane kina sawa"

"Banida mijin Auren ai Salis shiyasa banyi ba ko zaka taimaka ka nemo min namiji mai irin sunan ka mai irin komai naka dai"

Salis tsabar takaici bai kara mata magana ba yaja tsaki tare da nufar cikin gidan ya shige yana mamakin abinda Luba tayi da ya kasa gane mai hakan ke nufi

Koda ya shiga bai damu da ya fadawa Aisha ba dan yasan ko ya fada mata ma ba jawa Luba kunne zatayi ba tunda bata san abinda zai hadasu.

A yau Yana zaune a office wata Zainab ta budo kofar ta shigo kawarsa ce Kuma tsohuwar budurwarsa da suka had'u a kasar waje haduwar sa da ita a waje ta koya masa mumanan dabiu rashin mata a kusa yasa ya fara biyeta suna watsewa ita ta kwadaita masa san yaji yana san ya ringa sanin taste din mata daban daban ta kara da dora shi akan wani harka dake mugun shigo masa da kudi mumunan dabiar da ya koya a waje Kuma sirrinsa da bayaso kowa ya taba sani,har ya kusa gama abinda ya Kai shi can Yana tare da Zainab ba Kuma iya zainab din ba yana neman wasu ma,

ganowar da Zainab tayi Yana tsalle tsallen yasa suke yi wani irin fada gata da tsananin kishi duk a tunanin ta bashida aure ta Kuma d'auka zai Aureta din.

Sai da ya kusa dawowa Nigeria ya fito ya fada mata yana da Aure bazai iya aurenta ba.

Kaca kaca suka yi da ita har ya dawo gida Nigeria da kudurin tunda ya dawo wajen iyalinsa zai ajiye wanan halin nasa cikin kudura ta ubangiji Kuma tunda ya dawo bai Kara Neman kowace mace ba duk da wani zubin idan patience masu larurar da zai ga jikinsu idan yagani yakan ji Kamar ya koma ruwa sai ya danne.

Ido ya zubawa zainab din har ta zauna kasan ransa Kuma mamaki yanda akayi ta shigo Nigeria har tasan office dinsa.

Sai da ta zauna ta sakar Masa murmushi tana yayi mamakin ganinta ko

Murmushi ya maida mata yana aa baiyi mamaki ba ya sa aka kawo Mata lemo,suka hau hira,har a cikin hirarsu take fada masa yanda tayi kewarsa ta hau masa magana da jikinta.

Zainab tasan kansa take yaji bazai iya jurewa ba Koda ta zaga wajen da yake zaune suka kaiwa juna cafka.

K'ofar da aka turo yasa suka saki juna da sauri

Hankalin Alhajj Salis yayi mugun tashi da ganin Luba a tsaye taci kwalliya Kamar zata je biki da alama itama mamakin yanda ta gansu ne ya daskarar da ita.

Zainab kuwa ta gyara rigarta cikin turanci tace mata bata iya knocking bane kafin ta shigo ya zata fado kai tsaye baa bata izini ba"

Alhaji Salis dai kunya yasa yaji kamar an like Masa baki tamkar Aisha ce ta Kamashi haka yaji.

Luba kuwa ta watsawa zainab harara ta samu waje ta zauna

Salis ya ce mata lafiya mai tazo nema a office dinsa"?

"Hmm ashe dai haka ake cin amanar kawata wanan Kuma wacece?

"Luba mai kikazo nema a office dina Ina ruwanki da koma wacce mai hadina dake wai kika takura min kwana biyu"?

"Ka sallameta magana zamu yi"

"Ke din banza da zaki saka na sallami wata dalla tashi ki barmin office"

"Hmmm Salisu kenan wlh daga nan gidanka nayi sai na fadawa Aisha abinda kake aikatawa kaji na rantse maka"

"Kin dade baki fada ba dalla fita kibani waje"

Luba mik'ewa tayi tana "zaka kuwa gani wlh sai na fada

Ta fice daga office din sai Salis yaji Kuma hankalinsa ya tashi yabi bayanta da sauri.

Da gudu ya cimmata sabida saurin da take ta zubawa ya sha gabanta Yana "Dakata Luba ba abinda kike tunani bane karki je ki hadani da Aisha Mai kika zo nema"?

"Ai da baka fito ba wlh sai naje na sameta na fada mata"?

"Toh na fito ba sai kinje ba ya akayi"?

"Aure nakeso nayi Salisu nagaji da zaman haka ba Aure"

Yamutsa fuska Salisu yayi Yana "Toh idan kina san auren Ina ruwana ko wani taimakon kike so ayi miki ai da kin fadawa Aisha ba sai kinzo wajena ba"

"Kai kafi cancanta nazo wajenka ai neman taimakon a gaskiya na gaji ma da kumbiya kumbiya Salisu na kamu da sanka nasan zakaji banbarkwai sabida Aisha kawata ce naso na daure amma wlh na kasa"

"Luba a cikin hayyacin ki kike kuwa ko kina Shan kwayane"?

Ni salisu mijin kawar ki kike so"?

"Toh Ina so yasan wani kawance Salisu ai ba ruwan so da wanan ni yarda kawai nake nema nasan Aisha nada saukin Kai indai na fada mata bazata damu ba zata fahimceni"

"Lailai bansan baki da hankali da tunani ba sai yau ke ko a mafarki akace miki zan aureki sai ki yarda Luba duk matan duniya na rasa wacce zan aura sai ke yanzu ko nine nazo nace Ina sanki dan Allah sai ki yarda bayan kinsan yanda kike da Aisha? dama haka kike? san abun duniyar naki ya Kai har haka?yanzu zaki iya cin amanar Aisha"

"Salisu wai me abin cin Amana anan matsawar a musulunce ba haramun bane ai ba laifi bane dan kawaye sun auri miji daya"

"Aisha batayi dacen kawa ba idan na koma gida dole na fada mata wacce ke dole na fada mata tasan irin zaman da zatayi dake"

"Ai kafin ka fada mata zanje gida na sanar mata abinda kake aikatawa kai ma dole na fada mata yanda kake cin amanarta babu kunya babu tsoron Allah"

"Kije ki fada mata kin Dade baki fada ba ai karshen kawancen ku yazo wuyanta na fada Mata"

Luba bata Kara ce dashi komai ba ta dau hanya ta tafi.

Salisu da mamakin zancen da Luba tazo Masa dashi ya koma gida ko zainab ma bata Kara gane kansa ba har suka rabu akan zasu had'u a masaukinta.

Yana komawa gida bayan yaci abinci a madadin ya fito ya fadawa Aisha abinda ya faru sai ce mata yayi "Aisha yanzu idan nace ki rabu da Luba sai kiji haushina ko"?

Take fara'ar fuskarta ta gushe tana "Mai ya faru Kuma Abban Ashraf"?

"Aisha Luba ba matuniyar arziki bace ba ki rabu da ita yanda kika d'auketa wlh ba haka ta d'auke ki ba na dade Ina fada miki jinina bai d'auketa ba ki rabu da ita Aisha"

"Wai wani abin Luba tayi dan Allah mai yasa ka tsani Luba Abban Ashraf na rasa mai ta ma nidai dan Allah Abban Ashraf karka rabamu dan Allah idan ma wani abu tama kayi hakuri yanzu kana raba mu zata ce sabida mun ga mun yi kudi mu ke so mu wulakanta ta ka ga hakan bai dace ba kar ka manta tun kafin na san zan hadu da kai nake tare da ita"

"Hmm Aisha kenan tunda kin dage toh shikenan Ina jiye miki ranar da zaki yi nadamar saninta a rayuwarki ne shi yasa nake so ki rabu da ita tun yanzu"

"Babu ma ranar Abban Ashraf dan ka tsaneta ne kawai bansan Kuma mai ta maka haka da zafi ba wlh bata kara aron kayana ba"

"Hmmm Ai shikenan"

Dama yasan za'ayi haka bazata tab'a yarda ba haka ne yasa ya kyalleta dan yasan ko fada mata yayi ba yarda zata yi ba"

A haka Luba ta cigaba da masa naci ta ringa ziryar daga office dinsa shi kuwa ya bud'e mata wuta wajen yi mata rashin mutunci ko Kare bazai dauki wulakanci da yake mata ba inda ya Kara jinjinawa fuska biyun da take dashi idan suka hadu a gidansa bata nuna masa komai.

A haka suka fara Shirin komawa sabon gidansa.

LUBA

Daga lokacin da Salisu ya mata Rashin mutunci ta kudurta a ranta samo miji Wanda yafi salisu yanda zata rama duk wulakanci da yayi mata idan zata samu ma ta Wanda ya dameshi a kudi har da zai ma iya daure Salis din.

Sai dai duk san ta samu mai kudin duk masu zuwa wajenta basu kamo kafarsa ba.

Ba abinda ya Kara rikita mata lissafi irin tsalallen gidan da yake gwangwaje Aisha dashi da ita gidan ma baya gabanta sau tari idan ta kwanta haka zatayi ta mafarki da gidan idan ta tashi tunanin irin gidan da za'a kai ta sai ta tuno gidan Salisu da yake ginawa duk haduwar gidan wai Aisha kawarta da kyale kyale bai dama ba ita zaa Kai,yanzu ta koma gidanan ta kara Zama hajiya ga suturu.masu tsada ga miji mai kyau wai dame ma Aisha ta fita da ita ta kasa samun irin Salis.

Gashi duk san ta samu Wanda ya kai Salis din kudi ta kasa samu ci baya ne agareta ace ta auri Wanda bai dame Hamza a kudi ba ci baya ne a gareta ace aurenta na farko bata dace na na biyun ma haka kenan haka Aisha zatayi ta kere mata tana binta gidanta.

"Mai zai hana itama ta Auri Salisun ta dandana arziki itama"

Tunanin nan da tayi ya sata mik'ewa zaune dan a kwance take ba wanda zata samu irin daular da take mafarki sama da Salisu mijin Aisha kawarta Aisha sanyin halinta

yayi yawa da take ganin Sam bata da wayo daga lokacin da take iya d'aukar sabon Kaya ta bata batare da ta saka ba ta jinjina rashin wayonta tasan idan ma tace mata tana san Salisun ta tsarata zata iya yarda,abu dayane tasan sai tayi da gaske Salisu zai saurareta dan taga daga lokacin da ta kashe aurenta ya fita sabgarta yake mata wani gani gani da kuwa ya mata wanan rashin mutunci ta lura ko ganinta bayaso yayi,tsanarta ma take hangowa a idonsa idan taje gidan dak'yar yake amsa gaisuwar ta.

Amma haka zata fara cusa kanta a wajensa kila ta samu wataran ya saurareta daga lokacin da ta fara wanan tunanin ta daina kula samarinta ta kara raina abinda suke dashi,a yanzu yanda zata auri Salisu kawai shine burinta zata yi duk yanda zata yi ta Aureshi,ta lura Salis nasan gayu tunda yake gwangwaje Aisha da kayayyaki masu tsada sai dai ita Aisha gabad'aya bata dorawa kanta wanan gayun ba barta da tsafta Kamar me zaka ganta tsaf amma shafa hoda ma wahala yake mata a haka Luba taci kwalliya daddare ta nufi gidansu Salisu A ta aika ayi mata sallama dashi kamar yanda ta tsammata hakan ce ta faru dan rashin mutunci ya mata ta kudurta a ranta zata ringa jurewa kila watarana a dace a daya barin Kuma ta ringa Shiga jikin Aisha tana sanin duk halin da take ciki a gidanta kayane dai ta daina ara dan tasan nan da wani lokaci idan tayi hakurin watarana zata zama tamkar Aisha ko finta ma,a haka su Aisha Suka fara shirin komawa gidan da take mafarkin samu ji take dama itace sai taji ta Kara matsuwa taji wataran itama ta mallaki gidan.

Tsananin San gidan yasa a ranar da suka tare itama tace sai ta kwana ba karamin hidima akayi a tariyar ba ba inda bata Shiga ba a gidan sama daya kasance bangaren Salis ne kawai bata samu shiga ba tsaruwar gidan ya kara kwadaita mata San Aurensa.

Bayan waleema tariyar gidan wasu sun tafi dangin Aisha wasu kuma suka ce kwana zasuyi

Aisha kuwa kamar ta bi kowa ta goya dan murnar kwanan da suka ce zatayi ita kuwa Luba a hankali ta ringa karantar komai na gidan karfe tara Salis ya dawo gidan cikin shigar sa ta golden din shadda sai bulbula kamshi yake Kamar wani ango

Luba sai ta kasa d'auke idonta a kansa har sai da su ka hada ido dashi ya dalla mata wani mugun harara ya haye sama yaran Suka bishi gabad'aya ciki kuwa har da Zainab da Muhasim.

Luba a zaune kawai take a cikin su Aisha dake ta zabga hira amma hankalinta na Sama wajen Salis.

A hirar da Aisha take yi taji wai a cikin Yan uwan ta zata kwana har suna tambayarta yanzu Salis zata bari ya kwana shi kadai tace iya yau dai zata kwana cikinsu.

Luba ji tayi wani dadi ya rufeta Kamar tasan hakan zai kasance tazo da shirinta.

Sai ta koma palo tayi zamanta Kamar kallo take, burinta Salis ya fada tarkonta.

Wajen goma taga yaran suna saukowa da gudu Aliyu na "Abba ya koro mu yace muje mu kwanta mun dameshi"

"Ai gwara da ya koro ku bakwa ji"

Cewar Aisha a daidai lokacin da take cewa su wuce dakinsu su kwanta

Muhasim Kuma tace Wai yace ta bashi ruwa a kai masa na saman ba sanyi"

Aisha tace taje Kitchen ta d'auko masa

Luba ta d'auke kunnenta tamkar duk batasan mai ake ba ganin muhasim ita kadai tayi kitchen din yasa ta mik'e ta bita a daidai lokacin da ta muhasim ta sunkuya dan ta d'auko ruwan

Luba tace "ke zaki kai Masa ruwan ne"

"Eee haka yace na kai.masa ya Sha idan mun karasa home work din sai muje mu kwanta"

"Oo home work kuke yi"?

"Eee"

To bari na nemo.miki kofi ki zuba Masa Kinga kin hutashe shi

Ta d'auko kofi ta juya mata baya tare da jefa maganin da tazo dashi a ciki ta daga ruwan ta juye sai da ta tabbatar ya narke ta juyo ta mikawa muhasim tana "Maza jeki kai masa ki tafi da ragowar ko zai Kara"

Muhasim cikin ladabi ta karba ta fita.

Luba tayi sauri ta fito ta zauna a palon a daidai lokacin da Aisha ta fito daga dakinta tana "Kawata bakya Jin baccine Kinga yanda idona ke yaji sabida baccin da nake ji"

"Tab wane irin bacci ana zaune kalau ke ki tare a irin wanan gidan ki iya bacci ai idan nice bazan iya bacci ba wlh"

"Kashh kijiki dan Allah mai zai hana ni bacci kuwa tab"

"Aikuwa bana Jin bacci kallo ma zanyi gwara na Danna gidan yan gayu"

Aisha ta kyalkyale da dariya

"Yanzu sama zaki hau kenan a sha soyaya"

"Aa haba Luba ai sai su Aunty suga rashin kunyata yau dai ai shima yace na kwana cikin Yan uwana naji dadi yanzu haka ma sun yi baccin ma shiyasa nima nake Jin baccin kizo muje mu kwanta ki hakura da kallon nan gobe ba sai kiyi kallon ba"

"Aa kije kiyi kwanciyarki mallama"

"Toh ai shikenan bari na koro yaran nan su barshi yayi baccin shima basa tashi home work sai daddare mutum ya dawo a gajiye su dameshi"

Ta nufi stairs Luba duk sai hankalinta ya tashi tana tsoron taje ya hanata dawowa dan tasan kwayar na iya masa aiki a kowane lokaci.

Sai dai tana hawa ta sauko ita da Khadija tana "nidai na tafi na kwanta kawata sai kin shigo wancan mai rubutun Yan koyon har yanzu ta kasa gamawa.

Ta shige dakinta.

Minti goma a tsakani Luba ta hawa sama cikin sanda dak'yar ta gane d'akin Salis din sabida dakuna wajen hud'u ne sauran a rufe nashi Kuma a dan bud'e

Burinta Muhasim ta fito daga d'akin a hankali ta tsaya a bakin k'ofa ta hau lekasu.

Muhasim.na zaune a kasa tana ta rubutu Salis shi Kuma Yana saman kujera ya dafe kansa kafafunsa a harde

Tafi minti Ashirin tana leke kafin ta ga muhasim ta mike tsaye tana "uncle na gama"

Tana k'ok'arin yin waje Salis ya bude idonsa da suka kada Suka yi ja ya yafito muhasim din akan tazo.

Luba ta dafe kirjinta tare da gwalo ido.

Muhasim na zuwa bai yi wata wata ba ya jawota ya hau matseta dan lokacin da na shanunta tunda tana da Sha shidda lokacin.

"Uncle ka cikani uncle"

Muhasim tace tana k'ok'arin kwatar kanta luba kuwa cikin tashin hankali ta fada d'akin tare da Kiran sunan Salis.....

WANAN LITTAFIN NA KUDINE BIYA 500 TA WANAN ACCT 0272061655 WEMA BANK NAFISA NUHU KO KATIN MTN KO AIRTEL TA WANAN LAYIN 08033719070 DOMIN KI MALLAKI NAKI KI MUTANEN NIGER KUMA KU TUNTUBI WANAN LAYIN
+227 96 82 89 84 DUK WACCE TA MIN SHARING NA BAR TA DA *RABBI ZAI FIDDA MIN HAKKI NA DA IZININ ALLAH DOMIN BA YAFEWA NAYI BA*

NI DA KISHIYOYINA

NA SADNAF

PAGE 19

Luba nesa da office d'in Salis ta tsaya taga shigar muhasim office din tasan security da ke kusa da wajen bazasu tab'a barinta ta Shiga ko ta tsaya kusa da bakin k'ofar office din ba ji take kamar tayi tsuntsuwa ta Shiga tana ta mamakin mai muhasim tazo yi a office din Salis din ya zama dole ta gano mai ta zo yi a office din ita kadai ta Kuma san ba aikota akayi ba tunda uniform din islamiya ne a jikinta kasa Hakuri tayi ta nufi office din nasa,tun kafin ta karasa security suka nufota dan suna benci a zaune.

Kasa tayi da murya tana "Ba Shiga zanyi ba a bakin office din Zan zauna zan jira wata kanwata"

Suka girgiza Mata Kai akan basu yarda ta Shiga ba kamar ta fasa ihu haka ta ringa ji sai take ganin kamar Salis ma wani abu suke yi da muhasim din,anya kuwa ba abinda ya Shiga tsakanin Salis da muhasim.

Baa san ranta ba ta koma wajen da take zaune ta zauna tare da zurawa office din ido burinta ta ga fitowar muhasim ta bugi cikinta.

Salis

Yana cikin rubutawa wata patient magangunan da zata siyo muhasim ta turo k'ofar tare da sallama.

Salis ya saki biron hannunsa a lokacin da yayi tozali da ita gabansa har faduwa sai da yayi takarda hannunsa ya mik'awa patient din Yana zata iya tafiya muhasim kuwa na tsaye kanta a sunkuye hawayen dake k'ok'arin zubo mata take tasan maidawa.

Salis mik'ewa yayi a lokacin da yaga patient din ta fita ya nufi wajen da take tsaye Yana "Muhasim lafiya kuwa Mai ya faru"?

Kukan da take dannewa ya kwace Mata ta sunkuya a wajen Salis hankali a tashe ya karasa wajenta Yana k'ok'arin kamo hannunta ta ja da baya da sauri tana "Karka tab'a ni"

janye hannunsa yayi da sauri yana "Yi hakuri daina kuka ki fadamin abinda ke faruwa"

"Wata biyu kenan ban ga period dina ba sai yau da mallamin yake koya Mana menstrual cycle na gane idan aka daina ganinsa cikine da mutum ciki na haihu uncle Kuma sai namiji ya tab'a mace take iya samun ciki Kuma uncle Kai ne ka tab'ani"

"Innalillahi wa Inna ilaihi rajiun innalillahi wa Inna ilaihi rajiun muhasim ciki ne dake kike nufi"?

Kuka muhasim ta Kara rushewa dashi da ta ga yanda hankalin Salis ya tashi

"Baza ki tab'a samun ciki ba insha Allahu kiyi shiru ki daina kuka bari na zo na miki test kinji bakida komai dan Allah ki daina kuka kiyi shiru

Salis ya mike da sauri ya fito daga office din ya nufi lab dan ya d'auko tsinken gwaji hankalinsa idan yayi dubu sai daya tashi taya muhasim zata samu ciki

Addua kawai yake Allah yasa ba cikin ne da ita ba dan idan shine dole ya zubar mata dashi tsawon rayuwarsa bai tab'a tsintar kansa a tashin hankali haka ba sai da ya nemi muhasim kullum abin na ransa taya tashin hankalin neman ta bai gama sakinsa ba Kuma wani sabon tashin hankali zai Kara b'ullo masa

Luba kuwa akan idonta ya fito daga office din tayi sauri ta b'uya sabida Kar ya ganta yanda ta ganshi a hargitse yasa ta kara tabbatar wa kanta akwai abinda ke faruwa.

Ba jimawa taga ya dawo ya Kara Shiga office din hannun sa rike da Abubuwan da batasan ko menene ba.

Salis na shiga office din ya nufi wajen muhasim Yana tashi ki shiga bandaki kiyi fitsari anan ki kawo min

Kuka Muhasim ta cigaba da yi a dan tsawace yace "Dan Allah ki bar min kukan nan Mana Kara daga min hankali kike kije kiyi fitsari ki kawo min kiyi sauri"

Muhasim mik'ewa tayi tare da karbar robar a hannunsa ta shige bandakin tayi fitsarin a ciki ta kawo masa.

Hannunsa har rawa yake wajen karba ya zura tsinken gwajin a ciki ya cire ya ajiye sai safa da marwa yake Yana goge gumin fuskarsa addu'a kawai yake Allah yasa ba cikin ne da ita ba duk da yasan indai period ya d'auke da wuya idan ba ciki bane.

Bayan minti goma ya juyo kirjinsa na dukan tara tara ya dauki tsinken gwajin yaga layi biyu baro baro ya saki tsinken gwajin tare da kwada sallati da k'arfi

Muhasim cikin kuka tace "Cikin ne dani ko uncle shikenan rayuwata ta kare Ina Yar yarinyata dani na samu ciki yanzu mai zancewa Abba da mummy ko saurayi Abba baya bari mu kula wa Zan ce ya min cikin"?

"Yi shiru muhasim ba Wanda zai tab'a sanin kinyi ciki zubar miki dashi zanyi"

Wani irin ja baya tayi tana "ban shirya mutuwa ba uncle zuwaira Yar bayan layinmu kowa yasan ciki ta zubar ta mutu"

"Ba zaki mutu ba muhasim kinsan ni likita ne nasan allurar da zan miki bazaki mutu ba idan baki bari na zubar miki ba ai sai kowa yasan kina da ciki sai asirina ya tonu kinsan Kuma ba'a san raina na tab'a ki ba"

Cikin ihun kuka muhasim ta fara "Wlh banaso na mutu uncle mutuwa akeyi idan aka je zubar da ciki gwara kawai na bar cikin idan yaso sai nace bansan Wanda yamin ba uncle duk Kai ka jawomin ko zance baa barin mu muyi ko saurayi bani dashi uncle kazo ka tab'ani yanzu na samu ciki nidai bazan iya zubar wa ba bana so na mutu uncle"

Kuka take sosai
Salis duk ta rudashi ya rasa yanda zaiyi da ita Yana so ya rufe mata baki ma kar ta jawo hankalin masu wucewa ta saka masa ihun Kar ya tab'ata ya dafe kansa Yana sallati wlh ji yake kamar shima yayi zaman dirshan yayi ta kuka, kuskure daya tak,Jin dadin mintuna rashin hakurin awani ya jawo mai wanan masifa barin cikin nan na nufin tonan asirinsa kamar shi ace shi yayi wa muhasim fyade ta samu ciki,muhasim yar yayan matarsa abin yayi muni yasan muhasim zata iya rufa masa asiri taki fadan wanda ya mata ciki amma yasan zata sha matsar da har sai ta fadi gaskiya.

Kansa har ciwo yaji yana Masa ya zubawa muhasim Ido da idannunta duk sukayi luhu luhu wani irin tausayinta yake ji yasan ya cutar da raywuarta na har abada ya mata tabon da bazata manta dashi ba.

Kamar shima zaiyi kukan yace "muhasim kiyi shiru dan Allah kina ji wlh wlh bazaki mutu ba idan na miki allura na baki magani kika Sha shikenan ni likita ne nasan kalar alluran da zan miki bazaa samu matsala ba ita wace kike fadan ta mutu kila ba likitan

da ya kware ne ya zubar Mata da cikin ba shiyasa zubarwa yazo da matsala har ta rasa ranta ki yarda dani yanzu kika bar cikin nan dole wlh Yaya mustapha ya miki dukan da har sai kin fito kin fada masa ni na miki a duk yanda ya d'aukeni yaga wai ni na Masa wanan cin amanar tamkar kaninsa haka ya d'aukeni muhasim ko abu zaiyi wlh haka zai nemeni yayi shawara dani,danginku gabad'aya sun d'aukeni tamkar dan uwa ba siriki ba da kunya su gano ni na miki haka muhasim Aunty Aisha ma sai ta rabu dani mutuncina ma zube wa zaiyi a wajen kowa muhasim dan Allah ki rufa min asiri kaddara ta riga fata ba yanda zanyi ki bari na miki allura nan ki sha maganin da zan baki kina zuwa gida kiyi kwanciyarki zaki ringa dan ciwon mara kad'an kadan a hankali zaki ga jini ya fara zubo miki sai ki sa pad dan Allah muhasim"

Shirun da tayi ne yasa yace "Yauwa muhasim ngd kinji na miki alkawari cikin nan na fita zan siyo miki keken dinkin da kike ta cewa kina so"

Ya mik'e da sauri yayi waje dan bashida allurar da zai mata a office din.

Muhasim kuwa tana ganin ya fita itama ta fito daga office din da gudu tayi waje dan bazata tab'a bari ya zubar mata da ciki ba tasan kasheta kawai yake so yayi.

Luba kuwa tana ganin fitowar ta itama ta mik'e da sauri tabi bayanta.

Sai dai gudu take bata tsaya taren abin hawa ba Luba kuwa nesa da asibitin ta tsaya ta tari abin hawa fuskarta lullube da mayafinta tana samun abin hawan ta hango Salis ya fito daga asibitin a rude.

Ita kuwa ta shige cikin machine din tana "Ka tsaya ka d'auki wacan yarinyar mai uniform dincan.

Ko ba'a fada mata ba tasan akwai wani abun dake faruwa bata ta gasgata zargin da ke ranta amma idan zargin da take ya tabbata hakan na nufin samun cikar burinta.

Duk horn din da ya ringa zubawa muhasim bata juyo ba sai da suka wuceta kadan Luba ta leko da kanta tana "Muhasim Ina zakije haka daga Ina kike?waye ya biyoki kike gudu"?zo ki hau muje"

"Da sauri muhasim ta shige machine din tana cigaba da kuka

Luba kuwa ta jawota jikinta ta hau bubbuga bayanta alamar rarrashi tana "yi shiru mana ki fada min mai ya same ki kike kuka haka naga uniform din makaranta ne a jikin ki mai kika zo yi nan"?

Muhasim kuka ta cigaba da yi batayi magana ba

Luba kuwa ta cigaba da rarrashin ta tana "tana shikenan tunda baza ki fadamin ba bari na Kai ki gida na fada musu ba makaranta kika je ba yawon ki kika tafi"

Da sauri muhasim ta dago cikin sheshekar kuka tana "Dan Allah Aunty karki je ki fada a gidanmu"

"Toh daga Ina kike?Mai ya Sameki kike ta kuka haka ni sai naga ma Kamar daga asibitin uncle din ki kika fito ko wajensa kika je"? innalillahi wa Inna ilaihi rajiun ko wani abu ya miki irin na ranan da aljanunsa Suka tashi dinan"?

Luba tace tare da zaro idanduna waje

Muhasim kuwa cikin kuka ta gyada mata kai Luba tayi sauri ta tsayar da mai machine akan ya saukesu dan sun kusa Isa unguwarsu muhasim din

Hannun muhasim ta ruko bayan ta sallami mai machine din tayi wani lungu dasu tana cigaba da sallati dake kara tunzura muhasim ta fashe da kuka sai da ta samu wajen da ba kowa ta zaunar da muhasim akan wani dakali itama ta zauna ta aro damuwa a fuskarta har da dan hawaye tana "Yanzu bayan ranan da na kwace ki a hannunsa sai da ya Kara tab'aki"?

Gyada mata kai Muhasim tayi
Luba kuwa ta cigaba da "A yaushe ya tab'aki"?

Muhasim sai taji ta kasa mata magana Luba kuwa cikin rarrashi kamar irin tana tausayinta dinan tace "ki fadamin na taimaka miki Kinga ranan ni na taimaka miki ba Wanda yasani yanzu idan kika fada.min ma taimaka miki zanyi"

"Yace Kar na fadawa kowa"

Kar ki damu kinji muhasim ba Wanda Zan fadawa sai dai ma na taimaka miki Kamar yanda na taimaka miki ranan"

"Aunty ranan ne a gida ya dawo daga wajen aiki Ina saman palonsa Ina lilo Yana ganina ya kamani ya Kai ni daki yamin fyade yace kar na tab'a fadawa kowa,tunda ga lokacin na bar gidan ban sake komawa ba yau ana mana darasi a biology na gano Ina d'auke da ciki har na wata biyu da sati biyu shine naje na fada masa yace wai zubar min zaiyi Kuma ni nasan idan aka zubar da ciki mutuwa akeyi"

Ta rushe da kuka Luba ta damke bakinta tare da zaro ido hakan da muhasim tagani yasa ta Kara shiga tashin hankali tana "Uncle ya cuceni Aunty wlh Abba baya barin mu zance bama kula samari Aunty Khadija ce ma mai samari ni banida samari sai Yan makarantar mu da suke cewa suna sona,idan Abba ya gano inada ciki wlh sai ya kusa kasheni gashi uncle yace Kar na fadawa kowa na rufa masa asiri na rasa yanda zanyi Aunty"

Luba rawa ne kawai bata tashi ta taka ba cikin da muhasim ke d'auke dashi shine zai zama silar da zata samu cikar burinta Amma a zahiri tashin hankali ta aza a fuskarta tana "Innalillahi wa Inna ilaihi rajiun yanzu abinda uncle ya aikata miki kenan ya za'ayi ya miki fyade ki samu ciki yace Kuma zai zubar miki so yake ya kasheki ai idan kika sake kika bari ya zubar miki da cikin nan mutuwa zakiyi yanzu yi shiru ki daina kuka zan taimaka miki insha Allahu kina ji"
Da sauri muhasim ta hau share hawayenta tana gyada Kai

"Karki sake ki tab'a fadawa kowa kina da ciki ko uncle din ma karki sake ki yarda ki Kara had'uwa dashi karki Kara zuwa office dinsa idan yazo gidanku karki fito so yake ya kasheki sabida asirinsa ya rufu ni nan zan taimaka miki kina jina"?

"Ina jinki Aunty"

"Zanje na saka a miki Addu'a cikin da kansa zai fita batare da kowa yasani ba karki sake ki tab'a fadawa kowa kina amai ne"?

"Aaa Aunty"

"Yauwa zanje na saka ayi miki Addu'a kinji karki sake ki sa damuwa a ranki kiyi Kamar bakida komai kicigaba da zuwa makaranta kina abubuwan ki cikin zai fita da kansa idan akayi addua kinji"?

Muhasim ta zamo daga dakalin ta durkusa tana

"Nagode Aunty nagode da taimakona da kike sanyi Allah ya saka miki da alheri"

"Tashi tashi ba komai jeki samu ruwa ki wanke fuskarki idan an tambayeki mai ya samu fuskar ki haka kice kwaro ne ya fada miki maza jeki gida tunda lokacin tashin ku ma yayi zan nemeki da kaina karki sake ki yarda ki Kara had'uwa da uncle dinki mugune so yake ya cutar dake"

"Bazan sake yarda na hadu dashi ba Aunty Kuma ba Wanda Zan fadawa"

"Kince bakya amai ko?dan idan kina amai zaa San kina da ciki"

"Ban tab'a amai ba Aunty bakina ne dai bana Jin dadinsa"

"Toh karki damu cikin na fita zakiji bakinki ya dawo daidai"

"Toh Aunty ngd Allah ya saka miki da alheri"

"Ba damuwa jeki kawai"

Muhasim da sauri ta mik'e ta dau hanyar gida

Luba ta saki wani irin murmushi Kamar tayi ta ihun murna tasan muhasim bata da wayo ko na sule biyar bazata tab'a fadawa kowa ba a yanzu Salis dole ya aureta ko Kuma ta tona masa asiri.

Ya zama dole ta fesawa Aminiyarta wanan labari

Bata zame ko ina ba sai gidansu Asabe da zuwanta ta kwashe komai ta fada mata Asabe ta hau tayata murna tana wanan karon ko dan rufin asirinsa dole ya yarda ya aureta"

Salis

Hankalinsa ba karamin tashi yayi ba a lokacin da ya dawo ya tarar da muhasim ta tafi.

Da sauri yayi gate ya hango tana tikar gudu har tayi nisa ma

Da gudu ya koma ciki ya koma office dinsa tare da d'auko mukulin motarsa sai dai motarsa kin bashi hadin kai yayi dan duk iya yinsa motar kin tashi tayi.

Haka ya rufe motar ya fito ya tare abin hawa yabi bayan muhasim ko zai ganta sai da har Suka kure titin bai ga alamarta ba,Yana tsoron ta tafi gida a haka a tambayeta ta tona masa asiri

Gwara yabi bayanta sai dai har yaje nesa da gidansu ya tsaya bai ga alamar kowa ba yasan yaci a yanzu ta karaso tuna zata iya komawa makarantarsu tunda lokacin tashin su baiyi ba yasa ya nufi islamiyarsu dan nan su Ashraf sukeyi suma makaranta daya ya saka su shi ke d'aukar nauyin na islamiya da bokonsu duk da yana da kudin, yayan Aisha bai sakar Masa komai ba wani zubin Yana rigashi biyawa yaran gabadaya fadar mutuncinsa bata bakine bazai so yasan barnar da ya masa ba.

A lokacin dayaje wayancewa yayi da zuwa ya duba yaran.

Ajin Afrah da muhasim daya Khadija ce da Ashraf suke aji daya

A wajen mallamin yake ji wai muhasim batazo ba a yanzu ne su khadija Suka ce idan an tashi zasu biya gida suji ko lafiya dan Khadija na gidansa har a lokacin Aisha ta riketa ta karfi da yaji.

Zufa ce ta keto Masa Yana tunanin mai ya hana ta karasowa makaranta ko.dai.gida ta wuce.

Bai tsaya dogon tunani ba ya fito ya nufi gidansu muhasim din Kamar kirjinsa zai fado haka yakeji sabida fargaba yana shiga k'ofar gidan yayi kicibis da Yaya mustapha da gani fita zaiyi amma sabida zuwansa yasa ya koma Yana "Kaine tafe a yanzu"?

"Eee nine Yaya naje duba wani abokina ne a kasan layi shine nace bari na biyo mu gaisa"

Ka kuwa kyauta

Ya kwalawa Aunty mamy Kira dake kuryar daki ta fito tana ganinsa ta washe baki Suka gaisa ta d'auko masa ruwa.

Yaya mustapha ya hau jansa da hira a cikin hirarsu yake bashi labarin Yar abokinsa da ake yiwa fyade an kama wayanda suka mata fyaden yanzu.ma fitowar da yayi can zaije station din ya Kara da "wlh abokina nada hakuri ai ni bazan iya Kai su wani hukuma ba da hannuna zan kashe mutum"

"Allah ma ya rabamu da mumunan kaddara Abban Khadija"

Salis jikinsa rawa kawai yake yana yake sai yake ganin kamar Yaya mustapha.na iya gano abinda ya aikatawa muhasim mik'ewa yayi dan yagane muhasim bata dawo gida ba yacewa mustapha zai tafi.

Tare suka fito a daidai lokacin da suka hango muhasim ta taho daga nesa kirjin Salis ya hau bugawa da k'arfi Yaya mustapha Kuma ya gyara tsayuwarsa yana "ita Kuma wanan mai ya sameta haka ko dai duka yau ta Sha a wajen mallamin su"

Muhasim kuwa duk da ta goge fuskarta kana ganinta kasan kuka taci Koda ta iso ganin Salis yasa wani sabon kukan ya kwace mata tana zuwa ta shige gidan da gudu Yaya mustapha ya bi bayanta Yana "Ke lafiyarki kuwa"

Salis hankali a tashe yabi bayansu dan gani yake muhasim.na iya tona masa asiri.....

Sai Monday insha Allahu

HUMKAM INCENSE gidan kamshi da maganin mata muna turaren wuta na tsuguno Wanda yake matse HQ sosai Yana karawa dandano Yana maganin infection kowani iri muna da shuumar humra, hatsabibiyar turare,bita zaizai Mai abin mamaki munada turauka na daukar hankali
08132506044
TILL WE MEET*
ZARATY WANNAN HMMMM YA HADU NACE YA HADU SHIN KINTAVA AMFANI DA TURAREN DA ZAISA MIKI LAUSHIN FATA? KINIMI ZARATY YANA DA KAMSHI DA RIKE JIKI YANASA FATA LAUSHI TURAREN KOWA
Jas oud 3 IN 1 ZAKI TURARA GIDAN KI DASHI JIKINKI DA KAYANKI JAS OUD YA HADA ABUBUWA DA DAMA YANA RIKE JIKI SOSAI YANS KAMA GIDA YANA RIKE KAYA
AKWAI HUMRAR MOWA GUMBAR MOWA GARIN MOWAR TSUMIN MOWA DAN MATSI
SHU'UMAR HUMRA NA MANYAN MATA MATAN DA SUKA SAN KANSU SIRRINKI A SHIFIDAR DAKIN MAIGIDAN KI MUNADA SHUUMAR TSUMI
*DESIRE MAINE DA YAKE SAKA JIKI DA GASHI KAMSHI SOSAI IDAN KINA BUKATAR GANIN PHOTON KAYANA KIMIN MAGANA NGD
AKWAI SABON TURARE ME MATUKAR MUHIMMANCI ACE DUK WATA MATAN AURE DA TAKE DA HALI TA MALLE KESHI (NI DA MIJINA) SHINE SUNAN SA,SAI MOWAR MACE TURARENWUTA NA TSUGUNO YANA MATSE JIKIN MACE YANA MAGANIN INFECTION YANA DAUKE WARIN GABA YANASA KIJI CIKIN JIKINKI YA MATSE SOSAI YANASA KAMSHIN HQ

Sister's duk wacce batayi anfani da sabulun mg's ba ko kit dinsu inamai shaidamuku anbarku acan baya domin duk wnd yajaraba mg's sai sanbarka duk wani Mai tantama Akan kayan gyaranjiki toh tabbas yacire sabulun mg's domin yahadu bakarya zegyarajiki yafidda dattin fata Dama duk wani matsalan fata duk Wanda kefama da matsalan fata walau pimples ko spot, sunburn acne, knuckles,wrinkles,stretch mark dama dukkan wani prblm yajaraba mg's bi'iznillah komai zaizama labari bayan jikinku yy fresh zaisa jikinku yy smooth yadinga glowing,gawanda basa San anfani da Mai zaku iya using sabulun mg's batare da kunbukaci wani Mai b Mai bukata should Chat
08062991549
07046881166
07067210195
Call 08064532391

Team glow

WANAN LITTAFIN NA KUDINE BIYA 500 TA WANAN ACCT 0272061655 WEMA BANK NAFISA NUHU KO KATIN MTN KO AIRTEL TA WANAN LAYIN 08033719070 DOMIN KI MALLAKI NAKI KI MUTANEN NIGER KUMA KU TUNTUBI WANAN LAYIN
+227 96 82 89 84 DUK WACCE TA MIN SHARING NA BAR TA DA *RABBI ZAI FIDDA MIN HAKKI NA DA IZININ ALLAH DOMIN BA YAFEWA NAYI BA*

NI DA KISHIYOYINA

NA SADNAF

Yaya mustapah Yana Shiga cikin gida ya tarar muhasim sai kuka take aunty mamy na tambaya ta Mai ya sameta Amma ko sauraronta bayi kuka kawai take .
Kafin yayi magana saiga salis ya shigo da saraurinsa shima sai zufa yake kamar wadda ya tiki aiki.
Ran Yaya mustapah ya bacci ganin sai magana akewa muhasim tayi banza da mutane baisan sadda ya nuga Mata tsawa ba.keeee muhasim akwai sa an wasanki anan?
Ana Miki magana Amma kinwa mutane shuru ko ba dake nake ba?
A a Yaya a bita a hankali muji maiya sameta.muhasim lafiya Kika shigo gida kina kuka?
Salis ya fada cikin dakiyarsa Amma shi kadai yasan Mai yake ji acikin zuciyar sa ji yake shima kamar yayi ta zunduma ihu.

Kamar a mafarki yaji muhasim tace abban cikine dani□ai Yaya mustapah baisan Sanda ya zube ba aunty many Suma tayi😒

Ahahdbdbdjdhdhdbdbdgdhd do you want to go to the beginning of the year and I have been talking t u are so many people are so nake ka shiga dizuu's palace of novel and I will let you long enough to know to be frank with my first time insha Allah Zan musu daga I love it when my□□□□□□□

Dizuu tana muku barka da weekend♀♀♀♀♀♀

Nima sadnaf nake jira □

Shin kina aiki amma kina neman sana’an da zaki samu Karin kudi ko kuma kina sanaa Amma kina son ki fara wani sabo?Oriflame zai Baki daman yin Sanaa a cikin gida kuma ki rika samun maqudan kudi. Kamfanin yana kuma bada daman tafiya kasar waje kyauta idan har kayi aiki mai kyau.Kana buqatan akalla 20k da zaka fara siyan Kaya da register. Kayan kamfanin suna da kyau ga inganci kuma tana bada su a fara shi mai Rahusa. Ku tuntubi 08033122483 domin Karin bayani ko kuyi Mata magana ta what’sapp
https://wa.me/message/J7RPPP5WB42SF1

WANAN LITTAFIN NA KUDINE BIYA 500 TA WANAN ACCT 0272061655 WEMA BANK NAFISA NUHU KO KATIN MTN KO AIRTEL TA WANAN LAYIN 08033719070 DOMIN KI MALLAKI NAKI KI MUTANEN NIGER KUMA KU TUNTUBI WANAN LAYIN
+227 96 82 89 84 DUK WACCE TA MIN SHARING NA BAR TA DA *RABBI ZAI FIDDA MIN HAKKI NA DA IZININ ALLAH DOMIN BA YAFEWA NAYI BA*

NI DA KISHIYOYINA

NA SADNAF

PAGE 21

Salis tamkar ta buga masa guduma akai haka yaji

Ita kuwa ta cigaba da "ka Aureni na rufa maka asiri idan kuma kana ganin baza ka iya Aurena ba ba matsala amma asirin ka kam sai na tona sabida kowa yasan halin ka sai ka san yanda zaka yi da abin kunyar da ka aikata wai duk matan duniya ka rasa wacce zaka nema kayi wa fyade sai Yar yayan Aisha iya nan bai ishe ka ba ka hada da karkata mata baki sabida asirin ka ya rufu"

"Luba wlh bani na karkata mata baki ba ko neman ta da nayi ba'a hayyacina bane ba Luba dan Allah banda zancen aure ki fada min ko nawa kikeso wlh ko Rabin dukiyata ce zan baki"

"Bani hanya na wuce kafin na tara maka jama'a ni kake nunawa kyama da tsana haka da ka Aureni gwara ka bani Rabin dukiyar ka to wlh ko duk dukiyar ka zaka bani bazan karba ba rufin asirin ka shine ka so ni ka Kuma aureni tonan asirin ka Kuma shine kak'i Aurena"

"Luba taya zan aureki domin Allah taya kina kawar Aisha Aminiyarta tun na yarinta nazo na aureki ki duba mana dangantakar da ke tsakanin ku da kunya na kalli idonta nace zan auro ki ki saka kanki a matsayin ta ace baki rabu da Hamza ba kina gidan ki Aisha na Zawarci kwasam yazo yace miki zai auri Aisha ya zaki ji dan Allah nasan wlh idan ba'ayi Wasa ba sai kin rabu dashi"

"Haramun ne Auren kawaye Salisu duk a abin nan ban ji in da ka ce haramun ne Aure na ba Kuma da ka ke misali wlh indai nice Zan yarda dan haka ma Kara karfafa Mana zumunci zaiyi mai a ciki nidai zabi ya rage naka ka bani hanya na wuce"

"Aisha zata iya rabuwa dani akan na aureki Luba mutane zasu ga Kamar naci amanarta"

"Karka damu mutanen da zasu ga kamar kaci amanarta sune na farko wajen tsine ma idan Suka gano cewar kai din mazinacine macuci azzalumu ai bazan ma dole ka aureni ba inaga ko dauka da Wasa nake bazan iya tona ma asiri ba"

Ta fara k'ok'arin yin waje Salis ya tare hanya yana "Na yarda zan Aure ki Luba amma taya zan b'ullowa Aisha"?

Luba sai a lokacin ta saki murmushi ta koma kan kujera ta zauna tana "Yafi komai sauki ai Kai mijinta ne kana sama da ita Kuma dole ta maka biyayya ka fada mata zaka Aureni nasan ka dan tsarata shikenan bata da wani matsala ko zata yi fushin ma na dan lokacine"

Salis dafe kansa kawai yayi Yana Jin wani zazzabin tashin hankali na neman rufe shi taya Luba tasan shine yayi wa muhasim fyade har yanzu kirjinsa bai daina bugawa da tsoron wani yasan abinda ya Shiga tsakaninsa da muhasim ba yasan idan har ya bar Luba ta tona masa asiri ba mai yarda wai bashi ya karkata mata baki ba har yau yana cikin tunanin Wanda ya mata wanan aika aikan.

Tambayar da ke nukurkusan sa da san yaji yanda akayi har Luba tasan wanan abu da yayi Imani ba Wanda yasani sai Allah
"Luba ya akayi kika san ni na yiwa muhasim fyade?

Luba kwanakin baya ke Kika saka min magani Kika sa nayi abinda banyi niyya ba Luba idan har bake kike da saka hannu a abinda ya faru ba ya aka yi kika san abinda ya Shiga tsakani na da muhasim Luba tashi daya na tsinci kaina cikin azabar bukata dake hanani zaman lafiya da sukuni luba kina da hannu a abinda ya faru idan baki da hannu ba yanda za'ayi kisani kin biyo ta hakane sabida kawai ki samu cikar burinki"

"Ta nan ka b'ullo kenan na farko na yarda na sa ma kwaya a ruwa amma na biyun a Ina ka gani da har na saka kayi wa muhasim fyade ? Wlh fyaden da kayi wa muhasim yin kanka ne,yaushe rabon da ka gani a gidan ka ?taya zan San kayi mata fyade har ta samu ciki idan kana so kasan yanda akayi nasani bari na fada maka yarinyar da bakinta, ta fada min na tsinceta a hanya tana ta kuka da na rarrashe ta ta fito ta fada min kayi mata fyade ta samu ciki kace Kuma zaka zubar mata da cikin taki yarda,wlh a ranar tace ita zata fito ta fada wa iyayenta dan taga so kake ka kasheta,ni na rarrasheta akan Kar ta fada musu sabida Ina san rufin asirin ka,a haka ta ringa fada min duk yanda kake bibiyar ta da yanda kake bin ta makaranta sabida kawai ka shawo kanta Salis idan har ba ita ta fada min ba taya zan sani ko washegarin ranar da zaka karkata mata baki mun had'u da ita tace min kace tunda taki yarda ka zubar Mata da cikin zaka yi maganinta tana kuka tace Aunty Luba Ina tsoron ya kasheni nace ta kwantar da hankalin ta duk burga ce ba abinda zaka iya yi,Ina yawan zuwa baa bari na shigo ne amma na Dade inaso na sanar da Kai nasan komai sai Kuma gashi ka karkata mata baki sabida zalunci"

"Wlh bani na karkata mata baki ba Luba nemanta ma da nayi ba a cikin hayyacina bane"

"Ka addana rantsuwar ka zai ma amfani a wajen yayan Aisha da Aisha mutunci ya riga da ya zub'e daga lokacin da asirinka ya tonu ni kaga ma tafiyata ni na fasa ma auren naka nafiso a gane Kai mugune mazinaci"

"Ki rufa min asiri Luba wlh na yarda zan aureki nidai kimin alkawarin ba Wanda zai tab'a sanin wanan maganar har duniya ta nade"

"Indai ka aureni ka yarda nima ba saki a tsakanina da Kai,duk abinda nake so zaka min Kuma zaka kaunaceni kamar yanda kake kaunar Aisha nayi alkawarin ba Wanda zai tab'a sani"

Salis kamar ya dora hannu aka yayi ta rusa ihu zuciyarsa sai rayya masa take da ya hada luba da bango ya shaketa har sai ta daina numfashi bai tab'a sanin muhasim zata iya bude baki ta fadawa wani ba da a yanzu ba lubar ta samu ba kila da ta dade da tona Masa asiri.

Hadiye tsana da bakin luba da yake gani yayi Yana "Luba zan aureki nayi alkawari kin san bazai yu na yaudareki ba sabida rufuwar sirrina ba a yanzu zan aureki ba sai idan an kwana biyu kinsan yanzu ana cikin alhinin da tashin hankalin abinda ya samu muhasim na karkacewar baki da wuya Wanda Allah shine shaidata wlh wlh banida hannu a abinda ya sameta,a yanzu idan na fito da maganar auren ki da yawa za'a dauka ban damu da abinda ya same ta ba a yanzu ma babu kwanciyar hankalin da

zamu iya aure dan haka inaso ki daga min kafa har zuwa muhasim ta haihu nan da shekara daya haka da rabi"

"Ina laifin dai tana haihuwa muyi auren wane irin nan da shekara daya har da rabi"

"Ki dai yi min wanan taimakon Luba ai kinsan aure ya riga da ya zama dole idan akayi auren yanzu dukan zai yiwa Aisha yawa ga na abinda ya same su ga na Karin Aure ki bari nan da shekara dayan"

"Salis Ina tsoron ka zaka iya kasheni kafin shekara dayan nan tunda nasan baka kaunata amma inaso ka san cewar idan har ka kasheni Ina da mutane biyu wlh da zasu bankada sirrin ka"

"Rashin imani na bai kai har haka ba Luba bazan iya kashe rai ba"

"Wanda yayi fyade ya karkatawa mutum baki zai iya kissan Kai"

Salis cije lebb'ensa yayi Yana Jin zafi a zuciyarsa ya tsani tace ya karkatawa muhasim bakin nan yasan yanzu wani sabon shafin kaddara ce ta buda masa sai dai yayi addua Allah ya bashi ikon cinye wanan jarrabawa.

A takaice ranar zancen karfi da yaji yayi da Luba ta ringa zuba masa mulki san ranta Koda ta tashi tafiya ma sai dage masa tayi akan shi zai mai da ta gida.

Kamar zuciyarsa ta fashe haka ya maida ta gida.

Daga nan ya nufi gidansa Yana Jin inama Yana da yanda zai gujewa Luba bai hango yanda zai iya auren ta ba.

A lokacin daya isa gida haka ya tarar da Aisha da kumburarren ido,da gani taci kuka ta gode Allah tunda suka gano halin da muhasim ke ciki ta ke cikin wanan halin bai iya Mata magana ba ya zub'e akan kujera ya dafe kansa dake Sara masa Yana bakin cikin ganin Aisha a cikin Wanan damuwar.

Muryar ta ya katse masa tunanin da ya tafi

"Abban Ashraf wlh na kasa daina kukan tausayin muhasim duk Wanda yake da saka hannu a cikin wanan halin da muhasim take ciki Allah ya Hana shi Jin dadin duniya da lahira ga fyade ga ciki ga karkakata Kai wanan wane irin zalunci ne har na koma ga Allah Ina tsinewa Wanda ya mata wanan aika aika"

"Ya isa haka Aisha duk abinda ya samu bawa mai kyau ko akasin haka daga Allah ne ya Kamata ki yarda abinda ya sameta a rubuce yake sai ya sameta Yana cikin kaddararta Allah ya bata ikon cinye wanan jarrabawa addua zamu dage mata dashi Allah ya kawo mata karshen wahalar nan bai dace ki matsawa kanki da irin wanan damuwar ba idan kina haka Mai Yaya mustapha da Aunty mamy zasu ce ai sai ki Kara daga musu hankali ke fa ya Kamata kiringa rarrashin su"

"Tausayin yayana nake ji kaga yanda ya koma sabida tashin hankali Ina tsoron zuciyarsa ta buga Allah ya isa tsakaninmu da Wanda ya mata haka Allah ya tona masa asiri"

"Ya isa haka Aisha ki tashi ki d'auko min abincina ki sausauta wa kanki damuwar nan kafin ki kamu da ciwon zuciya"

Aisha mik'ewa tayi ta nufi kitchen tana share hawayen dake zubo Mata

Salis kuwa ya hau sallati kasa kasa a zuciyarsa hankalinsa na balain tashi idan yaji Aisha na irin wanan tsinuwar yasan bashida hannu a karkata mata baki amma yasan shi ya mata fyade ta samu cikin ko da ta kawo abincin bai wani iya ci ba dan ya aiketa ne sabida ya kau da maganar.

A ranar ko runtsawa bai yi ba Yana ta tunanin yanda zai kaucewa auren Luba da yake ganin bazai iya ba da wane ido zai kalli Aisha yace zai auri Luba taya ma hakan zai yu wane irin kallo mutane zasu masa Luba ta zame masa kaddara da ace yasan Luba zata zame masa balai haka da tun farkon auren sa da Aisha ya rabasu.

Tashin hankalin da yake ciki a yanzu sai ya nin ka na baya dan gefe ga Luba gefe gefe daya ga Aisha da yayanta da ya zama silar jefa su a cikin tashin hankali ba abinda ya Kara karya Masa zuciya sama da kukan da yaga Yaya mustapha nayi da hawaye mutum ne shi mai kib'a sai gashi duk ya zub'e sabida tashin hankalin da yake ciki,taya zai so su tab'a sanin shi yayi wa muhasim fyade har ta samu ciki,cikin da kullum yake Addu'a Allah ya kawo sanadin da zai zub'e idan babu rabon ya zub'e Allah yasa abinda muhasim din zata Haifa yazo ba Rai.

Sosai ya saki bakin Aljihu yake hidimanta musu duk wani magani ko test shi yake d'aukar nauyin su.

Luba kuwa tamkar har ya aureta sabida hidimar da yake yi da ita,kullum a cikin tambayarsa kudi take,ta k'arfin tuwo tasa ya ringa zuwa zance wajenta ya mugun tsanarta amma haka ya daure sabida rufin asirinsa.

Abinda ke Kara bashi mamaki da shu'umancin ta yanda take ziryar asibiti har da dan hidimarta,Yana ji yanda Su Aisha da Yan uwanta ke yabon ta.

Aisha har wani Kara bashi labarin irin damuwar da luba tayi da larurar da ya samu muhasim take baya iya ce mata komai dan Luba ta daina bashi mamaki yanda ta siye zuciyar Aisha da zai fito yace mata tace tana Sansa karyatawa zata yi.

Da Aisha zata nutsu ma ta kalleshi zata san shi ma ba'a hayyacinsa yake ba ko d'akin da aka kwantar da muhasim baya san Shiga dan gani take zata iya bud'e baki ta tona masa asiri.

A Haka har aka sallamesu daga asibiti akan larurarta shafan Aljannu ne,Inda ya dan samu kwanciyar hankali katsina akayi da Muhasim sabida Kar kowa yasan cikin dake jikinta,haka Aisha ta ringa zarya daga bauchi zuwa katsina.

Lokacin haihuwar Muhasim na karatowa Yana addu'ar Allah yasa abinda zata Haifa Kar yazo da rai

A ranar da aka sanar musu anyi mata aiki an cire mata 'ya mace hankalinsa sai da ya kara tashi dan a yanzu gani yake kamar za'a gane yarinyar yarsa ce sai dai cikin ikon Allah bata d'auko kamaninsa ba, a lokacin da Yaya mustapha yace zaa Kai yarinyar gidan marayu ba karamin Dadi yaji ba hakane yasa daya shawarce shi ya bashi goyon bayan a kaita gidan marayun tunda ba'a san waye mahaifinta ba sai dai kwana biyu da dawowarsa sai ga Aisha ta taho da jaririyar wai zata rik'e ta har ga

Allah ba haka yaso ba so yayi ya nesanta kansa da jaririyar amma gudun Aisha ta dago shi yasa ya hakura ta hada Nana da Ummi ta ringa shayar dasu,abinda ke dan bashi mamaki bai wuce yanda Aisha ke matukar kaunar Nana ba tamkar tasan nana jininsa ce.

Taya zai so Aisha tasan shine mahaifin Nana bazai so ta tab'a sani ba zai auri Luba a matsayin kaddararsa gwara taji labarin aurensa da Luba da taji labarin shine mahaifin Nana.

Luba kuwa Kamar mai jiran muhasim ta haihu ta sako shi a gaba akan ya tura gidansu a daura musu aure Kuma ita ba anan take so ta zauna ba Abuja take so ta zauna ta hau gindaya Mai sharruda.

Dak'yar ya samu ya shawo kanta akan ta bari a Kara kwana biyu kafin suyi maganar Aure baya so suyi gaggawa ya riga da yace zai aureta ba fasawa zai yi ba.

A takaice da kyar ta yarda aka kara wata takwas a wanan lokacin yafi kowane lokaci shiga tashin hankali gani yake Aisha idan taji labarin auren nan zata iya rabuwa dashi,gashi Luba ta dage akan ita bata San munafirci tafiso a fadawa Aisha.

Da kudi mai yawa ya samu Kan Luba ta yarda akan zai aureta a b'oye idan an samu shekaru zai fito ya fadawa Aisha a yanzu bazai so Aisha ta sani ba tunda dama Yana aiki a Abuja zai ajiye Luba a Abujan kawai yasan Aisha bazata tab'a sani ba.

Dak'yar Luba ta yarda har aka daura musu aure bazai iya lissafa kudin da ya kashe mata a hada lefe ba duk wani Kaya da tasan Aisha na da shi sai da ta saka shi ya siya mata irinsa ban da kudaden da take ta karba a hannunsa.

Sosai yake taka tsantsan baya so Aisha ta tab'a gano shi hakane yasa ya mata karyar ayyuka sun masa yawa a can.

Luba kuwa ko da ta tare baya iya kwanciya da ita sabida baya Jin kaunarta yasan yayi tsalle tsalle a baya,ba Kuma dan Yana kaunarsu ba Luba ce yake Jin bazai iya kwanciya da ita ba.

Karyar rashin lafiya ya ringa shirga Mata ganin an tafi sati daya yasa ta haukace Masa akan sai ya kwanta da ita raina mata hankali yake yi ba abinda yake damunsa ita fa auren da suka yi so take ya gwada Mata soyayya yanda yake gwadawa Aisha idan ba haka ba tona masa asiri zata yi.

Abu kadan sai tace zata tona masa asiri sai da ya tilasta wa kansa kwanciya da ita a haka ma sai ya dirkakawa kansa magani yake iya kwanciya da ita,a cikin wata daya har makota sun san ta,da shishigi ta ringa zaryar office dinsa na Abuja har sai da duk abokanansa suka san matarsa ce da makirci take yawan hana shi zuwa bauchi gangar jikinsa ne kawai a Abuja Amma zuciyarsa na wajen Aisha,tunda ya auri luba zuciyarsa kullum cike take da fargaba akan kowane lokaci Aisha zata iya ganowa ya auri Luba a b'oye,hakane yasa yake ta iya k'ok'arinsa wajen ganin ya hana Aisha muamalla da Luba,sai dai ya lura Luba burinta kawai taga ta tona kowa yasan ya aureta.

A Haka har Luba ta munafirce shi da ta haihu ta gayyato Aisha batare da yasani ba,Aisha bata cancanci haka daga wajensa ba yasan ko me zai ce mata bazata tab'a yarda ba'a san ransa ya auri Luba ba idan yace zai mata bayani hakan na nufin tonuwar asirin sa da yasa Yama auri luban.

A Haka ya samu mahaifiyar sa ta shawo Kan Aishan da tunda daga lokacin da ta gano ya auri Luba ta goge shi a zuciyarsa yayi bankwana da wani farin ciki da Jin dadi kaddara ta Kara shigo Masa da Hindatu rayuwarsa ya aureta shekara da shekaru yana yiwa Luba biyayya sabida kar ta tona Masa asiri shekara da shekaru yana kashewa Luba kudi,shekara da shekaru yana fama da zullumi da fargaban Luba na iya tona Masa asiri a kowane lokaci sai gashi a yau Luba ta tarwatsa masa gida ta hanyar tona Masa asiri agaban Aisha da yayansa,a gaban Aneesa da bata san ma Yana da boyayyen sirri ba.

Present

"Abba Abba"

Yaji muryar Ashraf akan sa

Bud'e idonsa yayi a hankali ya sauke akan Ashraf daya tsugunna a gabansa shima kana ganinsa kasan hankalinsa a tashe yake.

Sai da ya hadiye yawu yace "Abba ka koma cikin daki ka kwanta bana so su ummi suga halin da kake ciki yanzu zan bi bayan Hajiya umma bazan bari ta karasa gidan ba"

Da sauri ya ruko hannun Ashraf Yana "Kayi sauri kaje Ashraf karka bari ta fadawa yayanta dan Allah ka shawo kanta mu rufe sirrin nan idan har maganar nan ta fita mutuncin ku Kuma zai zub'e"

"Abba kayi hakuri da tambayar da zan Kara ma Dan Allah kana da sa hannu a karkacewar wuyan Aunty muhasim"

"Ashraf wlh wlh banida sa hannu a abinda ya same ta da Ina da sa hannu tunda asirina ya Riga da ya tonu Zan fada ma gaskiya amma wlh banida sa hannu a abinda ya same ta nine dai mahaifin Nana "

Ashraf gyada kansa yayi Yana "Bari na bi bayanta Abba"

Yayi hanyar waje

Salis ya mik'e jiri na dibansa yayi hanyar dakin Aneesa tamkar karamin yaro haka ya zube akan gado hawaye na bin fuskarsa.

Luba

"Ai abinda za'ayi gida zaki tafi kafin musan yanda zamu bullowa lamarin nan amma batun na bar ki ki zauna anan kema ai kinsan ba mai yuwa bane haka kawai Allah ya rufa min asiri nayi Aure dakyar Ina lalabawa kizo kimin kwace kamar yanda Kika yiwa kawarki haba Luba da hankalina fa ni ba shashasha bace"

"Asabe yanzu bazaki iya rufamin asiri ba Asabe duk abinda na Miki a rayuwa ni zaki wulakanta na zauna dake din shine bazaki iya ba"

"Ikon Allah uban me kike min wai hala kin d'auka ni Aisha ce Kinga tashi maza ki bar min gida kafin nasa a sakar Miki karnuka"

Luba hawaye ne ya hau zubo mata tana k'ok'arin Magana

Asabe ta mik'e ta fara kwallawa Mai gadi Kira tana "ka bud'e min kejin karnuka Kan nan".....

HUMKAM INCENSE gidan kamshi da maganin mata muna turaren wuta na tsuguno Wanda yake matse HQ sosai Yana karawa dandano Yana maganin infection kowani iri muna da shuumar humra, hatsabibiyar turare,bita zaizai Mai abin mamaki munada turauka na daukar hankali
08132506044
TILL WE MEET*
ZARATY WANNAN HMMMM YA HADU NACE YA HADU SHIN KINTAVA AMFANI DA TURAREN DA ZAISA MIKI LAUSHIN FATA? KINIMI ZARATY YANA DA KAMSHI DA RIKE JIKI YANASA FATA LAUSHI TURAREN KOWA
Jas oud 3 IN 1 ZAKI TURARA GIDAN KI DASHI JIKINKI DA KAYANKI JAS OUD YA HADA ABUBUWA DA DAMA YANA RIKE JIKI SOSAI YANS KAMA GIDA YANA RIKE KAYA
AKWAI HUMRAR MOWA GUMBAR MOWA GARIN MOWAR TSUMIN MOWA DAN MATSI
SHU'UMAR HUMRA NA MANYAN MATA MATAN DA SUKA SAN KANSU SIRRINKI A SHIFIDAR DAKIN MAIGIDAN KI MUNADA SHUUMAR TSUMI
*DESIRE MAINE DA YAKE SAKA JIKI DA GASHI KAMSHI SOSAI IDAN KINA BUKATAR GANIN PHOTON KAYANA KIMIN MAGANA NGD
AKWAI SABON TURARE ME MATUKAR MUHIMMANCI ACE DUK WATA MATAN AURE DA TAKE DA HALI TA MALLE KESHI (NI DA MIJINA) SHINE SUNAN SA,SAI MOWAR MACE TURARENWUTA NA TSUGUNO YANA MATSE JIKIN MACE YANA MAGANIN INFECTION YANA DAUKE WARIN GABA YANASA KIJI CIKIN JIKINKI YA MATSE SOSAI YANASA KAMSHIN HQ

Sister's duk wacce batayi anfani da sabulun mg's ba ko kit dinsu inamai shaidamuku anbarku acan baya domin duk wnd yajaraba mg's sai sanbarka duk wani Mai tantama Akan kayan gyaranjiki toh tabbas yacire sabulun mg's domin yahadu bakarya zegyarajiki yafidda dattin fata Dama duk wani matsalan fata duk Wanda kefama da matsalan fata walau pimples ko spot, sunburn acne, knuckles,wrinkles,stretch mark dama dukkan wani prblm yajaraba mg's bi'iznillah komai zaizama labari bayan jikinku yy fresh zaisa jikinku yy smooth yadinga glowing,gawanda basa San anfani da Mai zaku iya using sabulun mg's batare da kunbukaci wani Mai b Mai bukata should Chat
08062991549
07046881166
07067210195
Call 08064532391

Team glow♀

WANAN LITTAFIN NA KUDINE BIYA 500 TA WANAN ACCT 0272061655 WEMA BANK NAFISA NUHU KO KATIN MTN KO AIRTEL TA WANAN LAYIN 08033719070 DOMIN KI MALLAKI NAKI KI MUTANEN NIGER KUMA KU TUNTUBI WANAN LAYIN
+227 96 82 89 84 DUK WACCE TA MIN SHARING NA BAR TA DA *RABBI ZAI FIDDA MIN HAKKI NA DA IZININ ALLAH DOMIN BA YAFEWA NAYI BA*

NI DA KISHIYOYINA

NA SADNAF

PAGE 22

Luba

"Asabe nice fa yanzu ni zaki wulakanta dan Aurena ya mutu"?

"Auwalu kana Ina wai ka Sako min karnukan nan nace"

Asabe tace tana Kara daga muryar ta

Luba tsakanin mamakin Asaben yasa ta kasa motsawa dan ko a mafarki bata tab'a tunanin Asaben zata iya mata haka ba

Tana k'ok'arin Magana taji Haushin karnuka a mugun tsorace ta juya ta kuwa hangosu a koshe su biyu sun dallaro Harshe sun yo wajen da take tsaye suna haushi

Baa tab'a sakin karnukan sai daddare tsoron karnukan yasa ba'a fiye zuwa ma gidan Asaben ba dan tsohon soja take Aure.

"Yauwa sake su,suyi mata rakiya
"Tunda dai bani na kashe mata Aure ba, ita ta kashewa kan ta aure sabida rashin hankali ta doso gidana Wai a gidana zata zauna kafin komai ya lafa Kafin na ankara sai dai naji ana rangada guda.

ihu Luba tasa da taga sun yo kan ta gadan gadan tayi palon Asabe da gudu,Asabe ta hankado ta tare da rufe k'ofarta.

Luba ta hau zagaye gidan tana ihu karnukan na binta a guje har suna neman cafota dan sun cafo mayafin ta.

Da k'yar ta samu ta shige d'akin mai gadi kafarta na gurdewa,tana Jin maigadin na k'ok'arin Mai da su cikin kejin su.

Nishin azabar kafarta da gurde kawai take hawaye na zubo Mata.

Shigowar mai gadin yasa ta mik'e dak'yar tana cije lebbenta dan kafarta zugi kawai yake Mata.

Da dingishi ta fice daga gidan tana tafe tana hawaye ko biyar babu a hannunta kunyar ma doson gidan nasu take,akan fadan da iyayen ta suka koma yi Mata akan yanda take tafiyar da rayuwar aurenta a gidan Salis yasa ta tsiri gaba dasu sai ta ga dama take zuwa gidan nasu,a yanzu ma ta lura ido kawai suka kawo suka zuba mata, ba wani hidima da take musu burinta kawai da kansu su fito suce ta musu abu kafin ta musu Amma indai ba tambayar ta suka yi ba gani take basu da wani matsala,rabata da komai da Salis yayi yafi komai daga mata hankali Rabin dukiyar ta da take Kuma takama tana dashi Yana wajen Asabe,Asaben ma bata tsaya ta saurareta ba ta mata koran kare,Rabon da tayi tafiya a kafa haka ma ta manta,

Ciwon da kafarta ke Mata yasa ta tsayar da abin hawa ta nufi gidan da zumar idan taje sai ta karbi kudin motar ta bayar.

Tafiyar minti goma ya Kai ta gidan iyayenta Koda ta sauko sai taji ta kasa ma shiga gidan an tafi wata biyar rabon ta da gidan nasu,horn din da mai Napep ya mata yasa ta shige gidan da sallama.

Ba kowa a tsakar gidan sai take Jin kanta Kamar wata bakuwa a baya idan zata zo ko sallamar bata yi haka take Shiga tana yatsina fuska daga tace ya taga gidan haka,ya ko ina kaca kaca ba kintsi,haka zata yi ta yatsine fuska tana fesa turaren da tazo dashi,har Kuma ta baro gidan bata saka komai a bakinta sai dai taci abinda ta zo dashi, mahaifiyarta najin ciwon abinda take yi idan ta kasa hakuri haka zata rufeta da fadan tama daina zuwa gidan ai tunda tayi kudi ta canza iyaye kawai.

Mahaifin ta kuwa baya ce Mata komai sai dai yace taje gata ga duniyar nan shi dai yafi kowa Jin zafin auren Salis da tayi ba yanda zaiyi da ita ne dan bazai manta mutuncin da Aisha ta musu ba.

A hankali ta kara kwada sallama taji muryar mahaifiyar ta da suke cewa Inna larai ta amsa sallamar a daidai lokacin da ta fito daga d'akin.

Luba da sauri ta sunkuyar da Kai tana "Inna Ina kwana"

Bata amsa ba sai da ta kalli gefe da gefenta tace "Toh ni ko dai idona ne suke min gizo ba Luba bace"

Kukan da take rikewa ya kwace mata tana "Nice Inna dan Allah ki bani naira dari zan bawa mai machine"

Tsananin mamaki yasa Inna bata motsa ba ta saki baki tana kallon Luba sai da Luba ta Kara cewa ta taimaka mata da darin Inna ta koma d'aki ta fito da dari a hannunta ta bawa luba.

Luba ta fita ta kai wa mai machine din ta dawo ta zub'e a tsakar gida ta rushe da kuka.

Har lokacin mamaki bai saki Inna ba dan a iya sanin ta Luba ma idan zata zo gidan horn ma take musu a motar ta yau Kuma sai taga lubar tazo a kafa har tana neman kudin machine a wajenta ga fuskarta a kumbure ta dade da cire damuwar Luba a ranta,ido kawai suka zuba mata dan sun san dole watarana tayi dana sanin wofintar dasu da tayi,dan bata da sama dasu din.

Dakin ta ta koma tayi zamanta tana cigaba da kulla man gyada da man jan da take siyar wa.

Shigowar ta da zub'ewar da tayi a gabanta cikin kuka tana "Inna Salis ya sakeni,Salis ya sakeni saki uku ya kwace komai daga hannuna ko kaya bai bari na d'auka ba"

"Ashe sakin ki akayi shiya sa ki ka zo gidan nan ai na d'auka kina da gidan da yafi wanan,ashe dai muna da gidan da zaki zo? Yau dai ga ranar mu ashe,an saki hajiya ta dawo gida Allah ya kyauta"

"Inna dan Allah kuyi hakuri karku yi fushi dani nasan abinda nayi ban kyauta ba"

"Ai ba sai kin bamu hakuri ba hajiya ai duniyar kika zab'a ya tun ba'aje ko ina ba zaki karaya ice dai zaki iya zama a gidan da ba kintsi gidan da ke miki wari ya Kamata ma ki nemo turare karki shaki wari"

Luba hawaye kawai take bata iya Kara magana ba dan tasan magana mahaifiyar ta ke kwaba mata,
Inna bata Kara nunawa tasan tana d'akin ba har ta gama kulla man ta mik'e ta bar mata d'akin.

Luba kuwa ta mik'ar da kafarta dake mata zugi ta buga uban tagumi ta kasa yarda da duk abinda ke faruwa da ita,bata tab'a kawowa kanta sakin da Salis zai mata idan ta tona Masa asiri ba,bata tab'a kawowa kanta dawowa gidansu tayi zawarci ba,bata tab'a kawowa kanta rasa tarin dukiyar da take dashi da duk Salis ta ke karbewa kudi tana barazanar idan bai bata ba zata tona masa asiri,bata tab'a kawowa kanta wai Asabe da ta dauke ta a matsayin aminiya ta bata fiye da Rabin abinda take dashi akan ta juya mata sabida amincin dake tsakaninta da ita zata iya murzawa idonta toka ta Mata irin wanan cin mutuncin akan ta nemi ta zauna a gidanta zuwa wani dan lokaci kila idan ta Kai ta wajen mallamanta a samu a asirice mata Salis ya Mai da ta dakinta

Asabe ma bata tsaya ta saurareta ba ballantana tace ta bata kudadenta dake wajenta.

Yanzu shikenan duk wani karfinta da mulkinta da duk wani takamar ta rushe shi da hannunta Mai yasa tunanin ta bai tab'a bata idan ta tonawa Salis asiri itama nata asirin zai tonu ba,mai yasa tunanin nata bai tab'a bata akan idan ta tonawa Salis asiri tamkar ta saka almakashi ta datse igiyar dake tsakanin su ne ?taya sai da ta kawo girma zata dawo gida tayi Zawarci,shikenan duk san taga ta raba Salis da duk matansa ta zauna dashi ya tashi a banza kenan itace ma zata rabu dashi,shikenan Hindatu ta samu abinda take so kenan ta bar mata gidan?

Taya zata soma rayuwa agidan nan ta hau karewa dakin mahaifiyar ta kallo bashi da girma balle a samu wadatar iska.

Yanzu daga Ina zata fara shikenan ta tashi ba miji ba kudi kenan ta zama bazawara kenan Luba da Aisha na zaune a matsayin matan Salis Ina da sake ya zama dole Asabe ta bata kudadenta taje ta nemi mai mata aiki ta koma gidan Salis idan komawarta bazai yu ba gwara ayi abinda zai sake su gabad'aya kowa ya rasa tama san Aisha ta gama auren sa tunda duk ta fada mata maganganun da zata tsani Salis Hindatu da Aneesa zata yi aiki akan su Asabe kuwa ta karfin tuwo sai ta bata kudinta.

Haka ta zauna a daki tana sake sake har mahaifin ta ya dawo.

Sai dai a lokacin da Inna ta bashi labarin sakin da aka mata ta dawo gida murzawa idonsa toka yayi akan bazata zauna Masa a gida ba taje ta nemi gidan da zata zauna ya dade ma Yana Addu'a Allah ya nuna masa wanan ranar.

Luba duk yanda taso ta masa magiya da kuka haka ya watso ta waje.

Tunda take a rayuwata bata tab'a tsintar kanta a cikin tashin hankali irin wanan ba wai yau itace ta wayi gari bata da komai har wajen da zata zauna babu sabida mahaifin ta ya koreta bata tab'a sanin mahaifinta na da zuciya haka ba sai yau.

Bata da waya a hannunta balle ta Kira sultan ko ilham a waya a yanzu ba masu taimaka mata sai su duk da suma taga alamar Hamza ya cusa musu kiyayyrta a zuciyarsu idan ba ita ta neme su ba basa tab'a nemanta, auren Salis da tayi yasa bata damu da kudin da hamzan yayi ba har matansa sun kai biyu,sanin ba wajen da zata iya zuwa yasa ta nufi gidan hamzan da shima ba boyayye bane zata wayance da zuwa gidan akan ganin su sultan.

Aisha

Da ikon Allah ta isa gidan Yaya mustapha dan jirine kawai ya ringa dibarta ga azabar ciwon Kai ta ma daina kukan fili ta koma na zuci.

A lokacin da ta isa gidan karfe bakwai da rabine na safe,Bata da karfin buga k'ofar sai Nana ce ta ringa buga gate din har aka zo aka bud'e.

Yanayin da Umar ya ganta yasa ya saki sallati Yana "Aunty Aisha lafiya kuwa mai ya same ki"?

Bata iya bashi amsa ba dan bibiyu take ma ganinsa da dafa bango ta Shiga palon ta zub'e akan kujera ta rushe da sabon kuka,wai Salis shine yayi wa muhasim fyade,Wai Nana Yar Salis ce wani irin suya take ji a kirjinta wanan cin Amana sa zalincin da Salis ya mata ya munana.

Muryar Yaya mustapha da taji a kanta yasa ta bud'e idonta da suka kankance sabida kuka.

Yaya mustapha kuwa hannunta ya ruko cikin tashin hankali Yana "Aisha mai ya faru lafiya kike kuka waye ya mutu"?

Tashi tayi zaune cikin shesheka tana "Yaya inama mutuwar akayi da nafi kowa Jin dadi Yaya gwara mutuwa da wanan tashin hankali innalillahi wa Inna ilaihi rajiun"

"Mai ya faru haka Aisha ki Gaya min wani abune ya samu Salisun"?

"Nana mai ya samu Ammin taki"?

Aisha kallon nana tayi taga tana kallon bakin k'ofa hakane yasa ta kallo bakin k'ofar dan taga mai ya d'auke mata hankali"

Muhasim ta hango a keke Umar na k'ok'arin fito da ita daga d'aki wuyanta na nan a karkace.

Runtse idonta tayi da k'arfi tana tuna tsawon shekarun da Muhasim ta d'auka a haka shekara goma Sha biyar sai dai a kwantar a tayar ashe Salis ne ya jefata a cikin wanan halin.

"Sai na kwatar miki yancinki muhasim sai Inda karfina ya Kare muhasim wlh wlh sai na kwato miki yancin ki"

"Wai me yake faruwa ne Aisha"?

"Yaya Salis ne"!!!!

"Hajiya ummaaaa dan Allah ki bari

Ashraf ya dura gaban Aisha tare da rufe mata bakinta da hannu biyu.....

Wlh rasuwa aka mana tun safe Ina can gidan rasuwar sai karfe Tara na dawo Kar kujini shiru shiyasa na danyi wanan kuyi maneji.

INGANTACCEN MAGANIN SANYI TOILET INFECTION MAI WANKO DUK DATTIN MARA KOWANI IRIN SANYI NE ZAI MAGANCE SHI DAYARDAR ALLAH SHIN KINAFAMA DA RASHIN SHA AWA? RASHIN NI IMA RASHIN GAMSUWA SHIN KINYI SHEKARA DA SHEKARU KINA NEMAN HAIHUWA RIKICEWAR JINI CIWON JIKI CIWON MARA YAYIN AL ADA DUKA WANNAN MAGANIN YANA WARKARWA ME CIKI BATA SHAN MAGANIN SANYI NA 4K YAKE INA KATSINA INA AIKAWA KO INA A FADIN KASAR NAN HARDA KETARE MAZA DA MATA MAGANIN SANYI MAI GYARA MU AMALAR AURE KOBAKI SHA KOMAI BA NA KAYAN MATA WANNAN YA ISHEKI KEDAI KISHA KEDA MIJINKI NINAGAYA MAKI BAKI TABA SHAN MAGANIN SANYI IRINSHI BA HANZARTA KIZO WURIN AUNTY ZEE MOM MUJAHID
08162859027
KATSINA

HUMKAM INCENSE gidan kamshi da maganin mata muna turaren wuta na tsuguno Wanda yake matse HQ sosai Yana karawa dandano Yana maganin infection kowani iri muna da shuumar humra, hatsabibiyar turare,bita zaizai Mai abin mamaki munada turauka na daukar hankali
08132506044
TILL WE MEET*
ZARATY WANNAN HMMMM YA HADU NACE YA HADU SHIN KINTAVA AMFANI DA TURAREN DA ZAISA MIKI LAUSHIN FATA? KINIMI ZARATY YANA DA KAMSHI DA RIKE JIKI YANASA FATA LAUSHI TURAREN KOWA
Jas oud 3 IN 1 ZAKI TURARA GIDAN KI DASHI JIKINKI DA KAYANKI JAS OUD YA HADA ABUBUWA DA DAMA YANA RIKE JIKI SOSAI YANS KAMA GIDA YANA RIKE KAYA
AKWAI HUMRAR MOWA GUMBAR MOWA GARIN MOWAR TSUMIN MOWA DAN MATSI
SHU'UMAR HUMRA NA MANYAN MATA MATAN DA SUKA SAN KANSU SIRRINKI A SHIFIDAR DAKIN MAIGIDAN KI MUNADA SHUUMAR TSUMI
*DESIRE MAINE DA YAKE SAKA JIKI DA GASHI KAMSHI SOSAI IDAN KINA BUKATAR GANIN PHOTON KAYANA KIMIN MAGANA NGD
AKWAI SABON TURARE ME MATUKAR MUHIMMANCI ACE DUK WATA MATAN AURE DA TAKE DA HALI TA MALLE KESHI (NI DA MIJINA) SHINE SUNAN SA,SAI MOWAR MACE TURARENWUTA NA TSUGUNO YANA MATSE JIKIN MACE YANA MAGANIN INFECTION YANA DAUKE WARIN GABA YANASA KIJI CIKIN JIKINKI YA MATSE SOSAI YANASA KAMSHIN HQ

WANAN LITTAFIN NA KUDINE BIYA 500 TA WANAN ACCT 0272061655 WEMA BANK NAFISA NUHU KO KATIN MTN KO AIRTEL TA WANAN LAYIN 08033719070 DOMIN KI MALLAKI NAKI KI MUTANEN NIGER KUMA KU TUNTUBI WANAN LAYIN
+227 96 82 89 84 DUK WACCE TA MIN SHARING NA BAR TA DA *RABBI ZAI FIDDA MIN HAKKI NA DA IZININ ALLAH DOMIN BA YAFEWA NAYI BA*

NI DA KISHIYOYINA

NA SADNAF

PAGE 23

"Dan Allah hajiya umma ki bari karki yi haka ki dubi su Aliyu ki duba abinda zai je ya dawo"

"Wai me ke faruwane Ashraf Kuna Kara daga min hankali mai yake faruwa"?

Yaya mustapha yace Yana jijjiga Ashraf

Aisha kuwa
Wani mumunan duka ta kaiwa hannun Ashraf da ya rufe mata baki cikin wani irin murya dake nuna tsantsan b'acin ran da take ciki ta fara magana tana "Sabida rufin asirin mahaifin ku daya kasance mugu azzalumi bazan ki tsayawa na kwatarwa muhasim 'yancinta ba Ashraf ka manta baya ne ka manta duk halin da muhasim ta Shiga?ka Manta irin halin da mu ka Shiga nida Yayana da Aunty mamy har yau yayana Yana fama da ciwon zuciya shekara goma Sha biyar yata wuyanta na nan a karkace komai sai dai ayi mata? Ashraf anya da zuciya a kirjin ka kuwa? Yanzu kana Lawyer kana goyon bayan zalunci kenan"?

Bani da sama da iyayena da yayana,yayana ya min gatan da bazan iya manta shi ba yayana bashi da burin daya wuce yaga ni cikin farin ciki dan haka nima Zan sadaukar da farin cikin ku dan na faranta masa sai na tsaya tsayin daka na kwatowa Muhasim 'yancinta"

"Hajiya dan Allah"

Kawai Ashraf ya ringa cewa

Ita kuwa Aisha hawaye na zubo mata ta kalli Yaya mustapha da ke tsaye tun kafin ma tayi magana ya dafe kirjinsa,Aunty mamy Kuma ta kasa tsayuwa ta durkusa akan gwiwarta duk Aisha suka zubawa Ido,Aisha kuwa so take ta bud'e baki tayi magana yanayin da taga Aunty mamy da Yaya mustapha yasa ta ma kasa bud'e baki tayi magana,sai hawaye kawai take,a daidai lokacin da Umar ya gangaro da muhasim tsakiyar su akan keke suka hada ido da Aisha hawaye ya ringa bin gefen idon muhasim.

Aisha ta fashe da wani irin kuka ta karasa gabanta taje daidai wajen kanta tana "Mai yasa baki tab'a fada min yana neman ki kafin ya samu cikar burinsa ba"?
Muhasim dama abinda yasa kika bar gidana kenan?dama abinda yasa kike gudun gidana kenan? mai yasa baki fada min ba a lokacin da ya fara fito miki da halinsa? muhasim da ace kin fada min da duk baki tsinci kanki a wanan halin ba"

"Amma karki damu cutar da ya miki bazai tafi a banza ba sai na tsaya na kwatar miki 'hakkin ki sai anyi masa hukunci daidai da abinda ya aikata Koda kuwa duk abinda nake dashi zai Kare.

Ta ruko hannun Nana ta kawota gaban muhasim da ba baki sai ido kawai take wurgawa hawaye na zubo Mata.

Kukan da yaci karfin Aishan yasa ta kasa magana ta hau rera kuka,wai mijinta uban yayanta shi yayi wa yar yayanta ciki har ta haihu ta d'auka yanda Afrah take a wajensa haka ya d'auki su Muhasim bata San yana da mugun nufi akan muhasim ba.

"Aisha dan Allah kar ki fada min abinda kwakwalwata bazata iya d'auka ba k'ar ki fada min abinda zai tarwatsa min zuciya daga maganar da kike yi na fara tunanin inda kika dosa dan Allah kice ba haka bane"

Aunty mamy ta karashe da rawar murya

Aisha sai ta kasa bud'e baki ta mata magana Ashraf kuwa sallati kawai yake ya dafe kansa.

Yaya mustapha kuwa a hankali ya juya ya fara k'ok'arin nufar d'aki

Aisha tayi saurin cewa "Yaya"

Ya daga mata hannu batare da ya juyo ba yace "Ba sai kin ce min komai ba nagane mai yake faruwa"

Daga haka ya shige dakinsa

Aisha kuwa ta kara rushewa da sabon kuka Aunty mamy kuwa cikin rawar baki ta daga hannu ta nuna Nana tana "Kina nufin Salisu mijinki shine mahaifin Nana shine Wanda yayi wa muhasim fyade ya Kuma karkata mata wuya"?

"Shine Aunty mamy Salisu ne mahaifin Nana shine ya mata fyade ya karkata mata baki"

"Innalillahi wa Inna ilaihi rajiun innalillahi wa Inna ilaihi rajiun Aisha mai mu ka masa da muka cancanci haka daga wajen sa wanan wane irin zalunci ne wanan wane irin cin Amana ne ya rasa wacce zai yiwa fyade sai muhasim shekara sha biyar 'yata sai dai a kwantar a tayar da aure tayi yanzu da tana gidan ta da yaran ta biyu ko uku a gaskiya bazan tab'a yafe masa ba Allah ya Isa tskanina dashi,ko baki kwato mata hakkin ta ba ni zan kwatowa yata hakkin ta wanan zalinci da mai yayi kama?dama ashe fuska biyu ne dashi ba dan Allah yake zaune damu ba dama shine yayi wa muhasim fyade yasan zata iya tona masa asiri shine ya karkata mata baki Allah ya saka min bazan tab'a yafe masa tashin hankalin daya jefa nida yata ba"

Kuka Aunty mamy kawai take tana jin ciwon dake zuciyarta na dawowa sabo fil

Aisha kuwa mik'ewa tayi tabi bayan Yaya mustapha a hankali ta tura k'ofar ta same shi a kwance yayi ringingine idonsa ya Kada yayi jajjir duk jijjiyoyin kansa sun tattashi.

Aisha ganinsa a cikin wanan halin ya Kara karya mata zuciya ta zauna a gefen gadon tana "Yaya ban tab'a sanin haka Salisu yake ba ban tab'a kawo wa zai iya yiwa muhasim fyade har ya iya karkata mata wuya ba, Yaya Salis ya wuce duk yanda nake tunani a jiya daddare na gano mugayen halayensa,a jiya daddare Luba ta tona Masa asiri Ashe tasan shine yayiwa muhasim Fyade ko a fuska bata tab'a nuna min ta sani ba duk daukana ma bata san ya nake da nana ba Ashe duk tasan komai Yaya wlh wlh sai nayi karar Salis a yau ba sai gobe ba sai na kwatowa Muhasim hakkin ta Yaya kayi hakuri ban tab'a sanin Salis zai iya cutar da muhasim ba anjima kad'an zanje nayi kararsa"

Har ta gama magana Yaya mustapha bai ce mata komai ba illa ajiayar zuciya kawai da yake ta saki.

Tasan halin yayanta bazai iya magana ba a yanzu kila sai anjima

Mik'ewa tayi ta fito ta tarar da har lokacin Aunty mamy na kuka.

Umar dasu Kabir duk sun buga tagumi Nana Kuma ta takure waje daya muhasim na Kan keke.

Aisha wajen da mamy ke zaune ta nufa ta ruko hannun ta tana "Ki bar kuka haka Aunty mamy karki damu Insha Allahu karshen zaluncun da Salis yayi mana yazo, zanyi Sharia dashi har sai ya fito ya fadamin abinda yayi wa muhasim bakinta ya karkace tunda har kika ga na hakura da aurensa na rabu da yarana kinsan na shirya dan na kwatowa Muhasim hakkin ta ki bar kuka haka anjima kad'a zan fita nayi kararsa a yanzu kaina ciwo yake min Ina bukatar nutsuwa"

Aunty mamy gyada mata kai tayi.

Aisha ta mik'e tsaye duk da jirin dake dibarta haka taja keken muhasim Nana na biye da ita a baya har suka shige dakin su Muhasim din.

Suna shiga d'akin ta Kai keken muhasim kusa da katifa da dabara ta dagata daga kan keken ta kwantar da ita akan gadon.

Wani irin tausayin muhasim ke nukurkusarta a zuciyarta,sai da ta kwantar da ita ta ruko hannyen ta tasan duk abinda zata ce tana jinta magana ne kawai bazata iya ba "muhasim zan tsaya miki har sai an yankewa Salisu hukunci da ya dace dashi a baya dama ya Dade Yana nemanki"?

Muhasim idonta ta lumshe ta sake bud'ewa.

Aisha lumshe idonta tayi hawayen da take ta san maida wa suka zubo mata.

Ta kwanta a gefen muhasim a yanda take Jin zuciyar ta ji take Kamar ta samo Salis ta raba shi da numfashinsa wani irin tsanarsa take ji a zuciyar ta,tafi jin ciwon abinda yayi wa muhasim akan Luba da ya aura.

Tafi minti talatin a kwance
Shigowar Umar da flask din shayi da kofi yasa ta bud'e idonta sai da ya ajiye flask din yana k'ok'arin fita tace masa ya taimaka mata da wayarta da ta bari a Palo.

Fitarsa da mintuna ya dawo da wayar ta a hannunsa ya mik'a mata wayar.

Ya juya ya fita

Ta kalli Nana dake kwance lamo kamar mai bacci ta bubuga kafarta tana "Tashi ki sha shayi Nana"

Da ido ta ringa bin Nanan har ta sauko daga kan gadon ta zuba shayin ta fara Sha.

Shekara da shekaru tana addua Allah ya tonawa Wanda yayiwa muhasim Fyade ko dan Nana tasan ma waye mahaifinta Ashe Salisu mijinta shine mahaifinta.

Lambar wata hajiya Hauwa ta Nemo a wayar ta,shekara shidda da suka wuce ta hadu da ita a saudiya da taje umara.

Suna mutunci da ita sosai duk da Luba ta koya mata hankali tsoron ma muamalla take da mutane amma hajiya Hauwa haka ta makale mata su ke dan zumuncin sama sama sau biyu ma tana zuwa wajenta,a cikin dan tarihin da ta bata mijinta babban lauya ne a wanan gab'ar ba Wanda zai taimaka mata sama da Hajiya hauwa da mijin nata.

Bugu biyu Hajiya hauwa ta d'auki wayar sai da suka gama gaisawa Aisha ta fada mata tana so ta shigo wajenta akwai taimakon ta da take so tayi.

Hajiya hauwa kuwa ta ce mata sai tazo yanzu zata turo mata address din gidan.

Godiya Aisha ta mata ta katse wayar tana k'ok'arin ajiye wayar yayanta ya turo k'ofar ya shigo.

Luba

A lokacin da ta isa gidan Hamza dak'yar mai gadi ya barta ta shiga dan dagewa yayi masu gidan basu san da zuwanta ba sai da ta hada da hankade shi ta shige ciki tayi cikin gidan da sauri

Gabanta ne ya yanke ya fadi a lokacin da ta hango Hamza ya fito daga gidan Sultan na daga gefensa hanunsa rik'e da wani jaka.

Rabon da ta saka Hamza a idon nata kuwa ta manta ko ba'a fada ba kana ganinsa kasan kudi sun zauna masa dan har wani tumbi ya ajiye.

Dake wa tayi a daidai lokacin da suka karaso wajen da take tsaye

Take murmushi dake saman fuskar sa ta gushe ya hade rai Yana "Baiwar Allah mai kike nema a gidana?

"Ikon Allah bangane mai nake nema a gidanka ba Mai kuwa zan zo nema a gidan ka wajen yarana nazo"

"Yaran da kika watsar dasu tun suna Yara Kika zo neman su a yanzu"?

"Hamza kaga baka fa isa ka rabani da yarana ba naga baka da burin daya wuce kaga ka rabani dasu Kuma ba mai yuwa bane dan ni na Sha wahalar cikinsu na haifesu wajen yarana nazo na musu kwana biyu"

Wani irin murmushi Hamza yayi Yana "Bazan rabaki da yaran ki ba amma ki bari su ringa zuwa wajen da kike ko ki tsaya daga waje su zo su Same ki daga yau kar ki Kara taka kafar ki ki shigo min gida kije daga waje yanzu zasu zo su Same ki"

"Ni hira nake so nayi da yarana na samu lokaci da su ko kwana biyune nayi dasu kafin na koma gidana"

"Sai dai ki tafi dasu bazan hanaki ba amma batun wai ki musu kwana biyu a gidana ba Mai yuwa bane dan Allah juya kifita"

"Umma mu je daga wajen bari na Kira ilham"

A takaice Luba tana ji tana gani Hamza ya koreta waje sultan da ilham kuwa suna gaisheta sama sama Sultan yace mata zai bi Abbansa zasu je unguwa daga haka ya shige cikin mota bai ma saurareta ba ballantana ta samu kudi a wajensa.

Ilham kuwa tana ganin Sultan ya tafi itama tacewa Luba zata shiga daga ciki tana taya Maminta aiki ne ta gaida gida.

Luba kuwa bata iya motsawa ba sabida tsananin bakin ciki ta kasa yarda yaran da ta Haifa a cikinta ne suke nuna mata halin ko inkula bata ga alamar soyayyarta a idonsu ba.

A yanzu wajen da zata kwana kawai take nema kafin gobe tasan yanda zata je gidan asabe ta bata kudadenta.

A.haka tayi ta bulayi a karshe sai a shagon abokin kaninta Sadi taje ta roke shi akan zata kwana dan a hanya ta had'u dashi Yana gaisheta ta roke shi akan ya nema mata wajen kwana kafin gobe.

Hakane yasa ya mata tayin shagonsa.

D'akin Nasa ba kintsi katifar wata mitsitsiya Luba kuwa har da kukan ta dan ko a mafarki bata tab'a kawowa wai zata tsinci kanta a cikin wanan halin ba.

Yunwar da take ji yasa bata tsaya cutar kanta ba ta d'auki furar da ya kawo mata ta kafa Kai ta kwankwade

Ya riga yace mata zai je ya nemi wani wajen ya kwana.

Tana Shan furar taji jikinta ya mutu a haka ta kwanta tana Jin bacci bacci.

Ido biyu ido rufe haka ta kwanta tsawon awa biyu tana kwancen ba bacci take ba amma jikinta a mace yake ko daga hannunta Bata iyawa.

Turo k'ofar dakin taga anyi a hankali a cikin duhun tana iya ganin gambon ya shigo cikin sanda ya hau tube kayansa.

Gabanta ne ya yanke ya Fadi so take ta mik'e tsaye amma ta kasa so take ta Masa magana yasan idonta biyu amma ta kasa kar dai saan dan cikinta ke san yi Mata fyade yaron jikinsa duk kyazbi ne hasali ma Almajirine.

Tana kallonsa ya gama tub'e kayansa yazo ya haye kanta.....

Sister's duk wacce batayi anfani da sabulun mg's ba ko kit dinsu inamai shaidamuku anbarku acan baya domin duk wnd yajaraba mg's sai sanbarka duk wani Mai tantama Akan kayan gyaranjiki toh tabbas yacire sabulun mg's domin yahadu bakarya zegyarajiki yafidda dattin fata Dama duk wani matsalan fata duk Wanda kefama da matsalan fata walau pimples ko spot, sunburn acne, knuckles,wrinkles,stretch mark dama dukkan wani prblm yajaraba mg's bi'iznillah komai zaizama labari bayan jikinku yy fresh zaisa jikinku yy smooth yadinga glowing,gawanda basa San anfani da Mai zaku iya using sabulun mg's batare da kunbukaci wani Mai b Mai bukata should Chat
08062991549
07046881166
07067210195
Call 08064532391

Team glow♀

Sister's duk wacce batayi anfani da sabulun mg's ba ko kit dinsu inamai shaidamuku anbarku acan baya domin duk wnd yajaraba mg's sai sanbarka duk wani Mai tantama Akan kayan gyaranjiki toh tabbas yacire sabulun mg's domin yahadu bakarya zegyarajiki yafidda dattin fata Dama duk wani matsalan fata duk Wanda kefama da matsalan fata walau pimples ko spot, sunburn acne, knuckles,wrinkles,stretch mark dama dukkan wani prblm yajaraba mg's bi'iznillah komai zaizama labari bayan jikinku yy fresh zaisa jikinku yy smooth yadinga glowing,gawanda basa San anfani da Mai zaku iya using sabulun mg's batare da kunbukaci wani Mai b Mai bukata should Chat
08062991549
07046881166
07067210195
Call 08064532391

Team glow♀

WANAN LITTAFIN NA KUDINE BIYA 500 TA WANAN ACCT 0272061655 WEMA BANK NAFISA NUHU KO KATIN MTN KO AIRTEL TA WANAN LAYIN 08033719070 DOMIN KI MALLAKI NAKI KI MUTANEN NIGER KUMA KU TUNTUBI WANAN LAYIN
+227 96 82 89 84 DUK WACCE TA MIN SHARING NA BAR TA DA *RABBI ZAI FIDDA MIN HAKKI NA DA IZININ ALLAH DOMIN BA YAFEWA NAYI BA*

NI DA KISHIYOYINA

NA SADNAF

PAGE 24

Gambo bidirin sa kawai ya ringa yi a kanta Luba ko hannun ta bata iya dagawa kukan zuci kawai take ta kasa yarda wai yau ita Gambo kazami da take aika idan taje gidan su har kudi take jefa masa akan yaje ya siyo sabulu yayi wanka,kiri kiri take nuna masa kyama sai gashi Wai yau itace ya haye cikinta Yana sarrafa ta kamar ya samu matarsa,doyin da take shakowa a jikinsa da bakinsa da yake dalolo mata da Sunan kiss kawai yasa ta kusa sumewa bazata iya lissafa tsawon lokacin da ya d'auka a kanta ba gashi har lokacin bata da k'arfi bude ma baki tayi magana

wahala yake Mata,yanayi yana hutawa sai da aka kira Sallah asuba ya sauka daga kanta Yana "Hajiya na dade Ina adduar Allah ya kawo min ranar da zaki zo hannuna na dandana zumar ki tunda ga lokacin da kike kyamata ta kina nuna min ban isa na hada kafada da Sadi ba,nake addua Allah ya bani nassara akan ki ko jininki Ina addua Allah yasa na miki ajiyar da zaki ringa gani ki ringa tunawa dani,dan idan kika duba d'akin zaki ga ba kayana a yau naso komawa kauyen mu nabi motar dare sai Kuma Allah ya hadamu na samu cikar burina wanan ya zame miki darasi dan Adam ba abin wulakantawa bane na bar ki lafiya"

Luba hawaye kawai take tana kallon sa har ya fice daga d'akin.

Ta dau tsawon lokaci a haka kafin ta fara dan Jin kwarin jikinta har lokacin kukan zuci take wai gambo da bai wuce saa ilham.ne ya mata wanan cin mutuncin ko Ina na jikinta ma wari yake,yau ita ce rayuwa ya juya da ita haka har ace duk tarin dukiyarta da takardun filayenta ta rasa wajen kwana ta Fado hannun Gambo ya kwanta da ita.

Ba komai a d'akin sai tarkacen kwanuka allo da katifar da take kwance a Kai,taya zata iya fita batare da ta wanke jikinta ko zata daina Jin abinda take ji a kasan ta ba.

Da rarrafe ta hau birkita d'akin dan tsayuwar ma bazata iya ba dak'yar ta samu ruwa a wani karamin buta ba abinda ruwan zai mata a haka ta watsa a gaban ta ta cire dan skirt din ta ta goge duk jikin ta kyankaymin kanta kawai take tana tarar yawu a bakinta sai da ta kara awa daya a d'akin dan sau biyu tana gwada tashi sai taji Kamar iska zai d'auketa da alama magani mai k'arfi gambon ya sa mata a furar.

Sai da ta dan ji dama dama ta mik'e ta fice daga d'akin tana Shan alwashin Nemo gambo a duk Inda yake dan ba abinda zai hana ta daureshi har sai taga gatansa.

Babban burin ta yanzu ta samu wajen da zata cuda jikinta ta wanke jikinta da take Jin ya Kama warin jikin gambo ta samu ta canza kayan jikinta ta tafi gidan Asabe ta bata kudadenta dan bazai yu da uwar kudadenta ta ringa bulayi tana neman wajen zama ba kudin ta na wajen Asabe zasu isheta ta siyi karamin gida ta juya sauran kudin ta yanzu wajen da zata fara zuwa tayi wanka ta canza kayan jikin ta take nema ko a mafarki bata tab'a tunanin Asabe zata juya mata baya ba,yanda Aisha ta Zama tamkar shashasha a wajenta ta ringa mulkarta haka Asabe ta ringa juyata tana mulkarta wani zubin sai taji Kamar ta rabu da ita sai Kuma ta fasa dan Asaben tana taimaka Mata sosai wajen samun cikar burinta,sai gashi daga mutuwar aurenta Asabe ta murzawa idonta toka,rashin basira da hauka ya Kai ta tonawa Salis asiri,sai gashi ita nata asirin ma yafi tonuwa daga lokacin da ya saketa har zuwa yanzu bata Kara samun kwanciyar hankali ba garari kawai take har da almajiri mai doyi da bai wuce saan dan cikinta ba ya mata fyade.

Ba inda zata je dai tayi wankan daya wuce gidan su tasan mahaifinta nada zuciya ko duk mutanen garin nan zata Kai akan a roke shi ya barta ta zauna bazai tab'a sauraran su ba da ace ta tab'a kawowa kan ta irin wanan ranar da ta zage wajen kyautata musu.

Gidan nasu ta nufa dan tasan a yanzu mahaifinta ya fita bazata same shi a gida ba ballantana ya hana ta shiga gidan.

A lokacin da ta isa gidan kuwa bata same shi ba sai Inna da yayarta Habiba da basa ko magana ballantana su hada inuwa daya dan rashin mutunci sosai ta karta mata da ta isheta da waazin abinda takeyi bai dace ba ya zaayi ace iyayensu ma bazata na mutunta su ba.

Ganin ta take matar mai kudi duk girman mutum yayi kad'an ya taka ta hakane yasa tayi wa habiba kaca kaca dan tasan sai dai habiban ta moreta ba ta da abinda zata bata, habiban kuwa ta Sha alwashin fita daga harkarta.

Inna ce kawai ta amsa sallamar da tayi habiba dankwalin kanta ta turo gaban goshinta tana "Mai matar Alhaji tazo nema a gidan talakawa baiwar Allah ko b'atan hanya kikayi"?

Luba ko kallonta bata yi ba ta fara k'ok'arin shiga cikin d'akin.

Inna ta dakatar da ita tana "Luba ki rufamin asiri kizo ki tafi karki jawomin dan wlh Baban ku yace idan har na sake na Kara barin ki kika zo gidanan bai yafe ba Kuma a bakacin Aurena"

Luba juyowa tayi cikin wani irin muryar masifa tana "Inna idan ban zo gidanan ba Ina kuke so naje"?

Ina da sama da kune shikenan dan Aurena ya mutu sai a nemi a wulakantani Inna ko Abba zai koreni ya Kamata ace ki biye mishi har Kina na rufa miki asiri nazo na fita,Ina da iyayen da suka wuce ku ne"

"A yanzu da aka sako ki Kika san kina da iyaye ai mallama kizo ki fice a gidanan ba abinda ya shafe mu da sakin da aka miki sai a yanzu da kika zama sakakiya kika San ma kina da iyaye har ma suna da gidan da zaki zo gidan da kike kyankyaminsa, gidan da idan zaki zo sai da turare,gidan da idan kika zo kike toshe hanci yau shine gidan da zaki zo ki zauna kiyi Zawarci ai wlh baki isa ba ko inna ta bar ki wlh sai na zuga Abba ya koreki ba dai duniya kika zaba ba wlh baki fara ganin komai ba"

"Sai ki bari idan akwai kudinki a gina gidanan sai ki koreni,idan kuma kina da k'arfi zaki iya zuwa ki fita dani, Abba Kuma ko ya koreni wlh sai na dawo ba inda zanje dan shine ya haifeni idan Kuma ya dage bazan zauna a gidanan ba sai ya kaini Inda zai ajiye ni shikenan mutum bazai yi kuskure a yafe masa ba idan ma banda kaddara ma wlh ko labarin sakin nawa ba mai ji kike wani tada jijjiyoyin wuya da kudina karki dauka a wulakance nake ko a yanzu kudin nawa Suka dawo hannuna ko da kudinki kema.kinsan baki isa kizo wajen da nake ba"

"Yayi kyau matar mai kudi kinsan kina da kudinki uban me Kika zo nema a gidan namu ai yanzu ki burgeni kije ki nemi gidan da zaki zauna din sanan duk cika baki kike ki bari Abban ya dawo ya Sameki a gidanan kiga yanda zaki kwashe dashi,ba dai ba abinda Kika sani sama da cin amana da wulakanta mutum ba insha Allahu sai Kinga yanda karshen ki zai yi duk wani mugun Abubuwan ki da kike yi a boye duk nasani kallon ki kawai nake domin shi sharri dan aike ne Allah ya baki dama duk kin tsulla tsiyar ki a yanzu lokacin da zaki girbi abinda kika shuka ne"

"Ai insha Allahu kuwa bazaki ga karsshena ba sai dai ni naga karshen ki mugun halin ki yasa bakya cigaba kina nan shekara da shekaru kina fama"

Mik'ewa Habiba tayi da sauri tayi kan luba,Inna ta mik'e da sauri ta tareta tana bata hakuri.

Luba kuwa taja tsaki ta shige daki ta tub'e kayan jikin ta ta jawo soso da sabulun inna dake kasan gado ta fito da daurin kirji sai da ta cika katon bokiti da ruwa ta shige bandaki.

Sai da ta kusa karar da duka sabulun a jikinta dan har yanzu tana Jin warin jikin gambo a jikinta tana Jin Inna da Habiban suna ta magana idan ba kaddara ba mai zai ma kawota har da Habiba zata samu damar mata maganganun banza.

Alwala ta daura ta fito,dan bata yi ma sallah asuba ba gashi ta fara Jin Kiran sallah azahar,kayan ta ta Kara wankewa ta shanya dan bata da kayan sawa dole su zata maimaita dan kayan inna bazasu tab'a shigar ta ba dan tafi Inna kib'a.

Salis ya cuceta da ya hanata d'aukar komai har wayata bai bari ta d'auka ba,bata tab'a zaton zai iya mata rashin mutunci da ya kai haka ba yau da ko iya kayanta ya bari ta kwashe dan kunnenta da sarka kawai sun isheta ga kayanta da duk masu tsada ne wa ma zai yarda motocin ta sun Kai biyu taya ta gama dandana irin wanan daular shekara da shekaru a cikin Rana daya ta zama abin tausayi har da kwana shagon da ko mai gadin gidan Salis bazai iya kwana a d'akin ba ta karfin tuwo sai ta komawa Salis idan bata koma ba gwara ya zauna shi kadai dadin abin Ba Asabe kadai tasan hanyar wajen mallamin ba itama zata iya zuwa duk da Rabin zuwan Asabe ke zuwa, bama tabin ta Kan mallaman sosai Asabe ke mata sintirn zuwa tana cazarta kudade masu yawa

Sai da ta iddar da Sallah ta fito daga d'akin fuskarta a hade tayi hanyar Kitchen dan wani irin yunwa take ji rabon ta da abinci mai kyau tun a gidan Salis.

Tana Jin Inna na ta fito mata daga kitchen

Tukunyar dake kan gawayin ta bud'e.

Tuwo ne da miyar kuka da alama na jiyane aka dumama sauko da tukunyar tayi gabad'aya ta zauna a kitchen din ta fara ci hawaye na taruwa a idonta rabon da taci wai abinci ma ba nama har ta manta ta Kuma Saba din idan abinci akayi ba nama bata iya ci .

Sai da ta Kai hannu taji babu komai ta cire hanunta daga tukunyar ta wanke hannunta ta fito daga Kitchen din.

Da alama Habiba ta tafi dan bata ganta ba Inna kawai ce a tsakar gidan ta hade rai tamkar yanda itama ta hade ran.

A d'akin Inna tayi zaman ta har sai da kayan ta suka bushe ta debo su daga Kan igiya ta saka kayan ta fito wajen Inna tana "Inna zanje wajen Asabe akwai kudadena da yawa a wajenta idan ta bani zan siyi karamin gida nayi zawarcina kawai dan nima nasan na girma da dawowa gida nayi zawarci banda Salis ya hanani d'aukar komai iya zobuna na da sarkokina sun isa na siyi gida har na juya sauran kudina nima Zan fi sakewa ingani a gidana ni kadai idan Kuma Allah ya taimakeni na koma dakina shikenan idan Kuma Asabe ta hanani kudina dole na dawo kuyi hakuri balle ma nasan dole ta bani kudina dan har station sai munje a Kan kudin nan.

"Ba zancen dole sai kin dawo bane muyi hakuri ni dama banida matsala Mahaifin ku ne dai yace bazaki dawo ba Kuma da kina da hankalin Kamata yayi kiyita bibiyarsa kina neman yafiyarsa har sai ya sauko amma dayake bakida hankali yanda zaki siyi gidan da zaki zauna kike nema wato munyi kadan ma ki bimu ki bamu hakuri,ni uwa ce bana so nayi munanan kalma a kanki sai dai nace Allah ya ganar dake gaskiya dan idonki ya riga da ya rufe"

"Inna wane irin hakurine ban bawa Abba ba jiya naga har kuka na ringa masa haka ya rufe ido ya koreni dan kawai ya ga na zama bazawara a lokacin da nake da kudina da mutuncina ai Bai min haka ba"

"A inda na Kara sanin bakida hankali kenan a lokacin da kike da kudin wa Kika bawa Mai Kika tab'a masa nuna min wani abu a gidanan da zaki ce ke kika kawo Kinga zo ki tafi bana san hayaniya lubabatu.

Luba waje tayi tana Jin wani sabon b'acin rai sabida kawai bata zo da nauyinta ba suke mata haka.

Tana fita titi ta samu abun hawa ta shige tare da fada masa Inda zai Kai ta dan ta d'auko dubu uku a cikin jakar Inna a yau ko ita ko Asabe.

Tafiyar minti goma ya karaso da ita gidan Asaben ta bawa mai machine din kudinsa ta fara kwankwasa gate din gidan Asabe bata san halinta bane a yau sai ta tara mata jama'a ta bata kudinta.

Bugun da take da k'arfi yasa mai gadi yazo ya bud'e k'ofar Yana ganinta ya fara k'ok'arin Mai da k'ofar ta kuwa hankada shi da karfinta tayi cikin gidan dan tasan karnukan suna cikin kejin su.

"Da gudu tayi cikin gidan mai gadi na binta a guje Yana tazo ta fita hajiya tace idan tazo Kar a bar ta ta shigo.

A kusan tare suka shiga palon ta kame kugunta dan ko ita ko Asabe.

Asaben dake Kan dining tana waya ta juyo tana kallon Mai gadi dake k'ok'arin fita da Luba katse wayar tayi ta mik'e tana "Jeka abin ka idan zata min hauka zan kiraka kazo min da karnukan"

Juyawa yayi ya fice
Asabe ta nufo wajen da take tsaye tana murmushi da kofin tangaran a hannunta.

Luba ido kawai ta zuba mata tana kallon yanda take walwali a cikin less dinta da ta siya da tsada ko sawa bata tab'a yi ba ta neme shi sama ko kasa ta rasa ashe Asabe ce ta d'auke Mata.

"Bazawara lafiya mai kike nema a gidana ko kin zo ki kwace min mijine tunda aurenki ya mutu"?

"Asabe wanan ba less dina ne a jikinki ba"?

kallon jikinta tayi ta dago da murmushi tana "Idan less din naki ne zaki iya kwata ne"?

"Asabe dama wai haka kike duk tsawon lokacin nan da na daukeki kawa aminiya Yar uwa Ashe fuska biyu ne dake,ki rasa wacce zaki wulakanta sai ni yau duk abinda kike takama dashi Asabe naga nawane baki tab'a tambaya ta abu na hanaki ba sai dan yanzu Aurena ya mutu nace zan zauna a gidanki zuwa wani dan lokaci kafin na samu na yi aiki akan Salis ya maidani gidana Kika fititike kika koreni har da rakiyar karnuka Asabe na cancanci haka daga wajen ki"?

"Luba nayi abinda zanyi ki dauki mataki a kaina har me kika min da zaki zo kina min ihu a ka gidana ne nace bazan bari ki zauna a gidana kimin kwacen miji kamar yanda Kika kwacewa kawarki ba ni ta daban ce da bazaki kwace min miji ba?halinki ne bansani ba ayi miki saki uku dan ke dakikiya ce kice zaki koma na bari ki zauna a gidana kafin na ankara nida mijina tsalle tsalle ne dashi ya hango wanan hancin naki daya cike miki fuska ya auro ki Luba na koreki bazaki zauna min a gida ba na sake fada a yanzu ma ki fitar min daga gida"

"Bani kudina kafin na fitar miki daga gida ai bakida ma gidan da zanzo kudina dake wajenki zaki bani"

Wani irin dariya Asabe ta kece dashi ta ajiye kofin hannun ta a center table ta mike tana "wane kudinki ne a wajena wane kudi kike magana"?

"Miliyan biyar da na baki ajiya da Dubu dari shidda da kikace mu hada muyi sarin Kaya su nake magana ki bani kudina na bar miki gidanki"

"Baki da kudi a wajena luba kudin ki anyi order Kaya Kaya Kuma basu iso ba ba dole na miki Kika kawo min kudinki ba dan haka bazaki zo ki daga min hankali ba"

Wani irin cakuma Luba ta kaiwa Asabe tana "Idan kin isa Allah ya tsine min albarka wlh wlh sai kin biyani kudina biyar dita bazata yi ciwon Kai ba kinji ma na rantse miki wlh idan ta kama har police station sai munje kin biyani kudina"

"Ki cikani Luba"

"Bazan cika ki ba sai kin bani kudina wlh mai ma nake batawa kaina lokaci ai nasan hanyar dakin ki wlh sai na birkita na dauko kudina barauniyar banza barauniyar wofi"

Ta saki Asabe ta fara k'ok'arin yin hanyar dakin Asabe

Asabe tace "Luba sirrinki kaf a tafin hannuna yake a yau ba sai gobe ba a yanzu gidansu Salisu zanje wlh duk sai na tona miki asiri kinsan Kuma Mai hakan ke nufi Kare rayuwarki zakiyi a kurkuku dan nasan ba abinda zai Hana shi daure ki kinsan Kuma nasan daya sirrin naki da idan na fada ba iya Salis ba idan duniya suka San abinda kika aikata kenan ko fitowa bazaka iya yi ba"

Luba a hankali ta juyo ta dawo da baya jikinta na d'aukar wani irin rawa kirjinta Kamar ya fado ido ta zubawa Asabe hawaye na wanke mata fuska

Asabe ta saki murmushi ta koma ta zauna tana "Duk wata kiringa kawo min Dubu hamsin a duk ranar da kika tsallake baki.kawo ba a ranar zan bankada sirrinki"

"Asabe mai na miki dana cancanci haka daga wajenki?Asabe ki cinye min kudina iya haka bai ishe ki ba sai kince na ringa kawo miki Dubu hamsin hamsin a Ina Zan samo dubu hamsin idan dan kudina Yana wajenki Kika b'ullo min ta haka Zan hakura da kudin Allah ya saka min zaki biyani acan lahira dan ba yafe miki nayi ba"

"Daga baya kenan na cinye kudi Luba yanzu kudi zaki ringa biyana na rufin asirin ki"

"Asabe mai na miki dana cancanci haka daga wajenki Asabe duk wani kudi da nake takama Ina dashi Yana wajen ki, duk sauran kudina suna banki Salisu ya hanani wayata ya kulle min acct jiya a shagon Almajiri na kwana biyar bani dashi Asabe Ina cikin irin wanan tashin hankalin zaki bullomin da maganar tonan asirina ko kudi"

"Zabi ya rage naki Luba ko kudi ko rufin asirin ki"

Kuka.luba ta fashe dashi tana " a Ina zan samo Miki kudi Asabe"

"Ba abinda ya shafeni ko kudi ko fallasar sirrinki idan ba kudi Kuma azo a ringa min aiki na kori Yar aikina ki maye gurbin ta kafin mijina ya dawo duk kin gama aikin ki sai ki tafi"

"Ke zanzo na ringa yiwa aiki Asabe"?ni Luba zanzo na ringa miki aiki sabida kawai kin san sirrina zaki tona min asiri ki rasa wulakancin da zakimin sai na zuwa na ringa Miki aiki"?

"Aiki ko Dubu hamsin sai ki zab'a"?

Asabe ta mik'e tayi hanyar waje tana kwalawa Mai gadi Kira.

Aisha

A gefen gadon Yaya mustapha ya zauna tare da dafe kans shiru ne ya ratsa d'akin sai da aka kwashi tsawon mintuna Yaya mustapha ya dago da jajjayen idonsa ya fara magana yana "Har yanzu na kasa yarda Salisu mijinki zai iya aikata irin wanan danyen aikin Aisha,na kasa yarda zai iya haikewa diyata da ta kasance ya a wajenki"?

Na kasa yarda zai iya irin wnan cin amanar?na kasa yarda shi yayiwa muhasim Fyade ya karkata mata wuya"?

Aisha karki.manta irin Fadi tashin da ya ringayi a lokacin da muka gano muhasim anyi mata fyade Aisha ko da zai yiwa kowa haka ban cancanci ni yamin haka ba dan.na d'auke shi tamkar kanina,shekara Sha biyar muhasim tana fama da wuya a karkace nine can nine Nan a nemowa muhasim magani,tunda muhasim ta Shiga halin nan nayi bankwana da duk wani farinciki ke kanki shaida ce a irin wuyan neman maganin da nake duk Rabin kudina a nemawa yata magani Aisha ace duk abinan mijinki Salisu shi ya jefa mu a cikin wnan halin"?

Yaya mustapha ya karashe cikin wani irin murya da ji kukan zuci yake

Duk maganar nan da yake Aisha kuka kawai take.

Sai da ya idda ta dago tana "Yaya shi yasa nace ma sai na yi kararsa wlh sai na kwatowa Muhasim hakkin ta ya cutar damu ya cutar da Muhasim zaluncin yayi yawa Yaya wlh sai nayi kararsa sai na tona masa asiri duniya tasan wanene shi"

"Aisha kiyi kararsa ko ki tona masa asiri bazai canja abinda ya riga da ya faru ba,yau badan ke ba nida kaina sai nayi kararsa bazan yi haka ba dan ba iya sunansa ne zai b'aci ba har da naki tunda kinriga da kin hada zuria dashi bazan yarda kiyi kararsa ba abu daya kawai zaki min shine ki ce ya fada miki abinda yayi wa muhasim wuyanta ya karkace burina yata ta dawo daidai idan ya fada miki shikenan banida matsala dashi.....

Ammnur _kayan mata tazo muku da zafafan kayan matan da babu algus 09080070762

Ina uwargida da ta haihu vjay dinta ya bude tana bukatar taji ta koma budurwa gam ga ammnur Nan ta kawo muku zafafan kayan mata Ina amare masu Shirin shiga daga ciki,Ina Zawara da suke so suji Basu da bambanci da budurwa

Enjoyment doesnt stop just because you have given birth. The afterbirth package is made to take care of you postpartum sexual needs . This package includes sweetner, wetner, tightener infection afterbirth herbs and more

Prices

Sauran kaya da zaki duba a wajen su na qara niima dadi da matsi sanan akwai na tsuma jiki na mata da na amare da uwargida Wato Madame package, suna da kayan farinjini, favour da kuma mallaka

1)Euphoria 12
2)Gorontula syrup
3)Her exellency cake
4)Exclusive thumi
5)Milky sweety
6)Magic insert
7)Tightening mallaka saop
8)Tightening honey pill
9)Women 001
10)Ebony lady
11) spiced tea
12)Mallaka chicken soup
13)Tightening powder
14) wetness powder
15) favour set
16) attraction set
17) bakar mallaka
18) shu'umar mallaka
19) hatsabibiyar mallaaka

20) horney honey syrup
21) libido booster set
22) breast enlargement
23) hips enlargement

HUMKAM INCENSE gidan kamshi da maganin mata muna turaren wuta na tsuguno Wanda yake matse HQ sosai Yana karawa dandano Yana maganin infection kowani iri muna da shuumar humra, hatsabibiyar turare,bita zaizai Mai abin mamaki munada turauka na daukar hankali
08132506044
TILL WE MEET*
ZARATY WANNAN HMMMM YA HADU NACE YA HADU SHIN KINTAVA AMFANI DA TURAREN DA ZAISA MIKI LAUSHIN FATA? KINIMI ZARATY YANA DA KAMSHI DA RIKE JIKI YANASA FATA LAUSHI TURAREN KOWA
Jas oud 3 IN 1 ZAKI TURARA GIDAN KI DASHI JIKINKI DA KAYANKI JAS OUD YA HADA ABUBUWA DA DAMA YANA RIKE JIKI SOSAI YANS KAMA GIDA YANA RIKE KAYA
AKWAI HUMRAR MOWA GUMBAR MOWA GARIN MOWAR TSUMIN MOWA DAN MATSI
SHU'UMAR HUMRA NA MANYAN MATA MATAN DA SUKA SAN KANSU SIRRINKI A SHIFIDAR DAKIN MAIGIDAN KI MUNADA SHUUMAR TSUMI
*DESIRE MAINE DA YAKE SAKA JIKI DA GASHI KAMSHI SOSAI IDAN KINA BUKATAR GANIN PHOTON KAYANA KIMIN MAGANA NGD
AKWAI SABON TURARE ME MATUKAR MUHIMMANCI ACE DUK WATA MATAN AURE DA TAKE DA HALI TA MALLE KESHI (NI DA MIJINA) SHINE SUNAN SA,SAI MOWAR MACE TURARENWUTA NA TSUGUNO YANA MATSE JIKIN MACE YANA MAGANIN INFECTION YANA DAUKE WARIN GABA YANASA KIJI CIKIN JIKINKI YA MATSE SOSAI YANASA KAMSHIN HQ

WANAN LITTAFIN NA KUDINE BIYA 500 TA WANAN ACCT 0272061655 WEMA BANK NAFISA NUHU KO KATIN MTN KO AIRTEL TA WANAN LAYIN 08033719070 DOMIN KI MALLAKI NAKI KI MUTANEN NIGER KUMA KU TUNTUBI WANAN LAYIN
+227 96 82 89 84 DUK WACCE TA MIN SHARING NA BAR TA DA *RABBI ZAI FIDDA MIN HAKKI NA DA IZININ ALLAH DOMIN BA YAFEWA NAYI BA*

NI DA KISHIYOYINA

NA SADNAF

Aisha

"Yaya Salisu bai cancanci rufin asirin mu ba Yaya idan har zai iya Mana wanan cin amanar ya Rasa wacce zai nema sai muhasim yaya bai tsaya iya nan ba ya hada da karkata mata baki sabida Kar ta tona masa asiri zaluncin yayi yawa karka ce zaka yi hakuri sabida ni idan kayi haka bazan ji dadi ba muhasim itama 'yace Kamar kowa ka bari mu kwatar mata hakkin ta karka ce wai sabida ni baka so ayi karar sa mutuncinsa ya zub'e,
Yaya mutuncinsa ya riga da ya zub'e a lokacin da Luba ta tona masa asiri a gaban yayansa,Yaya kila ba iya Muhasim Salisu ya tab'a yiwa irin wanan zaluncin ba kila ya dade yanayi gwara ayi kararsa asirinsa ya tonu sabida a a ceto wayanda zasu Kara

fadawa tarkonsa Yaya idan har Salis zai iya neman maza bai cancanci a rufa masa asiri ba Luba duk ta tona masa asiri a wajena ban tab'a sanin mugu nake aure ba wlh irin su Salis a cikin Al umma masifa ne gwara kawai muyi kararsa a kwatar mata hakkin ta"

ido Yaya mustapha ya zuba mata har ta idda magana yana "Kina nufin Luba ce tace miki Salis ne yayi wa Muhasim fyade Kuma har ya karkata mata wuya Yana neman maza Kuma"?

"Itace ta tona masa asiri Yaya"

"Kuma ya amsa da bakin sa shi yayi wa muhasim fyade"?

"Eee Yaya yace Nana yarsa ce da bakinsa ya amsa haka"

Sai da yaya mustapha ya d'au tsawon lokaci kafin ya mik'e Yana " idan har da gaske shi ya amsa da bakin sa shine mahaifin Nana zan yarda amma banaso ayi abin da zamu zo daga baya Muna Jin kunya dan wanan Luba tun daga lokacin daya aureta nake ce miki ban yarda da ita ba,a yanda nasan tsanar da ya mata har Yana fadamin lokaci daya naji labarin auren sa da ita nasan akwai boyayyen Al amari da Allah kawai ya barwa kansa sani ki nutsu muyi bincike mai kyau nayi mamaki da ya iya aikata irin wanan mumunan abin da nake ganin da hankalinsa bazai tab'a aikatawa ba kila Kuma San zuciya ya Kai shi da aikata haka"

"Yaya ka daina k'ok'arin kare shi ya riga ya amsa da bakin sa shine mahaifin Nana Kuma wlh Yaya shi ya karkata mata baki sabida kar ta samu bakin da zata tona masa asiri"

"Ya akayi toh luba ce tasan sirrin nashi"?

"Ba Wanda yasan wanan sirrin sai ita kenan?akwai abinda nake san kema ki hango da kanki amma a yanzu lafiyar muhasim shine a gabana shine burina koma menene Allah ya bayyana mana gaskiya bazaki yi kararsa ba ki tambaya min shi kawai idan dai Yana da sa hannu karkacewar wuyan muhasim dan gani nake idan har ya amsa shine mahaifin Nana idan shine zai iya fada ya ce sabida rufin asirinsa yayi haka a lamarin nan ya Kamata ace bincike akayi mai zurfi Aisha batun tona masa asiri bai taso ba ko dan su Ashraf nima bazan so mutuncin babansu ya zub'e ba"

Yaya wlh "

"Ya isa Aisha ban yarda ayi kararsa ba zan nemi Ashraf muyi magana dan idan nace yazo kunya bazai bari yazo ki bar maganar kai shi karan nan kawai"

Daga haka ya fice daga d'akin Aisha ta bishi da kallon mamaki dan bata tab'a tunanin zai hanata Kai shi kara ba har bayan wanan cutar da ya musu ace a barshi ba sai an kai shi Kara ba,duk abinan tasan sabida baya so mutuncin Salis ya zub'e ne Salis bai cancanci wani rufin asiri ba tunda har ya iya cin amanar yayanta.

Kiran da ke ta shigowa wayarta ya katse mata tunanin da ta tafi.

Koda ta d'auko wayar Salis ke kiranta

Katse Kiran tayi tare da jan dogon tsaki sai a lokacin taga alamar ya tura mata sako kamar zata goge dan ko kadan batasan wani abu daya dangance shi, sai Kuma ta

fasa ta bud'e message din "Aisha ki rufamin asiri karki gayawa Yaya dan Allah karki fada masa Aisha wlh sharrin shaidan ne ni kaina bansan ya akayi na nemi muhasim ba idan kin tuna a shekarun baya da na ringa kasancewa cikin tsananin bukata har lokacin muke mamakin yanda akayi na koma haka,a lokacin ne wanan kaddara ya fada min a ranar da kikaje asibiti idan Zaki iya tunawa abin ya motsa min kamar zan fice a hayyacina na dawo gida ban tarar dake ba na kasa dannewa bansan mai ya hau kaina ya jani nayi wa muhasim fyade sai da na dawo daidai na gane abinda na aikata wlh wlh ba da gangan na nemeta ba kimin adalci ki tuno yanayin da nake Shiga Kamar zan mutu idan ban samu nutsuwa ba ki tuna Aisha da ace ni mazinaci ne da zaki tab'a Kamani Ina neman mata da a lokacin bazan addabeki ba zan na zuwa wajen wasu su magance mun matsalata ne amma haka nake dawowa gida,da ace a ranar nasan bazan same ki ba bazan dawo gida ba da ace nasan ranar bazan same ki a gida ba wlh na gwammace na nemi koma wacce da na nemi muhasim,daga lokacin da abinan ya faru ban Kara samun nutsuwa ba kema kin Sha tashi ki gani a zaune Ina tunani,amma ki yarda dani bayin Kai na bane Kuma wlh Allah bani da hannu a karkatawar bakinta idan har nine tunda asirina ya riga da ya tonu zan fito na fada miki"

Aisha tsaki tayi ta goge message din tare da danna masa blocking dan ta riga da tasan tsara zancensa yayi karya yake yi,daga lokacin da ya auri Luba ta daina yarda dashi,ba abinda zai yi a idonta taga farinsa tariga da tasan zaiyi duk yanda zaiyi dan.ya wanke kansa bata yarda bashi ya karkata wa muhasim baki ba.

Sallamar Afrah da ummi da taji a Palo yasa ta zubawa k'ofar ido har suka turo k'ofar suka shigo,da ganin Afrah taci kuka ta gode Allah.

"Hajiya umma dan Allah kiyi hakuri mu koma gida"

Cewar ummi ta zauna a gefen gadon

Afrah Kuma ta zauna a kasa ta tankwashe kafarta tana "Hajiya umma Abba ne ya turo mu akan mu baki hakuri dan Allah hajiya umma ki dan saurareshi yanzu haka mun baro shi bashida lafiya"

"Bazan goyi bayan zalunci ba Afrah ke ba yarinya bace kingane duk abinda ke faruwa ki koma ki fada masa ya gaya miki abinda yayi wa muhasim wuyanta ya karkace idan har bai fada ba dole nayi karar sa ya fada a kotu,duk da Yaya ya dage amma bazan biyeshi ba,sabida muhasim bata cancanci haka daga wajen mu ba itama ya ce kamar kowa zan tsaya na kwato mata hakkin ta shekara Sha biyar sai dai a kwantar a tayar sa'ointa daga masu Yara uku sai biyu wlh bazan yafe masa wanan zalincin da ya mata ba"

Ta karashe tana fashewa da kukan dake dankare a zuciyarta na tausayin muhasim a baya bata ji tausayin ta haka ba sai da ta gano Salis ne yayi wa muhasim fyade.

Yaya mustapha yana fita daga d'akin ya fita can waje ya zauna ya zauna akan benci Yana kara nazartar maganganun Aisha baisan mai yasa ya kasa yarda da duk Salis ne ya aikata wa muhasim wanan zaluncin ba banda Aisha tace ya amsa da bakinsa akan shine mahaifin Nana da ya karyata,akwai abubuwa a baya da yake kara tunawa game da Salisu,ya sha zargin asiri Luba tayi masa ya aureta,idan ya tuna yanda yake fada masa.
ya tsani Luba tashi daya yaji labarin wai ya aureta, anya Luba ba burinta taga ta raba Aisha da salisu ba yasa ta biyo ta haka akwai Abubuwan da yake so Salis ya warware Masa da kansa.

Wayarsa ya d'auko a Aljihu ya nemo lambar Salis yayi dailing.

Sai dai har ya masa kira uku bai d'auka ba sai text din sa daya shigo da "Bazan iya d'aukar wayar ka ba Yaya kunyar ka nakeji bansan mai zance ma dan Allah dan Annabi ka yafe min"

Yaya mustapha mayar da wayarsa yayi cikin Aljihu ya shiga ciki ya d'auko mukullin motar sa ya tayar ya nufi gidansu Salis.

Luba

Da mugun sauri ta damko Asabe ta shaketa tana "Kinyi kad'an Asabe kinyi kad'an ki wulakanta ni,bazan baki ko sisina ba Kuma bazan miki wanke wanke ba wlh kin Dade baki tona min asiri ba ai bani kadai keda asirin da zaa rufa ba kema kina da sirrin da zan tona miki ko kin manta mu taru mu tonawa juna asiri mu ji kunyar gabad'aya har ni zaki ce nazo na ringa miki wanke wanke kinyi kad'an na miki wanke wanke ki tona min asiri na tona miki naki kudina Kuma da kikaci wlh sai ma kin biyani"

Asabe murmushi ta saki tana "Luba na wuce duk yanda kike tunani zan baki mamaki wlh sai na tona miki asirin,asirina da kike cewa zaki tona ba na kashe kishiyata bane na saka mata guba a shayi ta sha ta mutu,wa zakije ki fadawa ya yarda?

Wajen Wanda zaki tona min asirin kinsan kamun da na masa?

An gaya miki bansan zakice zaki iya tona min asiri ba lailai yanzu na Kara yarda ke dakikiya ce tunda har kince bazaki min wanke wanke ko ki ringa biyana dubu hamsin ba a yau zan tona miki asiri kina fita Zan dau mayafina wlh duk sai na bankada sirrinki kije ki bankada nawa"

Luba a hankali ta saki rigar Asabe hawaye na gudu a fuskarta tace "zan ringa biyan ki dubu hamsin din amma kiyi hakuri na samu a yanzu banida hanyar samun kudi ko biyar bana magani kudadena na wajenki sauran kudina da kaddarata Kuma salis ya hanani"

"Wanke wanken ne dai bazaki iya min ba"?

"Zabi kika bani na gwammace na ringa biyan naki"

"Ina nan Ina jiranki wlh naji shiru kinsan halina na daga miki kafa a watan nan karshen wata naji dumus"

Luba bata iya ce mata komai ba ta juya tayi hanyar waje tana Jin Asabe na mata dariya

Tana fita ta fashe da kuka sai da taci kukan ta ta gode Allah kafin ta tsayar da abin hawa ta nufi gidan Salis tana Addu'a Allah yasa baya gidan dan so take ko yaya ne ta dauko sarkokinta da dan kunne da kayanta masu tsada tana da ma ajiyayyun kudi a d'akin tunda har Asabe ta hanata kudinta bata da zabin daya wuce taje gidan Salis idan har ta samu ta kwaso kayanta ta samu nutsuwa sai tasan yanda zata biyo wa Asabe tunda har tayi mata haka zata bata mamaki"

A lokacin da ta isa gidan kasa shiga tayi sai da ta tambayi maigadi ko Salis na nan yace mata dazu ya fita baya nan.

Da sauri ta shiga cikin gidan dan tasan ba wanda ya isa ya hanata kwasar kayanta.

Tana shiga tayi hanyar dakinta gadan gadan.

"Ikon Allah wa nake gani haka lafiya mai kike nema a gidanan shin ba An sallameki ba"

Da wani mugun kallo ta bi Hindatu da ta fito daga kitchen taci kwalliya da wani uban less wato murna ma take ta bar mata gidan

Tsaki taja ta bud'e k'ofar zata shige Hindatu tayi sauri ta bi bayanta tana "Mallama zo ki fita wlh ba abinda zaki d'auka umarni ne daga wajen mijina yace na bar miki sai ya sab'a min".....

Tafiya nayi wlh muna biki sai nine na samu kaina ayi hakuri dan Allah

 in ka ji busa tabbata Sarauniya ce ta ƙaraso, ina kuke matan ƙwarai, mata ba muna mata ba, shin kin jaraba kayan *HONEY-DROPS* me kike jira har yanzu?, Manyan mata, mata masu aji na ta dafifi wajen kwasar kayan gyara, me ya sa za ki kashe kanki da ƙuruciyarki, ko tsohuwar ma na zuwa karɓar nata, kina fama da matsalar bushewar gaba, ɗaukewar sha'awa da ni'ima, ƙaiƙayi ko ƙurajen gaba, jin zafi yayin tarawa da maigida, sanyi ya taɓa miki mahaifarki?, Kina ta allura da shan magunguna ba su miki aiki ba, wane kalar infection kike fama da shi?, Staphylococcus, Gonorrhea, Syphilis, UTI, STDs ne?, Share hawayenki kukanki ya ƙare je ki nemi *HONEY-DROPS INFECTION FLUSHER* ke da sanyi sai dai ki ba da labari, kin gama cacar kuɗi, cikin kwana uku zaki fitsarar da duk wani sanyi da dattin da ke tattare a mararki, ki gyara zamanki gidan aurenki don sanyi kashe mace yake har buzunta, duk wani magani da za ki sha muddin da sanyi a jikinki iyakar shi cikinki, ba zai sauka ba. Magani ne ingantacce made of herbs, In kin gama da wannan akwai na gyaran other room, akwai Exclusive Gumba ta manyan mata ke nan, ko matar Gwamna ita take sha, ga Gumbar babbar mace mai tada tsohuwar soyayya, akwai fa tsuumi na matan gaske, akwai *HONEY FLOOD TSUUMI* kan ƙiftawar ido ni'ima ta yi ta kwararo miki, akwai BUJENTA JAGAB, da Tsuumin Ɗafau, daga jin sunan kun san akwai zance na bar muku ku ƙarasa, akwai sauran kaya masu zafi

Muna da bridal package

Diamond - 100k
Gold - 50k
Silver - 30k

Ga kuma na postpartum (wanda suka haihu don dawo da martabarsu)

Diamond - 50k
Gold - 30k
Silver - 15k

Kuna iya samun mu ta 08167888934, ko 08067770852

Sister's duk wacce batayi anfani da sabulun mg's ba ko kit dinsu inamai shaidamuku anbarku acan baya domin duk wnd yajaraba mg's sai sanbarka duk wani Mai tantama Akan kayan gyaranjiki toh tabbas yacire sabulun mg's domin yahadu bakarya zegyarajiki yafidda dattin fata Dama duk wani matsalan fata duk Wanda kefama da matsalan fata walau pimples ko spot, sunburn acne, knuckles,wrinkles,stretch mark dama dukkan wani prblm yajaraba mg's bi'iznillah komai zaizama labari bayan jikinku yy fresh zaisa jikinku yy smooth yadinga glowing,gawanda basa San anfani da Mai zaku iya using sabulun mg's batare da kunbukaci wani Mai b Mai bukata should Chat
08062991549
07046881166
07067210195
Call 08064532391

Team glow♀

WANAN LITTAFIN NA KUDINE BIYA 500 TA WANAN ACCT 0272061655 WEMA BANK NAFISA NUHU KO KATIN MTN KO AIRTEL TA WANAN LAYIN 08033719070 DOMIN KI MALLAKI NAKI KI MUTANEN NIGER KUMA KU TUNTUBI WANAN LAYIN
+227 96 82 89 84 DUK WACCE TA MIN SHARING NA BAR TA DA *RABBI ZAI FIDDA MIN HAKKI NA DA IZININ ALLAH DOMIN BA YAFEWA NAYI BA*

NI DA KISHIYOYINA

NA SADNAF

PAGE 26

Luba ko kulata bata yi ba tayi wajen akwatin da take ajiye sarkokinta dan ko da k'ok'awa ne sai ta dauki sarkokinta da kudadenta.

Tana k'ok'arin bud'e akwatin Hindatu dake bayanta tana tazo ta fita ta fusge tana "Wlh ba abinda zaki d'auka a gidanan ki bari idan Alhaji ya dawo kin San kin isa sai kizo ki d'auka sai da kika tabbatar baya nan kika wani zo d'aukar abu a d'akin nan"

"Hindatu ki bani akwatina,wlh zan miki rashin mutunci ki bani nace"

"Kinsan dai a dake bazaki iya dukana ba idan kina da k'arfi zaki iya zuwa ki kwata ko kunya bakiji ba kika kwaso jiki kika taho d'aukar kaya"

Kan Hindatu Luba tayi dan ko da balai sai ta kwashe sarkokinta dan bata da Kuma wani abu sama da kadaddorin ta na gidan salis tunda Asabe ta cinye mata na wajenta.

K'ok'awa suka fara yi duk yanda Luba taso ta karbe akwatin a hannunta ta kasa a karshe dabara ya Fado mata ta kafa mata hakori a hannu akan dole ta saki akwatin tana ihu.

Luba kuwa ta d'auke akwatin sarkokin ta hau Kan gadon ta jawo babban akwatin ta dake saman drawer kayanta ne tsadaddu a ciki har da kudin da zasu kai dari da hamsin, ta sauko dashi kasa Hindatu kuwa taje ta tsaya a bakin k'ofa tana rantsuwar ba inda zataje da kayan,ko kulata Luba batayi ba dan wanan shine damar da take dashi,akwai Abubuwan da takeso ta kwasa da yawa amma ba dama idan dai ta samu ta tsira da akwatin kayanta da na sarkokin ta tasan ta samu na rufin asiri,sai da ta kwashe duk kudaden da take boyewa ta saka a cikin akwatin sarkata, wayarta da ta gani a drawer da take matukar bukatarsa ta d'auka da sauri dan shima zai kai dari biyu ta cusa a cikin breziyar ta, ta fara jan akwatin da hannu daya,daya hannun nata rike da karamin akwatin.

Tasan sai Hindatu ta hanata fita hakane yasa ta shafa aboniki a hannunta.

Hindatu kuwa tsayuwarta ta gyara tana "wlh bazaki fita da komai ba kinji na rantse miki yau din ma Alhaji nasan mantawa yayi bai kulle d'akin ba,

Bani hanya na wuce Hindatu "

"Bazan baki hanya ba barauniya ki bari idan Alhaji ya dawo sai kizo idan kin isa.

Luba ajiye akwatin tayi,

Ta nufi Hindatu da ta gyara tsayuwarta,tana zuwa ta shammace ta ta shafa mata man akan idonta.

Hindatu ta saka ihu ta fara tsalle tana murza idonta,

Luba kuwa ta ture ta gefe ta d'auko akwatin ta tayi waje da sauri,

Sai dai tana zuwa Palo Salis na shigowa.

A razane taja da baya tare da sakin akwatin,wani irin tsoronsa ya rufeta dan wani wuta take hangowa a idonsa ko a mafarki bata tab'a kawowa kanta ranar da zataji tsoron Salis ba.

Jikinsa har wani rawa yake Yana daga tsaye yana binta da mugun kallon tsana.

"Yauwa Alhaji gwara da ka dawo ka kamata haka kawai ta shigo Ina kitchen ta shige daki dan na hanata ta hau ni da k'ok'awa har da cizo"

Cikin wani irin murya Salis yace "Dama a baya nace ni zan zama ajalinki kin dauka wasa nake miki wlh bazaki bar gidanan da kafafunki ba sai dai a fita da gawarki"

"Aa Alhaji Kar dai kayi kisan kai ka rabu da ita ta tafi"

Ja da baya Luba ta fara ta kankame akwatin sarkokinta a hammatar ta tana "Dan Allah ka barni na tafi da kayana Alhaji banida kayan sawa iya wanan na jikina ne kawai dani, nidai kayi hakuri nasan ban kyauta ba rashin zurfin tunani ya Kai ni ya baroni dan Allah ka rufa min asiri na tafi bazan sake zuwa gidanan ba Alhaji ka dubi yaran dake tsakanin mu ka sausauta min wanan tsanar da kake min,ni na yarda zan je na Nemo Aisha nace mata sharri nake maka ba Kaine babban Nana ba dan Allah ka rufa min asiri"

"Wlh wlh ko tsinke bazaki fita dashi daga gidnan ba domin duk wani abu da kike takama dashi da kudina na siya na gwammace na zubar da ko cokalin da na siya da kudina da ki mora a yau kina tunanin ni kika tonawa asiri,bakisan kanki Kika tonawa ba,nayi dana sanin duk tsawon shekarun nan da na dauka kina firgitani kina Sakani a fargaba,nayi dana sani da na barki kika ringa juyani san ranki,nayi dana sani da na aureki sabida gudun ki tona min asiri Wanda aurenki da nayi shine babban kuskuren da nayi,nayi da nasani da na boyewa Aisha abubuwan da har yasa ta daina yarda dani ta cire kaunata a zuciyarta,luba iya saki da duka bazai goge abinda nake ji a kanki ba a yanzu da nake ganin ki a gabana ji nake kamar na kasheki dan ba wacce na tsana a rayuwa sama dake,ki ajiye min duk abinda kika dauko kizo ki fita"

"Aa dan Allah ka barni na tafi da kayana banida komai karka manta na Haifa ma yara har uku ka dubi halin da nake ciki ka barni na tafi da kayana"

Salis a fusace yayi kanta da gudu
Ta juya itama
Ta fara ihu neman taimako tana neman wajen da zata shige Hindatu itama hankalinta a tashe da yanda jikin Salis din ke rawa dan idan har ya Kama Luba sai ya rabata da numfashinta.

Luba kuwa d'akin Hindatu ta shige tana danna k'ofar dan ta kulle Alhaji Salis ya hankada k'ofar da k'arfi ta fasa ihu a daidai lokacin da ya shako mata wuya da k'arfi.

Hindatu kuwa waje tayi a guje ta Kira mai gadi,suka yi cikin gidan gabad'aya a daidai lokacin da Ashraf shima ya dawo a cikin motarsa yanda yaga sunyi cikin gidan da gudu yasa ko parking din kirki bai yi ba yabi bayansu a guje shima.

Mai gadi duk yanda yaso ya kwace Luba a hannun Salis kasawa yayi sai da Ashraf ya shigo da magiya da komai kafin suka samu ya saki Luba da kiris ya rage ta sume.

Yana sakin ta tayi waje hannunta dafe da wuyanta ta fice waje da gudu taso ko karamin akwatin ta d'auka sai dai Hindatu ta hanata

Wayarta kawai shine a jikinta
Ko takalmi da mayafi babu sau biyu kenan Salis na gwada aikata lahira tasan ta kara bari suka hadu sai ya aikata lahiran Salis da take juyawa san ranta duk abinda take so jiki na rawa yake Mata yau shi wai yake neman rabata da ranta,

"Aunty Luba Aunty Luba"

Taji muryar Ashraf a bayanta tsayawa tayi ta juya tana kallonsa har lokacin numfarfashi take ba abinda ke rabata da Ashraf sai harara da zagi,dan haka kawai ta tsane shi

Koda ya iso inda take hararsa take shi kuwa idonsa kyar a kanta Yana kallonta

"Lafiya ka tsayar dani ka tsare ni da ido ko na zama sa'ar ka"?

"Bazan tsayar dake haka kawai batare da wani dalili ba tambaya kawai nake so na miki"

"Bazan tsaya ka min tambayoyin ba har ni zaka tsayar sabida bakada kunya karka ga wai dan na rabu da mahaifin ku wlh bazan d'auki raini ba"

Luba tace tare da jan tsaki ta fara k'ok'arin tafiya Ashraf yayi sauri yace"ya akayi kika san Abba shine mahaifin Nana"?

"Kaje ka tambaye shi yanda akayi nasani bani zaka zo kayi wa wanan Tambayar ba"

"Aunty Luba ya akayi ke kadai kika san sirrin shi"?

"Kaje ka tambaye shi nace maka zai gaya maka yanda akayi nasan abin kunyar da ya aikata sanan dan na tona Masa asiri ya sakeni,abin kunya dai mahaifinku ya riga da ya aikata,kaje ka tambaye shi a Ina yake samun irin wadanan kudin da yake facaka dashi kasan karya ne dai ace iya albashinsa da asibitinsa ke shigo Masa da kudi haka,har zaka Zo kana min tambayoyi ga Wanda ya dace kaje ka Masa tambayoyi acan"

Luba ta karashe tana Jan dogon tsaki zuciyarta fal da bakin cikin yanda bata samu ta d'auko akwatin sarkarta ba"

Ashraf sai da ya daina hangota ya juya jikinsa a sanyaye ya koma ciki ya shige dakinsa ya kwanta yana Kara nazartar maganganun Luba,ya dade yana zargin ta hanyar da mahaifinsa ke samun irin Wanan kudaden, ya tuna lokacin da sukayi fada da wani abokinsa Hakeem yace mahaifinsa dan yankan Kai ne,ko kad'an bai tab'a zargin Mahaifinsa ba ta hanyar halal yake neman kudinsa va tunda Yana harkar Ngo Yana da asibitin kansa Kuma Yana aiki da babban asibtin dake Abuja daga lokacin da ya amsa da bakinsa akan shi yayi wa muhasim fyade yaji ya tsorata da lamarin mahaifin nasa dan ko da wasa bai tab'a kawowa zai iya aikata haka ba,auren Luba da yayi da halin da mahaifiyarsa ta shiga duk ya daga musu hankali dan duk da basu gama mallakar hankalinsu ba sun san auren cin Amana suka yi,ko da ya girma hankali ya ringa saka wa mahaifin nasa ido, burinsa ya gano ko dai dagaske Yana yankan Kai din sai dai ko kusa bai ga alama ba,a jiya zargin haka ya Kara tasowa a ransa da Luba ta tona masa asiri akan shi yayi wa muhasim fyade baisan mai yasa yake san zargin Yana da hannu a karkacewar wuyan ta ba har Yana danganta hakan da kila bayan ya mata fyaden yayi kudi da ita ta zama haka, zargin itama Luba kawai yake dan dole akwai wani boyayyen alamari dole itama tana da hannu a duk Abunda ya faru.

Ringing din wayarsa ya katse masa tunanin daya tafi yaga "Uncle mustapha"

Ke Kiransa dagawa yayi yaji yace Yana waje yazo

Ashraf mik'ewa yayi ya fita waje nesa da gidansu ya hango Yaya mustapha yayi parking motarsa,wajen motar ya nufa da isarsa Yaya mustapha ya fito daga motar Yana "Ina Abban ku Ina ta kiransa baya d'aukar wayata"

"Dazun nan ya dawo gida bansan mai yasa bai d'auki wayarka ba,uncle dan Allah kayi hakuri da abunda ya faru ka yafewa Abba sharrin shaidan ne"

"Ashraf karka damu na yafe ko ban yafe ba abinda ya faru ya riga da ya faru ba abinda zai iya canza hakan,ko a mafarki ban taba kawowa wai Salis zai iya aikata haka ba amma ya zakayi da kaddara ni magana nakeso muyi ta fahimtar juna,tunda har mun riga da munsan shine mahaifin Nana dole zaa zargi ko shi ya karkata mata baki,inaso ya ajiye jin nauyina a gefe ya fadamin iya gaskiyarsa,bazan so nayi kararsa akan zaluncin da yayi wa Yata ba dan Yana auren kanwata idan har sunansa ya b'aci tamkar sunan kanwata ne ya b'aci Kuma abin zai shafeku shiyasa nakeso

muyi abin mu cikin gida ba Wanda yasani kullum burina da Addu'a ta shine Allah ya bawa muhasim lafiya shekara Sha biyar an tafi na Sha shidda sai dai a kwantar da ita a tayar,so nake naji abinda akayi mata ta koma haka,kila Yana gudun asirinsa ya tonu shiyasa ya mata haka bandai sani ba nafiso sai munyi magana dashi tukunna"

"Uncle mustapha ngd da fahimtarka nasan Abba ya kasa d'aukar wayar ka ne sabida Yana Jin kunyar ka amma yanzu Zan Shiga ciki na fada masa kana kiransa,ko zaka zo mu Shiga ciki?

Girgiza masa Kai Yaya mustapha yayi yace Yana cikin motarsa Yana jiransa.

Ashraf ya nufi cikin gidan Koda ya Shiga d'akin Aneesa ya nufa dan anan Alhaji Salis yake kulle kansa

Alhaji Salis

Shi kadai yasan kalar tashin hankali da yake ciki tunda Aisha ta bar gidan ita da Aneesa ba barinsu gidan yafi daga masa hankali ba,bai san ya Yaya mustapha zaiji idan ta bashi labarin shine yayi wa muhasim fyade,Yaya mustapha ya daukeshi tamkar dan uwa bama shida abokin shawara sama dashi a yanzu ba abinda zaiyi ya iya wanke kansa a wajensa,sai a yanzu yake nadamar boye b'oyen da yayi wa Aisha da ace tun farko ya sanar da ita yanda Luba ke bibiyarsa tana San shi har zuwa kaddara da ta fada masa ta ringa masa barazana da kila duk bai tsinci kansa a wanan tashin hankalin ba,shima baisan mai ya toshe masa tunani ba Aisha tana da saukin kai da fahimta da zata fahimce shi,zuciyarsa cike take da fargabar mai zaije ya dawo wane irin mataki Yaya mustapha zai d'auka idan yasan shine yayi wa muhasim fyade ba wanan yafi daga masa hankali ba,bazasu tab'a yarda bashi ya karkata wa muhasim wuya ba,a lokacin da Ashraf ya dawo gidan Kamar kwai ya fashe masa a ciki bai ce masa komai ba dan yasan Aisha ta riga da ta fallasa Shi d'akin Aneesa ya shige yana Jin kansa kamar ya fashe,bai tab'a tsintar kansa da Jin kunya mai tsanani ba irin wanan hannunsa rawa kawai yake wajen shigar da lambarta ya hau kiranta sai dai Yana ringing take katsewa hakane yasa ya tura mata text duk da yasan da wuya ta saurareshi,tun Yana sa rai da reply dinta har ya hakura gidan ma kansa ba dadi yake masa ba dan yaran kamar Suma kunyar abinda ya aikata suke ji.

Hakane yasa ya fice daga gidan ya hau motarsa ya fita Yana zaga gari kiran worker da ya shigo wayarsa ya katse masa tunanin da ya tafi ya tsurawa wayar Ido kamar Yana so yaga fuskar Mai Kiran sai da ya masa kira uku kafin ya iya dagawa "Alhaji an Kama su lukman"

"Innalillahi wa Inna ilaihi rajiun innalillahi wa Inna ilaihi ka bari dan Allah kar ka karamin tashin hankali akan Wanda nake ciki"

"Wlh yanzu nan na kira John yace sun Shiga hannu nidai adduata Allah yasa Kar sunana ya fito kasan suka tona asiri da matsala"

"Dan Allah kacewa John ya wurgar da sim dinsa Kar ayi tracing dinsa duk abinda za'ayi ka fada masa zamu bashi ko nawane Kar sunan mu ya fito already Ina cikin wani babban tashin hankali ga wani na Shirin b'ullo min uje da matsala idan asirin mu ya tonu a yau nake Shirin kiranka akan na bar harkar nan idan kudine an tara zai ishe mu har karshen rayuwar mu kar watarana asirin mu ya tonu sai gashi kuwa asirina na neman tonuwa"

"Insha Allahu sunanmu bazai fito ba indai baa samu an Kama John ba ko an Kama shi ba lailai ya Kira sunan mu ba"

"Innalillahi wa Inna ilaihi rajiun uje dan Allah ku rufamin asiri bansan da wane zanji ba da matsalar gidana zanji ko da wanan masifar dake tunkaroni"

"Bari na Kira John ya karya sim din nasa"

"Kayi sauri ka kirashi Ina jiranka"

Salis ya kashe wayar kirjinsa na bugun tara tara yana ganin watan tonan asirin sa ne ya kama ya kifa kansa akan steering yana "Zainab kin cuceni"

Kiran da ya sake shigowa wayarsa yasa yaji kirjinsa ya sake dokawa da k'arfi daya ga Yaya mustapha ke kiransa.

Taya zai iya daga wayarsa Yana kallon Kiran har ta katse

Da wane zaiji da tashin hankalin daya tunkaro shi zaiji ko da rashin Aisha da Aneesa ko da asirinsa daya riga da ya tonu.

Da Wanan tashin hankalin ya dawo gida yazo ya tarar da Luba da a rayuwarsa ba wacce ya tsani gani kamar ta duk masifar nan da yake ciki ita ta jawo Masa.

Yanda ta kuntata masa dole shima ya kuntata mata yasan kuntata mata kawai da zaiyi ta shiga gararin rayuwa bai wuce ya hanata d'aukar Koda cokali ba sosai yaga tsaurin idonta na zuwa d'aukar kayanta yaso sun barshi ya kasheta suka hana shi.

Muryar Ashraf da bugun k'ofar da yake ya katse masa tunanin da yake.

Murya can kasa ya masa izinin shigowa

"Abba Yaya mustapha ke sallama da Kai a waje"

Wani irin mik'ewa Salis yayi tare da zaro ido yana "kace masa bana nan Ashraf bazan iya hada ido dashi ba kunyarsa nake ji dan Allah jeka ce masa bana nan"

"Abba wlh ba wani tashin hankali yazo dashi ba mun yi magana ta fahimtar juna dashi yace magana kawai zakuyi so yake ka fada masa idan kana da hannu a larurar muhasim, Abba dan Allah ka fito ka fada masa kawai gaskiya kawai"

"Wlh Ashraf banida hannu a larurarta nasan ba lailai su yarda bani bane tunda har ni na Mata fyade ni kaina bansan Mai ya sameta ba bansan Wanda ya mata haka ba"

"Abba toh ya akayi Aunty Luba tasan Kaine mahaifin Nana haka kawai naji Ina zarginta"

"Zan baka labari kila ka gano idan tana da hannu a ciki tunda Kai lawyer ne muje wajen Yaya mustapha Kar mu barshi yayi ta jira muje ka rakani"

Tare suka fito Salis jikinsa duk ba kwari har wani buya yake a bayan Ashraf har suka Isa wajen motar Yaya mustapha.

Ya dauka Yaya mustapha zai hade rai ko ya hau gaya masa magana sai dai ga mamakinsa hannu ya miko masa akan suyi musabiha kamar yanda Suka Saba shi kuwa ya sunkuyar da kansa ya kasa mik'a masa hannun.

Yaya mustapha yace ya shigo motar sa suyi magana Ashraf shima ya hau bayan motar har dashi za'ayi maganar.

Luba

Sai da ta siyar da wayarta ta siyi karamin waya kafin ta d'auki hanyar gida,wayar an siye shi da dan daraja kafin ta siyar da wayar ma sai da ta duba acct dinta taga ko Salis fada kawai yayi ba rufe mata acct d dinta ba sai dai tana dubawa taga ya rufe duk acct din nata.

Tuna yanda Hindatu ke walwali a gidan ita kadai ya daga mata hankali,bata hango yanda zata iya rayuwa a wahalce ba da ace ma ta samu ta kwashe kayanta da sauki iya kudin nan ba inda zaije Mata ya zama dole ta bazama nemo mai taimaka Mata ta koma gidan Salis.

A Mata aikin da sai yanda tayi dashi,a mata Kuma aiki akan Asabe bakinta da wuyanta ya karkace taga ta bakin da zata tona mata asiri ta Zama abin tausayi.

A lokacin da ta isa gida a tsakar gida ta samu mahaifinta a zaune ko dar bataji ba dan wlh duk korar da zai mata ba inda zataje ko jiya da ace tasan zata hadu da dan iskan gambo da duk korar da zai Mata bazata tafi ba.

Irin kallon da yake wurga Mata yasa ta tsaya cak ta sunkuyar da kanta

"Mai kika zo nema lubabatu kin dauka Wasa nake dake ko wlh wlh bazaki zauna min a gidanan ba kije ki nemi gidan da zaki zauna a lokacin da nake ce miki zakiyi nadamar abinda kikeyi kin dauka Wasa nake ko?a lokacin da nake cewa lokaci na zuwa zaki zama abin tausayi kin dauka Wasa nake ko"?kin dauka banji kincewa kawarki bani ne mahaifin ki ba,ni marikinki ne Mahaifinki ya Dade da rasuwa kin dauka duk bansani ba ko Luba wlh idan Kinga na bar ki kin zauna a gidanan toh ki tabbata da kudinki na Gina gidanan"

Luba zub'ewa tayi a kasa cikin kuka tana "Baba idan ka koreni wajen wa zanje Baba Naga na baka hakuri na nemi yafiyarka dan Allah ka yafemin ba mai tallafa ta a daidai lokacin nan sai ku banida sama daku ba masu rufa min asiri sai ku yarinta yasa duk nayi abinda na yi amma a yanzu nayi nadama Baba dan Allah karka koreni"

"Tashi kifita kibarmin gida ko ganinki banaso nayi na Dade da yafeki a cikin yarana wlh Baki fara ganin komai ba duk abinda kika shuka wlh sai kin girbe shi kifita nace"

Ya mik'e Yana jawo gatarin dake gefensa.

Yanda ya nufota yasa ta kwasa da gudu tayi waje.

Tana kallonsa ya saka sakata.

Ita kam batasan wa zai bata wajen kwana ba, gashi duk batayi zaman mutunci da mutane ba ballantana ta samu mai taimaka mata.

Haka ta zauna a k'ofar gidan har aka kira Sallah isha tuna tana da lambar mijin Asabe yasa taji wani sanyi a zuciyarta.

Jiki na rawa ta nemo lambarsa dan asabe ta tab'a kiranta da lambarsa haka kawai ta tsinci kanta da Saving lambar ashe da rabon zai mata rana,tasan dan akuyane shi tana tsara shi zai tsaru sai tayi yanda tayi ma ya aureta Koda asirine a yanzu Kuma ba wacce take burin ma ganin bayanta sama da Asabe da ace ta taimaka mata duk da bata Shiga Wanan gararin ba.

Kira uku ta masa ana hud'u taji an d'auka.

Muryar Asabe taji tana "Kambalai nan Luba ke kike Kiran mijina?".....

Wlh banida lafiya zazzabi nake fama dashi dak'yar nayi typing..

Ammnur _kayan mata tazo muku da zafafan kayan matan da babu algus 09080070762

Ina uwargida da ta haihu vjay dinta ya bude tana bukatar taji ta koma budurwa gam ga ammnur Nan ta kawo muku zafafan kayan mata Ina amare masu Shirin shiga daga ciki,Ina Zawara da suke so suji Basu da bambanci da budurwa

Enjoyment doesnt stop just because you have given birth. The afterbirth package is made to take care of you postpartum sexual needs . This package includes sweetner, wetner, tightener infection afterbirth herbs and more

Prices

Normal 150k
Regular 250k
Premium 500k
Exclusive 1million

Sauran kaya da zaki duba a wajen su na qara niima dadi da matsi sanan akwai na tsuma jiki na mata da na amare da uwargida Wato Madame package, suna da kayan farinjini, favour da kuma mallaka

1)Euphoria 12
2)Gorontula syrup
3)Her exellency cake
4)Exclusive thumi
5)Milky sweety
6)Magic insert
7)Tightening mallaka saop
8)Tightening honey pill
9)Women 001
10)Ebony lady
11) spiced tea

12)Mallaka chicken soup
13)Tightening powder
14) wetness powder
15) favour set
16) attraction set
17) bakar mallaka
18) shu'umar mallaka
19) hatsabibiyar mallaaka
20) horney honey syrup
21) libido booster set
22) breast enlargement
23) hips enlargement

 in ka ji busa tabbata Sarauniya ce ta ƙaraso, ina kuke matan ƙwarai, mata ba muna mata ba, shin kin jaraba kayan *HONEY-DROPS* me kike jira har yanzu?, Manyan mata, mata masu aji na ta dafifi wajen kwasar kayan gyara, me ya sa za ki kashe kanki da ƙuruciyarki, ko tsohuwar ma na zuwa karɓar nata, kina fama da matsalar bushewar gaba, ɗaukewar sha'awa da ni'ima, ƙaiƙayi ko ƙurajen gaba, jin zafi yayin tarawa da maigida, sanyi ya taɓa miki mahaifarki?, Kina ta allura da shan magunguna ba su miki aiki ba, wane kalar infection kike fama da shi?, Staphylococcus, Gonorrhea, Syphilis, UTI, STDs ne?, Share hawayenki kukanki ya ƙare je ki nemi *HONEY-DROPS INFECTION FLUSHER* ke da sanyi sai dai ki ba da labari, kin gama cacar kuɗi, cikin kwana uku zaki fitsarar da duk wani sanyi da dattin da ke tattare a mararki, ki gyara zamanki gidan aurenki don sanyi kashe mace yake har buzunta, duk wani magani da za ki sha muddin da sanyi a jikinki iyakar shi cikinki, ba zai sauka ba. Magani ne ingantacce made of herbs, In kin gama da wannan akwai na gyaran other room, akwai Exclusive Gumba ta manyan mata ke nan, ko matar Gwamna ita take sha, ga Gumbar babbar mace mai tada tsohuwar soyayya, akwai fa tsuumi na matan gaske, akwai *HONEY FLOOD TSUUMI* kan ƙiftawar ido ni'ima ta yi ta kwararo miki, akwai BUJENTA JAGAB, da Tsuumin Ɗafau, daga jin sunan kun san akwai zance na bar muku ku ƙarasa, akwai sauran kaya masu zafi

Muna da bridal package

Diamond - 100k
Gold - 50k
Silver - 30k

Ga kuma na postpartum (wanda suka haihu don dawo da martabarsu)

Diamond - 50k
Gold - 30k
Silver - 15k

Kuna iya samun mu ta 08167888934, ko 08067770852

WANAN LITTAFIN NA KUDINE BIYA 500 TA WANAN ACCT 0272061655 WEMA BANK NAFISA NUHU KO KATIN MTN KO AIRTEL TA WANAN LAYIN 08033719070 DOMIN KI MALLAKI NAKI KI MUTANEN NIGER KUMA KU TUNTUBI WANAN LAYIN
+227 96 82 89 84 DUK WACCE TA MIN SHARING NA BAR TA DA *RABBI ZAI FIDDA MIN HAKKI NA DA IZININ ALLAH DOMIN BA YAFEWA NAYI BA*

NI DA KISHIYOYINA

NA SADNAF

PAGE 27

Luba

Da sauri ta kashe tana "Yar balai wayarsa ma na hannunta"

Sam ba haka taso ba dan so tayi ya d'auki wayar ta tasan ko yayane zai iya sama mata wajen kwana ko hotel ne zai iya Kama mata,dan namamajo ne na karshe har cewa Asabe take ko akafa aka daura mata shi sai ta cire ta yar dan bazata iya da mai san matan masifa ba,ita kuwa Asabe sabida abin duniya take zaune dashi a haka ko tsoron ya saka mata cuta bata yi.

Kiran Asabe ne ya hau shigowa wayar ba k'auk'autawa ita kuwa ta ringa rejecting Kiran,sai ga text nan ta turo da "Wlh ido na idon ki Luba sai kin gane shayi ruwane har ni zaki gwadawa bariki ki hau Kiran mijina wato abinda kika yiwa Aisha nima Zaki min daga mutuwar auren ki wlh wlh sai na wulakantaki na kaskantar dake indai kika ce zaki gwada cin amanata Kuma wlh sai na tona miki asirin gwara kije daga can kurkuku ma yafi min kwanciyar hankali dududu yaushe auren naki ya mutu kwana biyu kacal har kin fara neman mijina shegiya karuwa idona idonki wlh sai kin yabawa aya zakinta"

Luba cije lebbenta tayi cikin takaici tana Jin dama ta iya mata reply ta wanke ta da soso da sabulu, sai dai ba wanan damar tunda bataso ta tona mata asirin amma fa dole tayi maganin Asabe ko ta wajen auren mijinta dan ta kuntata mata ko ta karkata wuyan shegiya.

Sauron dake ta kaiwa fatarta cizo yasa ta hau susa,kasan ta ma kaikaiyi kawai yake mata, sai ta sosa take Jin dadi,tana tsoron ace wani kazantar Gambo ya saka mata, zuciyarta har tashi take idan ta tuna yanda ya mata, tsinuwa kuwa ya sha yafi cikin kwando, gambo da Asabe tayi alkawari sai ta wulakanta su.

Yanzu idan tace zata tab'a kudin nan ta kama hotel karewa zaiyi,tasan kudin nan sai dai tayi ta maneji tana siyan abincin.

Contact din wayarta kawai take bi tana duba Wanda zata iya Kira ya taimaka mata,a haka tayi tozali da lambar Sultan danta.

Dailing lambar sa tayi sai da ta kusa katsewa taji ya d'auka

Ta Kira sunansa da "Sultan"

"Naam Ina wuni Mama"

"Sultan yanzu da ranka nake shan wanan wahalar har ace wajen da zan kwana ma narasa sultan nifa mahaifiyar ka ce kasan darajar uwa kuwa? kanaso kayi albarka kuwa"?

"Mama lafiya kuwa mai ya faru kike jeromin wanan maganganun"

"Sultan mijina sakina yayi tun shekaranjiya nake garari a garin nan abincin da zan sakawa cikina ma babu ballantana azo wajen da zan kwana, mahaifina ma an shiga tskanin mu ya koreni,banida wajen zama,kwana biyu kenan Ina fama da Kaya daya har ace Ina da kamar ka sultan na ringa Shan wanan wahalar har yaron da bai Kai ka ba ya wulakantani ya ci mutuncina"

Sultan shiru yayi bai ce komai ba dan a yanzu bai san mai zai ce mata ba sun taso su biyu tare da mahaifin su,da ya matukar gwada musu so da kauna,duk da yana yaro bai manta yanda Luba ta watsar dasu tayi tafiyarta ba Suka ringa rayuwa kamar marayu,daga makaranta sun sha zuwa wajen ta amma haka zata rufe ido tace su koma wajen ubansu ita bama taso asan ta tab'a haihuwa su daina sintirin zuwa gidansu har akwai lokacin da suka je gidan ta rufe shi da duka sabida ya kirata da Sunan mama a gaban Wanda take zance,ire iren Abubuwan nan yasa basa jinta a zuciyarsu ko kad'an ilham ma tafi shi ruko dan ta Sha cewa ita bata da uwa ta mutu,bata tab'a waiwayar su ba har sai da mahaifin su ya fara samun Yan canji,takan kirasu a waya idan ta bushi iska tazo ta gansu Wanda da zuwanta da Babu duk dayane a wajen su dan matan babansu sun rike su tamkar su suka haifesu, sun ma fi Jin kaunar su a kanta"

"Yana ji ka min shiru ko baka ji mai nace bane"?

"Toh mama mai zance yanda kike magana ne Kamar irin nasan an sakeki ne bayan ni bansan an sake ki ba"

"Toh a yanzu ka sani gani nan a titi na rasa wajen kwana kazo ka nema min wajen kwana ko hotel ne ka Kama min ai baka isa kace min baka da kudi ba"

"Mama wlh banida kudi Abba bai fiye bamu kudi ba duk abinda dai muke so yimana yake yi Kuma ni kinsan ba aiki nake ba ki roki su Inna su barki ki zauna tunda bakida wajen zuwa"

"Sultan yanzu ni zaka cewa baka da kudi,? sultan wulakanta ni zakayi nifa na tsugunna na haifa ka da motar ka da babbar wayarka a hannu ko su bazaka siyar dasu ba ka nema min wajen zama kafin komai su daidaita? idan har baka min ba wa zaka yiwa sultan? Yanzu karfe tara har da rabi banci komai ba ga sauro dake ta cizona ku kuna cikin Ac da gado ni Ina titi a zaune"?

Shiru sultan yayi dan ji yayi kansa ma ya fara ciwo sai da ta kara magana yace "Kina Ina Yanzu"?

"Ina k'ofar gidanmu a zaune"?

"Toh gani nan zuwa"

Ya katse wayar luba ta hau cewa "Banda b'atan basira ma irin nawa duk abinan na manta Ina da yaron da zai iya taimaka min kila da jiya da shegen ubansa ya koreni da na kirashi a waya da kila ya nema min wajen kwana naje na samu tsinannen yaron nan ya min fyade na rantse da Allah sai na wulakanta yaron nan"

Tace tana sosa gabanta minti sha biyar a tsakani ta hango sultan ta kuwa mik'e da sauri tana washe baki ai ko bai sama mata wajen kwana ba ta kwana a motarsa kafin ya nemo mata gidan haya ta zauna.

Tun kafin ma ta tsayar da motar ta bud'e tana k'ok'arin shiga sultan yayi saurin cewa "Wai so nake na shiga na roki baba ya barki ki zauna a gidan mama wlh banida inda zan Kai ki kema kinsan ko gida na kai ki Abba ba yarda zaiyi ki zauna ba"

Tsaki taja ta shige cikin motar tana "Karma ka wahalar da kanka wajen ma zuwa wajen baba dan yayi nisa idonsa ya rufe da san yaga na wulakanta burinsa yaga Ina garari a titi nima Banda kaddara mai zai kawoni gidan nidai muje ka Kama min d'aki gobe sai ka nemo min gidan haya na zauna na dan lokaci"

"Mama Dubu hudu ne kawai dani bai zai isa a Kama Miki daki ba sanan Ina zan samo kudin da zan kama miki haya"?

"Idan baka san yanda zaka yi karya ka samu kudi a wajen baban ku ba sai ka siyar da wayar ka ko motar ka ka Kama min haya Ina da kamar Kai bazai yu na ringa garari a titi ba,wane irin wahala ne ban sha akan ku kuna Yara ba sai dan yanzu ka min abinda bai taka Kara ya karya ba sai kace min wani baka da kudi"

Ya riga da yasan kalar rigimarta baice komai ba ya tada motar Suka dau hanyar wani karamin hotel dake bayan gari Dubu uku ne kwana daya har suka isa hotel din bambami take baice mata komai ba dan ya riga da ya Yanke mai zai yi Dubu hud'un ya fito dashi ita kuwa ta tambayeshi nawane kwana daya yace mata dubu biyar ne,Dubu daya ta d'auko ta bashi ya barta a cikin motar sai da ya lalubo dubu daya ya cika ya Kama mata na kwana biyu aka bashi mukulin d'akin,ya fito wajenta.

Suka koma ciki tare shi ya bud'e mata d'akin ta shige tana "A yau nima da ban Haifa ba sai na hadiyi zuciya na mutu jiya da ace na kiraka da duk abinda ya Sameni jiya da bai sameni ba wanan wane irin hotel ne d'akin wani iri kamar ba hotel ba ko dai yake ya dai fi rufin asiri da na ringa bin mutane ana wulakantani karbi ka samo min abu naci dan yunwa nake ji ka hado da dan bredi naci da safe idan Kuma zaka kawo min abincin karyawa da safen shikenan "

Kudin kawai ya karba yayi waje minti goma a tsakani ya kawo mata abincin

Ta karba tana "Yauwa dan albarka kai baka iya dan dabaru wajen karbar kudi a wajen Abban naku ba yanzu karya zaka masa akan motar ka ta lalace ka yanka masa kudi yana baka ka kawo min muje mu kama haya idan da canji na samu na dan siyi kayan sawa iya wanan na jikina ne kawai dani wlh Salis ya wulakantani ko tsinke bai bari na d'auka ba ba abinda ya bari na d'auka"

"Ba damuwa mama zan k'ok'arta insha Allahu"

"Allah ya maka albarka gobe zaka kawomin abincin karyawar"?

"Eee insha Allahu"

"Yauwa dan Allah dan Allah ka hado da dan romo romo an kwana biyu baa hadu ba"

Gyada.mata kai Sultan yayi ya mata sai da safe Yana fita ta baje a tsakiya gadon taci ta koshi ta shige bandaki ta daura alwala tazo ta Rama duk sallolin da batayi ba tana iddar wa ta kwanta ta hau sosa gabanta da taji yana mata masifar kaikai yi tana

"Allah ya tsinewa yaron nan Albarka ya saka min cuta dole na nemi kudi na tafi asibiti.

Bacci na fara d'aukar ta kaikaiyi zai saka ta tashi ta fara susa.

Alhaji Salis

Shiru ne ya ratsa motar bayan ya gama bawa Yaya mustapha labarin duk abinda ya faru Kama daga yanda Luba ta fara bibiyarsa har zuwa lokacin da ta saka masa magani dan ya nemeta a ranar muhasim ta tsallake bai mata fyade ba har zuwa yanda Luba ta cigaba da bibiyarsa da yanda ya wayi gari da bukata komai sai da ya kwashe ya fadawa Yaya mustapha dan gani yake a yanzu fadar gaskiyar shine mafita a gareshi.

Ashraf kuwa kansa a sunkuye har ya gama bada labarin yana kara bibiyar labarin a kansa.

"Kayi babban kuskure wajen b'oyewa Aisha yanda Luba ta ringa bibiyar ka da ace ka fada mata da tuni ta dade da rabuwa da ita"

"Yaya wlh a lokacin ko na fada mata bazata rabu da ita ba dan akwai lokacin da na rabasu haka ta hau fushi dani, wlh tsoron Luba ta tona min asiri akan abinda na aikata Wanda Allah shine shaidata baa hayyacina nayi wa muhasim fyade ba wlh wlh ba'a hankalina nake ba Yaya muhasim 'yace a gareni bazan tab'a yi mata haka da gangan ba da ace Kuma Ina da hannu a karkata mata wuya wlh Yaya da na fada maka tunda asirina ya riga da ya tonu banida hannu a abinda ya same ta"

Shiru ne ya Kara ratsa motar tsawon mintuna kowa da tunanin da yake a zuciyarsa.

Kafin Yaya mustapha yayi gyaran murya yana "Daga labarin da ka bamu duk yanda akayi Luba tasan wani abu damu bamu sani ba bansan Mai yasa nake zarginta ba bana jin muhasim zata iya tararta ta fada mata tana d'auke da juna biyu akwai dai abinda ke b'oye.

Ashraf gyada kansa yayi Yana "Tabbas nima daga labarin da Abba ya bayar na Kara tabbatar da zargin da nake mata bazan iya tunawa ba akwai ranar da naji suna hira da kawarta a dakinta wanan bakar kawar tata mai bille sunan muhasim da naji ta Kira yasa na tsaya sai Kuma naji sun kara kasa da murya ban kawo komai ba sai ayanzu sa Abubuwan nan ke faruwa naji na Kara tabbtar da zargina amma ba komai uncle ku bar komai a hannuna zanyi bincike insha Allahu"

Gyada kai yaya mustapha yayi Yana "nima a yanzu gabad'aya zargina ya koma kanta kayi bincike da kyau"

Salis kamar an cire Masa wani gundumemen dutse akansa haka yaji yaji Dadi da yanda Yaya mustapha bai d'auki zafi kamar yanda yayi tunani ba har sukayi sallama dashi Suka fito daga motar shi da Ashraf sukayi cikin gidan.

Suna Shiga Palo wayarsa ta fara ringing ganin worker ke kiransa yasa yaji kirjinsa ya buga kasa d'aukar wayar yayi ya shige daki da sauri.

Ya daga wayar maganar da Uje ya Masa ya sa shi sakin sallati yana "Shikenan asirina ya sake tonuwa uje da wane irin ido Zan kalli mutane idan suka gano halin da muka jefa kanmu innalillahi wa Inna ilaihi rajiun"

Shigowar Ashraf d'akin yasa shi sakin wayar sabida jikinsa rawa kawai yake.

Ashraf ya zuba masa ido,

Uje kuwa sai hello hello yake

Ashraf yace "Abba akwai wani sirri bayan na muhasim da kake ganin ya Kamata nasani"?.....

Wlh wlh bana Jin dadi dak'yar nake rubutun nan

Ammnur _kayan mata tazo muku da zafafan kayan matan da babu algus 09080070762

Ina uwargida da ta haihu vjay dinta ya bude tana bukatar taji ta koma budurwa gam ga ammnur Nan ta kawo muku zafafan kayan mata Ina amare masu Shirin shiga daga ciki,Ina Zawara da suke so suji Basu da bambanci da budurwa

Enjoyment doesnt stop just because you have given birth. The afterbirth package is made to take care of you postpartum sexual needs . This package includes sweetner, wetner, tightener infection afterbirth herbs and more

Prices

Normal 150k
Regular 250k
Premium 500k
Exclusive 1million

Sauran kaya da zaki duba a wajen su na qara niima dadi da matsi sanan akwai na tsuma jiki na mata da na amare da uwargida Wato Madame package, suna da kayan farinjini, favour da kuma mallaka

1)Euphoria 12
2)Gorontula syrup
3)Her exellency cake
4)Exclusive thumi
5)Milky sweety
6)Magic insert
7)Tightening mallaka saop
8)Tightening honey pill
9)Women 001
10)Ebony lady
11) spiced tea
12)Mallaka chicken soup
13)Tightening powder
14) wetness powder
15) favour set
16) attraction set

17) bakar mallaka
18) shu'umar mallaka
19) hatsabibiyar mallaaka
20) horney honey syrup
21) libido booster set
22) breast enlargement
23) hips enlargement

Ayiri yiri □□□□□kuna Ina mata matafa nake nufi bamuna mataba 😀😀A&Z COLLECTION takawomuku ingantatun supplement□□□□
Muna da supplement na Infection
Munada da supplement na gyaran jiki Wanda zaisa jikinki yayi kyau fata tai laushi da sheki □□□munada na gyaran breast succiko su tashi tsaf gwanin Sha awa□□ munada na matsi dazai matsaki ciki dawaje bawai ki iya farkoba kuma yasaukarmiki da ni ima
Muna da na gyaran gashi Wanda zaifitomiki da gashi 😍😍
Dawanda zakiyi haske duka jikinki bawai fari na bleaching ba 😀😀

A&Z dealer ce kayanmu suna da sauki sosai price dinmu price din sari ne zaki samu kayanmu cikin sauki alhmdulillah□□□□
Ga kadan daga ciki

1 Royal jelly karami 2500
2 Juliet Eve 8500
3 Amirna 8k
4 Vitamin c 2500,2300
5 vt e 2k
6 collogen + glutathione 2k
7 whitening gummies 2200
8 surga wanita 2500
9 khusus 3500
10 majakani 2500

Price din sari□□□□nasan kodaga haka zaku gane A &Z gidan sauki ne□□□□□□□□
Masu siyan daidai kuma bambancin kadanne

Muna garin Kano Dan neman Karin bayani Kira ko whaspp 09037870422

Karku manta muna tura Kaya duk garin dakuke inkiyi siyayyama dayawa muyi Miki free delivery □□□yan Kano kayanku har kofar gida cikin aminci□□□

WANAN LITTAFIN NA KUDINE BIYA 500 TA WANAN ACCT 0272061655 WEMA BANK NAFISA NUHU KO KATIN MTN KO AIRTEL TA WANAN LAYIN 08033719070 DOMIN KI MALLAKI NAKI KI MUTANEN NIGER KUMA KU TUNTUBI WANAN LAYIN
+227 96 82 89 84 DUK WACCE TA MIN SHARING NA BAR TA DA *RABBI ZAI FIDDA MIN HAKKI NA DA IZININ ALLAH DOMIN BA YAFEWA NAYI BA*

NI DA KISHIYOYINA

NA SADNAF

"Abba b'oye boyen da kayi a baya shi ya jefa ka a cikin wanan matsalar da yasa har hajiya umma ta bar gidanan Abba ni dan ka ne bazan so ka tozarta ko ka wulakanta ba idan har kasan akwai wani abu da kake ganin kana b'oye mana da ya shafe ka gwara ka fito ka fada min idan baza ka iya fada wa kowa ba ni ka fada min Abba zan iya taimaka maka da shawarwari"

Salis rawar da jikinsa keyi gumi na karyo masa yasa shi zama a gefen gadon ya dafe kansa har Ashraf ya idda maganarsa yaji ya kasa ma bud'e baki yayi magana taya zai kalli fuskar dansa ya fada masa hanyar da yake bi kudade ke shigo masa,a baya idonsa ya rufe da san ya zama hamshakin mai kudi hakane yasa da Zainab ta nuna masa hanyar bai yi wani dogon tunani ba ya amsa tayin dan kudadene ke shigo musu da yawa zainab kuwa Allah kadai yasan kadarorinta takunsa da ya iya ne yasa ba mai tab'a zarginsa.

A shekarar nan ya fara tunanin barin harkar dan akaran kansa yasan watarana asirinsu zai iya tonuwa.

Muryar Ashraf daya zauna gefensa ya katse masa tunanin da ya ke ya dago yana kallonsa da jajjayen idon sa da suka kada suka yi ja har lokacin wayarsa sai ringing yake da haka Ke Kara daga masa hankali

"Abba dan Allah ka fada min menene b'oyayyen sirrin ka da kasan idan har ya tonu zaka shiga matsala muma mu Shiga tashin hankali"?

"Ka tayani da Addu'a kawai Ashraf Allah ya fiddani fada ma masifar da na jefa kaina ba abinda zai kareka dashi sama da tashin hankali tashi ka tafi inasan na kadaice na samu nutsuwa"

"Abba dan Allah"!!!

"Ashraf ka fita nace ko"?

Ashraf mik'ewa yayi a hankali ya fice daga d'akin yana jin hankalinsa na Kara tashi ba abinda yake darsuwa a ransa sama da mahaifinsa kila Dan yankan kai ne ko Kuma kidnapping yakeyi ya zama dole ya sa mai ido ya Kuma fara bin didiginsa ko zai gano wani abu"

Ashraf na fita ya d'auko wayarsa dake yashe a kasa,sai yaji tashin hankalin daya Shiga a baya nafila ne akan wanan daya tunkaro shi.

Kamar uje jira yake ya d'auki wayar kiransa ya kara shigowa, baya so ya daga yaji wani sabon tashin hankali kila duk an kamo su,bai san sanda ya mik'e tsaye ya fara safa da marwa a d'akin ba tunanin daya dar su a zuciyarsa yasa shi nemo lambar da yayi Saving da L worker dan duk wayanda suke harkar da worker ya musu saving,

har Kiran ya kusa tsinkewa kafin yaji ta d'auki wayar da "Alhajin Allah"

"Jidda kinji labarin an Kama John a hanya zaizo wajenki"

"Innalillahi wa Inna ilaihi rajiun wlh banji labari ba a Ina aka kamasu?ya akayi aka kamasu"

"Dazun nan uje ya kirani yake fada min yanzu abinda nake so da ke ki sallami yaran nan gabad'aya ki basu kudi mai dan yawa ki cire layinki ki Yar dashi idan da hali ma ki bar kasar duk abinda za'ayi kome za'ayi dan Allah karki Kira Sunana ki kira sunansu John ki kafe akan su kika sani"

"Ni fata kake a kamani ne Alhaji taya zan bari ma a kamani ai insha Allahu idan har an rik'e alkawari bazasu tona ba nidai bari na fara Shiri"

Kit yaji ta Yanke wayar

Zazzabi da rawar da jikinsa keyi yasa shi koma Kan gado ya kwanta ya lumshe ido Yana tuno ranar da Zainab ta fara gabatar masa da harkar da Rabin kudinsa ta nan yake samu,sai yaji dama zai iya maida hannun agogo baya da sam bai amshi tayin da ta masa ba.

"Ana samun mahaukatan kudi am telling you karka tsaya wani dogon tunani Salis,larabawan nan basuda hankali in ponds suke biya"

"Zainab wanan abin is very risk wlh har yanzu jikina rawa yake da abinda nagani bazan iya ba gaskiya wane irin rayuwa ne wanan sai kace ta dabobbi"

"Hahah nima da farko haka na ringa cewa amma bashi zaka duba ba kudin kasan mai za'ayi ni zan baka kudaden da zai fasa ma kwakwalwa Wanda duk ta haka na same su nifa badan Ina kaunarka ba wlh bazan koya ma harkar nan ba idan kana ganin dan albashin wata daya da bai Kai dubu dari Ba zai isheka kayi irin rayuwar da kake so to Shikenan sai na rabu da kai
Ta mik'e ta jawo wani akwatinta sai data ta zura hannunta ta fara fito da bandir din dalolli Salis ya gwalo ido Yana kallonta sai da ta ajiye guda goma ta rufe akwatin tana "wanan ni na baka kyautarsa a cikin irin kudin da nake samu idan har zan iya baka irin wannan kudin kasan ba kananan kudi ake samu ba ka je ka sake tunani"

A cikin irin kudin ya turo gida aka siya masa katon fili ya ringa yo aike ana masa gini.

Daga lokacin ya tsunduma kansa a cikin wanan harka a yanzu zainab din ma baya jin labarinta duk ta Inda zai sameta babu,baisani ba ko an kamata ko baa Kamata ba yasan dai ta samu wani bature ta aura shekaru goma da suka wuce.

Kiran dake shigowa wayarsa ya Kara katse masa tunanin da ya tafi ganin mai Kiran yasa yaji wani sanyi na ratsa zuciyarsa yasan tana kaunarsa fushi yasa ta bar gidan,a yanzu kuma mai haddasa masa fitina ta hana shi zaman lafiya ta bar gidan a yanzu idan Allah yasa asirinsa ya rufu a yanzu ne zai samu nutsuwar da yake so ya samu yasan tunda har Yaya mustapha ya fahimce shi zai tilastawa Aisha itama ta dawo gidansa.

Koda ya d'auka a madadin yaji muryar Aneesa muryar Hajiya Binta yaji ta ratso wayar da sallama.

Sai yaji ya kasa amsa sallamar Yana tsoron Kira tayi akan ya saki Aneesa ba dai Aneesa tana nufin ta shirya rabuwa dashi ba,sunansa da ta kira da "Salisu baka jina ne"?

Can kasan murya yace "Ina wuni hajiya"

"Yanzu haka na baka 'yata wata bakwai kawai yarinya duk ta fige ta lalace Ashe dama zuwa kayi ka hadeta cikin matan ka suke gana Mata azaba alkawarin daka d'aukar mana kenan"?

Salis bai iya magana ba dan bai san mai zai ce ba tunda har Aneesa ta iya fadawa Hajiya Binta karya da gaskiya yasan ta hakura da auren ne so take kawai su rabu tunda ya tafi watani bai bata hakkin ta ba Wanda har hakan yasa ta d'auko cucumber tana so ta gamsar da kanta.

"Ka Aiko min da takardar ta dan ta gama aurenka na Dade Ina hango Mata irin wanan ranar ta kafe ta dage ai ga irinta nan da taji wuya ta dawo Salisu ka aiko min da takardar yata nace kaji ko baka ji ba"?

"Hajiya kuyi hakuri karku yanke hukunci cikin b'acin rai inasan Aneesa itama tana sona"

"Ai bani zan raba ku ba ita da kan ta ta nemi na kiraka akan ka saketa ka saketa ta je ta nemi daidai saanta ta aura Kai Kuma kaje kaji da matan ka na baka nan da kwana uku ka Aiko min da takardar ta idan baka aiko ba idan mun had'u a kotu sai ka bata takardar ta"

Kafin yayi magana ta Yanke wayar,ya ajiye wayar a hankali yana "Allahuma ajirni fi musibati wa aklifnin khairin minha"

Kansa kamar ya fashe sabida ciwo ya rasa ma tunanin da zai yi bai san da wan zai ji ba da asirinsa dake neman tonuwa da barin Aisha gidansa ko da sakin Aneesa ta nema a wajensa.

Mik'ewa yayi daga kwancen da yake dan a yanda yake jinsa dole sai ya sha maganin bacci a bakin k'ofa suka yi karo da Hindatu taci ado sai walwali take hannunta d'auke da faranti.

"Alhaji tun dazu Ina jiran ka fito naji shiru shiyasa nace bari na biyo ka da abinci ka samu kaci ko kad'an ne"

Matsar da ita yayi gefe ya nufi dakinsa dan ko magana a yanzu Kuma baya so yayi burinsa kawai ya sha maganin da zai mantar dashi damuwar da ya tsinci kansa Yana bukatar nutsuwa kafin yasan abinda ya dace yayi babban burinsa yanzu asirinsa ya rufu gani yake komai kuma zai zo masa da sauki.

Koda ya Shiga d'akin drawer dinsa ya jawo ya deb'o magangunan ya watsa a bakinsa ya d'auki ruwa ya kora yana k'ok'arin kwanciya Hindatu da ta biyo shi har d'akin tana k'ok'arin zuba abinci ta dakatar da zuba abincin tana "Alhaji dan Allah ka sasautawa kan ka Wanan damuwar da ka sa kanka ka kwantar da hankalin ka ni nasan idan aka kwana biyu a lokacin zuciyar ta tayi sanyi ai bawa bai isa ya wuce kaddararsa ba hakuri zata yi nima so nake gobe naje na bata baki,ai yanzu matsalar ka ta kau tunda har ka rabu da luba dama itace take haddasa komai"

"Hindatu dan Allah kifita so nake nayi bacci na samu nutsuwa idan na tashi zanci abincin"

"Bari na maka tausa sai kaji dadin baccin"

"Hindatu dan Allah ki fita nace"

Hindatu harara ta watsa masa tayi waje tana "Kamar ni na aike shi yaje yayi wa Yar mutane fyade"

Taja tsaki tare da rufo masa k'ofar.

Aisha

"Yaya kai yanzu duk ka yarda da maganar da ya fada maka wlh Allah karya yake duk yanda zai Kare kansa kawai yake nema,idan har da gaske Luba na bibiyar sa mai yasa bai tab'a fada min tana bibiyarsa ba"

"Idan ya fada miki tana bibiyarsa ai ba yarda zaki yi ba sau nawa yana ce miki ki rabu da ita ko ni nan sau nawa na miki fada akan ki rabu da ita ba matuniyar arziki bace daga lokacin da mamy tace min tana zuwa aron sababin kayan ki,taya duk zai zauna ya tsaramin wanan zancen idan ba'ayi haka ba,ke naga alama bakida zurfin tunani da wayo a yanzu ma baki yarda ta saka mishi magani a ruwa ba a ranar da kuka tare"?

"Yaya duk rashin hankalina dai da yace min ta tab'a cewa tana san shi wlh dole na rabu da ita,ni a lokacin cemin kawai yake na rabu da ita baya santa bai tab'a fada min dalilinsa ba,ni Kuma a lokacin abinda yasa ban rabu da ita ba sabida ba abinda tamin, bansan ta yanda lokaci guda zance mata mu rabu ba,ni yanzu duk ba wanan ba ba maganar Luba na bibiyarsa da yanda ya aureta muke ba ya aka yi ya karkatawa muhasim wuya"?

"Daga labarin daya bani bashi ya karkata mata wuya ba dan har Qur'ani naga Yana k'ok'arin daukowa akan zai dafa na hana shi,a duk zargin da muke yanzu Luba tana da masaniya akan abinda ya samu Muhasim zata iya komai dan ta cimma burinta ni na dade ina zargin ta tun kafin ma mijinki ya aureta nasan ba dan Allah take zaune dake ba kema kinsan na sha fada miki,ki bud'e kwakwalwarki ki fadada tunanin ki ki koma baya ki duba tarayyar ku,daga lokacin da ta fara kwadayin irin niimar da Allah ya baki ya Kamata kisan cewar ba matuniyar arziki bace ba badan Allah take tarayya dake ba zata iya komai dan ta mallaki mijinki ta Kuma yi abinda zata juyashi a yanzu bamu san Wanda ya karkatawa muhasim wuya ba amma a labarin da ya bani yace Luba ita taje har office dinsa tace muhasim ce ta fada mata ya akayi duk ba Wanda yasan hakan sai ita yaushe suka yi haka da muhasim a yanzu bincike dai Ashraf zaiyi a matsayin sa na lawyer insha Allahu zamu gano idan tana da hannu a lamarin nan zan Kuma dage da Addu'a insha Allahu gaskiya zata yi halinta"

"Karki manta tunda har Salis ya saketa zataso kowa ma ya rasa ciki kuwa har dake kiyi amfani da kwakwalwarki"

Daga haka Yaya mustapha ya fice daga d'akin.

Da ido Aisha ta bishi har ya fice tana mamakin zuciya irin na yayanta har mutum ya aikata ma irin wanan zaluncin kuma wai har ka ringa k'ok'arin kareshi kwanciya tayi tana k'ok'arin ture maganganun Yaya mustapha dan Sam bataji ta yarda da Salis ba a yanzu ba abinda salis zai fada Kuma ta yarda dashi.

"Burina inga na samu miji irin mijinki tamkar dai Salisu"

"Kawata wlh baki dace da gidanan ba ni na dace da gidanan"

Maganganun da Luba ta fada mata a baya Suka ringa dawo mata, ta tuno lokacin da suka tare a sabon gida yanda ta dage bazata kwanta ba kallo zata yi labarin da Yaya mustapha ya bata ya sakata mik'ewa zaune "idan har ta saka maka magani a ruwa mai yasa baka fadamin ba"?

"Ni ko dai a ranar yayi wa muhasim fyade tunda a sama na barsu suna home work"

Ta Kara jefawa kanta tambaya tana dafe kirjinta.

Luba

Wasshh tace tana runtse idonta cikin azabar zafin daya ratsa gabanta sabida fitsarin da taje yi jiya kwana tayi tana susa har dan jini jini gabanta yayi har da kukanta.

A tattale ta fito daga bandakin ta zauna a gefen gadon tana "Allah ya tsinewa yaron nan Albarka yaron nan ya cuceni.

Wayarta ta d'auko dan ta Kara duba lokaci taga har tara ta wuce shiru Sultan bai zo ba,ita yanzu ba ta ma abincin karyawar take ba burinta kawai ya Kai ta asibiti ta samawa kanta magani dan bazata iya da wanan kaikaiyin da gambo ya samata ba.

Sai dai tana ta Kiran lambar sultan Yana ta nuna mata busy,batasan wane irin waya yake yi haka ba.

Lambar ilham ta kira sai da ta mata miscal uku kafin ta d'auka bata tsaya jiran gaisuwar ta ba dan tasan sai tayi raayi take ma gaisheta.

"Ina yayanki yake? nake ta kiransa haka Ina ta kiransa Yana waya"

"Bana gida naje makaranta"

"Ilham dan Allah ki baro makaranta kizo ki sameni kinji Yar lelena Ina bukatar taimakon ki banida lafiya"

"Mama muna da test da zamuyi Ina Bintu ta rakaki Mana"

"Ilham nifa mahaifiyarki ce kiji nace miki banida lafiya kizo ki rakani asibiti kice bazaki zo ba na Kira Bintu bansan da bintun ba na kiraki"

"Mama test ne damu da zanzo Yanzu ma ga mallamin nan ya shigo ki sake Kiran ya sultan kila ya gama wayar"

Kafin Luba tayi.magana taji ta kashe wayar.

Luba tabi wayar da kallo tana Jin wani abu na tsaya mata a kirji ta kasa yarda wai yayanta ke Neman wulakanta ta yaran da ta haifa a cikinta har gwara ma sultan da ilham,Koda ta sake Kiran sultan busy taji hakane yasa ta gane blocking dinta yayi.

Tafi minti goma tana zubar da hawaye,cikin kwana biyu ta jigata taga tashin hankali a cikin ma masu gudunta har da yaran cikinta.

Mik'ewa tayi ta had'e kafarta dak'yar dan ita kadai tasan mai take ji a kasanta.

Mayafinta ta yafa tayi waje.

Koda ta fita abin hawa ta tara ta nufi asibitin da suke zuwa dan fitowar ta tunanin haka ya fado.mata dan tasan basu san ma ta rabu da Salis ba dole su bata maganguna.

A takaice da Kuka wiwi Luba ta bar asibitin dan likita yace mumunan infection ne da ita mai wuyan Jin magani ya dai hadota da maganguna akan ta ringa amfani dashi tana Kuma zuwa asibitin a Kai akai.

Sai dai tana dawowa hotel din taga Asabe a jingine a jikin motar ta

D'auke kanta tayi kamar bata ganta ba dan a yanzu bata da k'arfin da zatayi masifa dan a yanzu ma kaikaiyi take ji ta zura hannunta a zani tana k'ok'arin susa.

"Ke dalla dakata kike d'auke kanki kamar baki gani ba"...

Assalamu alaikum Yan uwa Ina godiya da adduoi da kulawarku a gareni ngd kwarai Allahu ya bar zumunci na samu sauki Alhamdulillah Ina muku fatan alheri

Sister's duk wacce batayi anfani da sabulun mg's ba ko kit dinsu inamai shaidamuku anbarku acan baya domin duk wnd yajaraba mg's sai sanbarka duk wani Mai tantama Akan kayan gyaranjiki toh tabbas yacire sabulun mg's domin yahadu bakarya zegyarajiki yafidda dattin fata Dama duk wani matsalan fata duk Wanda kefama da matsalan fata walau pimples ko spot, sunburn acne, knuckles,wrinkles,stretch mark dama dukkan wani prblm yajaraba mg's bi'iznillah komai zaizama labari bayan jikinku yy fresh zaisa jikinku yy smooth yadinga glowing,gawanda basa San anfani da Mai zaku iya using sabulun mg's batare da kunbukaci wani Mai b Mai bukata should Chat
08062991549
07046881166
07067210195
Call 08064532391

Team glow♀

Sister's duk wacce batayi anfani da sabulun mg's ba ko kit dinsu inamai shaidamuku anbarku acan baya domin duk wnd yajaraba mg's sai sanbarka duk wani Mai tantama Akan kayan gyaranjiki toh tabbas yacire sabulun mg's domin yahadu bakarya zegyarajiki yafidda dattin fata Dama duk wani matsalan fata duk Wanda kefama da matsalan fata walau pimples ko spot, sunburn acne, knuckles,wrinkles,stretch mark dama dukkan wani prblm yajaraba mg's bi'iznillah komai zaizama labari bayan jikinku yy fresh zaisa jikinku yy smooth yadinga glowing,gawanda basa San anfani da Mai zaku iya using sabulun mg's batare da kunbukaci wani Mai b Mai bukata should Chat
08062991549
07046881166
07067210195
Call 08064532391

Team glow♀
WANAN LITTAFIN NA KUDINE BIYA 500 TA WANAN ACCT 0272061655 WEMA BANK NAFISA NUHU KO KATIN MTN KO AIRTEL TA WANAN LAYIN 08033719070 DOMIN KI MALLAKI NAKI KI MUTANEN NIGER KUMA KU TUNTUBI WANAN LAYIN
+227 96 82 89 84 DUK WACCE TA MIN SHARING NA BAR TA DA *RABBI ZAI FIDDA MIN HAKKI NA DA IZININ ALLAH DOMIN BA YAFEWA NAYI BA*

NI DA KISHIYOYINA

NA SADNAF

PAGE 29

Luba cigaba tayi da tafiyar ta Asabe kuwa ta sha gabanta tana " A wane dalili zaki kira yusuf jiya a Ina kika Samu lambarsa?kin d'auka wasa nake miki ko ke a yanzu bazaki tab'a ramin kanki ba kenan?kin d'auka ni Aisha ce da zan zauna ki kwace min miji?

"Asabe dan Allah ki bani hanya na wuce banasan tashin hankali ni ba da gangan na Kira mijinki ba sultan nakeso na Kira nayi kuskure wajen kiransa"

"Wlh karya kikeyi ni inada lambar mijinki ne da zaki ajiye lambar mijina a wayarki luba banida mutunci idan kika ce zaki ja dani wlh wlh sai naga karshenki ki fito da wayarki ki goge lambar mijina a yanzu nan a wayarki ko na miki rashin mutunci ai sai ma na tona miki asiri daga nan wajen Salisun nayi duk sai na tona miki asiri idan aka kulleki zan ga da yanda zaki na yiwa mutane kwacen miji"

"Asabe ban cancanci wanan zaluncin daga wajenki ba kin kwace min dukiya kin hanani,kinsa inata garari a titi iya wanan bai miki ba sai kin hada da yimin barazana Zaki tona min asiri alhalin koma mai na aikata ke kika bani shawarar nayi haka idan har kinsan hallaci wlh baza ki min abinda kike min ba jiya da na kira yusuf bansan inda zan kwana ba bansan Wanda zai taimaka min ba baba ya rufe ido ya koreni yace bazan zauna masa a gida ba banida inda zanje , korar da Baba ya min yasa na kira yusuf jiya dan na rokeshi kudi ko zan samu na samu na iya kama wajen kwana amma bawai haka kawai na tsiri kiransa ba ko zan yiwa kowa kwace wlh Asabe bazan iya miki ba"

"Ai tunda kika yiwa Aisha ba Wanda bazaki iya yiwa ba Luba kefa kina da san kai da san zuciya halinki da nasani yasa nak'i bari ma ki zauna a gidana amma a yanzu kin dan bani tausayi hajiya Luba zan taimaka miki muje daga mota"

Ta juya Luba ta bita da wani irin kallo tana ayyana abubuwa a ranta

A mazaunin driver Asabe ta zauna Luba ta zauna a daya b'arin hannunta cikin zaninta tana susa

"Luba idan kika min akuya wlh zan miki na wuce duk yanda kike tunani zan barki ki zauna a gidana da sharadin a duk ranar da na kamaki da laifin cin amanata a ranar wlh wlh ba abinda zai hanani tona miki asiri a ranar zan miki abinda har ki koma ga Allah baza ki mantani dani ba,idan Yusuf ya dawo banaso ko motsin ki yaji har lokacin da zai fita ko haduwa bana so ma ku tab'a yi zan yi k'ok'ari naga na baki rancen kudi kije wajen Mallam ya miki aiki akan Salisu duk da kinsan zaman haramun zaku yi

tunda ya riga daya sake ki saki uku idan Allah yayi kin koma zaki bani miliyan biyar kin yarda ko baki yarda"?

"Indai Mallam yamin aiki na koma zan baki miliyan bakwai na miki alkawari"

"Jeki debo kayan ki mu tafi"

"Banida wani Kaya sai na jikina ai na fada miki ba abinda nake dashi yanzu ma haka daga asibiti nake banida lafiya"

Tab'e baki Asabe tayi ta jawo murfin motar ta rufe suka dau hanyar gidanta

Luba kuwa hamdala kawai take a ranta zata biyewa Asabe ne kawai dan ta samu cikar burinta dama wajen zaman da babu yafi daga mata hankali idan Asabe tasan wata ai batasan wata ba idan takamarta mugunta zata nuna mata ko aji daya batazo ba.

Koda suka isa bayan boys quaters Asabe ta kaita tana wani huhura hanci ita a lailai ga ta zata taimaka mata tsabar wulakanci duk girman gidan ta rasa wajen da zata ajiyeta sai d'akin da tarkace ake sawa

"Yanzu zan d'auko miki katifa akwai bandaki a ciki nan dai yafi miki babu ko ni fa dan inada zuciya musulunci ma yasa na taimake ki dan ni so nayi wlh na miki rashin mutunci dazu bansan Kuma mai yasa na canja ra'ayina ba ki goge lambar Yusuf yanzu a wayarki Ina kallonki

Luba lambar Yusuf ta dubo ta haska mata kafin ta goge,duk da haka Asabe bata yarda ba sai da ta karbi wayar ta shigar da lambar Yusuf taga baya cikin contact dinta tayi blocking lambar tare da goge lambar tana "bari na dubo miki Kaya a cikin tsofaffin kayana ki ringa sawa"
Daga haka ta fice daga d'akin.
,duk yanda Luba ta so hadiye bakin cikin wulakanci da Asabe ta mata kasa hadiyewa tayi sai da ta fashe da kukan bakin ciki tana karewa dakin kallo wulakantata kawai dama Asabe ke San yi dan ko d'akin mai gadi yafi wanan girma ko a mafarki akace mata zata tab'a Shiga gararin rayuwa irin wanan karyatawa zatayi rashin hankali da rashin zurfin tunani ya kaita ya baro ta cutar da kanta ta tonawa kanta asiri dan ba Salis ta tonawa asiri ba ta tuna girman dakinta da haduwarsa ko a yanzu kayan da bata dinka ba na kasan akwatinta ya kusa Sha biyar tsadaddu Wai duk yanda take da Asabe yau Asabe ita ke wulakanta ta haka da ace tana da wajen zama wlh ba abinda zai tab'a sakawa ta biyo Asabe,a bata da yanda zatayi ta biyo Asabe minti goma a tsakani sai ga Asabe da Kaya ta rungumo tana zuwa ta watsa a tsakar dakin,Luba tabi Kayan da kallo duk tsofafin kayan Asabe ne duk babu na arziki ma a ciki.

"Sai anjima kenan sai kifito ki dan shashare mana gidan kafin mai gidan ya dawo ya naga Wai kina b'ab'ata Rai ne" ko ban miki k'ok'ari ba?

Murmushin yake Luba tayi tana "kinyi k'ok'ari ngd"

"Aa toh na d'auka zakice ban k'ok'arta Miki ba sai ki dan fito anjima kiyi abinda zakiyi kafin ya dawo ko"

Luba gyada Mata kanta tayi dan bazata iya magana ba da ido ta bita har ta fice daga d'akin

"Dan Allah ki bani rancen kudin nan Luba idan baki taimaka min ba wa zai taimaka min haba Aminiyata"

"Asabe ba hanaki zanyi ba banida kudi ne Amma ki bari Alhaji ya dawo Zan tambaye shi nasan bai isa ya hanani ba kinsan idan inasan abu ya hanani yanzu nan zance zan tona masa asiri"

Dariya Suka kwashe dashi sai da Asabe ta take cikinta ta hada da take away a lokacin batayi aure ba da kuwa Salis ya dawo haka ta saka shi a gaba sai da ya bata kudin,ta Kira Asabe akan tazo ta karba wanan kad'an daga cikin Abubuwan da tayi wa Asabe bazata iya fadar ma morar da Asabe ta mata ba Wai yau ita ta kawo gidanta da Sunan Yar aiki ta cije lebbenta a lokacin da ta tuno baya tana "Asabe kafin ki wulakani ni zan wulakanta ki"

Tana susa ta dan gyara d'akin ta Shiga bandaki tayi wanka a cikin kayan da ta kawo mata ta dauko daya ta saka tafi Asabe kib'a dole kayanta suyi mata kadan amma haka tasa a jikinta.

Ta shafa maganin ta a jikinta ko kasanta zai rage mata kaikaiyi
Wato har kumbura jikin ta yayi sabida tusa inama tana da halin da zata shafawa asabe wanan masifar da ta shafa mata.

Yunwa take ji amma ba yanda zatayi dan tasan ta nemi Asabe ma ta bata abinci sai ta wulakanta ta.

Karfe biyu ta fito daga d'akin tayi cikin gidan sai take Jin wani banbarakwai a baya a motarta take zuwa Asabe tazo ta tareta wai yanzu ita zata je ta mata wanke wanke har da shara.

A Palo ta tarar da ita ta mimike kafa akan kujera tana Shan fruit basu cewa juna komai ba tayi kitchen dan ta fara wanke wanken tana shiga kitchen tajiyo muryar Asabe tana "Kar fa ki taba komai wanke wanke kawai zakiyi ki fito sai anjima zan zo na dorawa mijina girki da kaina"

Luba bata ce komai ba ta fara wanke wanken tana tausar zuciyarta dan tasan tana dab da samun cikar burinta zata shanye duk wulakanci da Asabe zata mata.

A takaice tana ji tana gani ta zama yar aikin Asabe sabida kawai ta samu wajen da zata saka hakarkarinta,abincin ma bana arziki take bata ba kamar ta roka,ko kad'an ba mai yarda wai sun tab'a wani kawance dan Asabe har wani aikenta takeyi sabida kawai ta wulakanta ta wanan kenan.

Salis

A cikin sati guda idan ka ganshi dauka zaka yi ya shekara Yana jinya sabida tashin hankali a yanzu lambar uje ma baya tafiya gani yake a kowane lokaci Yan sanda na iya duro masa.

A yau ya shirya fita asibitinsa bawai dan yasan zai iya tsinana komai ba sai dan so yake ya dan Kara samun nutsuwa kafin yasan abin yi.

Iyayen Aneesa sun matsa masa har sai da ya saki Aneesa saki daya,rabuwarsa da Aneesa ya kara hargitsa shi.

Koda ya isa office haka ya ringa sakawa Yana kuncewa a karshe ya d'auko wayarsa ya fara k'ok'arin Nemo lambar hajiya fauza turo k'ofar da akayi da shigowar Hajiya fauza da wasu a cikin fararen kaya yasa gabansa wani irin faduwa amma yanda yaga Hajiya fauza fuskarta ba wani tashin hankali yasa shima ya aro jarumtaka ya dake Yana amsa sallamar da suka masa sukayi musabiha da mutanen da kana ganinsu kasan hukuma ne seat ya nuna musu akan su zauna suka girgiza masa Kai "dayan ya fito da I D card dinsa Yana "Alhaji idan bazaka damu ba muna so "zamu tafi da Kai office akwai Yan tambayoyin da zamu maka"

"Dafatan ba wani abune ya faru ba"?

"Sai dai munje daga office din zaka ji"

"Alhaji Salis mik'ewa yayi Yana "Muje"

Sallati kawai yake a zuciyarsa Yana Addu'a Allah ya rufa masa asiri tunda yaga Hajiya fauza yasan asirin sa ya gama tonuwa amma zai dake duk tambayar da zasu masa sai ya musanta musu.

Koda suka isa wani office suka Kai shi ba karamin k'ok'ari yayi wajen Aron jarumtaka ba, iya fuskar Wanda Suka Kai shi wajensa ya isa ya Kada Masa yayan hanji dan fuskarsa sam ba annuri takardar dake gabansa ya matsar gefe yana "Alhaji Salisu gidan marayun nan daka bud'e shin mallakin ka ne ko na wani"?

"Mallakina ne ba na wani ba"

"Da kyau ko zaka iya fada mana manufarka ta bud'e wanan gidan marayun"?

"Dama ana bud'e gidan marayu da wani manufa ne ai ana bud'e gidan marayu ne sabida a taimaka wa Yara marasa galihu da wayanda suka rasa iyayensu ko"

"Alhaji muna zargin ba dan wanan manufar ka bud'e Wanan gidan marayun ba ka bud'e ne sabida wata biyan bukatar ka ko zaka iya fada mana Inda aka Kai Yan matan da samarin dake gidan marayun Alhaji ka fito kawai ka fada mana gaskiya karka wahalar damu"

"Ba inda nake Kai su Ina dai d'aukar nauyin karatunsu tamkar yanda kowa yasan Ina d'aukar nauyin komai daya shafi Wanda ke gidan marayun nan ko a yanzu haka karatu suke yi a waje"

"Baka shirya fada Mana gaskiya ba Alhaji domin akwai yaran ka da muka kama itama mai kula da gidan marayun ta dage ba inda kuke Kai yaran yanzu Ina wanan yarinyar take"?

Mutumin ya tura masa hoton wata Yar budurwa da bata fi shekara Sha biyar ba gabansa Yana "wane kasa ka turata karatu kuma a yanzu ya za'ayi mu sameta"?

"Banida masaniya dan iyakacina d'aukar nauyinsu bazai yu na Kuma ringa bibiyarsu ba Hajiya fauza ita tasan komai a kansu zata iya sanin kasar da take da Kuma yanda za'a sameta"

"Muktar"

Mutumin ya kwalla Kira da sauri ya shigo ya Sara masa yace "jeka shigo min da mai kula da gidan marayun nan".

ASHRAF

A cikin kwarewa da aikinsa ya fara bincikensa kuma Allah cikin ikonsa Yana ta samun duk abinda yake so Yanzu saura kad'an ya kamalla bincikensa.

A yau gidan Yaya mustapha ya nufa wajen karfe uku na yamma a lokacin da ya isa gidan Yaya mustapha baya nan Aisha da Aunty mamy ya tarar a falo sai muhasim dake Kan kekenta da alama duk ba kowa a gidan.

Har kasa ya duka ya gaida Aisha da Aunty mamy kafin ya samu waje ya zauna Yana "hajiya umma na fara bincike ne akan case din muhasim yanzu akwai tambayoyin da zan yiwa muhasim idan bazaku damu ba inaso Zan Kai ta d'aki"

"Kana da hankali kuwa muhasim da bata iya magana zaka yiwa tambayoyi"

Murmushin Ashraf yayi Yana "Nasan bata magana ai hajiya umma ki barni kawai nayi aikina"

"Kayi haukanka dai"

"Jata ka kaita d'akin Ashraf karka biye mata batasan ku din Allah ya muku baiwa bane idan har kasan da yanda zakayi din ka kaita d'akin"

Ashraf mik'ewa yayi Yana dariya ya hau Jan keken muhasim yayi d'akin su da ita wuyanta na nan a karkace tana ta wurga idanu

A gabanta ya zauna ya bud'e jakarsa ya fito da wani farin takarda da biro a hannunsa

Cikin murmushi ya kalli Muhasim da shi take kallo wuyanta na karkacen hakan yasa yaje ta wajen da zata iya ganin komai

Ya fara magana yana "Aunty muhasim nasan duk abinda zan fada kina jina amma bazaki iya bani amsa ba,inaso na gano wanda ya karkata miki wuya ne duk tambayar da na miki idan hakane ki lumshe idonki idan ba haka bane karki lumshe idonki kinji"?

Gani yayi ta lumshe idonta ya saki murmushi dan yasan taji mai yace

Hoton Salis ya fara daukowa ya haska mata Yana "Shi ya miki fyade ko"?

Lumshe idonta tayi hawaye na zubo Mata

Ta sake bud'e idonta yace "Kuma shi ya karkata miki wuyanki sabida Kar asirinsa ya tonu ko"?

Sai yaga ta tsura masa ido bata lumshe idon ba

Gyada kansa yayi Yana "nagane shi ya Miki fyade amma bashi ya karkata miki wuya ba"

Ajiye hoton yayi ya d'auko hoton Luba ya haska mata Yana "ita ta karkata miki wuya ko"?

A madadin ta lumshe idonta jijjiga ta farayi idanunta na Kara yowa waje Wanda hakan ya balain bawa Ashraf tsoro har sai da ya saki hoton yayi kanta Yana sallati.

Luba

Karfe 11pm na dare ko kad'an batayi bacci ba a yau take so ta aiwatar da shirinta dan Yusuf mijin Asabe yayi tafiya.

Da mukulin da ta sata ta bud'e k'ofar palon ta shige tare da nufar d'akin Asabe cikin sand'a.

A hankali ta tura k'ofar dakin ta shiga a bandaki ta ringa jiyo motsinta bata ganta a d'akin ba,bandakin ta nufa ta tsaya a bakin k'ofa minti biyar a tsakani Asabe ta bud'e k'ofar ganinta a tsaye a bakin k'ofa yasa ta tsorata tare da ja da baya tana "Luba uban me kike nema a dakina waye ya baki iznin shigowa dakina"?

Murmushi Luba ta saki tana "Asabe kenan wato sai na nemi izninki zan shigo d'akin ki"? Asabe ke karamar Yar iska ce ni Zaki kwacewa kudi ki Kuma maidani Yar aikinki sabida bakida kunya nabiki ta lallami ki bani kudina kin hanani na Miki kuka ki bani kudina kin hanani tunda kin hanani kudina zan dauki kudina ta karfin tuwo"

"Luba fitar min a d'aki bansan ma wani tsautsayi yasa na kawoki gidana ba na manta ke din Yar akuyace bakisan hallaci ba"

"Zaki iya cigaba da juyani a lahira Asabe ba dai a gidan duniya ba"

Luba ta zaro wukar da ta boye a bayanta

Asabe kuwa ganin wukar yasa ta ja da baya tana "Luba kasheni zakiyi"? Idan har dan kudinki Zaki kasheni wlh a yau zan baki"

"Kin makara Asabe"

Ta Shiga bandakin Asabe ta fara k'ok'arin tsalla ihu luba ta daga wukar ta caka mata a cikinta Asabe ta zube a kasa....,..

Ayiri yiri □□□□□kuna Ina mata matafa nake nufi bamuna mataba 😀😀A&Z COLLECTION takawomuku ingantatun supplement□□□□
Muna da supplement na Infection
Munada da supplement na gyaran jiki Wanda zaisa jikinki yayi kyau fata tai laushi da sheki □□□munada na gyaran breast succiko su tashi tsaf gwanin Sha awa□□ munada na matsi dazai matsaki ciki dawaje bawai ki iya farkoba kuma yasaukarmiki da ni ima
Muna da na gyaran gashi Wanda zaifitomiki da gashi 😍😍
Dawanda zakiyi haske duka jikinki bawai fari na bleaching ba 😀😀

A&Z dealer ce kayanmu suna da sauki sosai price dinmu price din sari ne zaki samu kayanmu cikin sauki alhmdulillah□□□□
Ga kadan daga ciki

1 Royal jelly karami 2500

2 Juliet Eve 8500
3 Amirna 8k
4 Vitamin c 2500,2300
5 vt e 2k
6 collogen + glutathione 2k
7 whitening gummies 2200
8 surga wanita 2500
9 khusus 3500
10 majakani 2500

Price din sari□□□□nasan kodaga haka zaku gane A &Z gidan sauki ne□□□□□□□□
Masu siyan daidai kuma bambancin kadanne

Muna garin Kano Dan neman Karin bayani Kira ko whaspp 09037870422

Karku manta muna tura Kaya duk garin dakuke inkiyi siyayyama dayawa muyi Miki free delivery □□□yan Kano kayanku har kofar gida cikin aminci□□□

Ayiri yiri □□□□□kuna Ina mata matafa nake nufi bamuna mataba 😀😀A&Z COLLECTION takawomuku ingantatun supplement□□□□
Muna da supplement na Infection
Munada da supplement na gyaran jiki Wanda zaisa jikinki yayi kyau fata tai laushi da sheki □□□munada na gyaran breast succiko su tashi tsaf gwanin Sha awa□□ munada na matsi dazai matsaki ciki dawaje bawai ki iya farkoba kuma yasaukarmiki da ni ima
Muna da na gyaran gashi Wanda zaifitomiki da gashi 😍😍
Dawanda zakiyi haske duka jikinki bawai fari na bleaching ba 😀😀

A&Z dealer ce kayanmu suna da sauki sosai price dinmu price din sari ne zaki samu kayanmu cikin sauki alhmdulillah□□□□
Ga kadan daga ciki

1 Royal jelly karami 2500
2 Juliet Eve 8500
3 Amirna 8k
4 Vitamin c 2500,2300
5 vt e 2k
6 collogen + glutathione 2k
7 whitening gummies 2200
8 surga wanita 2500
9 khusus 3500
10 majakani 2500

Price din sari□□□□nasan kodaga haka zaku gane A &Z gidan sauki ne□□□□□□□□
Masu siyan daidai kuma bambancin kadanne

Muna garin Kano Dan neman Karin bayani Kira ko whaspp 09037870422

Karku manta muna tura Kaya duk garin dakuke inkiyi siyayyama dayawa muyi Miki free delivery □□□yan Kano kayanku har kofar gida cikin aminci□□□

WANAN LITTAFIN NA KUDINE BIYA 500 TA WANAN ACCT 0272061655 WEMA BANK NAFISA NUHU KO KATIN MTN KO AIRTEL TA WANAN LAYIN 08033719070 DOMIN KI MALLAKI NAKI KI MUTANEN NIGER KUMA KU TUNTUBI WANAN LAYIN

+227 96 82 89 84 DUK WACCE TA MIN SHARING NA BAR TA DA *RABBI ZAI FIDDA MIN HAKKI NA DA IZININ ALLAH DOMIN BA YAFEWA NAYI BA*

NI DA KISHIYOYINA

NA SADNAF

PAGE 30

"Idan kinje lahiran sai ki tona min asirin shegiya tsinanniya"

Luba tace tana kara hankada Asabe dake wani irin makyarkyata jini na zuba a cikinta.

Zagi ta cigaba da auna mata har sai da taga Asabe ta daina motsi ta baro bandakin tare da rufe kofar ko dar bataji ba balle nadama tayi wajen drawer Asabe ta hau hargitsa mata kaya sai da ta kwashe duka gwalagwalanta da kayanta masu tsada.

Ta zuba su a akwatin da ba komai a ciki ta cigaba da hargitsa d'akin har sai da ta samu kudade a karkashin gado shima ta zuba su a cikin akwatin.

Ta rufe akwatin ta Kara lek'a bandakin ta Kai hannunta hancin Asabe da tayi shame shame a cikin jini taji bata numfashi ta fito daga bandakin tayi hanyar waje tana Jan akwatin sai da ta kara bincike d'akin mijin Asabe ta samu kudade a ciki ta kwashe duka ta saka a akwatin ta zauna palon tana tunanin garin da zata koma dan barin garin zata yi dadin da taji Yusuf bai San tana gidan ba sai maigadi,ta karanci Mai gadin Yana da ibada da fita massallaci Yana tafiya massallaci zata bar gidan.

Haka ta zauna a palon tana kissime kissime da akwatin a gabanta har sai da ta ji kiran sallah Asuba.

Ta mik'e a hankali ta nufi wajen window tana leka maigadin.

Tana kallon lokacin daya fito Yana hamma da butarsa a hannu sai da taga ya fita tare da rufe kofar tayi sauri ta fito tana Jan akwatin dan hijabi tasaka har kasa,sai da ta fito daga gidan hankalinta ya kwanta.

Sauri kawai take zubawa ko a yanzu batasan Inda zata dosa ba tafiyar kawai take a kafa ba ma abin hawa balle ta hau ya kaita tasha dan garin Lagos taji a ranta zata tafi dan ba yanda za'ayi a iya biyota har can Lagos tasan ma da wuya asirinta ya tonu a gane ita ta kashe Asabe tunda ba wanda yasan tana gidan mai gadi ma tasan ba lailai ya zargeta ba yanda ta Kara hargitsa ko'ina na gidan tasan zasu zargi Yan fashine suka shigo gidan suka kasheta.

Ta tuno yanda ta bar Asabe a cikin jini taja tsaki a fili tana "Ke Kika jawowa kanki da ace kin bani kudina cikin ruwan sanyi da ban aika ki lahira ba Kya je ki hadu da kishiyarki lami da kika kashe haba sai dukan yamin yawa ga rashin kudi ga rashin miji da wane zanji"

Kamar dai mahaukaciya haka taringa tafiya tana surutai haka ta ringa tafiya har sai da gari ya fara haske masu abin hawa suka fara dan wucewa ta tsayar da wani tace ya kaita tasha.

Koda suka isa Tasha wajen da ake lodin Lagos tayi,irin zungureren motar nan masu kwasar fasinjoji da yawa ta samu sai da ta samu awa wajen uku kafin ya cika su dau hanyar Lagos da bata tab'a zuwa ba sai wanan karon.

Salis

Duk yanda yake d'aukar abin zai zo da sauki sai da suka rik'e shi akan sai sun tura shi station zasu cigaba da gudanar da bincikensu hankalinsa idan yayi dubu sai da ya tashi bai ga alamar kudin cin hanci zaiyi aiki a wajen su ba.

Wai a haka ma dan Yana da kudi suka dan daga Masa kafa.

Koda suka je station din aka mika case din wajen Dpo akan zaa cigaba da gudanar da bincike akan sa.

Alhaji Salis fadar tashin hankali da yake ciki b'ata bakine baiso sanar wa da kowa halin da yake ciki ba dan gani yake abin kunya ne ma wani yaji labarin wai zargin da ake masa,a ba yanda zaiyi da cin hanci suka bashi wayarsa ya nemi Ashraf a waya akan yazo ya same shi a station Hajiya fauza ma an kulleta duk da itama ta kafe akan taimakawa yaran suke ba wani manufa da suke dashi na kai yaran waje.

Minti sha biyar da Kiran ASHRAF sai gashi yazo station din sai da ya gwada musu I'd card dinsa kafin suka barshi yaga Salis da ya kara zabgewa sabida tashin hankali.

"Abba mai yasa Suka kawo ka nan Abba kaga abinda nake gudu ko"

"Ashraf yanzu kayi yanda zakayi a bada belina muje daga gida tukunna zan gaya maka komai"

Ashraf sai da yayi dagaske Suka bada belin Salis sabida yaje musu a matsayin lawyer Salis.

Koda suka d'auko hanyar gida ba Wanda yacewa wani komai Salis kuwa rufe idonsa kawai yayi Yana Jin inama duk abinan dake faruwa a mafarki ne,a lokaci guda duk asirinsa ya tonu.

Yanda zai bawa Ashraf labari kawai take tunani yanda zai samu ya wanke kansa daga zargin da ake masa kawai yake dan sauran dan mutuncin nasa daya rage idan har labarin zargin da ake masa ya fita yasan zub'ewa zaiyi a idon kowa har gwara.masa ma fyaden muhasim da wanan abun kunya da Allah wadai dake neman samunsa.

Dana sani keya ce Allah yasan yayi matukar nadamar halin daya jefa kansa zai iya cewa san zuciya ya kai shi tunda Yana dan samun na rufin asiri ta harkar Ngo din da yake zainab da dage ta ringa kwadaita masa har sai da ya tsunduma harka Yama fita zakewa a harkar.

Koda suka isa gida d'akinsa ya shige sai yaji Yana Jin kunyar Ashraf Mai yasa bai tab'a tunanin irin wanan lokacin na zuwa da asirinsa zai tonu yaji kunyar mutane da na yayansa.

Sallah kawai yayi ya kwanta baisan Kuma binciken da za'ayi iya wajen da zai tsaya ba,baisan ya akayi har aka gano su ba.

Shigowar Ashraf d'akin yasa yayi saurin maida idonsa ya rufe Yana jinsa har ya zauna yasan kallonsa yake tsawon mintuna biyar a tsakani Ashraf ya fara magana yana "Abba inaso ka bani labarin sirrin da kake boyewa da har ta Kai da asirn ka ya tonu da tun farko ka fadamin da kila na samu maka hanyar da asirinka zai rufu Abba lokacin boye boye ya wuce ka fadamin kawai iya gaskiyar ka ni lawyer ne zanyi iya k'ok'arina domin na kareka duk da nayi rantsuwa akan goyon bayan gaskiya duk runtsi duk wuya amma babu yanda zanyi tunda rufin asirinka rufin asirin mu ne gabad'aya"

Ajiyar zuciya Salis ya sauke kafin ya bud'e idonsa ya sauke akan Ashraf cikin wani irin murya ya fara bashi labari

Waiwaye

Da Zainab kawai yake muamalla a lokacin dayaje waje karatu,hasali ma zai iya cewa ita ta makale mishi duk da kana ganinta kasan kudi ya zauna mata a matsayinsa na dalibi haka take kashe masa kudi,kamar bata san ciwon kudin ba har yakan yi mamakin yanda take samun kudin,dan a labarin da ta bashi lyayenta sun rasu ba kuma samari yake ganinta dasu ba ballantana ya zargi ko su ke.kashe mata kudi,abinda ya kara daure masa kai ba iya shi kadai take kashewa kudin ba duk wayanda take mu'amalla dasu suna morarta,abinda ke dan daure masa kai bai wuce yanda take muamalla da mata da yawa a wata Kuma zatayi tafi kasar Dubai sai ta kwana biyu kafin ta dawo.

A lokacin da tayi tafiya salis Kuma ke samun damar da zaiyi nashi tsalle tsallen dan a gidanta ma yake zaune.ita ta sabar masa da wani irin rayuwa na san Mata.

A irin wanan lokacin ta dawo daga tafiya Yana makaranta yana dawowa ya tarar da ta dawo.

Da niki nikin akwati sai da suka samu nutsuwa da juna suna hira yake tsokanarta da Ina tsarabar da ta yo mishi dariya ta saka masa tana ba ta kawo.masa wani tsaraba ba shi kuwa ya mike yana bata isa ba baiyi wata wata ba yayi wajen akwatin nata ya fara k'ok'arin bud'e k'aramin.

Kafin ta taso har ya bud'e akwatin

A tsorace ya mike tsaye Yana gwalo idonsa waje dan.tunda yake bai tab'a kudi mai yawa haka ba,ita kuwa ta karaso ta rufe akwatin tana dariya yanda ya zaro ido.

A ranar ya kasa hakuri har sai da ya tambayeta da Ina take samun kudi haka?

Tace mishi ya bata lokaci zai fada mata idan shima yanaso ya zama mai kudin duk zata nuna masa hanya.

Haka ya ringa naci Yana binta dan ta fada masa Inda take samun kudin amma tana kakaucewa a karshe da ta gaji da nacinsa ta masa alkawarin tafiya dashi.

A haka watarana ya shirya yabi Zainab zuwa dubai,a nan ya gano kazamin rayuwar da Zainab take kudi ke shigo Mata,ita ke nemo wa larabawan masu kudi Yan mata da suke muamalla dasu,muamallan ma irinta da dabobbi su Kuma su biyata ita Kuma ta biya yan matan.

Larabawan basu dauki bakakken fatan a bakin komai ba dan ba iya amfani suke dasu ta baya ba har idan zasuyi ba haya ko wani abu a jikin matan sukeyi da suka zabi

neman kudi ta karfin tuwo zainab bata tsaya iya nan ba ta hada da muamalla da miyagun kwayoyi.

A ranar salis bai iya bacci ba sabida tashin hankali ya kasa yarda da irin rayuwar da yaga masu kudin nayi da yan matansu bak'akk'en fata wani ma bashi ke amfani da macen ba karensa zai samowa mace lafiyaye shi ma yaci dadinsa da mutum.

Har suka dawo zainab bata gane kansa ba dan shi dai abinda ya gani ya daga masa hankali daga labarin da Zainab ke bashi tana safarar Yan mata da kwayoyi ta kaiwa larabawan nan su bata kudi,tana nunawa Yan matan taimakon su zatayi da hanyar nema musu aiki ko wani abu basa sanin ainihin aikin da zasuyi sai idan ta Kai su.

Ta Kara da "sabida kaunar da nake ma na gwada maka hanyar da nake samun kudi,aikin likita ko wani abu ba inda zai Kai ka idan dai har kana so kayi mugun kudi sai ka hada da wanan sana'ar da nake da ke shigo min da kudi kafara da safarar cocaine sannu a hankali idan ka koma kudi sun zauna maka sai ka fara hadawa da wanan da shi yafi shigomin da kudi"

"Zainab bazan tab'a iya wanan sana'ar ba har yanzu da nake zaune Ina ta mamakin abinda na gani wanan wane irin rayuwa ne sai kace ta dabobbi Ina ma zan samo mutane Kai bazan iya ba harkar cocaine dinan akwai hatsari"

Murmushi zainab ta masa a ranar ta Masa kyautar daya kusa fasa masa kwakwalwa tuni yaji tunaninsa ya rabu gida biyu duk da bai ji zai iya ba haka zainab ta ringa kwadaita masa da kad'an kad'an ya fara harkar cocaine din har shima kudade suka fara shigo masa ta hada shi da masu kudin gaske.

A haka watarana zainab ta kamashi da wata kawarta sukayi kaca kaca da ita dan har maganar Aure take masa wanda ko mahaukacin Kare ne ya cije shi ba abinda zaiyi da ita.

Koda ya dawo gida Nigeria a haka ya cigaba da sana'arsa a boye ba Wanda yasani da larabawan nan da Zainab ta hadasu,a hankali suka fara masa maganar ya musu hanyar da zai na turo da Yan mata da samari zasu rubanya kudin da suke bashi.

Tuni ya fara tunanin ta yanda hakan zai yu batare da an tab'a gano shi ba hakan yasa ya Nemo wata Hajiya fauza wata bazawara ya bata wanan kwangilar akan ta ringa musu hanyar zai na bata manyan kudi.

Ita ta bashi shawaran ya bud'e gidan marayu su fake da taimakawa marayu da marasa gata idan yaso sai su fake da turasu kasar waje karatu suna turasu wajen larabawan.

Da haka Salis ya hada kazaman Sanaa guda biyu idan Suka tura Yara waje da Sunan karatu wajen hajiya jidda da ta silar zainab yasanta a wajenta yaran ke sauka ita ke musu aikin daga can shima Salis na biyan ta John ke jigilar kai su yaran da suke kaiwa basa tab'a sanin ba karatun aka tura su ba sai sunje daga can shima sai an kwana biyu.

Shi dai Salis direct shi ake turowa kudin.

Kasa bud'e idonsa yayi a lokacin da ya gama bawa Ashraf labari Yana Jin Ashraf na sheka sallati shi kansa a zaunen da yake ji yake kamar kasa ta bud'e ya shige sabida

kunya taya zai so mutane su san ba dan Allah ya bud'e wanan gidan marayun ba sai a yanzu yake matukar nadama da bai tsaya iya safarar cocaine din ba.

Fitar Ashraf daga d'akin da karar rufe masa k'ofar da yayi yasa ya bud'e idonsa a hankali yasan a yanzu Ashraf ya tsane shi sai yaji Kuma Yana daya sanin bashi labarin.

Luba

Bata tab'a zuwa Lagos ba tasan dai garin akwai nisa ba kadan ba tun tana kalle kalle tana tunanin sun kusa isa Lagos har sai da tazo bacci ya d'auketa a motar karar bindiga da taji kamar a mafarki yasa ta bud'e idonta hankalinta a balain tashe duk fasanjojin motar su rude da ihu motarsu zagaye da kattin maza duk hanunsu rik'e da manyan bindiga har wasu ma sun shigo cikin motar duk fasinjojin sun durkusa akan gwiwarsu sun daga hannayensu sama yanda Luba taga sunyi itama haka tayi tana sallati tana "Allah karka Basu ikon ganin akwatin nan Allah ka rufamin asiri iya kudin nan da gwalagwalan su kadai nake dashi ya Allah ka rufamin asiri"

Bata ma san a fili take adduar tana kuka ba sai da suka dora mata bindiga aka tayi saurin yun shiru suka cigaba da caje motar tsabar bata san ma a rabata da akwatin Bata yarda sun ajiye mata boat ba agaban ta ta ajiye akwatin.

Jikinta rawa kawai yake a lokacin da suka fara k'ok'arin jan akwatin a sabida dukiyar nan ta kashe Asabe taya lokaci guda zata bari su rabata dashi.

Rik'e akwatin tayi tana "Kumin rai dan Allah na baku Rabin kudin nan karku rabani da akwatin nan" na!!!

Gindin bindigar Suka buga Mata akai bata Kara sanin Inda kanta yake ba,bata san tsawon lokacin da ta d'auka a sume ba sai da ta farfado ta ganta a wani waje kamar tasha idonta ya sauka a saman rubutun da akayi a wajen da take zaune this is Lagos shine your eyes"

Zumbur ta mik'e ta fara dube duben akwatin ta har lokacin a cikin motar take amma ita kadai ba kowa da alama sun iso Lagos din.

Ihu ta kwalla tana "Ina akwatina"

Wani wada ne ya leko motar da broken yace "you Don wake up" (kin tashi"

Since yesterday we Don reach Lagos since you Don wake up come down come dey go your house (tun jiya muka iso Lagos tunda kin farka sauko ki tafi gidanki)

"Ina jakata"?

Luba tace a haukace tana cigaba da dube duben motar ko ciwon da taji kanta nayi bataji ba haukace musu tayi da kuka da ihun sun bata Jakarta ita bazata sauka ba.

Tuni mai motar ya watso da ita daga motarsa wayarta ma sun d'auke hannu ta dora aka ta fara kuka wiwi tana asirinta ya tonu...

Naceba♀

Kina bukatan jikinki yazama so fresh ba kwarzane ko daya ballantana kuraje ko tabo, sunburn,acne, ko knuckles? Kije kigwada products na mg's insha Allah zakiga ynd fatarki zedawo fiye da tsammaninki zakigyara jikinki naturally batare da kinbata fatarki ba jikinki yayi fresh kiyi smooth kizama kalar Madara kirar models kiringa walwali kina haskawa duk inda kikayi😍
Kidena kokonto cewa kingwada baki Dace ba insha Allah kijaraba products dinsu bi'iznillah zakiji dadinshi kayansu akwai kamshi especially sabulun kamshin yakama jikinki ko kindade da wanka jikinki zaidinga fidda ni'imtaccen kamshi bayinki ma zakiji kamshin dazai Kama😍sunada kit special domin amare Wanda indai kinyi using kit dinnan Baki bukatar kikara Kai kudinki gurin dilke domin ainihin yanda fatarki zehaska yagoge kidinga shining abun sewanda yagani😍

Mai bukatar kayan mg's chat:08062991549,07046881166,07067210195
Call:08064532391
Hausawa nacewa adade anayi sai gaskiya Kuma siyan nagari maida kudi gida
 tested nd trusted
Natural/organic

Ayiri yiri kuna Ina mata matafa nake nufi bamuna mataba 😀😀A&Z COLLECTION takawomuku ingantatun supplement
Muna da supplement na Infection
Munada da supplement na gyaran jiki Wanda zaisa jikinki yayi kyau fata tai laushi da sheki munada na gyaran breast succiko su tashi tsaf gwanin Sha awa munada na matsi dazai matsaki ciki dawaje bawai ki iya farkoba kuma yasaukarmiki da ni ima
Muna da na gyaran gashi Wanda zaifitomiki da gashi 😍😍
Dawanda zakiyi haske duka jikinki bawai fari na bleaching ba 😀😀

A&Z dealer ce kayanmu suna da sauki sosai price dinmu price din sari ne zaki samu kayanmu cikin sauki alhmdulillah
Ga kadan daga ciki

1 Royal jelly karami 2500
2 Juliet Eve 8500
3 Amirna 8k
4 Vitamin c 2500,2300
5 vt e 2k
6 collogen + glutathione 2k
7 whitening gummies 2200
8 surga wanita 2500
9 khusus 3500
10 majakani 2500

Price din sari nasan kodaga haka zaku gane A &Z gidan sauki ne
Masu siyan daidai kuma bambancin kadanne

Muna garin Kano Dan neman Karin bayani Kira ko whaspp 09037870422

Karku manta muna tura Kaya duk garin dakuke inkiyi siyayyama dayawa muyi Miki free delivery yan Kano kayanku har kofar gida cikin aminci

WANAN LITTAFIN NA KUDINE BIYA 500 TA WANAN ACCT 0272061655 WEMA BANK NAFISA NUHU KO KATIN MTN KO AIRTEL TA WANAN LAYIN 08033719070 DOMIN KI MALLAKI NAKI KI MUTANEN NIGER KUMA KU TUNTUBI WANAN LAYIN
+227 96 82 89 84 DUK WACCE TA MIN SHARING NA BAR TA DA *RABBI ZAI FIDDA MIN HAKKI NA DA IZININ ALLAH DOMIN BA YAFEWA NAYI BA*

NI DA KISHIYOYINA

NA SADNAF

PAGE 31

Luba

Ba Wanda ya bi ta kanta haka aka ringa wuceta tana kuka wiwi sarkokin asabe sun kai guda biyar da ta d'auka ko iya su kawai sun isheta rayuwa kudi kuwa zasu yi Dubu dari shidda sabida kudin ta kashe Asabe sai gashi tashi daya barayi sun rabata da komai daga ita sai hijabin jikinta da atamfar jikinta,duk kukan da take tana birgima ba Wanda ma ya tsaya ya tambayeta mai ke faruwa ballantana ta sa ran zata samu taimako a wajen wani, hasali ma wani ma tsawa ya daka mata a akan ta koma gefe ta zauna a bakin hanya da ace tasan haka legas yake da bata soma zuwa ba da tasani ma Abuja ta tafi,wanan wane irin rashin saa ne.

Haka ta koma gefe tana cigaba da kuka da kalle kalle bata San daga Ina zata fara ba wajen wa zata dosa ba wanda ta sani a Legas ballantana tace zataje ta nemi taimako Rabin mutanen ma da take gani duka yarabanci suke sai turanci,bata ga alamar bahaushe dan uwanta ba.

Tsawon awa shidda tana zaune ga kaikaiyin da ya dameta,ga mugun ciwon Kai,sai a yanzu take nadamar ma kashe Asaben da ta sani ta rufawa kanta asiri ta cigaba da mata wanke wanken tana jurewa,da ta sani ma iya kudin ta kwashe ta kulle Asabe a bandakin da kila duk bata tsinci kanta a cikin wanan balain ba.

Mik'ewa tayi tana cije lebbenta sabida kafafunta da taji suna mata ciwo zaman waje daya bazai kareta da komai ba gwara ta bazama neman taimako ko zata dace.

Fitowa tayi daga tashar tana cigaba da dube dube garin Legas din ma a hargitse ta ganshi kowa ta kansa yake tasan da ace wani garin taje da an samu mutanen da zasu tambayeta Mai ya sameta take kuka haka.

Tafiya kawai take batasan ma Inda zata dosa ba motoci da babura ma kamar sunfi mutane yawa haka take gani.

Wani waje ta hango da ake siyar da abinci ta nufi wajen tana Addu'a Allah yasa bahaushiya ce mai wajen,Koda ta isa da muryarta data dashe ta hau sallama.

Sai dai ba Wanda ma ya dago ya kalleta Yan Mata ke ta kaiwa suna kawowa da abinci suna sallamar mutane duk da ga shigarsu tasan ba hausawa bane ba Kuma musulmai bane dan guntun skirt suka saka.

Sai da ta Shiga ciki daya daga cikin Yan matan ta waigo tana tambayarta mai zaa bata da harshen turanci.

Luba bata iya turancin sosai ba amma duk abinda zaace tana ji "Taimako nake nema Dan Allah Ina Mai wajen take"?

Wani irin kallo yarinya ta mata da tasan ilham yarta ma zata girmeta

Da turanci tace mata idan ba abinci zata siya ba ta fita ta bata waje ta barta a tsaye.

Duk abinan wayanda suke wajen suna cin abinci ba Wanda ya dago wai ya kalleta ballantana su san taimako take nema Kuma ko magana zasuyi yarabanci sukeyi.

Tana ji tana gani Yan matan nan suka koreta gashi magriba ta kawo kai yanzu ta inda zata kwana kafin ta san nayi take dan legas ba wajen zamanta bane gwara ta nemo taimako ta koma wani garin dan bata Isa ta doshi bauchi ba.

Gajiya tayi da tafiya kukan ma ta gaji da yinsa bata ga alamar akwai Wanda zai taimaka mata ba hakane yasa ta Kara samun waje ta zauna ta buga tagumi.
Minti talatin a tsakani taji wani dan acaba da ya sauke fasinja a gefen titi yayi magana da hausa.

Wani irin mik'ewa tayi ta nufi wajensa da mugun gudu,dan k'ok'arin tayar da machine yake.

Zubewa tayi a gabansa tana "Ka taimaka min dan uwa ni bakuwa ce bansan kan garin nan ba Ina hanya zanzo Yan fashi suka taremu sai da suka kwace komai a hannuna hatta wayata sai da suka rabani dashi basu barni da komai ba ka taimaka min na samu wajen da zan kwana kafin na samu kudin da zan koma garin mu tunda safe nake bulayi a garin nan ina neman musulmi bahaushe da zai taimaka min dan uwa dan Allah ka taimaka min"

"Ke mai kika zo nema a garin Legas kinsan legas kuwa"?

"Tsautsayi dan uwa tsautsayi ya sakani zuwa duk dukiyata na tattaro na taho da zumar na zo na ringa kasuwanci sai gashi duk sun rabani da komai ba Wanda nasani a garin nan ma ballantana naje ya taimaka min nidai dan Allah ka taimaka min"

Shiru dan acaban yayi yana karewa Luba kallo Luba kuwa ta cigaba da magiya

"Ya isa haka ba taimaka miki ne bazan ba wlh bansan inda Zan kai ki bane dan nima maneji nakeyi da wani abokina a shago daya shirun da kika ga nayi inata nazarin Inda zan Kai ki ne kafin ki san nayi"

"Nidai ko Ina ne ni ko zaure ne zan kwana"

"Toh shikenan ki hau mu tafi akwai wata bayarabiya da nake kaiwa kasuwa muna mutunci da ita sosai bari na Kai ki wajen ta ko zata barki ki kwana"

Luba mik'ewa tayi da sauri ta haye machine din ya jasu suka tafi.

Tafiyar mintuna suka iso wani gida unguwar ma gabadayan ta sai a hankali ba wani gidan arziki a wajen Luba kalle kalle kawai ta ringa yi.

Koda ya sauka shi kadai ya fara Shiga gidan ba jimawa ya fito yace mata ta shigo.

Gidan da gani na hayane ba mutum daya ne a gidan ba dan sai da suka wuce dakuna wajen biyar kafin taga dan acaban ya Shige wani daki, tabi bayansa.

"Ga matar nan madam dan Allah a taimaka mata ta kwana zuwa gobe ko jibi ko abinci bata saka a cikinta ba"

Matar kallon Luba kawai take kana ganinta kasan ba bahaushiya bace ba dan ga tsagun fuskarta Nan irin na yarabawa.

Da broken tacewa dan Acaban ba komai yayi tafiyarsa kawai Luba godiya ta ringa musu har da dan acaban da ya mik'e ya tafi.

Tunda kuma dan acaban ya tafi daga Luba har matar ba wanda ya cewa kowa komai Luba sai da ta gaji da zaman tace "Madam dan Allah ki taimaka min da abinci wlh yunwa nake ji"

Matar mik'ewa tayi ta fita waje Jim kadan ta dawo da plate a hannunta ta ajiyewa Luba bakin Amala ne da miyar wake.

Luba jiki na rawa ta fara Loma abincin a bakinta a takaice a kasa ta kwana a palonmatar ta shige daki da yaranta.

ASHRAF

Ya Sha zargin Mahaifinsa da ba ta hanyar halal yake samun kudinsa ba amma bai tab'a kawo tunanin mahaifinsa na safarar mutane zuwa kasar waje ba, dama gidan marayun da ya bud'e badan Allah da annabi ya bud'e ba dama taimakon Yara da yake akan karatu badan Allah bane ba?bakin fentin da Salis kesan shafa musu kenan,ga fyade ga mumunan Sanaa baya Jin zai iya tsayawa Salis, ya mahaifiyar su zata ji idan ta Kara gano wanan mumunan halin da Salis ya jefa kansa a ciki.

A ranar Ashraf ko runtsawa baiyi ba sabida tunani baya jin zai iya Kare Salis a kotu dan abin ya girmama tunaninsa yafi karfinsa sai dai Salis ya nemo wani lawyer din ya tsaya masa.

Kwana biyu a tsakani yan sanda Suka Kara zuwa neman Salis da ko waje baya fitowa a yanzu ya sadakar da asirinsa ya riga da ya tonu, dama yasan Ashraf bazai iya tsaya masa ba,sabida abinda ya aikata ya munana"

A yanzu wani irin nadama yake Mara amfani, Addu'arsa kawai Kar maganar taje kunenn Aisha da Yaya mustapha duk da yasan abune mai wuya tunda shi din sanane ne.

Tunda ya bawa Ashraf labari bai Kara saka shi a idonsa ba yasan Ashraf.kunyar abinda ya aikata yake ji.

Kwana biyu a tsakani yan sanda suka Kara zuwa har cikin gida suka zo suka tafi dashi.

A ranar sai da suka kulle shi dan munana ayyukans a na Kara fitowa hajiya Fauza ta sha azaba ta fito ta ta fadawa yan sandan gaskiya hakane yasa Suka Kara Kama Salis suka kulleshi.

Sai dai duk yanda Suka so Salis ya amsa laifinsa da bakinsa kin amsawa yayi.ya dage sharri aka masa ba halinsa bane ba.

Ashraf ma duk yanda yaso ya Kara karbar belin mahaifinsa basu bashi ba.

Tsabar tashin hankalin da yake ciki shima har wani ramewa yayi.

Gwamnati tuni ta kwace lasisin asibitin Salis aka rufe gidan marayunsa.

Aka cigaba da gudanar da bincike ana shirye shiryen mik'a Salis kotu.

Ashraf kuwa shima shiri kawai yake dan bazai iya zuciya ya bar Salis a cikin halin nan ba duk da mahaifinsa bai cancanci haka ba amma haka zai daure ya tsaya masa dan yaga ya wanke shi a idon jamaa.

Ana saura kwana biyu zasu fara zaman kotu yaje gidansu Yaya mustapha dan su gaisa da Aisha dan kwana biyu kenan baije ya gaishe su ba tunda ya gano.sirrin mahaifinsa ya ke iya k'ok'arin sa wajen ganin ya wanke Salis dan ji yayi bazai iya juya masa baya ba.

Muna da supplement na Infection
Munada da supplement na gyaran jiki Wanda zaisa jikinki yayi kyau fata tai laushi da sheki □□□munada na gyaran breast succiko su tashi tsaf gwanin Sha awa□□ munada na matsi dazai matsaki ciki dawaje bawai ki iya farkoba kuma yasaukarmiki da ni ima
Muna da na gyaran gashi Wanda zaifitomiki da gashi 😍😍
Dawanda zakiyi haske duka jikinki bawai fari na bleaching ba 😀😀

A&Z dealer ce kayanmu suna da sauki sosai price dinmu price din sari ne zaki samu kayanmu cikin sauki alhmdulillah□□□□
Ga kadan daga ciki

1 Royal jelly karami 2500
2 Juliet Eve 8500

3 Amirna 8k
4 Vitamin c 2500,2300
5 vt e 2k
6 collogen + glutathione 2k
7 whitening gummies 2200
8 surga wanita 2500
9 khusus 3500
10 majakani 2500

Price din sari□□□□nasan kodaga haka zaku gane A &Z gidan sauki ne□□□□□□□□
Masu siyan daidai kuma bambancin kadanne

Muna garin Kano Dan neman Karin bayani Kira ko whaspp 09037870422

Karku manta muna tura Kaya duk garin dakuke inkiyi siyayyama dayawa muyi Miki free delivery □□□yan Kano kayanku har kofar gida cikin aminci□□□

WANAN LITTAFIN NA KUDINE BIYA 500 TA WANAN ACCT 0272061655 WEMA BANK NAFISA NUHU KO KATIN MTN KO AIRTEL TA WANAN LAYIN 08033719070 DOMIN KI MALLAKI NAKI KI MUTANEN NIGER KUMA KU TUNTUBI WANAN LAYIN
+227 96 82 89 84 DUK WACCE TA MIN SHARING NA BAR TA DA *RABBI ZAI FIDDA MIN HAKKI NA DA IZININ ALLAH DOMIN BA YAFEWA NAYI BA*

NI DA KISHIYOYINA

NA SADNAF

PAGE 34

"Kikace bake kika d'auke min kudi ba Habiba wanan menene"?

Habiba Kuka ta rushe dashi tana "Wlh bani na d'auke ma kudi ba bansan ya akayi kudin ya Shiga Jakata ba"

"Yanzu abinda zaki koma yi kenan Habiba kiringa sata kina d'auke d'auke kudin nan nada kafar da zai zo ya Shiga Jakarki ne? Wane irin mumunan hali Kika koyo haka ace nida gidana ban isa na ajiye abu ba sai kin d'auke?kin canja gabad'aya girkinki ba dadi komai naki ya lalace"?

"Sabitu wlh wlh ban taba d'aukar maka sule biyar ba zan iya dafa maka Qur'ani mai zanyi da kudinka inada sanaar da nake yi,tunda kake dani ka tab'a neman abinka ka rasa kwana biyu rigima kawai kake nema dani, burin ka kawai kaga kana kamani da laifi"

"Ni yanzu ki bani amsa wanan kudin ya akayi suka shigo Jakarki a gabanki dai yanzu kudin Suka Fado daga cikin Jakarki kinyi asara Habiba sata kiri kiri"

Habiba na k'ok'arin Magana ya daka mata wani irin tsawa daya sa Luba dake manne a jikin kofa ta ja da baya tana "ka saketa mana sai wani bata lokaci kake"

Tana k'ok'arin komawa jikin k'ofar waziri dan Sabitu ya shigo fuskarsa a mugun hade dan mahaifiyarsu ta rasu,daga baya sabitu ya auro Habiba ta Kuma rikesu tamkar ita ta haifesu,yana waje da abokinsa yake jin tashin muryarsu hakane yasa ya

shigo,ganin Luba yasa ya hade rai dan haka kawai yaji jininsa bai d'auketa ba tunda tazo gidan.

Luba kuwa da sauri ta wayance da "Tun dazu nake Jin tashin muryarsu inaso na Shiga d'akin ne ma ka shigo"

"Bani hanya na wuce"

Yace yana Kara hade rai da sauri ta matsa ya tura k'ofar da sallama

A daidai lokacin da sabitu yake nuna Habiba da yatsa Yana "Wlh bazan d'auki wanan halin da kika tsiromin dashi ba har ki iya d'auke kudin da kika san ba nawa bane rashin kudin na iya sawa a d'aureni, kikayi mirsisi kik'a fitomin dashi toh wlh ko duniya kika haifa min sai kin koma gidan idan kin nutsu sai ki dawo"

"Abba mai ke faruwane?

"Cikin fushi Sabitu ya hau zazzaga masa bayanin kudaddensa da Habiba ke ta d'aukewa ya kara da "Wlh ba Wanda yake d'auke min kudi sai ita duk yaran nan ba mai shigowa d'akin nan dagani sai ita amma ba kunya ba tsoron Allah haka zan shigo da kudi ta kwashe gabad'aya ga kwana biyu girkin da take yi bashida Dadi sam daga ta tsullawa Miya ruwa sai dai kaji gishiri yayi yawa na rasa Ina ta koyo wanan muguwar dabia inaga sai ta koma gida zata nutsu ta shiga hankalinta"

"Haba Abba Aunty Habiba ce zata d'aukar ma kudi"? Haba Abba wlh kowani ne yace ma zata iya d'aukar ma kudi kai mai karyatawa ne shekara nawa Kuna tare bata tab'a tunanin d'aukar ma kudi ba sai yanzu"?haba Abba"

"Toh waye ya d'auke min kudin Waziri yanzu nan Ina caje Jakarta kudin suka fado,kudin suna da kafar da zasuje su shiga Jakarta ne wanan fa zahiri na kamata ba wai labari aka bani ba"

"Abba wlh Aunty Habiba bazata tab'a d'aukar ma kudi ba Allah kadai yasan yanda kudin ya shiga Jakarta"

"Nidai ka zama shaida wlh daga yau na kara neman abu na rasa sai ta koma gidansu dan bazan iya zama da barauniya ba"

Daga haka sabitu ya fice daga d'akin Yana kunkuni ji yayi ma Habiba duk ta fice masa a rai.

Waziri kuwa hakuri ya hau bawa Habiba dake ta rusa uban kuka dan har ga Allah taji ciwon abinda sabitu ya mata a iya saninta kwandalarsa bata taba d'auka ba har yanzu tana ta mamakin yanda akayi kudin yaje cikin jakarta dagaske bata bari Yara su shiga d'akin.

Ita kadai ke Shiga d'akin ta gyara ta kulle sai idan ya dawo ma take bud'e k'ofar.
Dan Sabitu Sam bayaso ma ana shigar musu d'aki Koda kuwa Yara ne.

Dakyar waziri ya kara bata baki Yana "Amma abinan da daure kai yake Aunty Habiba ki kara saka ido ko akwai Wanda yake shigowa d'akin"

"Waziri Abban ku hanya kawai yake nema da zamu rabu wlh ba mai shiga d'akin dan kulle k'ofar nake da kaina idan zanje makaranta sai ya dawo ma nake bud'e k'ofar

zancen abinci Kuma Kun san yanda girkina yake haka kawai ya tsiromin da tsirfan Ina tsulla gishiri da ruwa idan rabuwa yake so yayi dani ai ba sai ya biyo ta haka ba gwara ya sauwake min sai na tafi da wanan cin mutunci da wulakancin da yake min"

"Kiyi Hakuri Aunty Habiba nidai Ina zargin Kamar ana shigowa d'akin ki dai kara saka ido"

Habiba bata ce komai ba ya Kara bata Hakuri har yazo fitowa ya dawo baya Yana "Naga mukullin d'akin Nan"

Habiba mik'ewa tayi ta jawo drawer ta d'auko mukullin ta mik'a masa ganin guda uku ne yasa ya cire daya ya maida mata ta karba batare da ta tambayeshi dalilin dayasa ya cire mukullin ba.

Yana bude k'ofa Luba ta ja da baya da sauri tana "Ai najiku shirune shine nace bari naji ko lafiya"

Wani mugun kallo ya watsa mata ya fice Yana Jin sam bai yarda da ita ba daga yanda take kame kame ma bayajin tana da gaskiya dan haka dole yasa ido ya gano mai shiga d'akin,duk abubuwa basu fara faruwa ba sai da tazo gidan.

Luba kuwa Palo ta koma ta zauna kamar ta fashe dan bakin ciki duk wanan uban wahalar da take sha dan ta hada Sabitu da Habiba,sabitu yak'i sakin Habiba sam ba haka taso ba,dan ta d'auka a yau sai ya sallami Habiba sai gashi bai saketa ba,ba kalar makircin da gwara kansu da batayi dan su ringa fada da juna ba,tunda har Habiba ta sokata a gaba da gori dole itama aurenta ya mutu ta danna zawarci taji.

Tana zaune taga Habiban ta fito bata ko kalli wajen da take ba ta fara k'ok'arin shiga kitchen tayi sauri ta mik'e tana "Ni Wai Aunty Habiba mai ya hadaki da mijinki ne haka tunda zu naji Yana waya Yana kin Masa sata ke barauniya ce ya gaji da Zama dake bakiga kalar zagin da naji Yana miki ba har sai da na kasa daurewa na masa magana akan bai dace ba ko me kika masa bai dace ya tona miki asiri ba"

Habiba duk yanda taso danne hawaye da kukan dake neman kwace mata kasawa tayi har sai da kukan ya kwace mata, Sam bataso ma Luba tasan halin da suke ciki ba,taya sabitu zai Kira a waya ya ringa ce mata barauniya abinda tasan bata aikata shi ba.

A ranar bata iya ma girki ba sai da yaran suka dawo Aliyah yarta ta dafa musu taliya zuciyarta fal take da bakin ciki abinda sabitu ya mata.

Koda ya dawo yanda ya hade rai haka ta hade ranta, bakin cikin abinda Luba ta fada mata ya aikata yasa yana shiga d'akin ta bi bayansa cikin kuka ta hau magana tana "Sabitu yanzu nice na zama abar wulakantawar ka yanzu har ka fita waje kana waya akan ni barauniya ce ka gaji da Zama dani ka ringa zagina yanzu Koda halina ne bazaka iya rufamin asiri ba kenan"?har a gaban kanwata ka ringa zagina sabitu kenan bazamu iya fadan mu mu biyu batare da kowa yasani ba"?

"A Ina nayi waya na zageki har na ce ke barauniya ce kanwarki Kuma ba dole tasan abinda Kika aikata ba tunda tana zaune a gidan idan har kinsan kina Jin kunyar wani yasan satar da kike min ai sai ki daina tunda kince ma nace miki barauniya na zageki nayi ki dau mataki ko ki zuciya ki daina satar"

Yaja tsaki ya juya mata baya tare da rufe kansa da bargo.

Habiba kuwa haka ta tsaya tana kallonsa tana danne kukan dake neman kwace mata tariga tasan Sabitu hanya kawai yake nema da zai rabu da ita,
karo na farko da suka raba shimfida dan bargo ta shimfida a kasa ta kwanta tana kukan bakin ciki Sabitu kuwa ya mik'e ya d'auko wandonsa ya tattara kudadensa yayi pilo dasu Yana kafin bacci ya kwasheni a d'auke min kudin.
Habiba a ranar sai bacci barawone ya saceta

Tayi mamkin yanda ya daura damarar fushi da ita dan har abincinta ya daina ci tun tana basarwa har tazo abin na damunta.

Yanda yake kafa kafa da kome ya shigo dashi yafi matukar Kona mata rai tana mugun takaicin irin zaman da suke yi duk yanda ta Kai da tayi zuciya sai ta kasa har sai da ta bashi hakuri,a takaice daga ranar suka kara shiryawa Habiba ta ringa kafa kafa da da duk abinda yazo dashi wai dan Kar ma ya nemi wani abu ya rasa.

ASHRAF

"Innalillahi wa Inna ilaihi rajiun wanan ai Asabe ce kawar Luba Ashraf wai ya kake so ka saka zuciyata ta buga ne"

Cewar Aisha tana kara kallon hoton Asabe da ta karba a hannun Ashraf da yasa muhasim mik'ewa

Ashraf komawa yayi ya tsugunna a gaban muhasim Yana "Aunty muhasim ki kwantar da hankalinki kinji ba abinda zasu iya miki wanan ce ta miki haka"?

Ya Kara karbe hoton daga hannun Aisha dake ta kwada sallati dan a yanzu a rude take mai Kuma ya hada luba da muhasim,mai ya hada Asabe da muhasim kanta ya kulle,ta d'auka hoton Salis muhasim zata gani ta firgice haka,sai gashi hoton Luba da Asabe ne ya firgita ta mai hakan ke nufi"

Jiki na rawa ta tsugunna a gaban muhasim da har lokacin idonta ke kulle jikinta na rawa

Ta ruko hannunta tana "Muhasim ki bud'e idonki na kasa ganewa Salis ne ya Miki fyade taya kuma Asabe ko Luba zasu karkata miki wuya bayan nasan kafin larurar nan ta Sameki a gidana kawai kike haduwa da Luba ki bud'e idonki kiyi min alama nagane dan na kasa gane mai hakan ke nufi"

"Muhasim a hankali ta bud'e idonta da suka kada sukayi ja hawaye na gudu a fuskarta Ashraf ya Kara d'auko hoton Luba Yana "Wanan ce ta miki haka"?

Tsurawa hoton ido tayi har lokacin jikinta na rawa Ashraf cikin dan mamaki ya d'auko hoton Asabe Yana "Ko wanan ce"?

"Nan ma bata lumshe idonta ba illa kallon hoton kawai da take"

Ashraf a hankali ya kalli Aisha yana "Kaina ya kulle hajiya umma duk tambayar da nake mata tana min alama da ido Amma hoton Luba da Asabe banga tana motsi ba"

Ashraf sake gwada Mata mugani dama nace maka Mahaifinku ne yayi mata haka sabida rufin asirinsa"

Hoton Luba Ashraf ya Kara daukowa ya mik'e tsaye Yana kallon muhasim da ta zura masa Ido ya haska mata hoton ya dora hannunsa a wuyansa Yana "Aunty muhasim wanan ce ta karkata miki wuya da baki"?

A hankali ta lumshe Idonta hawaye na gudu a fuskarta.

Aisha ta mik'e da sallati tana "yanzu Luba ce ta miki haka"?

Luba ce ta karkata miki baki sabida karki samu bakin magana mai kika mata?Mai kika tare mata Mai hadinki da ita da zata Miki haka?dama duk tsawon shekarun nan da aka d'auka ana binciken wayanda Suka aikata miki wanan zaluncin Luba ce ta karkata miki wuya ta aure min miji tana baje mulkinta wlh sai na kashe Luba da hannuna sai ta fadamin dalilin daya sa ta miki haka mai hadinki da ita a baya duk abinda tamin nayi hakuri amma wanan karon wlh sai naga bayanta"

Aisha ta karashe tana Mai na mata a rayuwa dana cancanci haka daga wajenta"?mai nayi mata iya sanina ban tab'a mata komai dana cancanci zalin cin nan daga wajenta ba"

"Hajiya umma ki kwantar da hankalin ki yanzu ai asirinta ya tonu duk Inda ta Shiga a garin nan Zan saka a kamota ni nasan duk Abubuwan nan dake faruwa wlh da sa hannunta karki yi mamaki duk sabida Abba ya aureta tayi haka tunda tasan Abba baya kaunarta kema a baya da bakin ki kin fada Mana irin tsanar da Abba ya Mata,ta rasa ta hanyar da zata bi ya saurareta shine ta hada Abubuwan da ta hada ni nasan laifinta yafi na Abba yawa amma bazan saurin yanke hukunci ba sai tazo hannu"

"Ashraf a yau ba gobe ba idan har Luba tana garin nan inaso a kamota wlh sai ta Kare rayuwarta a gidan yari"

"Ba ita kadai ba ai har da kawarta Asabe nasan bakinsu daya a yanzu ma sai na nemo Asaben zanyi wa wani abokina a Nemo duk Inda Luba ta Shiga a kamota"

Aisha a ranar bata iya runtsawa ba sabida tunani Wai Luba ce ta karkatawa muhasim wuya a hankali ta ringa komawa baya tana tuno abubuwa har lokacin tunanin ta ya kasa bata abinda Muhasim ta Mata da zata karkata mata baki,jikinta ba karamin sanyi yayi ba da zargin salis da ta ringayi a yanzu sai taji zuciyarta na rayya Mata Luba nada hannu ma a fyaden da Salis yayi wa muhasim.

Gidan Habiba

Sabitu tun Yana kafa kafa da kudinsa har ya dawo ya cigaba da ajiye kudinsa dan a yanzu yaga kamar Habiban ta nutsu kwana biyu girkinta lafiya Lau ba komai ba Kuma ta masa d'auke d'auke ya kaddara a ransa kila bukatu yasa tayi abinda tayi a baya.

Habiba kuwa sosai ta ringa saka ido dan taga ko akwai mai shigar mata d'aki duk itama tasan ba mai shiga tunda kullewa take.

A yanzu idan akwai wacce ta ji ta takurata ta hanata sakat bai wuce Luba da ta lura tana saka mata ido ba ta rasa yanda zata saka ta bar gidan,dan a gaban sabitu har wani biyaya take mata ko a gida da ta fadawa mahaifinsu Luba na gidanta fada ya rufeta dashi yana ta koreta kafin tazo tana dana sani,duk wulakanci da take mata duk

da har kasan zuciyarta baa san ranta take mata haka ba Luba bata gani haka ta cigaba da zama"

Luba kuwa duk wata hanya da tabi dan ta kara hada Kan sabitu da Habiba ta kasa samu,dan a yanzu damar da take dashi a baya bata dashi a yanzu wanan tsinannen dan sabitu Waziri nan ba karamin ido ya saka Mata ba a lokacin da take so ta aiwatar da kudurinta idan Habiban ta tafi islamiya a lokacin yake shigowa palon ya zauna.

Ko a yanzu juyi kawai take a shegen katifar da ta samu aka bata take kwana akai,a laben da tayi taji sabitu na maganar ta ajiye masa kudi jibi zai karba zaiyi tafiya mai gidansa ya aike shi.

Yanda zata samu ta Shiga d'akin kawai take tunani,har washegari sabitu ya bar gidan,Yara suka watse wajen Sha daya Habiba ta shirya ta tafi islamiya.

A Palo ta zauna da b'oyayyen mukulinta da take bud'e d'akin Tana ta Addu'a Allah yasa Kar wazirin ya shigo.

Ganin an tafi minti Ashirin bata ji motsin sa ba yasa ta leka tsakar gida da waje taga babu shi babu alamarsa.

Cikin tsananin farinciki ta rufe gate din gidan ta koma ciki ta nufi wajen d'akin Habiban ta bud'e da mukullin hanunta ta shige tana "insha Allahu ayau sai aurenki ya mutu ba dai ni kike wulakanta wa ba"?

Ta hau birkita d'akin tana neman wajen da ake ajiye kudin.

Waziri dake b'oye a bayan fulawowi a hankali ya shiga gidan cikin sand'a motsin Luba dayaji a d'akin Habiba yasa ya nufi k'ofar ya saka mukuli ya kulle ta waje ya bar mukullin a ciki.

Ya fito waje ya fara Kiran Habiba a waya Yana ta dawo gidan yanzu barawo ya shigo gidan.

Ya katse wayar ya kira sabitu shima a waya ya fada masa ya katse wayar tare da komawa palon Yana yau dubunki ta cika"

Kusan lokaci guda Habiba da sabitu suka iso gidan hankalinsu a tashe har suna hada baki wajen tambayar Ina barawon yake.

Waziri mik'ewa yayi ya nufi dakin Habiban ya murza key din tare da bud'ewa Suka shige gabad'aya Luba dake saman drawer dare dare ta saki ihu tana ta Shiga uku.....

Sister's duk wacce batayi anfani da sabulun mg's ba ko kit dinsu inamai shaidamuku anbarku acan baya domin duk wnd yajaraba mg's sai sanbarka duk wani Mai tantama Akan kayan gyaranjiki toh tabbas yacire sabulun mg's domin yahadu bakarya zegyarajiki yafidda dattin fata Dama duk wani matsalan fata duk Wanda kefama da matsalan fata walau pimples ko spot, sunburn acne, knuckles,wrinkles,stretch mark dama dukkan wani prblm yajaraba mg's bi'iznillah komai zaizama labari bayan jikinku yy fresh zaisa jikinku yy smooth yadinga glowing,gawanda basa San anfani da Mai zaku iya using sabulun mg's batare da kunbukaci wani Mai b Mai bukata should Chat

08062991549
07046881166
07067210195
Call 08064532391

Team glow♀

Ayiri yiri □□□□□kuna Ina mata matafa nake nufi bamuna mataba 😀😀A&Z COLLECTION takawomuku ingantatun supplement□□□□
Muna da supplement na Infection
Munada da supplement na gyaran jiki Wanda zaisa jikinki yayi kyau fata tai laushi da sheki □□□munada na gyaran breast succiko su tashi tsaf gwanin Sha awa□□ munada na matsi dazai matsaki ciki dawaje bawai ki iya farkoba kuma yasaukarmiki da ni ima
Muna da na gyaran gashi Wanda zaifitomiki da gashi 😍😍
Dawanda zakiyi haske duka jikinki bawai fari na bleaching ba 😀😀

A&Z dealer ce kayanmu suna da sauki sosai price dinmu price din sari ne zaki samu kayanmu cikin sauki alhmdulillah□□□□
Ga kadan daga ciki

1 Royal jelly karami 2500
2 Juliet Eve 8500
3 Amirna 8k
4 Vitamin c 2500,2300
5 vt e 2k
6 collogen + glutathione 2k
7 whitening gummies 2200
8 surga wanita 2500
9 khusus 3500
10 majakani 2500

Price din sari□□□□nasan kodaga haka zaku gane A &Z gidan sauki ne□□□□□□□□
Masu siyan daidai kuma bambancin kadanne

Muna garin Kano Dan neman Karin bayani Kira ko whaspp 09037870422

Karku manta muna tura Kaya duk garin dakuke inkiyi siyayyama dayawa muyi Miki free delivery □□□yan Kano kayanku har kofar gida cikin aminci□□□

WANAN LITTAFIN NA KUDINE BIYA 500 TA WANAN ACCT 0272061655 WEMA BANK NAFISA NUHU KO KATIN MTN KO AIRTEL TA WANAN LAYIN 08033719070 DOMIN KI MALLAKI NAKI KI MUTANEN NIGER KUMA KU TUNTUBI WANAN LAYIN
+227 96 82 89 84 DUK WACCE TA MIN SHARING NA BAR TA DA *RABBI ZAI FIDDA MIN HAKKI NA DA IZININ ALLAH DOMIN BA YAFEWA NAYI BA*

NI DA KISHIYOYINA

NA SADNAF

PAGE 35

Habiba da sabitu cikin tsananin mamaki suka zubawa Luba ido, da har lokacin ihun ta shiga uku take hannunta rik'e da jakar Habiba daya hannun Kuma kudin sabitu ne da ta d'auko a karkashin gado zata saka a jakar duk da sun Kamata ta kasa sakin jaka da kudin.

"Luba mai kike nema a dakina ya akayi kika Samu mukullin d'akina"? Mai jakata keyi a hannunki da kudi"?

Luba tsabar tashin hankali kasa motsi tayi

Waziri kuwa ya saki murmushi Yana "Aunty Habiba har sai kin tambayeta mai take nema a dakin ki Allah ne yayi yau asirinta ya tonu dan tunda tazo gidanan kuke samun sab'ani da Abba hakane yasa na fara zarginta, a ranar da Abba yace an kwashe mishi kudi na Kara gasgata zargin da nake mata dan dana shigo Kamata nayi tana muku labe, hakane yasa na Kara saka mata ido Allah cikin ikonsa na gano ita take zuba ruwa a Miya ko gishiri idan kika gama zubawa Abba girki a ranar bata san na ganta ba da biyu na karbi mukulin k'ofar dakin ki dan nasan kila itace take d'aukewa Abba kudi dan kawai ta hadaku fada a yau ma ta d'auka ba kowa a gidan shiyasa ta shigo dan ta Kara sacewa Abba kudi ni kuwa na kulleta a d'akin na kira ku dan kuga shaida"

Habiba rawan da jikinta yake yi yasa kafafunta kasa d'aukarta dan ta kasa yarda duk abinan dake faruwa luba ke haddasa mata,Luba kanwarta da ta kasance uwa daya uba daya tasan Luba zata iya aikata komai bata tab'a tunanin har ita da take jininta zata iya mata haka ba"

"Luba mai na miki kike san ki kashe min Aure"?Habiba tace tana fashewa da kuka

Sabitu kuwa jikinsa har wani rawa yake sabida mamaki da b'acin rai "dama kece kike kwashe min kudi kika ringa Sakani zargin Habiba"?

Dama kece kike ta hadani fada da Habiba?

Dama kece duk kike haddasa min fitina a gida"?

Luba sakin jakar hannunta tayi da kudin tunanin daya darsu a ranta yasa ta gwalo idanunta waje tana "Bama san hayaniya ku fita kubar d'akin nan Sarauniya tace Kar a dameta"

"Sarauniya taci ubanta sabitu yace tare da nufar wajen drawer"

Luba duk da ta tsorata ta cigaba da "Zaku gamu da fushin sarauniya idan kuka tab'a ta"

Sabitu kafafunta ya janyo ta fado tim a kasa kafin yayi wani motsi yaji muryar Habiba ta bayansa ta matsar dashi gefe ta jawo luba ta hau kirba tana " A yau ko Aljannun ne dake wlh sai naci ubanki waziri d'auko min Ashana a kitchen na Kona Yar iska"

Waziri dake kunshe dariyar dake cinsa na Aljannun karyar da tayi yayi waje.

Sabitu kuwa cewa yake"ba sai an d'auko Ashana ba bari na dauko dorina a cire mata Aljannun"

Luba ganin idan har bata yi magana ba zasu iya Mata dukan tsiya ko su kasheta yasa ta saki ihu tana "wlh karya nake banida komai kuyi hakuri ku yafemin sharrin shaidan ne"

"Kece ai shaidan din luba,har ace duk abinda ya Sameki duk halin da kike ciki baki daddara kinyi nadama ba Ina yayarki so kike kiga bayana,yanda aurenbki ya mutu so kike nima ki kashe min aure toh wlh daga kaina bazaki Kara kulla sharri ba

"Ai Habiba kinfi kowa laifi dama kinsan haka halinta yake shine baki fada min ba kika barni na barta zaune cikin gidana,anya shaidaniyar nan jininki ce"? Ai wlh sai tama fito min da duk kudina da ta sace ko na mik'ata wajen yan sanda"

"Aunty Habiba ki rufamin asiri!!

Marin da Habiba ta d'auketa dashi tare da rufeta da mugun duka ya katse Mata magiyar da take.

Sabitu kuwa cewa yake sai ta biyashi kudinsa.

Sai da Habiba tayi wa Luba jina jina ta jawo hannunta tayi hanyar waje da ita, tana tsine mata albarka.

Tana bud'e gate din gidan bakin motar Yan sanda ta faka a k'ofar gidan da wani karamin mota.

Abinda yaja hankalin Aunty Habiba da sabitu suka saki baki suna kallon Yan sanda maza uku da suka sauko daga motar da Yar sanda mace guda daya.

Luba wani sabon tashin hankalin ne ya Kara rufeta dan ta d'auka mijin Habiban ne ya kira mata yan sanda.

Wajen sabitun tayi da gudu tana "Na tuba dan Allah ka rufa min asiri karka kulleni"

"Wlh sai kin Kare rayuwarki a kurkuku"

Taji muryar Aisha ya daki dodon kunnenta

A hankali ta juya kirjinta na bugun tara tara dan idan ba kunneta ke san yaudarar ta ba muryar Aisha taji.

Koda ta juya hada ido tayi da Aisha da ta sha farin hijabi har kasa fuskar nan nata a mugun hade sai hucci take gefenta Kuma Ashraf ne a tsaye ya harde hannayensa a kirjinsa Yana kallonta.

Mace yar sandan ta nufo wajen da take tsaye tana "Madam you are under arrest"

Luba ja da baya tayi tana "Mai nayi da zaa Kamani"?

Fusgo hannunta mace Yar sandan tayi tana "idan munje station sai kiji"

"Ku tafi da ita duk abinda ake zargin ta da aikatawa zata aikata ta wuce duk Inda kuke tunani"

Habiba tace tana hararar Luba da ake sakawa ankwa a hannu hankalinta a mugun tashe sai cewa take mai tayi tana cewa Aisha "wane Sharrin kike bibiyana dashi duk da na rabu da mijinki"

Aisha ba karamin k'ok'ari tayi wajen danne abunda take ji a ranta ba,bata tab'a tunanin zata yi ido biyu da Luba bata shaketa ba,tunda Suka gano Luba na da sa hannu Ashraf ya hau nemanta,ba inda basu dubata ba itama kanta burinta taga Luba tazo hannu hakane yasa ta matsawa Ashraf akan kamo Luba har sai da a garin bincike suka gano Luba na gidan Habiba dan mahaifin ta ne ya fada musu da suka je gidan.

Yana Kiran Aisha tace bari ta fito tafiso a kama Luba a gabanta a cikin mota Ashraf ya ringa rokonta akan Kar tayi wani abu ta bari hukuma suyi aikin su.

Luba kuwa har suka isa station jikin ta rawa kawai yake da ace tasan Yan sanda zasu kamata da bata zo bauchi ba a cikin Abubuwan da ta aikata bata san wane asirin nata ya tonu ba, Rabin Abubuwan da ta aikata tasan ba wanda yasani sai Asabe,Asabe ce kawai zata iya tona mata asiri,ta kuma dade da aika Asabe lahira da wanan tunanin taji hankalin ta ya dan kwanta dan koma mai ake zargin ta aikata tasan basuda shaida idan ta kafe dole su rabu da ita.

Da isarsu station aka watsa ta bayan canter.

Awa daya a tsakani wani dan sanda ya daka mata tsawa akan ta fito.

Fuska a daure ta fito dan taga alamar sai ta hada da fuska da borin kunya

Koda aka karanto mata zargin da ake mata dan sanda ya hada da "Karki wahalar damu ki wahalar da kanki idan har kinsan kina da hannu a abinda ya samu yarinya nan kifito ki fada mana gaskiya ba sai kin wahalar da mu ba ta hakan zaki samu sausauci a hukuncin da zaa miki ya akayi kika karkatawa yarinya nan wuya da baki"?

"Officer wlh banida hannu a abinda ya samu yarinya nan nidai nasan tsohon mijina ne yayi mata fyade daya ga asirinsa zai tonu shine ya karkata mata baki"

"Ke ya akayi kika san shi ya karkata mata baki, kina wajen ya karkata mata baki"?

"Bana wajen amma nasan shi ya karkata mata baki"

"Karki wahalar damu ki fada mana gaskiya idan kinfi san Kuma a saka ki fadi gaskiya ta karfi da yaji sai mu saka ki"

Luba ko gezau batayi ba ta dage akan batasan komai a Kai ba su kamo Salis shine ya karkata wa muhasim wuya.

A takaice duk da uban azabar da suka ringa ganawa Luba,kafewa tayi akan bata da hannu akan case din Salis ne ya karkata wa muhasim wuya.

Ashraf kuwa yariga da yasan wacce luba a binciken da ya karayi ya Kara gano mugayen halayen Luba.

Burinsa yanzu ta amsa laifinta ta Kuma fada musu da me ta karkata wa muhasim baki.

Tuni ya nemi a mik'a case din kotu dan shi zai tsaya akan case din dan Aisha ta dage masa burinta kawai tasan mai ta yiwa muhasim wuyan ta ya karkace.

Kotu

Cike take dam da jama'a a cikin wayanda suka zo kotun har da Yaya mustapha Aisha da Aunty mamy,Salis ma baa barshi a baya ba sai dayazo.

Dan burinsa kawai gaskiya tayi halinta,shima a yanzu ba wacce yake mugun zargi sama da Luba.

Sai da aka gabatar da Sharia wajen biyu kafin a kira case din Luba da yan sanda biyu suka sakata a tsakiya

A cikin sati guda duk ta fice a hayyacinta kamar ba ita ba,tana kallon yanda Salis ke jifanta da mugun kallo Kamar ya jawota ya rabata da ranta.

Sai da ta shiga wajen da masu laifi ke tsayawa ta tsaya duk da jikinta rawa yake haka ta dake dan ko bindiga zasu saka mata bazata tab'a karbar laifinta ba a yanzu ma burinta a Kama Salisu suyi zaman yarin tare.

Koda aka karanto zargin da ake mata Ashraf ya nemi izini a wajen alkali sabida ya Mata tambayoyi dakewa tayi ta Kara fada musu Salis ne ya karkatawa muhasim baki sabida Kar ta tona masa asiri asan shi ya mata fyade

Ashraf ya saki murmushi yana "Mallama luba kikace tsohon mijinki shi ya karkata mata wuya sabida rufin asirinsa shin kina wajen ya karkata mata wuya ya akayi kika san shi ya karkata Mata wuya"?

"Yanda akayi nasan shi ya aikata mata wanan danyen aiki a lokacin kafin muyi aure Ina yawan zuwa office dinsa dan mu gaisa,toh a lokacin baya wani bani fuska lokaci lokaci idan na bushi iska nakan je dan mu gaisa a irin wanan lokacin watarana naje kafin na Shiga ma asibitin naga ita muhasim ta fito daga asibitin da gudu tana kuka inda take hankalina ya tashi dan nasan yarinya tunda Yar yayan kawata ce take nabi bayan yarinya dan naji mai ya sameta ta fito daga asibitin tana kuka.

Koda nabi bayanta sai da na rarrasheta da kyar na samu ta fadamin tsohon mijin nawa shi ya mata fyade ta Kuma gano tana d'auke da ciki,shine ya dage akan sai ta cire ko ya kasheta idan ba haka ba zai mata abinda bazata samu bakin magana ba a lokacin kwantar Mata da hankali nayi nace Kar ta damu ba abinda zai iya mata ni zan masa magana.

A washegarin ranar naje na same shi a office na nuna masa nasan abinda yayiwa Yar yayan matarsa dan haka idan baiyi wasa ba sai na tona masa asiri.

Hakuri ya bani akan Kar na tona masa asiri,jinsa kawai nayi a lokacin dan na yanke a raina Zanje na samu iyayen yarinya kawai.na fada musu.

Kwana biyu a tsakani yarinyar tazo ta sameni tana kuka akan Salis yace ko ta yarda ya zubar mata da ciki ko ya kasheta daga islamiya ma tazo ta sameni dak'yar na rarrasheta akan ta tafi gida a gobe sai na tona masa asiri.

Washegari ban kai ga naje gidansu yarinya ba naji labarin an tsinceta a bayan makarantarsu an karkata mata baki take nasan ba wanda zai iya aika aikar nan sai shi, a ranar naje na same shi a office dinsa na nuna masa nasan shi ya karkata mata wuya dan rufin asirinsa yanda yaga na dage zan sanarwa yan sanda yasa yayi tamin magiya akan na rufa masa asiri sharrin shaidan ne yanda akayi nasan shi ya karkata Mata wuya kenan"

Ashraf gyada kansa yayi Yana

"Hajiya Luba ya akayi duk yanda kike da kawar taki baki fada Mata abinda ke faruwa ba kike b'oye mata sanan kince yarinya zuwa take wajenki ta fada miki duk yanda tayi da shi tsohon mijin naki,ya akayi bata zabi ta sanarwa kowa ba sai ke"

"A lokacin banaso na raba kawar tawa da mijinta shiyasa ban fada mata ba"

"Toh mai yasa baki sanarwa Iyayenta ba"?

"Anan ne nasan nayi kuskure da ban fada musu ba"

"A lokacin da abin ya faru kunyi Aurene ko bakuyi aure ba"?

"A lokacin bamuyi aure ba sai da abin ya faru mukayi Aure"

"Ya akayi kika yarda kika auri wanda ya iya yiwa yarinya fyade har ya karkata mata baki bayan Kuma kinsan Yana da irin wanan mugun halin Kika yarda kika aureshi daga Kuma labarin da kike bamu tamkar dai shi tsohon mijin naki mijin kawarki ne"? ke kinsan shi ya aikata irin wanan danyen aikin bakiyi kararsa ba kike nemi ki rufa masa asiri sabida kema ki samu cikar burinki ya aureki ko"?

"Aaa a lokacin gani nayi idan na fito na fada zan Zama silar da zan rabashi da kawata shiyasa ban fada ba"

"Shin a gidanki muhasim ke zuwa ta Sameki ta fada miki halin da take ciki ko kuwa ke kike zuwa wajenta dan kisan halin da take ciki"?

Luba shiru tayi tana kallonsa Ashraf ya gyara tsayuwarsa Yana kallonta dan so yake ya biye mata kafin ya fito da shaidun da yake dasu akanta.....

Wlh nayi typing nayi mistake na goge sai da na sake wani sorry for the late update

Sister's duk wacce batayi anfani da sabulun mg's ba ko kit dinsu inamai shaidamuku anbarku acan baya domin duk wnd yajaraba mg's sai sanbarka duk wani Mai tantama Akan kayan gyaranjiki toh tabbas yacire sabulun mg's domin yahadu bakarya zegyarajiki yafidda dattin fata Dama duk wani matsalan fata duk Wanda kefama da matsalan fata walau pimples ko spot, sunburn acne, knuckles,wrinkles,stretch mark dama dukkan wani prblm yajaraba mg's bi'iznillah komai zaizama labari bayan jikinku yy fresh zaisa jikinku yy smooth yadinga glowing,gawanda basa San anfani da Mai zaku iya using sabulun mg's batare da kunbukaci wani Mai b Mai bukata should

Chat
08062991549
07046881166
07067210195
Call 08064532391

Team glow♀

WANAN LITTAFIN NA KUDINE BIYA 500 TA WANAN ACCT 0272061655 WEMA BANK NAFISA NUHU KO KATIN MTN KO AIRTEL TA WANAN LAYIN 08033719070 DOMIN KI MALLAKI NAKI KI MUTANEN NIGER KUMA KU TUNTUBI WANAN LAYIN
+227 96 82 89 84 DUK WACCE TA MIN SHARING NA BAR TA DA *RABBI ZAI FIDDA MIN HAKKI NA DA IZININ ALLAH DOMIN BA YAFEWA NAYI BA*

NI DA KISHIYOYINA

NA SADNAF

PAGE 36

"Ba gidana take zuwa ba muna dai had'uwa da ita a hanya ne"

Ashraf murmushi ya saki yana "yanzu kinyi magana biyu kenan kince yarinya tazo ta Sameki tana kuka akan shi tsohon mijin naki yace mata idan bata yarda ya zubar mata da ciki ba zai kasheta sai Kika rarrasheta akan ta koma gida zaki tona masa asiri" A ranar a hanya kuka had'u ta fada miki Kuma a wane hanya kuka had'u ta fada miki yace zai kasheta"?

Luba sai ta dirirce ta rasa ma karyar da zata masa

Ashraf ya juya ya kalli alkali Yana ya mai girma mai Sharia

inaso a bani dama Zan kira tsohon mijin ta na masa tambayoyi"

"Kotu ta baka dama"

Salis bai tab'a tunanin Ashraf zai neme ya fito ba,taya Ashraf zai masa haka kiransa da zaiyi na nufin tonan asirinsa a bainar jama'a ko kad'an bayaso ana maganar yayi wa muhasim fyade.

Ashraf sai da ya kara masa ido akan ya fito ya tashi jiki a sanyaye sai yaji Yana nadamar ma zuwa kotun ba haka yayi da Ashraf ba taya a bainar jama'a zaice yayi wa muhasim Fyade.

Koda ya fito wajen dake kallon Inda Luba ke tsaye ya tsaya suna fuskantar juna.

Sai da Alhaji Salis yayi rantsuwa akan zai Fadi gaskiya magatakarda ya koma ya zauna Ashraf ya tsaya a gabansa ya dago suka hada ido da Aisha da tayi saurin kau da kanta.

Karo na biyu da ya Kara tsintar kansa cikin tsananin kunyar abinda ya aikata sai yaji a ransa gwara ya Fadi iya gaskiyar abinda ya sani.

ASHRAF kuwa dakewa yayi Kamar ba mahaifinsa ba dan a binciken da yayi zai Kara wanke Salis ne a fyaden da yayi wa muhasim a wajen Aisha da Yaya mustapha.

"Alhaji ko zaka iya fada mana wane danganta ne tsakanin ka da wacce ake Kara"?

"Tsohuwar matata ce kawar kuma matata uwar yayana"

"Naji kace kawar matar ka ce Kuma ka aureta,shin Auren soyayya kuka yi ko kuma dai Auren ta kayi sabida ta rufa maka Asiri game da zargin da ake ma akan kayi wa yarinya fyade?zaka iya gayawa kotu yanda aka yi Kuka yi Aure"? Ya Kuma akayi kayi wa muhasim fyade"?

"Ita dai Luba kawar matata ce zan iya cewa Aminiyarta ce a lokacin da muka yi aure ita batayi ba sai daga baya,ni Kuma a lokacin bata jima da auren ba na samu scholarship na fita waje Kara karatu.
Ta silar matata na santa matata na mugun santa da har nake ganin bata kaunar b'acin ranta akan nawa,daga baya ma na lura ita kawartata ba matuniyar arziki bace ba sabida halayensu ma bai zo daya ba,tana da san kai da san abin duniya,a lokacin da ta kashe aurenta sabida mijinta bashida hali naso rabata da matata dan duk Wanda zai rabu da kai sabida babu ba mutumin arziki bane ba.

Koda na nemi matata ta rabu da ita k'i tayi a san na faranta mata na rabu da ita badan Raina naso ba dan gani nake yau da gobe zata iya sawa matata ta canja hali itama.

Tiryan tiryan Salis ya bada labarin yanda Luba ta hau bibiyarsa yana wulakanta ta sabida bazai iya auren cin amana ba har zuwa yanda Suka tare a sabon gida ta saka masa magani a ruwa ya Kara da "ta karfi da yaji takeso na aureta ko ta halin Kaka ko a yanzu inada gajeran recording din abinda ya faru a d'akina dan nasa k'aramin recorder a saman d'akina,idan kotu na bukata zan iya kawowa sabida aga shaidan yanda tazo d'akin nawa,tunda ga lokacin na Kara tsanarta na matsawa matata akan ta rabu da ita amma tak'i rabuwa da ita" dan har ta gwammaci b'acin raina da na kawarta haka ta cigaba da zuwa office dina tana nacin sai na aureta a irin wanan yanayin na wayi gari cikin tsananin bukata da har fita nake a hayyacina idan ban samu nutsuwa ba,a haka watarana Ina tsaka da aiki abin ya motsa min nazo gida Koda nazo sai ban samu matata ba Allah shine shaidata bansan mai ya faru ba sai da na dawo hayyacina naga Ashe muhasim na nema da tana da bakin da zatayi magana da kotu tayi mata tambaya, tundaga lokacin na rasa kwanciya hankalina na rasa mai yake min Dadi,yarinya tabar gidana dan dama a gidana take zaune.

Wata biyu a tsakani tazo ta sameni akan bata ga Al-adarta ba naso ta zubar da cikin dan abin kunya ne ace ni da kaina nayiwa Yar yayan matata ciki,sai tak'i bani hadin kai a zubar da cikin a lokacin Kuma Luba ta matsamin da zuwa office dina

A takaice tiryan tiryan Salis ya bada labarin komai bai boye komai ba har yanda Luba tazo ta same shi akan tasan shi yayiwa muhasim ciki ya Kuma yi mata fyade Inda

tace Masa idan bai aureta ba sai ta tona masa asiri ya Kara da "Ni nasan ba wani shakuwa suka yi da yarinyar ba sai idan tazo gidana ma take ganin yarinya bansan ya akayi tasan mai ya shiga tsakanina da yarinya ba,naso na zargi ko tana da sa hannu a halin da na tsinci kaina na yawan bukata tunda ta tab'a saka min magani sai Kuma na cire zargin haka a raina amma Allah shine shaidata baa cikin hayyacina nayiwa muhasim fyade ba zan iya dafa al Qur'ani na rantse"

"A lokacin da ta ringa bibiyar ka tana sanka har ta saka maka magani a ruwa a ranar da kuka tare a sabon gida shin ka fadawa matarka abinda ya Shiga tsakanin ku? sanan Ina matar taka take a ranar da batasan duk abinda ya faru ba"?

"Ban fada mata ba dan gani nake bazata tab'a yarda Luba zata ci amanarta ba dan ta bata yarda dari bisa dari sanan a ranar da ta fara saka min magani a ruwa ta bawa muhasim ta kawo min a ranar muka tare a sabon gida da yan uwan matata da yawa a gidan hakane yasa tace min zata kwana cikin Yan uwanta a ranar ba a dakina ta kwana ba"

Ashraf gyada kansa yayi yace zai iya komawa ya zauna ya juya ya kalli alkali Yana "Ya mai girma mai Sharia inaso kotu ta nazarci maganar wacce ake Kara da shi Alhaji Salis daga abinda ya faru zaa gane dole wacce ake Kara tana da hannu a cikin abinda ya samu yarinyar dan yarinya bata da wani kusanci da ita,da zata ringa zuwa wajenta tana fada Mata halin da take ciki,na biyu idan har dagaske yarinya ce ta fada mata shi Alhaii ya mata fyade idan ba dama tana da wani manufa a zuciyarta ba ya Kamata ace ta sanar da kawarta halin da yarinyar take ciki sai bata sanar da ita ba,daga maganin da ta saka wa Alhaji a ruwa sabida ya sadu da ita kotu zata gane zata iya yin komai domin ta samu cikar burinta dan haka inaso kotu ta sake bani dama zan kira Hajiya Aisha na mata wasu tambayoyi"

"Kotu ta baka dama"

Aisha tunda taji labarin duk abinda ya faru daga bakin Salis tayi mutuwar zaune ta ringa komawa baya tana tuna duk yanda Luba ta ringa sintirin zuwa gidanta da irin kallon da take bin Salis dashi a hankali komai ya fara dawo Mata na yanda Salis ke iya k'ok'arin sa wajen ganin ya rabasu.

Jiki a sanyaye ta mik'e ta nufi wajen da ake tsayawa ta tsaya tana kallon Luba da ta jike da gumi tana mata wani irin kallo,ko kad'an bataji ta wani tsorota ba tasan Ashraf bashida shaidan komai, idan har ta kafe akan karya yake ba yanda za'ayi kotu ta Yanke mata hukunci har sai an samu shaida.

Bayan Aisha tayi rantsuwar zata Fadi gaskiya ASHRAF ya tsaya a gabanta Yana "Hajiya Aisha ko Zaki iya fada mana mai alakarki da wacce ake Kara"?

tiryan tiryan Aisha ta kwashe komai ta fadawa kotu daga alakarta da Luba har zuwa lokacin da ta wayi gari ta aure mata miji ta Kara da "A duk abinan dake faruwa bata tab'a nuna min tasan Wanda yayi wa muhasim fyade ba,bata tab'a nuna min ma tasan muhasim nada ciki ba, shiyasa a yanzu da naji tana cewa tasan har muhasim nada ciki har muhasim taje wajenta kaina ya kara daurewa, dan a gidana take ganinta su gaisheta tunda aurenta ya mutu bata tab'a zuwa gidan yayana ba a gidana dai muke had'uwa har a wane lokaci ta samu kusanci da yarinyar da zata ringa zuwa wajenta tana fada mata halin da take ciki ya mai girma mai Sharia Ina rokon kotu ta taimaka wajen bincikar ta dan Muhasim nasan bazata tab'a tararta ta

fada Mata halin da take ciki ba sai dai idan ba dama tasan abu ya Shiga tsakanin muhasim da mijina ba har ta Kuma gano tana d'auke da juna biyu ba"

Aisha ta karashe tana share hawaye dan a yanzu ta yarda Luba tana da hannu a abinda yasamu muhasim.

"Ya isa hajiya Aisha kotu zata miki adalci insha Allahu tambayar da zan miki a yanzu shine shin kafin ku gano anyiwa muhasim fyade dagaske ne akwai lokacin da mijinki ya tsinci kansa da yawan bukata da sai ya samu nutsuwa yake dawowa daidai"

"Eee hakane Rana daya na wayi gari naga yana yawan bukata har yakan dawo gida sau biyu haka ko sau uku"

"Dama can haka yake ko Rana tsaka ya wayi gari a haka"?

"A gaskiya ba haka yake ba dan daga ni har shi lokacin muna ta mamakin yanda akayi ya tsinci kansa da yawan bukata"?

"Kuma baki zargi ko wani abu yaci ko ya sha dayasa shi wanan bukata ba"?

"Aisha shiru tayi ta tafi tunani mintuna a tsakani tace "Wlh bazan iya tunawa ba nadai san a ranar yaci tuwo daya dawo gida daga ya Shiga sama yayi wanka ya birkice min"

"A ranar kinyi bakine kafin ya dawo"?

"Aa Luba ce dai tazo gidan a ranar Tama dage min sai ta tayani girki,baa san raina ba nabarta tayi girkin dan Salis baya yarda yaci girkin da ba nawa ba"

"Kina nufin a ranar da kika fara ganin canji a wajen mijin naki Luba ce tayi girkin da yaci batare shi yasani ba".?

"Eee a ranar ita tayi min girkin"

Ashraf ya gyada kansa cikin gamsuwa

Aisha ta hada tambayoyin da ya mata ta Kara tuna a ranar da Luba ta dage zatayi girki a ranar Salis ya canja ta gwalo ido tana kallon Luba tare da nunata da hannu tana "wlh ita tayi girkin da yaci a ranar har ya canja sai a yanzu na tuna innalillahi wa Inna ilaihi rajiun"

"Zaki iya komawa ki zauna"

Ashraf yace Yana "ya mai girma mai Sharia iya hujojin nan ya isa yasa kotu ta gane hajiya Luba tana da hannu dumu dumu a cikin abinda ya samu muhasim dan sai da taje gidan tayi girkin da shi Alhaji Salis yaci ya zama mabukaci sosai,Wanda kila tayi hakane sabida ta Kara samun damar da zai kusanceta sai Allah baiyi ba har abin yazo da tsautsayi yayiwa Muhasim fyade na biyu duk yanda take da Hajiya Aisha da sintirin da take yi a gidan ko a fuska bata tab'a nuna mata tasan anyiwa muhasim fyade har ta samu ciki ba,Kuma bata da kusanci da muhasim da har zata saki jikinta da ita ta fada mata halin da ake ciki idan ba dama duk ita ta shirya abinda ya faru ba har tasan komai sabida ta samu ya aureta,dan haka Ina rokon kotu da ta taimaka tabi wa muhasim hakkinta Luba ita tayi silar da aka yiwa muhasim fyade ta Kuma karkata

mata wuya sabida Kar ta samu bakin da zata Fadi gaskiyar abinda ya faru muna rokon kotu da ta taimaka wajen tilasta mata ta fada mana abinda tayi wa muhasim ta karkata Mata wuya"

Alkali sai da ya gama rubuce rubuce ya tambayi Luba ko tana da lauyan da zai kareta ta girgiza kai akan Bata da lauya.

Alkalin ya Kara rubuce rubuce ya dago yayi bayani akan zaa daga karar zuwa sati uku masu zuwa sabida itama wacce ake kara ta samo lauyanta

Ashraf kuwa dama haka yafiso dan a zaman da za'ayi na biyu zai samo shaidar da dole asirin Luba ya tonu.

Aisha kuwa kuka ta ringa yi wiwi tana nadamar rabuwar da batayi da Luba ba a lokacin da Salis ya dage mata akan ya rabu da ita,sai a yanzu ta tuna daga lokacin da Salis yaci abincin Luba ya canja ashe duk abinan da ya faru Luba ce ta haddasa komai ashe duk abinan daya faru tafi kowa laifi tunda da ace ta rabu da Luba da bata samu damar da zatayi wa Salis abinda tayi har ya nemi muhasim ba,ta riga kowa barin kotun dan kunyar ma hada ido take da salis dan sai take ganin kamar itace ma ta jefa shi a cikin wanan matsalar.

Salis kuwa bai iya jan motar bama sai ASHRAF ne yaja motar dan bai tab'a sanin Ashe Luba ce tayi girkin dayaci har ya zama mabukaci ba,sai a yanzu ya Kara gane Luba ce ta jefa shi a wanan halin har ya nemi muhasim.

Har suka isa gida bai iya ce komai ba sai da yazo sauka ya juya ya kalli ASHRAF yana "Mahaifiyar ku itace silar da ta jefani a cikin wanan masifar wlh Aisha bata min adalci ba,daace ta rabu da Luba da kila duk ban tsinci kaina a cikin wanan halin ba"

"Abba godiya zaka yiwa Allah da gaskiya ta fara halinta nasan a yanzu hajiya umma dasu Yaya mustapha zasu gane cewar ba da gangan kayiwa muhasim fyade ba"

Salis bai ce komai ba ya fito daga motar yayi cikin gidan dan ji yayi kansa na masa ciwo.

Aisha kuwa Koda suka isa gida Yaya mustapha fada ya rufeta dashi yana duk abinan ma daya Faru ita ta jawo tafi kowa laifi dan da ace tayiwa mijinta biyayya ta rabu da luba da duk haka bata faru ba.

Lauyan gwamnati aka samowa luba da Luba ta tsara masa karya gabad'aya ta maida laifin Kan Salis ta dage akan shi ya karkata wa muhasim baki ita batasan komai akai ba ASHRAF so kawai yake ya wanke mahaifinsa sabida shi lauya ne Luba ta ringa kuka akan ya taimaka mata barrister kabeer ya Mata alkawari akan zai taimaka mata.

Ashraf shima sosai ya dage wajen Kara samo shaidu kafin ranar da zaa koma kotu.

A ranar kuwa da zaa cigaba da Sharia kotun tafi koyaushe cika Alhaji Salis na daga gaba Aisha ma gaba ta zauna wanan karon har da muhasim Suka zo da aka turo a keke"

Sai da akayi shariar mutane biyu kafin a kira shariarsu.

Luba ta fito ta tsaya a wajen da ake tsayawa zuciyarta tana Jin kwarin gwiwa zatayi nassara har wani murmushi ta ringa sakarwa Aisha da Salis da ba abinda take hangowa a idonsa sai wuta,tasan da zaa bashi dama zai iya harbeta har lahira.

Duk tambayoyin da Ashraf ya mata haka barrister kabeer ya ringa katse shi ya na kawo nasa hujojjin da "Ya mai girma mai Sharia lauyan Mai kara Yana so yayi iya k'ok'arinsa ne dan yaga ya wanke mahaifinsa ne amma babu tantama shi yayiwa yarinya fyade ya karkata mata baki sabida Kar ta samu bakin da zata tona masa asiri, wacce ake kara tasan sirrinsa ne sabida yawan sintirin da takeyi a office dinsa dan haka Ina rokon kotu da ta yiwa wacce ake kara adalci ta tilasta wa Alhaji Salis ya fadawa kotu gaskiyar abinda yayiwa muhasim ya karkata mata baki ngd ya mai girma mai Sharia

Ya koma ya zauna
Ashraf ya mik'e tsaye fuskarsa d'auke da murmushi Yana "Ya mai girma mai Sharia inaso kotu ta bani dama na gabatar da shaidar da kotu zata gamsu da cewa Wacce ake kara ita take da hannu a cikin abinda ya samu muhasim"

"Kotu ta baka dama"

Luba murmushi ta saki dan tasan ba wani shaidan da ASHRAF yake dashi.

Bakin k'ofa taringa kallo Dan taga shaidar da Ashraf yace Yana dashi.

Shigowar Asabe da mijinta Yusuf da ya ruko hannunta yasa Luba taja da baya kirjinta yayi wani irin bugawa Kamar ya fado taja da baya ta nuna Asabe da hannu tana "A!! S!!A!!B!!E ba kin mutu ba"?.....

Sister's duk wacce batayi anfani da sabulun mg's ba ko kit dinsu inamai shaidamuku anbarku acan baya domin duk wnd yajaraba mg's sai sanbarka duk wani Mai tantama Akan kayan gyaranjiki toh tabbas yacire sabulun mg's domin yahadu bakarya zegyarajiki yafidda dattin fata Dama duk wani matsalan fata duk Wanda kefama da matsalan fata walau pimples ko spot, sunburn acne, knuckles,wrinkles,stretch mark dama dukkan wani prblm yajaraba mg's bi'iznillah komai zaizama labari bayan jikinku yy fresh zaisa jikinku yy smooth yadinga glowing,gawanda basa San anfani da Mai zaku iya using sabulun mg's batare da kunbukaci wani Mai b Mai bukata should Chat
08062991549
07046881166
07067210195
Call 08064532391

Team glow♀

WANAN LITTAFIN NA KUDINE BIYA 500 TA WANAN ACCT 0272061655 WEMA BANK NAFISA NUHU KO KATIN MTN KO AIRTEL TA WANAN LAYIN 08033719070 DOMIN KI MALLAKI NAKI KI MUTANEN NIGER KUMA KU TUNTUBI WANAN LAYIN
+227 96 82 89 84 DUK WACCE TA MIN SHARING NA BAR TA DA *RABBI ZAI FIDDA MIN HAKKI NA DA IZININ ALLAH DOMIN BA YAFEWA NAYI BA*

NI DA KISHIYOYINA

NA SADNAF

PAGE 37

"Ban mutu ba Luba Bakiso ganina ba ko?kin d'auka kin kin kasheni?toh ban mutu ba gani yau a kotu duk zan tona sirrinki da ba Wanda yasani sai ni a tunaninki tunda kin kasheni asirinki ya rufu ko? Toh gani da raina yau zan tona miki asiri asan ke wacece"

Ashraf murmushi ya saki ya nuna mata wajen da zata tsaya yusuf ya saki hannunta ta shige wajen ta tsaya tana kallon Luba da ke wani irin karkarwa har lokacin nuna Asabe take da hannu

Ashraf kuwa ya juya wajen alkali Yana "ya mai girma mai Sharia inaso kotu ta bani dama na yiwa Asabe tambayoyin kafin na mata tambayoyin inaso kotu tasan cewa ita wanan baiwar Allah da zata bada shaida akan Luba ita keda hannu a duk abinda ya samu muhasim kawarta ce Aminiyarta da tasan komai akan ta ko nace tare suke yin komai,daga lokacin da Suka fara samun sab'ani Asabe ta nuna zata tona Mata asiri shine ta caka mata wuka ta gudu, a tunaninta ta kasheta shiyasa da ta shigo ta mata tambayar dama bata mutu ba,?ko a yanzu zamu iya ganin yanayin jikin Asaben dak'yar ta samu tazo kotun dan har yanzu bata warke ba mijinta yazo mana da camera dake d'auke da yanda ta cakawa Asabe wukar ta tattara komai ta gudu iya wanan kawai ya isa kotu ta gane Luba ta wuce duk yanda ake tunani idan har zata iya kashe kawarta Aminiyarta toh ba abinda bazata iya yi ba amma inaso mu ji komai daga bakin Asaben dan ita zata warware mana komai"

"Kotu ta baka dama kayi Mata tambayoyin"

Alkali yace Yana gyara zaman gilashin fuskarsa dan a yanzu case din ya dau hankalinsa tamkar yanda Kowa na kotun ya zaku Asabe ta fara bada labari ciki kuwa har da Salis da Aisha da suke ji kamar suje kusa da wajen da Asabe ke tsaye

"Nagode ya mai girma mai sharia"

Sai da Asabe tayi rantsuwar zata Fadi gaskiya kafin
Ashraf ya nufi wajen da Asabe ke tsaye

Yace "Mallama Asabe ko zaki iya bamu takaitacen labarin yanda kuka fara kawance da Luba ya akayi kika san sirrikanta da ba kowa ya sani ba"

"Luba dai kawata ce na hadu da ita a wani biki a lokacin auren ta ya mutu Nima a lokacin nawa auren ya mutu ganin dukan mu zawara ne yasa tamu tazo daya da ita, dan yanda nake son ado da kwalliya haka take so itama haka ma yanda nake so na samu miji mai kudi na aura dan na huta itama haka ra'ayinta.

A wajenta nake yawan Jin labarin kawarta Aisha yanda take auren miji mai kudi,har take bani labarin Rabin kayan da take sakawa masu tsada na Aisha ne, ai Aishan sam bata dace da auren miji mai kudi ba dan bata da wayo ko kad'an har take fadamin yanda take rabata da abubuwa ta karfi da yaji Kuma ko nawa takeso idan har kudi ne

zata d'auko ta bata,a haka tana ta kwadayin Auren mai kudi duk Kuma masu zuwa neman aurenta sai tace bataso tafison ta samu mai kudi irin mijin Aisha kawarta har take bani labarin haduwar gidan da yake ginawa da tsaruwarsa, nima nasan gidan a lokacin bansan na mijin Aisha bane ba, ita dai burinta a lokacin bataso Aisha tafita da komai, tafiso taga ma tafi Aisha ganin bata samu irin dai mijin Aishan ba rana tsaka tazo ta sameni akan ita a yanzu mijin ma Aishan takeso dan batajin zata samu miji mai kudi irinsa

nayi matukar mamakin yanda take da Aisha ace zata iya cin Amanar ta amma ban nuna mata komai ba nace mata ba haramun bane zata iya aurensa,anan take fadamin irin wulakancin da yake mata har yanda ta samu magani ta saka Masa a ruwa dan ta samu yayi amfani da ita ko Allah zai saka ta samu ciki ma ya aureta sai dai a madadin ma ta samu cikar burinta dataje office dinsa duka ta sha a hannunsa ita bata san ya zata yi ta shawo kansa ba tace ko da yanda zan iya taimaka mata ta samu ya aureta"

Shiru Asabe tayi ta saci kallon wajen da yusuf ke zaune dan fadar ta taimakawa Luba zuwa wajen mallami tamkar ta dab'awa kanta wukane

Kallon da Ashraf ya mata da "muna jinki"

Yasa ta tuno maganarsa da "Fadar gaskiyar ki shi ne naki rufin asirin domin nasan duk munanan Abubuwan da kika aikata kadan daga ciki shine yanda kika sawa kishiyarki guba a Shayi ta sha ta mutu,kinsan kema idan aka gano kin tab'a kisan kai wlh sai an daureki amma idan har duk abinda kuka yi da Luba duk kika fito kika fada a kotu ba mai Jin wanan sirrin naki"!!!!

Asabe d'auke idonta tayi daga kallon barin da yusuf ke zaune tayi ya zuba mata ido kawai Yana kallonta ta kalli Luba da rigarta ta jike da gumi sai girgiza kai take jikinta na rawa

"A lokacin Ina dan fama da jinnu masu kora min samari hakane yasa na dan san mallamai masu taimaka min da Addu'a a lokacin da ta nemi ko Zan taimaka mata shine na bata shawaran ko zata zo na rakata wajen mallamina yayi mata aiki akan Mijin Aisha.

A lokacin sai ta nuna min bata yarda da mallamai ba kudin mutane kawai suke ci,sai na ce mata mu dai gwada zuwa"

A lokacin da muka je Luba duk ta zayyane masa abinda ke tafe damu ce mana yayi mijin Aisha ya mugun tsanarta abu daya zai mata shine zai bamu garin magani a samu a zuba masa a abinci yaci,idan har yaci zai na kasance cikin tsananin bukata,ita kuma a wanan lokacin ta ringa zuwa office dinsa idan har ta samu ya kwanta da ita,ba abinda zai hana ya aureta dan ji zaiyi duk duniya ba wacce yake so sama da ita, ya Kuma ji ba wacce ya tsana sama da Aisha dan bama zai ringa Jin dadin kowace mace ba"

Shiru Asabe ta sakeyi tana sauke numfashi kallon da yusuf ke mata ya Kara daga Mata hankali dan tana tsoron Aurenta ya mutu,amma har gwara aurenta ya mutu da asan itace ta kashe matarsa uwar yayansa.

"Muna jinki"

Ashraf yace tare da gyara tsayuwarsa ya kallo wajen da Aisha ke zaune da ta rufe fuskarta da tafin hannunta da alama kuka takeyi, Salis kuwa idonsa jajjur yayi sabida b'acin rai kallon Asabe kawai yake.

"A ranar da muka karbo maganin bata samu zuwa gidan Aisha ba dan tace min zuba masa magani a abinci abu ne mai balain sauki dan Aisha shashasha ce kwana biyu a tsakani tazo ta sameni akan ta zuba maganin dan itace ma tayi girkin dan haka zata shirya sosai ta tafi office dinsa har take fadamin ai kayan da zata saka ma da kudin Aisha ta siya. Fatan nassara na Mata muka rabu akan zata zo ta bani labari idan komai ya wakana.

Sai dai a ranar daddare tazo tana kuka akan ya koreta ya ma yiwa security gargadi akan karsu sake su kara barinta ta shigo Masa office,taci kukanta ta gode Allah da ta gama na shawarceta akan mai zai hana ta hakura da mijin Aisha ta duba kawai a cikin manemanta ta aura tunda suma suna da kudin,sai ta daka tsalle akan duk uban wahalar nan da take sha akansa tashi daya kawai sai ta hakura ai ita haka zata cigaba da bibiyarsa har sai ya amince zai aureta.

A Kuma ranar take bani labarin ma akwai wani likita Dr Saeed dayace Yana santa a asibitin shima yake aiki da zata iya aurensa idan Yana da kudi sai dai bai kai mijin Aisha kudi ba,kafin ta tafi haka ta zage ta zagi mallamin da mukaje wajensa akan cutar ta yayi.

A haka ta ringa bani labarin nacin da take yiwa mijin Aisha amma baya sauraranta wata uku a tsakani tazo ta sameni bakinta a washe tana na tayata murna ai a yanzu dole ma Salis ya aureta na tambayeta mai ya faru?anan take fadamin ai taje office dinsa security sun hanata Shiga tana zaune taga muhasim Yar gidan yayan Aisha tazo ta shige office din Salis take zuciyarta ya bata wani abun tunda a kwanakin baya da ta zuba masa magani ma Allah ne ya tsallakar da ita da a lokacin zai mata fyade,ta cigaba da bani labarin yanda taso ta Shiga office din taji Mai muhasim taje yi a office din security suka hanata Shiga tana nan a labe taga Muhasim ta fito da gudu tana kuka,itama bata tsaya bata lokaci ba ta take mata baya dan tasan dole gagarumin abune zai saka taje office dinsa har ta fito tana kuka,a lokacin data fito tace muhasim ta mata nisa har sai da ta tari abin hawa suka tadota bata nunawa muhasim daga asibtin take ba tace tazo ta hau su karasa gida,a haka muhasim ta hau tana kuka Luba tace min ta ringa rarrashin ta tana bugar cikinta akan ta fada mata Mai yake faruwa tak'i fada mata har sai da ta mata barazana akan zataje gidansu ta fada akan ba islamiya taje ba, office din Salis taje, dak'yar ta samu Muhasim ta fada mata Salis ne ya Mata fyade ta gano tana da ciki shine yace ta zubar da cikin ita Kuma tana tsoron ta zubar da cikin ta mutu,Luba cikin murna ta cigaba da fadin"Wlh bakiga yanda na tsorata ta akan karta yarda ta zubar da cikin ba idan ba haka ba mutuwa zatayi Asabe ki tayani murna a yanzu nasamu hanyar da dolensa ya aureni"

"Idan kuma cikin ya zub'e fa ya zakiyi"?

Na jefa mata tambayar sai a lokacin jikinta yayi sanyi sai Kuma ta mik'e a zabure tana "Ai janyo yarinyar nan zanyi a jikina wlh bazan tab'a barinta ta yarda ta zubar da cikin ba dan da cikin jikin nan nata Zan ta barazana akan zan tona masa asiri nasan Yana mugun san Aisha bazai so asirinsa ya tonu ba a yanzu ma na nunawa yarinya zan taimaka mata cikin ya zub'e batare da an mata komai ba dan so nake nayita yaudararta sabida Kar cikin ya zub'e"

A ranar Luba ko bacci batayi ba dan a gidan mu ta kwana a haka ta ringa jawo muhasim jikinta tana fada mata duk yanda suka yi da mijin Aisha, ta Kuma cigaba da

zuwa office din Salis da har lokacin baya barinta ta shiga,duk halin da suke ciki tana fadamin.

Watarana tazo ta sameni tana "Ke Salis fa ya dage so yake ya zubarwa yarinya nan ciki tace min har makarantar su yake binta dan ya zubar mata da cikin ni kuwa idan har yayi nassarar zubar da cikin nan nasan bazai tab'a Aurena ba"

"Yanzu ya zaayi kenan"?

Na tambayeta sai tayi shiru tana tunani sai ta fara da ko "Saceta zanyi"?

Sai na girgiza mata kai

"Toh yanzu ya zanyi wlh wanan hanyar kawai gareni da zan samu Salis ya aureni"

Nidai a lokacin kaina ya kulle bansan shawarar da zan bata ba,haka tayi ta nazari har dare yayi Muka yi sallama da ita,kwana biyu a tsakani tazo ta sameni akan ta gano abinda zatayi hanya mai mugun sauki da zata samu auren Salis ta Kuma gara shi san ranta.

Ihun da Luba ta saka a gigice tana "ke kika zugani Asabe ke Kika kawo wanan shawarar wlh ba ni nayi niyya ba Kuma ke kika aiwatar da haka alkali a tambayi muhasim aji Wanda ya karkata Mata wuya wlh bani bace itace duk maganar da take karya takeyi so take kawai duk ta Dora min laifi"

Gudumar kotu ya buga akan tayi shiru dan zabure zabure take tana neman fitowa daga wajen sai ihu take.

Yan sandan dake gefenta suka tsawatar Mata tayi shiru tana shesheka Salis ya mik'e tsaye dan ji yayi Yama kasa zama,Aisha Kuma ta dafe kirjinta tana Jan sallati dan sai taji Kamar numfashinta ke san d'aukewa sai da komai ya lafa Ashraf ya kalli Asabe da itama ta fara gumin tana zare ido,

"Muna jinki ki cigaba da bayani"

"A lokacin tace min ta samu saurayinta dinan Dr Saeed akan ya taimaka mata, dan tana soyayya dashi,Yana kashe mata kudi,a lokacin ya nuna mata dama an masa transfer zai bar garin zai taimaka mata amma ita zata aiwatar bashi ba,Kuma shima idan ta samu cikar burinta ta masa alkawarin bazasu rabu ba,zasu cigaba da had'uwa idan ya shigo gari ya kuma yi mata gargadi akan Kar ta sake Koda ta kwabe ta Kira sunansa"

"Wane irin taimako ya Mata akan muhasim din"?

"Ashraf ka yarda dani wlh karya take ita ta hadani da Saeed din abokin saurayinta ne duk ita ta fadamin yanda Zan samu cikar burina muhasim kema zaki min shaida ko"?

Luba tace cikin ihun kuka tana cigaba da "Wlh kema sai na tona miki asiri ke Kika koya min duk abinda nayi"

Sai da aka Kara tsawatar mata aka samu tayi shiru Asabe kuwa sai ta tsinci kanta cikin tashin hankali dan Yusuf mik'ewa yayi tsaye Yana kallonta

"Muna jinki wane irin taimako ya Mata"?

"Allura ya hada mata yace ayi wa muhasim a wuya wuyanta zai karkace bakinta ma haka Kuma bazata tab'a iya magana ba"

Sallati aka kaure dashi a kotun Salis kuwa yayi kan luba da gudu yan sanda suka tare shi tare da ririke shi Salis ya hau ihun"Dama duk tsawon lokacin nan allura kika mata duk tsawon lokacin kika saka mukayi ta wahala Kika saka akayi ta zargina Allah ya tsine miki Luba Allah ya wulakanta keda kawarki Allah yasa ku a wutar jahanama kuka samin magani nayi wa Yata fyade iya nan bai isheku ba kuka karkata mata wuya dan Allah ku sakeni na kasheta inyaso nima a kasheni"

Yanda Salis ke fufusgewa yasa Yan sandan yin waje dashi Aisha kuwa akayi kanta dan numfashin dake mata wahalar shak'a yasa ta sume Yaya mustapha yayi kanta Yana sallati.

Luba kuwa ihu ta cigaba dayi tana "Wlh ita tayi Mata alluran ni rik'e muhasim kawai nayi,wlh bani na mata alluran ba karya take min Asabe kiji tsoron Allah ki Fadi gaskiya tunda asirinmu ya riga da ya tonu"

"Wlh karya kike yi bansan komai ba nidai labari kawai Kika bani"

Yanda kotun ya hargitse yasa alkali buga gudumarsa akan a tafi hutun minti talatin a dawo.

Salis Kamar mace haka ya zauna a barandar kotun Yana kuka, a gaban idonsa Aunty mamy da Yaya mustapha suka fito da Aisha Suka shimfida ta akan wani dakali suka ringa watsa mata ruwa suna mata fifita Koda ta farfado kuka kawai take tana Luba ta cuceta Allah ya Isa tsakaninta da ita.

Ashraf kuwa sai rarrashin ta suke Alhaji Salis daya hango yasa ya mik'e ya nufi wajensa da isarsa ya zauna a gefensa Yana "Abba ba kuka zakayi ba ka godewa Allah da gaskiya ta fito akasan duk abinda ya faru ba yin kanka bane sharrin Luba ne Abba dama akwai alluran da ake yiwa mutum wuyansa ya karkace haka da baki"

Gyada masa kansa yayi Yana "Akwai amma baa fiye samunsa anan ba sai kasar waje nayi matukar mamaki da yanda har suka samu alluran Suka yi mata tunanin mu a lokacin bai tab'a bamu akan allura aka mata ba"

"Kasan to Dr Saeed din"?

"Aaa bansan shi ba may be ta bakin Luba Asaben ce ta hadata da wani likitan amma babu wani Dr Saeed da muke dashi a asibitin a wanan lokacin"

"Abba zaa samu maganin toh da zai warkar da ita tunda angane mai aka Mata"?

Za'a samu idan aka fita da ita waje Luba ta cuceni ASHRAF mahaifiyarka ma ta cuceni dan duk ita ta bawa luba k'ofa taci galaba a kaina"

"Kayi hakuri Abba Allah ya riga da ya rubuta hakan zai faru baku isa ku k'aucewa kaddararku ba ka godewa Allah da asirinta ya tonu"

Salis bai Kara cewa komai ba a daidai lokacin da Yaya mustapha ya nufo wajen da suke zaune.

Ashraf shi Kuma ya mik'e yayi cikin kotun.

Minti talatin a tsakani aka koma cikin kotun gabadaya Luba idonta yayi luhum luhum sabida kuka,Asabe kuwa gumi kawai takeyi dan batasani ba ko itama kotun zasu iya zargarta su daureta.

Sai da Alkali yayi gargadi akan yin hayaniya da magana batare da an bada dama ba kafin yace Ashraf ya cigaba daga Inda ya tsaya.

Ashraf ya karasa gaban Asabe Yana "kikace Dr Saeed shine ya bawa Luba alluran da aka yi wa muhasim bakinta ya karkace da aka bata alluran ta kawo miki kin gani"?

Asabe sai tayi sauri ta girgiza kanta tana "Aa bata kawomin ba sai da tayiwa muhasim din alluran tazo gidanmu take fadamin"

"Ta Baki labarin yanda akayi ta mata alluran a Kuma Ina tayi mata alluran dan Muhasim a bayan makarantar su aka tsinceta a kwance"

"Eee a lokacin cemin tayi a ranar da aka bata alluran washegari taje makarantar islamiyarsu muhasim tace mata ta samo mata maganin da cikin zai zub'e dan haka gobe tazo ta sameta da sassafe ta shafa mata maganin a cikinta tana shafa mata cikin zai zub'e, ta kwatanta Mata gidan da zata zo ta sameta,shine washegarin ranar muhasim tazo gidanmu da sassafe Au taje gidansu Luba da sassafe ta sameta shine ta mata alluran ta tari abin hawa taje ta jefata a Bayan makarantar"

Murmushi Ashraf ya saki yana "Kinaso kice bakya wajen akayi alluran"?

"Eee gaskiya labari tabani"

"Amma yanzu Kuma kince tazo gidanku da sassafe ita muhasim din kenan a tare kuka mata alluran"

"Aaa gaskiya ba gidanmu tazo ba gidansu luban taje"

"Toh menene dayan sirrin Luba da kike san fadawa kotu"

"Yaran da Luba ta haifawa Salis"

Ihuuuu Luba ta saka

Asabe kuwa ta cigaba da magana tana "Bintu ce kawai Yar Alhaji Salis sauran biyun yaran Dr Saeed ne dan shima barazana ya ringa mata akan idan bata bashi hadin kai zai tona mata asiri"

"Kin kasheni Asabe kin cuceni ke Kika bani shawara fa Asabe ke kikayiwa muhasim allura fa bani ba wlh karya take min

Yanda ta ringa ihu da kururuwa yasa alkali buga gudumarsa Luba kuwa ta Yanke jiki ta Fadi.

Shigowar wani kotun da Yan sanda ke biye dashi a baya yasa Asabe ja da baya cikin ihu tana "Ghali".....

Sister's duk wacce batayi anfani da sabulun mg's ba ko kit dinsu inamai shaidamuku anbarku acan baya domin duk wnd yajaraba mg's sai sanbarka duk wani Mai tantama Akan kayan gyaranjiki toh tabbas yacire sabulun mg's domin yahadu bakarya zegyarajiki yafidda dattin fata Dama duk wani matsalan fata duk Wanda kefama da matsalan fata walau pimples ko spot, sunburn acne, knuckles,wrinkles,stretch mark dama dukkan wani prblm yajaraba mg's bi'iznillah komai zaizama labari bayan jikinku yy fresh zaisa jikinku yy smooth yadinga glowing,gawanda basa San anfani da Mai zaku iya using sabulun mg's batare da kunbukaci wani Mai b Mai bukata should Chat
08062991549
07046881166
07067210195
Call 08064532391

Team glow♀

WANAN LITTAFIN NA KUDINE BIYA 500 TA WANAN ACCT 0272061655 WEMA BANK NAFISA NUHU KO KATIN MTN KO AIRTEL TA WANAN LAYIN 08033719070 DOMIN KI MALLAKI NAKI KI MUTANEN NIGER KUMA KU TUNTUBI WANAN LAYIN
+227 96 82 89 84 DUK WACCE TA MIN SHARING NA BAR TA DA *RABBI ZAI FIDDA MIN HAKKI NA DA IZININ ALLAH DOMIN BA YAFEWA NAYI BA*

NI DA KISHIYOYINA

NA SADNAF

PAGE 38

Asabe jikinta ne ya hau karkawa,Wanda ta Kira da ghali ya tsaya a gefen witness box a daidai lokacin da Yan sanda suka watsawa Luba ruwa ta farfado.

Tana cigaba da ihun kuka ghalin da tayi tozali dashi a tsaye yayi zuru zuru yasa ta saki ihu tana "Alhamdulillah ya Allah ga Ghali nan Asabe idan kina tunanin ni zaki tona asiri naki ya rufu toh gashi nan Allah ya turo shi kema ya tona miki asiri.

Asabe tuni ta jike da gumi tana sallati a ranta tana ta mamakin ya akayi aka kamo Ghali uban me yazo nema a kotun ai indai Ghali ya tona mata asiri ta Kade har ganyenta ta saci kallon Yusuf dake tsaye idonsa jajjur,tamkar yanda shima Salis ya kasa zama har hular kansa ya cire dan fadar yaran Luba guda biyu ba nashi bane ba Abdul da khalifa ya matukar daga masa hankali yanzu duk wahalar da Luba ta ringa bashi akan yaran ba yaransa bane na wani ne, jikinsa rawa kawai yake Luba ta wuce tunaninsa dama duk tsawon lokacin nan tana zuwa wajen wani,taya ma zai yarda Bintu yarsa ce ba Yar wani ba,kallon ita da Asabe kawai yake, sanin Luba bai tab'a zame masa alheri ba sai sharri

Ashraf kuwa tsayuwarsa ya gyara ya maida hankalinsa kan Asabe Yana "kinsan ghalin ne naga kin Kira sunansa"?

Da sauri Asabe ta hau girgiza kanta tana "Bansan shi ba kama yayi min da wani"

Ashraf ya saki murmushi Yana "kinaso kice iya Bintu ce Yar Alhaji Salis sauran bashine mahaifinsu ba"?

"Eee hakane"

"Akwai Kuma wani sirrinta da kike ganin ya kamata kotu ta sani Bayan wanan"?

"Bai wuce juya masa tunani da tayi sai yanda tayi dashi ba,iya sirrinta dana sani kenan"

Gyada kai Ashraf yayi ya juya wajen Luba Yana "Hajiya Luba kinji abinda kawarki aminiyarki tace ke Kika yiwa muhasim allura da taimakon Saurayinki Saeed zaki yarda ki amsa laifinki batare da kin wahalar da Sharia ba ko kuma kina da ja"?

"Ina da ja asirina ya riga da ya tonu zan Fadi iya gaskiyata duk maganar da tayi karya take yi, duk wani abu da na aikata ita ta Sakani na aikata,a lokacin da na gano muhasim na d'auke da cikin Alhaji Salis ban taba tunanin tab'a lafiyarta ba Asabe itace ta bani shawarar haka,Dr Saeed da take magana Kuma abokin saurayinta ne,a lokacin ita ta hadani dashi akan na hakura da Alhaji Salis na auri shi Alhaji Saeed din tunda a lokacin bashida mata matarsa ta rasu,ni Kuma sai nace mata bai yi min ba dan bashida irin kudin da nake so ya zama mijina na da shi,sai ta bani shawarar na ringa wankarsa Yana da sakin kudi,yaso Aurena a lokacin naki yarda a lokacin da maganar muhasim ta b'ullo muka yi ta shawara da Asabe yanda zan samu cikar burina akan Alhaji Salis duk shawarar da muka yanke har na sace muhasim din bai yi ba sai da ta kawo shawarar ko ayi mata allurar da bazata tab'a iya magana ba ballantana tace Salis ne ya mata ciki,a lokacin na dauka iya alluran d'auke magana ne shiyasa jiki na rawa nace na yarda Muka je office din Dr Saeed din a tare,ita ta fada masa abinda muke so ya mana take ya nuna mana da hatsari alluran dan Yana iya zuwa da karar kwana,take naji hankalina ya tashi dan idan har muhasim ta mutu bazan tab'a samun cikar burina ba,sai da yace zai nemo Wanda bashida k'arfi sosai dan ba'a samun sa anan sosai kafin na yarda akan za'a mata alluran duk da a tsorace nake Asabe haka ta ringa zugani,kwana biyu a tsakani Dr Saeed ya aiko ghali akan ya kawo mana alluran baya gari yayi tafiya.

Ghali shine saurayin Asabe.

A lokacin ma Ghali muka so ya mata alluran yace bazai samu zuwa a ranar ba hakane yasa Koda na yaudari muhasim.akan tazo zan taimaka mata Asabe ce tace min zata iya mata alluran.

Washegari da sassafe muhasim taje gidansu Asabe da kwatancen da na mata,dama ta riga ta hadani da wani mai abin hawa na biyashi akan ya jiramu a bayan gida,a lokacin da muhasim tazo sai naji Kuma hankalina ya tashi dan Ina tsoron ta mutu ba Kuma wai dan Zan damu da mutuwarta ba sai dan burina da bazai cika ba.

"Wlh wlh da Asabe ta bani alluran ban iya mata ba rufe mata baki nayi da hannu daya na danne ta Asabe tazo ta danna Mata alluran a wuyanta sai da ta karar da

ruwan ta zare daga wuyanta,bani na mata alluran ba nidai na rike muhasim anyi mata alluran,tare muka kinkimi muhasim muka kai ta mota,na hau muka je muka jefata a bayan makaranta,Asabe Kuma itace ta kashe kishiyarta Rabi ta hanyar saka mata guba ghali shine ya hada alluran guban,yanda na ringa muamalla da Saeed da aurena haka take muamalla da ghali wanan shine iya gaskiyar abinda ya faru"

"Wlh karya take min bani na mata allura ba ni bansan wani ghali ba"

Asabe tace hankalinta a tashe Yusuf mijinta kuwa sallati kawai ya ringa kwadawa da k'arfi yanda Ya ringa k'ok'arin yin wajen Asabe yasa Yan sanda sukayi waje dashi.

Ashraf ya kalli Luba Yana "Yanzu Ina shi Dr Saeed din yake"?

"Bansan Inda yake ba dan gaskiya bana Jin Yana shigowa Nigeria yanzu dan indai ya shigo sai ya kirani mun had'u"

"Dagaske ne Bintu kawai ce diyar Alhaji sauran yaran naki na Dr Saeed ne"

"Gaskiya ne Abdul da khalifa ba yaran Alhaji Salis bane yaran Dr Saeed ne"

Gyada kai Ashraf yayi ya kalli Asabe da ta fara kuka dan tasan aurenta ya gama mutuwa idan ba'ayi Wasa bama yau sai an kulleta.

"Hajiya Asabe ko kina da abin cewa"?

Shiru Asabe tayi batayi magana ba

ASHRAF ya juya
wajen alkali yana "Ya mai girma Sharia inaso kotu ta bani dama zanyi wa dayan shaidan nawa tambayoyi"

"Kotu ta baka dama"

"Nagode ya mai girma mai Sharia"

Ashraf yace tare da juyawa wajen da Ghali ke tsaye yana "bawan Allah ko zaka iya fada mana sunanka da dalilin daya sa kazo kotu"?

"Sunana Ghali Usman nazo kotune sabida na Fadi iya gaskiyar abinda na sani Ina Kuma rokon kotu da ta taimaka tamin afuwa nasan nayi kuskure

"Da kyau Mallam Ghali wa ka sani a cikin hajiya Luba da Hajiya Asabe?

"Nasan duka su biyun"

"Mai alakarka dasu"?

"Kamar yanda Luba ta fada ni saurayin Asabe ne abokina ne saurayin luba"

"Ina shi abokin naka yanzu"?

"Allah ya masa rasuwa wata hud'u da suka wuce"

"Dagaske ne Kai ya bawa allura ka kaiwa luba"?

"Eee ni ya bawa ma akan na mata alluran dan a ranar zai bar gari nima a lokacin sai wani uzuri ya tasomin sai nace musu bazan samu na mata alluran ba sai dai su nemi wani ya Mata"

"Kishiyar Asabe da ta rasu ta hanyar shan ruwan shayi dagaske ne kaine ka Kai mata gubar da ta saka mata"

Sai daya dau tsawon mintuna Ashraf ya sake maimaita tambayar Ghali ya gyada kansa yana "ni na Kai Mata gubar bansan kishiyarta zata kashe ba"

ASHRAF wajen Asabe yayi da jikinta kawai ke rawa yace "Hajiya Asabe kince badake aka yiwa muhasim Allura ba gashi Saurayinki yace dake aka yiwa muhasim Allura,Kuma kishiyar ki rabi da ta rasu ke kika saka mata guba a cikin shayi ta rasu,kin aikata haka ko baki aikata ba"?

"Wlh sharri suke min dama Luba tayi alkawarin sai taga bayana ita taje ta biya wanan mutumin yazo yamin sharri amma ni bansan komai ba"

Murmushi Ashraf yayi Yana "Ba Luba ce ta biya shi ba a binciken da na ringayi na nemo shi ko a yanzu yana hannun Yan sanda"

Asabe wani irin ihu ta saka ta yanke jiki ta Fadi a sume"

Ashraf kuwa ya juya wajen alkali Yana "Ya mai girma mai Sharia daga shaidun da na gabatar gaban kotu ya Isa ya gamsar da kotu akan Luba itace silar jefa muhasim a cikin wanan halin tamkar yanda ta amsa laifinta da bakinta,tare suka hadu ita da kawarta suka zalunci muhasim suka kassara mata rayuwa shekara goma Sha shidda tana nan akan keke sai yanda akayi da ita,Ina rokon kotu da ta Yanke musu hukunci daidai da laifin da suka aikata nagode ya mai girma mai Sharia.

Daga Haka Ashraf ya koma ya zauna alkali rubuce rubuce yayi ya dago yana "Ko lauyan mai Kare wacce ake kara Yana da abin cewa"?

"Banida abin cewa ya Mai girma mai Sharia"

Barrister dake Kare Luba yace tare da komawa ya zauna.

Luba kuwa sai a lokacin taji hawayen nadama ya wanke mata fuska jiki a sanyaye ta kalli wajen da Aisha ke zaune da idonta yayi jajjur sabida kuka, ta kalli Salis dake tsaye shima idonsa ya Kada yayi ja daga irin kallon da yake mata tasan da zaa bashi bindiga tsaf zai harbeta,a hankali ta ringa bin mutanen kotun da ido,ba wani jininta dake cikin kotun tsabar bakin halinta,ba mai yarda tana da d'a kamar sultan Koda Wasa bata tab'a hararowa kanta irin wanan ranar da zata tsaya a bainar jama'a ta tonawa kanta asiri har mutane su san abinda ta aikata ba,abu dayane yanzu ya Sanyaya mata zuciya Asabe da ta saka duk ta aikata abinda ta aikata a tare zaa musu hukunci,muryar alkali ne ya katse mata tunanin da ta tafi ya daga zaman kotun zuwa sati biyu mai zuwa a ranar zai yanke musu hukunci ya bada umarni a kama Asabe itama a kulleta,Asabe da ta fafado daga sumewar da tayi ihu tasa tana tirtirjewa a lokacin da Yusuf ya wurga mata takardar sakinta a daidai lokacin da aka saka mata ankwa,aka tasa keyarsu akayi waje dasu.

Ashraf kuwa fadar farincikin da yake ciki b'ata bakine,dan shi yasan bak'ar wahalar dayasha kafin ya iya gano Asabe da Ghali,Yaya mustapha fa kuwa wajen Salis yayi da

har lokacin hawaye bai bar zubar masa ba ya dafa kafadarsa yana "Kayi hakuri kaddara ta riga fata Allah ya riga ya rubuta hakan sai ta faru,da ace Aisha ta rabu da Luba tun a lokacin da ka nemi ta rabu da itan da duk haka bata faru ba Aisha ta d'auka yanda zuciyar ta take haka na luban yake bata san ba komai a zuciyarta ba sai sharri"

"Wlh Yaya sai inda karfina ya Kare sai na tabbata anyi mata hukuncin mai tsauri ta cuceni ta zalunceni Ashe shegu duk ta ajiye min a gida ko bintun ban yarda nine mahaifinta ba wlh sai munje asibiti anyi gwaji"

Aisha kuwa har suka isa gida rusa kuka kawai take,ashe duk tsawon lokacin nan duk abinda ya faru laifin Luba ne bana Salisu ba,ta d'auka Salis da gangan yayi wa muhasim fyade,ta d'auka Salis da gangan ya auri Luba,ta d'auka Salis shi ya karkatawa muhasim wuya Ashe Luba da ta dauketa tamkar Yar uwa ta d'auketa da zuciya daya duk itace ta rusa mata gida,ta rusa mata farincikinta ta cutar mata da yayanta,da ace Salis ko sau daya ya bud'e bakinsa ya fada mata Luba tana da wani fuskar akan Wanda tasan ta dashi da ta dade da rabuwa da ita,duk da a lokacin ba lailai ta yarda ba zata dauka sabida kawai ya tsani luban ne,amma dai da ace har ya fada mata ba abinda zai hanata rabuwa da ita,sai ta ringa ji ma Kamar itama tana cikin wayanda suka cuci Salis din,kwana uku cir tayi tana zazzabi,a wajen Aunty mamy take jin cukun cukun da Salis yakeyi na fita da muhasim kasar waje.

Gabad'aya sai taji tana nadamar Abubuwan da ta ringa masa abaya Wanda da ace baya kaunarta ba Kuma shi da hakuri da ya Dade da sakinta yayanta kuwa duk da abinda ya faru ya riga da ya faru haka ya ringa zabga mata fadan ta Kira Salis ta bashi hakuri dan itama ta zalunce shi amma sam ta kasa kiransa dan batasan mai zata ce masa ba.

Salis

Ji yake kamar an sauke masa nauyin da ya dade Yana fama dashi a yanzu idan akwai abinda ya rage masa bai wuce yayi k'ok'arin fito da John da Hajiya Shafa ba dan a yanzu sai yaji ma Yana zargin baa cikin hankalinsa ya fada harkar saffarar yaran mutane ba kila ma Luba tana da hannu a ciki dan har ga Allah baisan ya akayi ya fara harkar ba,a yanzu kuwa ba karamin nadama yake ba,Rabin yaran ya sa an samo su ya basu kyautar kudi,dama bashi Suka sani ba sun san shine a matsayin mai taimaka musu.

Yanzu Kuma babban burinsa muhasim ta samu lafiya hakane yasa ya fara cuku cukun fita da ita ya riga da yayi wa wani likita ba indiye magana akan za'a kawo muhasim.

Luba

Zage zage kawai suke ita da Asabe suna tonawa kansu asiri har sai da ta Kai su ga dambe aka raba musu waje,Asabe kuwa hankalinta yafi na kowa tashi dan bata tab'a tunanin daga zuwa tonawa Luba asiri itama nata asirin zai tonu ba,tayi mugun nadamar zuwa kotun,da ace tasan nata asirin zai tonu da bata ma soma bawa Ashraf fuska ba,karshen dai duk abinda ta aikata gata nan a kulle da bandeji a nade a cikinta a Karo na farko da itama ta fara nadamar mugayen Abubuwan da ta aikata dan ta dame Luba a mugunta ta Shanye babban tashin hankalinta yanzu bata San hukuncin da zaa yanke musu ba zuciyarta cike take da fargaba da zullumi.

Tuni tabi ta rame ta lalace, tamkar yanda take hango Luba itama duk ta fice a hayyacinta matan da suka samu a cell din suma sai azabtar dasu suke.

A yau za'a koma kotu,Asabe kuwa rabon da tayi wani sallah cikakiya har ta manta sai gashi tana daga cell tana sallah da rokon Allah akan Allah yasa ba hukuncin kissa za'ayi musu ba.

Karfe goma aka tasa keyarsu da ankwa a hannnu ita da Luba akayi kotu dasu.....

Wane irin hukuncin ya Kamata ayi musu ne□□□□□

Sister's duk wacce batayi anfani da sabulun mg's ba ko kit dinsu inamai shaidamuku anbarku acan baya domin duk wnd yajaraba mg's sai sanbarka duk wani Mai tantama Akan kayan gyaranjiki toh tabbas yacire sabulun mg's domin yahadu bakarya zegyarajiki yafidda dattin fata Dama duk wani matsalan fata duk Wanda kefama da matsalan fata walau pimples ko spot, sunburn acne, knuckles,wrinkles,stretch mark dama dukkan wani prblm yajaraba mg's bi'iznillah komai zaizama labari bayan jikinku yy fresh zaisa jikinku yy smooth yadinga glowing,gawanda basa San anfani da Mai zaku iya using sabulun mg's batare da kunbukaci wani Mai b□ Mai bukata should Chat□
08062991549
07046881166
07067210195
Call 08064532391

Team glow♀

WANAN LITTAFIN NA KUDINE BIYA 500 TA WANAN ACCT 0272061655 WEMA BANK NAFISA NUHU KO KATIN MTN KO AIRTEL TA WANAN LAYIN 08033719070 DOMIN KI MALLAKI NAKI KI MUTANEN NIGER KUMA KU TUNTUBI WANAN LAYIN
+227 96 82 89 84 DUK WACCE TA MIN SHARING NA BAR TA DA *RABBI ZAI FIDDA MIN HAKKI NA DA IZININ ALLAH DOMIN BA YAFEWA NAYI BA*

NI DA KISHIYOYINA

NA SADNAF

PAGE 39-40

Kotu

Kotun cike take makil da mutane a cikin wayanda suka zo kotun har da mahaifiyar luba da yayarta Habiba jini ba Wasa ba a lokacin da suka ji labari sai hankalin su yayi matukar tashi a rade radin ma da suke ji a gari wai hukuncin kissa za'a yiwa Luba da Asabe duk yanda Habiba tayi tunanin zata iya share Luba sai taji bazata iya ba ita ta sanarwa mahaifiyar su halin da Luba ke ciki,ko mahaifinsu ma sai da jikinsa yayi sanyi dayaji wai hukuncin kissa za'a yiwa Luba badai nuna a fuskarsa ya damu ba amma jininsa ce Luba sai ya tsinci kansa cikin damuwa,irin wanan ranar ya ringa

hangowa Luba fada da nasiha ba irin wanda baya mata har sai da ya gaji ya kawo ido ya zuba Mata,fadan da yake mata akan Asabe tun lokacin da tayi Aure ya gano ba matuniyar arziki bace sai da Luba ta masa rashin kunya ta nuna ba haka ba,yau ga irinta nan duk da itama da nata bakin halin Asabe ta kai ta ta barota

Koda su Habiba Suka tafi kotun bai bisu ba.

Aisha da Aunty mamy a suna daga gaba dan Aisha Allah Allah ta ringa yi gari ya waye dan babban burinta taga an yanke wa Luba hukunci Mai tsauri inta Kama ma ayi mata hukuncin kissa ta hanyar rataya,bazata iya fasalta illar da Luba tayiwa rayuwarta ba.

Daga lokacin da aka shigo dasu kallo daya tayiwa Luba da suka hada ido ta d'auke kanta tana jinjina lamarin ubangiji Wai hukuncin dan Adam ne ya firgita luba haka hukuncin dan Adam ne ya maidata haka inaga ranar da duk zamu tsaya gaban Allah wani irin tsoron Allah ne ya Kara shigarta da ido ta raka Luba har ta shige witness box ko kad'an bata ji alamar tausayinta ba dan Luba tayi abubuwa da yawa da ya Kamata ayi mata hukuncin.

Luba tana daga tsaye da idonta da sukayi luhum luhum ta ringa bin mutanen dake cike a kotun sultan ta hango da ilham suna daga gidan gaba sun zuro Mata ido, d'auke kanta tayi da sauri tana Jin hawaye na kara gudu a fuskarta ta riga da ta makara ba dama ta maida hannun agogo baya ballantana ta gyara kuskurenta,duk abinda ta aikata nasan zuciya bata tab'a tuno da makomar yayanta ba,bata tab'a tunanin halin da zata jefasu a ciki ba,ita dai bukatar da ta saka a gaba shine kawai burinta, a yau sai ta tsinci kanta da kunyar yaran da ta Haifa a cikinta sabida San abin duniya ta rabu da mahaifinsu,ta wulakanta shi,ta watsar dasu taje tayi auren cin Amana duk a san abin duniya,sai a ayanzu ta yarda yan Adam suna da gajen hakuri,da ace yau tayi hakuri ta zauna da Hamza da kila tayi arzikin cikin kwanciyar hankali,yau gajen hakurinta san zuciyarta ya kaita ya baro,ta tashi a tutar Babu, ba miji ba yaranta ba dukiyar.

A hankali ta Kara maida kallonta cikin mutane ta hango mahaifiyar ta da ta rufe bakinta da hannu da gani kuka take tamkar yanda Habiba dake gefenta ke kuka, batasan lokacin da kukan da take rikewa ya kwace mata ba,inama tana da sauran lokacin da zata gyara kuskurenta,inama tana da lokacin da zata farantawa Iyayenta,inama duk rayuwar da tayi a baya ace mafarki ne,inama duk cutar da tayiwa Aisha ace ba dagaske bane mafarkine,lokacin inama inama ya riga da ya wuce,ta cutar da mutane da yawa da ya Kamata ta nemi yafiyar su.

Yanda take risgar kuka haka Asabe itama take risgar kukan,Asabe duk tafi Luba ma shiga tashin hankali.

A lokacin da Alkali ya fara karonta Abubuwan da suka aikata Asabe dafe kirjinta kawai tayi da taji Yana barazanar fadowa,Luba kuwa runtse idonta kawai tayi tana jiran hukuncin da alkali zai yanke musu,Jin alkali yace "kotu ta yankewa Lubabatu Bashir shekaru Ashirin a gidan yari batare da ko tara ko beli ba, Asabe lawan Kuma kotu ta yanke mata hukuncin daurin rai da rai Asabe sakin wani irin wawan ihu tayi tare da zubewa a kasa.

Luba kuwa ta rik'e witness box tana ihun alkali ya mata sausauci shikenan a gidan yari zata Kare rayuwarta nan da shekara Ashirin masu zuwa ai tasan tama mutu,ihu kawai take bata ma Kara sanin mai alkali ke cewa ba har yansandan suka zagayo wajen da take suka saka mata ankwa,Asabe Kuma aka kinkimeta dan sumewa tayi,cikinta Kuma na ta zubar jini,

Ihu Luba ta ringa yi tana mik'a hannu tana "Aisha ki yafe min mama Kinga za'a tafi dani ki yafe min ki rok'a min baba dan Allah Aunty Habiba shikenan rayuwata ta kare Salis ka yafemin, dan Allah karka kora su Abdul ba dan halina ba ka rikesu tamkar kai ka haifesu,bansan inda zasuje ba idan ka koresu tunda mahaifin su ya rasu Ka taimaka min Shine abinda tayi ta fadi har aka shige dasu mota.

Salis kuwa sai yaji ma hukuncin da aka yiwa Luba bai masa ba,yaso ace ita aka yiwa daurin Rai da Rai din,ko bata rokeshi ba Shima baiyi niyyar rabuwa da yaran ba dan

Aisha ma ko a jikinta a haka suka fara fitowa daga kotun,kowa na fadar albarkacin bakinsa.

Salis kuwa da Yaya mustapha suka tsaya a jikin motarsa Yaya mustapha ya hau shigo masa da maganar Aisha akan ya mata magana akan ta koma d'akinta.

Salis murmushi kawai yayi yana "karka matsa mata Yaya idan bataso ta dawo ka kyalleta ni yanzu komai ma ya ficemin a rai wlh"

"Aa sai dai idan Kuma ka daina ra'ayinta ne amma ai dolenta ta dawo"
Salis murmushi kawai yayi bai ce komai ba dan yaga ma kamar Aisha kunyarsa takeji shi dai a yanzu ya samu kwanciyar hankali abinda ya rage masa samun lafiyar muhasim da zasu tashi jibi a cikin masu kaita har da Ashraf.

Yasamu yayi cuku cuku an fitar da John da Hajiya Shafa yanzu Kuma yanda zai gyara lahirarsa kawai yake nema.

Kwana biyu a tsakani aka fita da muhasim waje Salis yaso binsu Kuma ya fasa dan ayyuka sun dan masa yawa.

Hindatu kuwa ganin ba kowa a gidan yasa ta zage wajen San taga ta karkato da hankalin Salis kanta,dan ta lura ta karfin tuwo Aneesa ke san dawowa rayuwar Salis kila ta danna zawarci taji ba dadi,idan Salis yayi bacci haka take d'aukar wayarsa tayi ta duba messages din da take turo masa take kuwa zata goge a karshe ma sai tayi blocking din ta,a yanzu idan akwai wacce take so ta dawo gidan bai wuce Aisha ba tana Kuma fatan idan ta dawo yazama iya su biyun kawai Salis zai zauna dasu,a wajen Afrah take Jin labarin Aisha sun fita waje da muhasim da duk wani abu ma da yafaru dan daga Ashraf har Salis din ba Wanda ya bata labarin duk abinda ke faruwa tayi matukar mamakin Abubuwan da akace Luba ta aikata Wanda har ya kaita da a kulleta duk da basuyi zaman Dadi da ita ba sai taji tana tausayinta.

Wata uku a tsakani su Aisha suka dawo gida nijeriya,ko a mafarki basu tab'a tunanin muhasim zata koma yanda take har ta warke ba sai gashi da karfin Addu'a da kwararrun likitoci da aka samu muhasim ta samu sauki wuyanta ya koma yanda yake haka ma bakinta,kuka kam a lokacin ta Sha har idonta na yaji,sai Fadi take bazata tab'a yafewa Luba da Asabe abinda Suka mata ba dan sun cutar da ita sun watsa mata rayuwa dan duk bayanin da Luba da Asabe sukayi ta gano Salis ba a hayyacinsa yayi mata fyade ba.

Yaya mustapha kuwa har da sadakansa sabida farinciki samun lafiyar muhasim.

Gidan yari.

Wani irin wahaltacen rayuwa Luba da Asabe ke yi a gidan yari da ko makiyin su baza su tab'a fatan suyi irin rayuwar da sukeyi a gidan yarin ba,Luba tayi nadama yafi cikin kwando,kwananta biyu a gidan yarin Yan uwanta suka je ganinta da yaranta haka ta ringa kuka tana neman yafiyar su,Asabe kuwa ta dan samu ma tabin hankali dan haka kawai zata fasa ihu ta hau fusge fusge tana fadar Abubuwan da tayi da bakinta.

Luba kuwa a yanzu wani irin ruwa ma take fitarwa a jikinta Mai shegen doyi gabanta fal yake da kuraje, a yanzu ma ware mata waje aka yi ita kadai tamkar yanda aka ware wa Asabe waje,da ace zasu iya maida hannun agogo baya da duk basu aikata abinda Suka aikata ba dana sani kuwa keya ce sai dai fatan Allah ya bamu ikon fin karfin zuciyar mu ya tsare Mana imaninmu.

Aisha kuwa a lokacin da Suka dawo Yaya mustapha sakota yayi a gaba akan ta koma d'akinta.

Aisha kuwa kunya da nauyin yanda zata koma gidan salis bayan duk cika bakin da tayi yasa ta cewa Yaya mustapha ita dai ya barta bazata koma ba, ganin Yaya mustapha ya nuna b'acin ransa gasu Ashraf da suka sakota a gaba da magiya yasa ta amince da zata koma.

A ranar Asabar Aunty mamy suka rakata ta koma gidan salis Kamar wata amarya ko Salis din ma baisan a ranar zata dawo ba,dan duk kin sanar masa suka yi.

Salis har ga Allah a lokacin da ya dawo yaji dadin dawowarta dan gani yake itace fitilar dake haska gidan.

Kulawar da ya kwashi shekaru bai samu ba a ranar Aisha ta bashi dan ba karya itama tayi kewarsa.

A yanzu Salis yasan ya samu nutsuwar da yake dashi kafin Luba ta shigo rayuwarsa,a yanzu yasan ya samu kwanciyar hankali,Auren muhasim da Afrah Yana cikin Abubuwan da suka matukar faranta masa rai,dan Muhasim ko shekara biyu batayi ba ta samu mijin Aure.

Har a yanzu Yar b'uya sukeyi da ita idan sun had'u dan kunyar juna suke ji

Luba kuwa yafiyar Allah kawai take nema dan a yanzu babban burinta Allah ya yafe mata Abubuwan da ta aikata,da taimakon su sultan dake zuwa dubata akai akai ta aikasu wajen Aisha da Salis akan su yafe mata ciki kuwa har da muhasim,dak'yar dak'yar ta samu da naci da komai suka ce sun yafe mata, mahaifinta ma kafin ya rasu yazo gidan yarin dubata ta nemi yafiyarsa yace ya yafe mata,Asabe kuwa abin nata yayi tsamari da sai da aka dangana da kaita asibitin mahaukata.

ANAN NA KAWO KARSHEN NOVEL DIN NIDA KISHIYOYINA KUSKUREN DA NAYI A RUBUTA NOVEL DINAN INA ROKON ALLAH YA YAFE MIN SAI MUN HAD'U A SABON NOVEL DINA INA MUKU FATAN ALHERI MASU BIBIYAR NOVELS DINA....